[9/6, 6:12 PM] Anty Rabi'at: _*UBAYD MALEEK*_

(Royalty versus love)

*_Mamuhgee_*

Bismillahir-rahmanirraheem

1

Qoqarin sauke kayan dake kan jakinsa yakeyi fuskarsa cikeda annuri da farin cikin jikinsa ma na nuna hakan sbd yanda yake sauke kayan da kuzarinsa da dukkanin himmarsa.,

Fitowa bayi matarsa Kuma uwar yayansa tayi tana kallonsa cikin tsananin mamakin ganinsa adaidai wannan lokacin,

Kallon sama tayi tana son kwatanta lokaci idan ta kwatanta daidai zata Kira lokacin da guraren uku zuwa hudu na yamma,

Duban uban kayan daya shigo dasu da jakin tayi tana sake bayyanarda mamakinta a fili na ganinsa Rana tsaka batareda lokacin zuwansa ganinsu yayi sbd a qaidancen aikinsa sai bayan sati bibbiyu yake zuwa ganinsu yayi kwana daya ya juya sai Kuma bayan satin biyu,

Yau kwanansa shida da komawa Amma gashi tana ganinsa harda kaya haka,

inda yake ta fito tsakar gidan tana ajiye butar hannunta tana Dan sake fuska kadan ta qarado tana karban qaton akwatin qarfensa dayake qoqarin saukewa daga kan jakin tana Dan nishin nauyin akwatin tace"

Abal Kaine yanxu?

Kallon kayan data sauke tayi tana maido kallonta kansa tace"

wannan dukannin kayan fa??

Fatan dai lafiya?

Yana qarasa aje daurin karshe dake kan jakin ya jasa zuwa wata rumfar dake can nesa da dakunansu wadda sukai daure dabbobinsu lokacinda suka taba kiwo yakaisa ya dauresa yadawo Yana zama kan saqin data shimfida Masa Yana cewa"

Alhmdlh ya ubangiji.

Ruwa taje tadebo Masa a qaton kofi me nauyi takawo gabansa ta ajiye tana zama gefensa cikin sauke ajiyar zuciya tana sake gaishesa wannan karon cikin yarensu na amheric tace"

Dehina metahi

(Barka da dawowa)

Shan ruwan yayi sosai Yana jinjina mata Kai Yana cewa"

Yawwa barkanku da gida,

Nasameku lafiya?

Alhmdlh"tace tana sake Masa kallon tambaya sbd gabaki daya hankalinta baa kwance yakeba da ganinsa gida yanxu sbd tafi kowa sanin tsanin qarfi da ikon masarautar delah take dashi akan ma'aikatansu Dan shekarunta ashirin harda yan Kai batareda mijinta ba saidai yazo yaganta duk bayan sati biyu yakoma saidai idan tace takai Masa ziyara wadda kafin tagansa ma aikine saiyanzu da shekaru sukaje saidai yayansu suje sugansa duk bayan kwana biyu saigashi yanzu tana ganinsa kwatsam haka ba tsammani.

Sauke numfashi tayi ahankali zatai mgn ya rigata da kallonta cikin tattara Yar nutsuwa a fuskarsa ta dattijantaka yace"

Jamila nasan hankalinki ba'akwance yakeba da ganina adaidai wannan lokacin,

Ki kwantar da hankalinki lafiyace tasanyani dawowa,

Babu wani abu daya faru kamar yanda kike tunani,

Nadawone gida wannan karon gabaki daya da yardar Allah shikenan zansamu yancina zanyi rayuwa taredaku cikin iyalina,cikin nutsuwa.

Wani guntun numfashi ta sauke wannan karon dukkanin jikinta nayin sanyi dajin abinda yake fada Wanda tasan ba iyakacin maganar kenanba akwai babbar maganar dake gaban wannan daya fara ta dago murya a sanyaye tana kallonsa tace"

NEGES?

'Dan dauke kai yayi ahankali cikin 'Dan jin nauyinta ya jinjina Kai ahankali yace"

Eh negestati.

Sama numfashinta yayi cikin wani irin yanayi na tsoro da muguwar bugawar da zuciyarta tayi ta sunkuyar dakai idanuwanta suka fara qoqarin cikowa da hawaye

Ya kalleta Kai tsaye yace"

Mahaifina yayi bauta a delah tun yanada kuruciya har tsufa ya kamasa Saida yakai baya iya wata bautar Ni yabayar ya yanci kansa a bautar dela,

Nayi bauta a delah tun Ina qaramin saurayina harna zama cikakken saurayi harna aureki muka Tara yaran dake gabanmu,

Nayi shekaru sama da talatin Ina bauta a delah,

Kinyi shekaru kusan ashirin ko fiye kina zaman kadaici batareda mijikinba,

Yarana sun taso Basu zauna da mahaifinsuba suka samu dukkanin kulawarsa,

Shin kina ganin bai kamata ba Nima nasamu yanci nadawo gidaba na huta 'daya daga cikin yayana ta fanshi 'yancina?

Jamila kinfi kowa sanin daganan har lokacinda Rai zaiyi halinsa ba barin delah zanyiba matuqar ba Wanda zan bayar maimakon yancina

Da inada 'da namiji bautar da mahaifina yayi haryabar duniya Nima nayi Shima ita zaiyi da haka zuriarmu zataita tafiya fa Amma yanzu daga kaina inshallah wannan gadon bautar yaqare sbd nine me 'yaya mata su ba bauta zasuje yiba *_NEGESTATI_* zasu zama.

Rintse idanuwanta tayi ahankali tana maida hawayenta sbd kada yaga rashin hakurinta ko rashin hankalinta ta dago batareda ta kallesaba tace"

Neges?

Acikinsu biyun waccece kazaba data zamo din?

Numfashi tasauke ahankali tana bayyanarda dukkanin damuwarta afili muryarta tayi tsananin sanyi tafara cewa"

Abal, dukkaninsu su ukun nice na haifesu,

Na rainesu,

Na zauna dasu nasan halin kowacce daga cikinsu,

MERIYAM bata cikin lissafi sbd itace qaramarsu gabaki daya shekarunta goma cif,

*_PADIMA_* da *_NURU_* sune ake magana akai.

Wani tsananin sanyi murya taqara zuciyarta tayi nauyi tanaji tun yanxu dukkanin burikanta da fatanta akan 'yayanta yana rushewa tareda dukkanin kuzarinta,

Hannu tasa ta dauke hawayen dasukeson sauko mata ta dauke kai ahankali tace"

Dukkaninsu inada burin ganin aurensu Kamar wanne 'yaya,

Nayi tanada da fatattaki akan rayuwarsu da aurensu,

bantaba kawo wani tunanin inda mahaifinsu yakeba zai iya juya qaddarar daya daga cikinsu daga zama Matar aure kamar kowace 'ya zuwa neges wato *_MACEN SARKI KO 'DAN SARKI KO JIKAN SARKI WADDA IYAKACINTA DASHI KWANCIYA DA HAIHUWANE_*,

Bantaba tunanin acikin yayana akwai wadda batada rabon igiyoyin aure su rataya akantaba saidai tazama _Negestati_ *(Kings mistress/kwarkwarah/abokiyar kwanciyarsa/abokiyar nishadin shimfidarsa).*

Kasa riqe hawayenta tayi wannan karon dukkanin jarumtarta saidai tanajin nauyi da kunyar bayyanarda damuwarta akan wannan hukuncin nasa sbd idan tayi Masa adalci ya cancanta ya huta Shima sbd ya bautu,

Ya hidimtu,

Ya wahaltu duk Dan qari sbd su da farin cikinsu baikamata ta nuna damuwarta afili ba duk da tasan aikin gama yariga Yagama tunda harya baro tasan yariga ya karbo shedar musayan yanci.

Abal kayi hakuri.

Girgiza mata Kai yayi Yana gyara zama yace"

Karki bani hakuri Jamila Dan dama dole zakiji ba Dadi saidai duk kuyi hakuri hukuncin Dana yanke kenan,

Maganar rashin jin Dadi anan dayace wato ta rabuwa da 'danka Amma kinsan irin rayuwar jin dadin da negestati keyi a daular nan banbancinsu da matan sarautar aurene Amma nawane suka sauya kaf zuriar danginsu daga talakawa zuwa attajirai.,

Banda burin 'yata tashiga delah dan ta maidamu attajirai saidai inada burin samun yancina Nima na huta daga bauta idan arziki yazo takawo Mana bazan qiba sbd kowa nason arziki kowa nason hada jini da delah dan haka Nima bazanqi naso samun jikoki daga delah ba sbd tabbaci ne na har abada da yardar Allah zuriarmu tagama bauta tashiga Kuma cikin littafin tarihin delah.

Murmushin qarfin hali tasaki tana qoqarin miqewa takawo Masa kunun madarar nonon raqumi da sabuwar danyar shinkafarsu tace"

Allah yasa hakan ne mafi alkhairi abal.

Amin" yace Yana gyara zama ganin ta dauko tasar kunun Yana hango haskensa tun daga hannunta.

Aje Masa tayi tafara kwashe kwayan dayazo dasu takai daki tadawo kenan su NURU din na shigowa gidan kowacce sanye da dogayen rigunan asalin yadin kuta,

Padima ce agaba kyakkyawar asalin brown/chocolate kalar fata,

Doguwace tanada jiki kadan musammn kirjinta acike yake Wanda yasa bayyanarda shafewar cikinta.

NURU ce abayanta hannunta riqe dana meryam,

NURU doguwace itama kyakkyawa me yellow brown skin asalin kyakkyawar amhara,

Batai jikin padima ba Amma tafi padima bajewar qugu Wanda yasa tafi padima suturta jikinta da kaya masu Dadi da rashin kamawa sbd boye irin kalar siffar da Allah yayi mata ta Jan hankali,

Tafi padima manyan idanuwa da fuskar marasa hayaniya sbd koyaushe fuskarta is simple sabanin ita padima da daka ganta zakasan tanada rawan Kai da jiji da Kai tareda jin kanta sbd kyawunta datake alfahari dashi duk da dai NURU da meryam sunfitashi haddama hasken fata sbd su kamarsu daya sosai da sosai sbd su mahaifinsu suka dauko shine asalin amhara wato asalin Ethiopian sai ita ta dauko mahaifiyarsu asalin hausa data surka da amhara din.

NURU da meryam kusan halinsu daya na rashin karauniya kuma meryam tafi shaquwa da NURU sbd itace Bata dukanta ko mata fada sabanin padima da Bata daukar raini ko kadan fada take mata musamman akan yanayin yanda takeson gudanar da rayuwarta.

Akwai saquwa sosai da kauna a tsakaninsu su duka da iyayensu,

Suna son junansu matuqa,

Suna kulawa da junansu tareda tsayawa junansu ako yaushe,

Kaman yanda ake karatun addini Dana boko Suma sunada wani qarin karatun wato karatun al'ada,

Sunyi karatun addini daidai misali,

Sunyi na bokon Wanda duk fiyeda rabinsa na aladunsune Dan haka gabaki daya idan kagansu Kai tsaye bazaka tantance sudin musulmaine kokuwa Dan al'adunsu a bayyane suke sosai tattare dasu.

Ganin mahaifinsu zaune yasa dukkaninsu tsayawa cak suna kallonsa cikin mamaki Banda meryam data qaraso da gudu ta fado kansa tana Masa sannu da zuwa cikin yare.

Kallon mamaki sukam suke Masa musamman dasukaga amminsu itama su take kallo zuciyarta fal da tunanin to shin cikinsu waccece za'a bayar amatsayin negestati,

NURU batada hayaniya,Bata iya doguwar hayaniyaba bare rigima baiwar Allah bazata iya da gidan sarautaba musamman delah dake cikeda fitintinu na mulki da sarauta sbd yawa da girman delah din idanma anbarta anan delah din idan Kuma asalin can daular dake qasar waje aka kaita inda asalin masarautar delah din take zuba zallan mulkinta Babu yanda NURU zata iya rayuwa a acikin asalin zuriar delah Sam Sam NURU bazata iyaba.,

Idan Kuma padima ce to itama akwai babban akasi sbd padima mace ce me tsananin son juya kanta bazata iya rayuwa acikin wainda mulki da iko yagama ratsa jininsuba sbd ita din zata zama bakowa bace acikinsu zasu juya rayuwarta Kamar suna juya kujeran zamansune Wanda taurin Kai da bakin padima zai hallakata acikinsu cikin qanqanin lokaci gashi a iya saninta babban burin padima shine auren mijinda yagama fita hayyacinsa akan Sonta wanda itace zata mulkesa acikin gidanta,

Burinta na biyu samun gidan arzikinda zata juya rayuwarta ta moru kyawunta bayyanardashi duniya tasanta acikin jerin kyawawa shiyasa babban burinta yakasance auren Koda bawane dake asalin delah dake qasar waje wato GIZAH,

Tanada burin komawa can Dan acan ne zata samu rayuwar datake shiyasa takeda kyakkyawar alaqa me qarfi da Ahmed Dan babban sarkin fada dake can giza Wanda ta shirya ta aminta da aurensa tabisa delah ta giza inda zaibi mahaifinsa yasamesa acan Wanda sai mai rabo ne keda sa'ar zuwa can.

Numfashi ammyn ta sauke tana dauke kanta daga kansu suna qarasowa ciki da mamaki suke Kiran sunan baban nasu cikin bayyana farin ciki da mamaki NURU tace"

Abal kana lafiya dai Ina fata?

Murmushi yasaki Yana cewa"

Alhmdlh nake NURU ganinku nazo yi.

Ajiyar zuciya padima ta sauke tana qarasowa itama sbd da har zuciyarta tafara shiga wani fargaba jin abinda yace yasata sakewa ta qaraso tana sakin murmushin farin ciki ta zauna gefen ammynsu tana cewa"

Abal harnaji tsoron ganinka sbd jin labarin yau anrabar da shedar sauyin yanci.

Daga abal din har ammy tare suka dago suka kalleta da sauri zuciyar ammyn na harbawa sbd sanin akwai akasin ra'ayi a alamrin musamman sbd yanda suka sabawa yaransu da rashin takurawa.

##MAMUH#

*_Haske writers_*

ZAFAFA BIYAR! ZAFAFA BIYAR!! ZAFAFA BIYAR!!!

Ina masu tambayar yaushe za'a fara? Ina masu jiran ranar? Toh gata fa tazo, mun zo muku da salo na daban wanda bamu taba zuwa muku da irin sa ba.

Me kike jira yar'uwa? Biya naki ki karanta halaliyar ki a nutse cikin kwanciyar hankali da jin dadi. Karki bari a baki labari, maza mallaki naki ta hanyar da aka tanada domin biya.

Littafan dai sune□□□

Gasu duka akan farashi mai rahusar gaske.

Kamar haka□□□□

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban ta whatsapp shedan biyanku(evidence of payment/Account name)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

□□□□□□□□□□

TEAM----ZAFAFA BIYAR□😘□😍

[9/6, 6:12 PM] Anty Rabi'at: *_UBAYD MALEEK_*

(Royalty versus love)

*Mamuhgee*

2

Treat/repair your skin with mg's skincare today,are you battling with pimples,

Black spot

cream reaction

eczema,acne, sunburn,spot, stretch mark, discoloration/skin damage, stretch mark then mg's skincare is the plug for you,mg's skincare gat solution to all ur skin prblms😍everyone deserves a blended skin when it comes to skin issue😭gv it to mg's skincare now is the time to take care of ur skin,this product is the real deal clears white patchesdark patchesdark feet's/knuckles reduces the appearance of greenveins,it clears pimples,spot and make ur skin fresh nd glow like never before just gv it a try nd ur skin will definitely thank you evn if you don't HV anything mg's skincare gat you a soap that will maintain ur skin nd make the skin to glow

Soap price:3k

Chat 08062991549 to plc ur orders

Call:08064532391

We deliver Nationwide buh delivery is not free

we can't wait to be a part of your beauty story

****

Fuskewa abal yayi Yana dauke kai daga zancen padima din ya maida hankali kan NURU dake tambayarsa lafiyarsa da qafarsa dake ciwo sbd yawan tsayuwa daya kashe qafafun sbd wani lokacin yakanfi awa uku hudu a tsaye a delah gurin aikinsa gakuma manyanci sai qafafun sukeson fara gazawa.

Fira sukahau Yi sosai da abal dinsu kafin daga baya NURU ta miqe tayi gurin ammynsu Dan tayata aikin sabuwar dahuwar dare datakeyi sbd abal din daya dawo badan haka ba kunun madarar raqumi sukeyi susha abinda da daddare sbd 'yaya matansu basacin abinci me nauyi da daddare a al'adarsu sai kayi aure kafara hayayyafa tukuna.

Sai magriba suka kammala lokacin padima hartayo wankan yamma tana zaune dakinsu tana shafawa jikinta mai batareda NURU ta kalletaba ta ajiye kallabinta data zame daga kanta dogon gashinta ya bayyana Wanda yasa padima turo Baki sbd Bata baiyi tsayin na NURU din ba,

Abu uku ne NURU takedashi duk nata kyawun takejin dama ita Allah yabawa duk ta hada,

Dirarriyar shape din NURU dayafi nata sosai sbd hips da Allah yabawa NURUn da qarin cikin NURUn dayafi nata shafewa sbd ita tafi NURU jiki sai gashin Nan na uku asalin yelloebrown fatar amhara da NURUn ta dauko Wanda yafi nata.

Wanka NURUn itama tayo taraka meryam itama tayo sukazo sukai sallah dukkaninsu atare kafin suka dungamo tsakar gida suka zauna cin abinci tareda iyayensu.

Kallon yanda sukecin abinci abal keyi Yana karantarsu Dan sake tantance wacce zai bada,

NURU yake kallo sosai Yana sake yaba sanyi da nutsuwarta saidai Sam bazai iya badataba sbd cutatuwa zatayi musamman idan yayi duba da baisan taqamaimai waye acikin delah za'a bawa 'yarsaba.

Kallonsa ya maida kan padima wadda Kecin abincin a kiyaye batason Bata bakinta sosai Sarai yasan halinta da babban burin son abun duniya shiyasa zuciyarsa ke wasi wasi akanta Dan idan taje giyar daular arziki da mulki suka bugeta Yana tsoron ta zama wata mutum dabam sbd tsananin son duniyarta da jijida kanta yanada yawa kowa yasanda wannan.

Numfashi yasauke Wanda yasa ammi kallonsa sbd tasan tunaninsa tana lure dashi da yanda yake karantarsu,

Itadai tunda abune na dole baza'a taba guje masaba to a gaskiyance gwara abada padima sbd tunda sunada wata 'yar bazata iya Bari abada NURU ba Dan baqaramar cutatuwa zatayiba,

Bazata iya rayuwa acikin sarautaba sam,

Tsaftatacciyar zuciyane da NURU zasu gurbato musu ita da rudin zalamar mulki da dukiya gwara padima tana zuciyar son abun duniya Dan haka zata iya gwagwarmaya acikinsu ta qwataci kanta dama 'yayan negestati dazata haifa.

Suna kammalawa dukkaninsu suka hau fira da abal dinsu bayan NURU ta tattare gurin itada meryam suka dawo suka zauna.

_____

*_No 554 U.MALEEK DELAH Aptmt_*

Jericho brighton New York City,New York.

Mum""Yar budurwar yarinyar da Bata wuce sha Tara ba ta furta cikin nuna takaicinta da damuwarta a fili tana kallon takardun hannunta data dauka daga gaban madubin bedroom din uwar Tata.

Qarasowa tayi idanuwa na cikowa da hawaye har gaban dining din ta daga takardun dake hannunta tana cewa"

Mum menene wannan??

Cikin wata irin cikakkiyar izza data gama Kama jininta ta dago a natse Kamar Bata fahimci damuwa da tarin baqin cikin data gani atattare da babbar 'yartaba wadda bazaka taba cewa 'yartaceba sbd itama tsufa ko wani manyanci ba gama kamata yayiba sakamakon auren wuri na sarauta da akai musu da mijinta shiyasa 'yartata tazamto Kamar wata qanwarta danma tafi Yar 'kyawun jiki da itakuma 'yar tafita kyawun fuska nesa ba kusaba sbd zallar Kamar mahaifinta data dauko.

Kallo daya tayiwa takardun kafin tamaida kallonta kan fuskar 'yar cikin wani irin sautin zallar iko da mulki tace"

AFIA menene naki akan wainnan takardun dake hannunki?

Wannan tsakanin nida abal dinki ne so stay out of it okay?

Dire mata takardun tayi da qarfi gabanta idanuwanta na cikowa da hawayen baqin cikin halin mahaifiyarta tace"

Mum wannan decision din naki na nufin rabuwa da abal fa,kinsan abal mgn daya yakeyi Wanda idan yayi Babu Wanda ya isa canzawa

Mum are you willing to take that risk?

Idan bakya tunanin kanki da rabuwa dashi mum please kiyi tunanin mu 'yayanki idanma Ni bakya tunanina kiyi tunanin farhat Mana,

Mum farhat bazata iya rayuwa Babu 'dayankuba tsakanin ke da abal idan kikai signing wannan contact din Kika tafi Tokyo shikenan fa kinbar delah har abada bazasu karbekiba kokin dawo daga baya please think and think and think mum"" taqarasa mganar hawaye na gangaro mata tanajin Ina zata Sanya zance mum dinta ta aje wannan rayuwar dama tafi ta turawa zama abin tsoro.

Spoon din boiled veggies da aka soya da kwai takai bakinta tareda shanye sauran black lemon tea dinta ta zari tissue ta goge bakinta kadan ta miqe tsaye sai alokacin ta fuskanci afia din dakyau ta kalleta cikin wani irin iko tace"

AFIA tuntuni nasan cewa zanbar delah duk ranarda na karbi contract din santrigo Tokyo na jirane dama sbd ki qara girma kiyi wayonda Zaki kula da farhat idan natafi hakama idan nadawo nasan Zaki tsaya tsayin daka su karbeni,

Santrigo Tokyo babban burinane Dana girma dashi na rayu dashi Dan haka aure bazai hanani cika burinaba ayanzu Dana samu dama,

Idan kinason duk wannan kar ayi azauna lfy kije kiyi convincing dad dinki yabarni naje Tokyo nayi aikina Dan bazan bar aikina Dana dauko shekaru fiyeda goma sha ba inayi akan tsantsar ikonsa da izzarsa ba.

Wani numfashin mamakin mum dinta tasake tana mata kallon mum kinyi nisa ta sake sauke wani numfashin tareda gyara tsayuwa ta kalleta cikin sanyin murya tace"

Mum kinfi kowa sanin mijinda Allah yabaki idan duk dukiyar Tokyo zakije abaki bazaki samu abinda yakai Wanda kike samu agunsaba,

Duk abinda Zaki samu a duniya bazaki samu abinda yakai _*UBAYD MALEEK DELAH*_ ba,

Mum Ina sake Baki shawarar kizauna adaki kiyi tunanin abinda kike Shirin aikatawa,

Zaki rasa mijinki,'yayanki biyu,dukiya,suna da matsayinki na Matar _MALEEK_ na GIZAH Wanda nake ji Miki tsoron rasawa har abada.

Ke mahaifiyatace bazanso ki rasa duka wainnan sbd abal shine abu na qarshe da mace zatai baqin cikin rasa samunsa a rayuwa.

Wani QAYATACCEN murmushi LAILAH tasaki tareda dafa kafadar 'yarta tace"

AFIA ke yarinyace

Kinason dad dinki fiyeda komai shiyasa kike ganin dukkanin hakan Amma abinda Baki saniba shine dad dinki mutum ne da duk duniya Babu me juyasa sai kakansa Wanda Shima halinsune yazo daya,

Inaga zaifi ki nutsu ki maida hankali kan karatunki ki Kuma kula da farhat Dan zata shiga damuwa sbd bananan Kuma dad dinku is a very busy man.

Kasa cewa komai tayi tabi bayan mum din Tata da kallon damuwa da baqin ciki harta haye sama.

Masu aikin gidan ne kusan su biyar sukazo suka fara tattara kayan dining din suna gaidata cikin tsananin girmamawa duk da dukkaninsu sun girmeta wasuma sun haifeta Amma sbd matsayinta na babbar 'yar maleek suke Bata mugun girma.

Ko kallonsu bataiba sbd halinda zuciyarta take ciki gabaki daya a jagule take bazataso auren iyayenta ya rabu ba akan iko,izza da isar dad dinta dakuma taurin Kai da burin duniya na mum dintaba,

Farhat kawai take dubawa sbd yarinyace sosai akanta sbd ita yanzu takeda 8years a duniya bazata iya ganin iyayenta sun rabu ba saidai abu daya tasani shine rabuwa kamarma sunyine Dan Babu abinda zai sauya taurin Kai irin na mum

Dad din Kuma aishi kankat ne Dan yafita zama riqaqqe saidai tana jin tausayinsa sbd mutum ne shi me tsananin qyanqyami na komaima

Suna rabuwa da mum za'a fara kawo Masa 'yayan manyan masarautu kokuma ma za'a iya kawo Masa negestati Wanda tasan tsananin qyanqyaminsane ya hanasa qara aure aure kamar sauran 'yan delah musamman shi dayake ubayd maleek na GIZAH,

Hakan nema yasa ya kebe kansa anan new York da iyalinsa Yana gudanarda rayuwarsa a qaidance yanda yake sonsa ba tarkacen hayaniyar masarauta duk da yasan dole wata Rana zai koma can da zama.

Bedroom dinta ta nufi ta fada kan gado tareda rintse idanuwanta hawayen ciki suka gangaro ta share da qarfi cikin takaici tace"

Bazanyi kukaba mum tunda haka Kika zabar Mana shikenan zamu runguma mu rayu Kamar marayu duk da munada uwa Amma ta zabi duniya akanmu.

Miqewa tayi tafada toilet tayo wanka tana fitowa tashirya a gaggauce ta zari ipad dinta ta fito ta nufi library din karatunsu tana qoqarin fitarda damuwar dake cikin ranta sbd mum tayi nisa batajin Kira sbd sunfi shekara akan wannan mgnar taqi barinta yanxu harta karbi takardun contract din shikenan komai yazo qarshe.

'dagowa tayi bayan ta zauna cikin library din ta kalli qaton makeken hotonsu na family daya cinye kwatan bangon library din ta qurawa dad dinta fararen idanuwanta da nashine ta dauko Zak,

Bawai Dan tana tsananin son dad dintaba Amma Bata taba ganin mutuminda ya hada irin qualities dinda ya hadaba,

Dad dinta is 99% takowane fanni.

Mum dinta takalla ta rintse idonta ta bude tana cewa"

She's perfect, she's beautiful tanada komai but she's nothing compare to dad Amma takeson barinsa meyasa?

Farhat da kanta takalla a hoton take hawayen datake riqewa suka gangaro mata ta miqe tabar gurin tana fasa karatunma.

_____

********NURU"" ammi takira sunan cikin tsoro da fargaba,

Abal meyesa kake ganin zabin NURU shine daidai bayan kasan NURU bazata iyaba.

Numfashi ya sauke Yana gyara kwanciya yace"

Padima gidan sarauta kamarna delah zaisa burinta ya fadada zai iya hallaka tunaninta da tarbiyarta.

Amma Kuma abal NURU tayi rauni da yawa kaduba.

Aa jamila kina dai tausayinta ne Amma itace zata fi mutunci a irin gurin sbd me hkr shine zaici ribar zama a delah.

Riqo hannunsa tayi tana marairaicewa da hawaye cikin idanuwanta sai jikinsa yafara sanyi Sam bayason ganin damuwarta sbd tsananin so da qaunarta dayake,

Kusan sati daya kenan sunata muhawarar wazasu bayar din kafin shi ya yanke NURU itakuma ta yanke padima.,

Ajiyar zuciya ya sauke sbd tunanin dayayi na girman Kai da burin padima na zuwa DELAH GIZAH bazai taba barin ta yardar musu ta yarda subadata a delah tanan ba tsaf yasan bijirewa zatayi sanin haka yasa yacewa ammin ya amince abada padima.

#MAMUH#

Haske writers□

ZAFAFA BIYAR□□□

ZAFAFA BIYAR□□□

ZAFAFA BIYAR□□□

(ZAFAFA BIYAR NEXT LEVEL)

(HUBILMAHX)□□□

_ASSALAMU ALAIKUM! INA MASOYA MA’ABOTA MAKARANTA LITTATTAFAN ZAFAFA?!
_

TO KU MARMATSO DOMIN NESA TAZO KUSA, HAZIKAN MARUBUTAN NAN DA SUKE KAWO MUKU DA’DADAN LITTATTAFAN NAN ZAFAFA GUDA BIYAR, SUN SAKE ZUWA DA KASHI NA 4.

SAFIYYAH HUGUMA

BILLYN ABDULL

MISS XOXO

HAFSAT RANO

MAMUH GEE

RIGIJI GABJI DINFA KENAN, DOMIN WANNAN KARON MA MARUBUTAN SUN SAKE KAWO MUKU WASU DADADAN MASU FADAKARWA, NISHADANTARWA, NISHADANTARWA UWA UBA KUMA AKWAI LAGWADAR SOYAYYAH...

*SAFIYYAH HUGUMA:* TAZO DA NATA SALON RUBUTAN MAI SUNA: *ALKIBLA*❤❤

*HAFSAT RANO:* TAZO DA NATA TAKEN RUBUTUN MAI SUNA: *MABUDIN ZUCIYA*□□

*MAMUH GEE* TA KARA ZUWA DA WANI SAMFURIN MAI SUNA: *UBAYD MALEEK*😘😘

NANA- HAFSAT *(MISS XOXO)* TA SAKE ZUWA DA WANI KALAR NA: *DALAAL*□□

*BILLYN ABDULL* TA KARA ZUWA DA WANI TAKEN MAI SUNA: *MAKAUNIYAR KADDARA*□□

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Gasu duka akan farashi mai rahusar gaske.

Kamar haka□□□□

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

□□□□□□□□□□

TEAM----ZAFAFA BIYAR□😘□😍*_UBAYD MALEEK_*

(Royalty versus love)

*_Mamuhgee_*

3

Tafiya takeyi cikin nutsuwar datafi Kama da jin Kai da taqama musamman yanda jikinta ke girgizar daukan hankali shiyasa duk Wanda ta hadu dashi a hanya yake hadiye Mata yawu musamman wainda sukasan padima ai tafi karfinsu sbd kyanta da ikonta tareda sanin Wanda suke soyayya dashi din daga delah yake wato Dan babban sarkin fadawa bama Wanda yake Nanba na can gizah.

Daga gurin karbo baqin lallensu take sbd koyaushe ita mace ce da Bata rabuwa da qyale qyale shiyasa yanada wuya kaganta Babu lalle faratanta na hannu Dana qafa shiyane qarin banbancin tsakaninta da NURU wadda duk wannan ta daukesa Kamar bayyanarda kyawu ne Wanda ita tafi ganin burgewarsa idan kayi aure kayi acikin gidanka.

Daga bayanta taji anriqo hannunta ta tsaya cak tareda wani juya idanuwanta wani qayataccen murmushi na sauko Mata sbd sanin Babu Wanda yake iya riqota haka sai mutum daya saidai kafin ta juyo ta hango su NURU tafe da sauri ta juyo ta jasa da gudu suka boye bayan wata qatuwar bishiya tana Dora Masa hannun abaki qasa qasa tace"

Shihhh su NURU na zuwa.

Wani shu'umin murmushi ya sakar Mata Yana gyada Kai kafin ya juya ya zubawa NURU mayun idanuwansa dukkanin yawunsa na katsewa akan NURUn,

Meyesa ba NURU ce wadda Allah yabasa sa'a akantabane Dan wlh baitaba jin mugun kwadayin maceba Kamar NURU gashi padimanma tai Masa Amma da zaa basa zabi da NURU zai zaba Dan duk Wanda yagama samunta a Mata ko a abokiyar haihuwa yagama dacewa,

Mummunan faduwa gabansa yayi daya tuno da hadda abal dinsu acikin yan sauyin 'yanci take ya waiwayo da sauri ya kalli padima Yana girgiza Kai Dan wlh bazai yadda yabarta tashige zuriar delah ba tabarshi Dan har abada bazai taba samun kyakkyawar mace kamarta ba tunda dai NURUn yasan ba samunta zaiyiba Kuma dai dole cikin dayan biyun ne ko padima ko NURUn,.

Ina Ina ina""yafada cikin ransa da sauri Yana girgiza kafin ya maida kallonsa kan bayan NURU data wuce Yana tunano da kaf delah yanzu duk Wanda za'a kaiwa negestati Babu Dan yaro yaro sbd yara yara shekara daya kenan cif da aurarda yayan masarautar delah din su goma sha daya Kuma a qaida saikayi shekaru uku

da aure zaka fara karban negestati sai wainda basuyi aureba sukuma baa Basu negestati sai sunyi aure.

Kallonsa padima tayi da manyan idanuwanta tana cewa"

Yaya dai?

Tunanin me kakeyi?

Wani murmushin bazata ya sakar Mata Yana sake jawota jikinsa Yana shafa hannuwanta Yana matsawa ahankali ya kashe ido Yana cewa"

Padi padi,

Padi nidai maganar gaskia zanje nasamu abal dinku yasan da maganarmu sbd so nake kafin kwana talatin dinsa tacika kinzama tawa mun wuce gizah..

Da wani kallo ta katsesa tana Dan zamewa idonta akansa tace"

Kwana talatin kamar dai wadda aka gaji da ita,

Amed nafada maka banason auren gaggawa sbd inason aurena yazama abinda zai burge kowa,

Banice baiwa ba abal dinane bawa Dan haka Ni inada damar yin bikin aurena kamar na kowanne 'yantacce,

Hakama Ina buqatan shiga boyon wankan ruwan madarar nono na tsawon sati biyu hakama Ina buqatan siracin nonon raqumi na tsawon sati biyun Shima sbd ranar dazan fito muka isa gizah aranar za'a tabbatarda nafi fiyeda Rabin matan sarautar kyawu.

Wani murmushin manufa tasaki tana sake riqe hannuwansa cikin kisisina Dan kuwa itadai babban burinta tasamu isa delah gizah inda asalin arxiki, mulki da sarauta suke

Kyawunta shine zai cika Mata burinta shikuma amed shine mukullun tafiyarta.

Cikin marairaice fuska yace"

Padima bazan iya Bari kwana talatin din abal dinku yacikaba sbd zai iya zamtowa kece zai bada bazan iya rasakiba padima mutuwa zanyi idan bake.

Wani kallon rashin fahimta take binsa dashi fuskarta na sauyawa tace"

Badawa Ina?

Gyara tsayuwa yayi Yana sake tamke hannunta yace"

Abal dinku ya karba shedar sauyin yanci.

Wani irin bugawa kirjinta yayi tana qwace hannunta daga nasa cikin son qara tantancewa tace"

Negestati??

Gyada Mata Kai yayi Yana cewa"

Eh padima Kuma Nanda kwana talatin ne za'a karba wadda zai bada kowane lokaci za'a zo afara gyaran ko ke ko NURU.

Wani irin daure fuska tayi zuciyarta na harbawa da qarfi a matuqar zabure take cewa"

Meyasa abal zai Mana haka?

Meyasa zai yanke hukuncin badamu negestati baiyi shawara damuba bama wannan ba"" da sauri ta rqio hannunsa son tabbatarwa tace"

Amed ko kasan waye za'a karbanwa negestati din?

A delah tanan ne ko a delah gizah be?

Fadamun da sauri amed inason sani ne idan a delah gizah za'a Kai.

Kallo biyu yake Mata,

Kallon Sonta da kallon yasan manufarta akansa Dan haka cutar cuta za'ayi yasani Sarai sbd yace gizah zasu take taredashi ta yanda idan an isa zatasan yanda zatai ta watsar dashi ko negestati ta zama acan din ta yarda shikuma Yana sane Sarai ba gizah din dazashi hakama yasan wannan tambayar datake Masa Dan taji idan Wanda za'a kaiwa negestati a gizah ne tsaf zata samu abal dinta tace abadata Amma yasan yanda zaiyi da ita ko taqi ko taso ita din tashi ce shi daya.

Bata fuska yayi kalar tausayi ya riqota Yana cewa"

Padima shiyasa bazan iya Bari abadaki ba sbd anan delah ne za'a bada Kuma qarin cikin abin a yanda naji abeela za'a kaiwa qila mutuminda shine kusan babba acikin jikokin delah ya tsufa ko me zaiyi da mace yanzu?,

Padima bazanso kije rayuwarki ta gurbata ba Zaki samu arziki da mulki Amma baida amfani sbd bazaki more rayuwarki yanda kikeda buri ba gwara muyi aure mutafi gizah acan nasan rayuwa zatai Mana dadi.

Jin Wanda za'a bawa negestati din yasake daga hankalinta tafara girgiza Kai tana cewa"

Badai ni padima yonas ba,

Sam rayuwata bazata mutu ba agurin bautawa tsohoba duk ya zugemin kyau da quruciyaba,

Padima darajata ta wuce Nan wlh bazan yardaba saidai NURU koma meryam za'a bada abada nidai wlh bazan yardaba.

Juyawa tayi ta nufi hanyar gida cikin tsananin tashin hankali batareda ko takansa tasake biba,

Duk rashin hankalinta da girman kanta bazata iya bijirewa iyayenta ba saidai zata fada musu bataso idan sun nace bazata iya musu taurin kaiba saidai

Abu biyune tasani matuqar aka bada ita negestati to rayuwarsu kaf tana cikin hadari sbd duk Wanda aka kaiwa ita ya kwana da ita zaijita ba budurwa ba Wanda hakan babban laifine hukunta kisa itada iyayenta duka idan sunada jini acikin delah wadda ta taba zama negestati shine zata roqar musu sassauci baza'a kashesu ba saidai za'a koresu daga qasar gabaki daya to gashi basuda Yar uwa ko daya delah dama burinta ta auri amed sukoma gizah inda tasan kyawunta saisa kaitsaye tasamu Dan sarauta bayan tasan yanda tayi ta rabu da amed yanzu ga wannan babbar maganar ta bullo yau ita wazata fito tafadawa kada abadata sbd ita din ba budurwa bace.

Koda ta isa gida har wani murdawar tashin hankali cikinta keyi tayi danasanin bawa amed kanta yafiso cikin kwando dari Dan kuwa Sarai tasan masifar hakan a addinance dakuma al'adance.

Tana shiga gida dakinsu tayi da sauri ta ajiye kayan hannunta tafito ta zari buta ta nufi bayi tana kaucewa kallon inda abal da amminsu ke zaune suna binta da ido.

Koda tashiga bayin kasa yin komaima tayi tafito tana qoqarin sakewa tazo gurinsu abal din ganin su NURU sun dawo ta zauna anacin gasasshen dankalin dasukeci da ita.

Kallon NURU abal dinsu yayi hakanan yake sakejin hankalinsa yafi kwanciya da zuwan NURU sbd ita din tafi cancanta duk da baisan waye za'a kaiwa ita ba Amma dai yasan delah basuda tarihi mara kyau Dan haka duk Wanda za'a kaiwa baida fargaba ko shamaki.

Padima yakalla yasake kalla zuciyarsa nasake tabbatar Masa da kamar kaita wani kuskure ne koba komai yafison yabarta ta aura Wanda take Dan burintane ita Kuma

NURU bada ita ba'a shiga haqqintaba sbd batada wani buri sai wanda su iyayenta suka yanke akanta.

Ajiyar zuciya ya sauke tareda kallonsu cikin nutsuwa yafara koro musu bayani komai tareda dorawa da cewa"

Padima kiyi hkr da wannan al'amari daza'a Kira da qaddararre sbd tabbas kowane uba zaiso ganin ya aurar da dukkanin 'yayan da Allah ya azurtashi dasu,

Naso ganin hakan Nima kamar kowane uba saidai Allah be nufa zanga na dukkanin 'yayana ba saidai biyu daga ciki Dan haka padima Ina Baki hkr dakuma umartaki dakiyi biyayya wa Ni mahaifinki dakuma al'ada da dole ki karbi wannan qaddarar dan haka saiki nutsu Zaki daina fita daga gobe sbd za'a fara Miki wanka da siracin sabuwar Madara za'a fara kawowa daga DELAH.

Tsit sukayi dukkaninsu kamar ruwa ya cinyesu musamman padima da jikinta yadauki mazari tafara hada zufan tashin hankali Wanda yasa umminsa shiga tunani me firgitarwa kafin wani yayi magana padimar ta bude Baki murya na rawa tace"

Abal...abal NURU.... NURU..Ni inason A....zungurinta umminsu tayi tareda katseta da cewa"

Kutashi kuje kuyi tunani inshallah Zakiyi farin ciki da hakan ba dama gidan arziki da mulki kikeso ba Inshallah zakiji Dadi.

Cikowa idanuwanta ke neman yi ta girgiza Kai tana cewa"

Ammi ba hakan bane ni...Ni..

Kuje nace padima.

Kamata NURU da jikinta yagama sanyi tayi Dan ita gabaki dayama ta firgice dajin abinda yake faruwa sbd ita ko delah akace za'a saitaji duk ta firgice bare ace itace zata shiga delah ta zama jininsu Sam firgici ma tunanin hakan yasata shiyasa tausayin padima yashigeta me tsanani duk da tasan padima ita zata iya duk da idan tashiga ita din ba komai bace Amma dai gwara ita zata iya.

Suna shiga daki padima ta zube kan shimfida tana sake shiga tashin hankali wlh Bata shirya mutuwaba,batason mutuwa Ina zata saka kanta dole ta samo mafita.

Duk irin lallashi da kulawarda NURU ke Mata cikin tsananin tausayawa Sam Bata fahimta sbd hankalinta baya jikinta.

Abu biyu da biyu ga zama negestatin tsoho mara amfani,ga tsoron agano ta taba kwanciya da wani Kuma ta shiga delah ga tsoron hukuncin hakan duk saitaji tana neman haukacewa wlh bazata iyaba Gwara abada NURU Dan ita tunda duniya Bata dametaba zata iya rayuwa da tsoho ko baida amfani itadai ba ruwanta can su qarata.

Har gari ya waye Bata rintsa ba sbd tsananin tashin hankali Koda ta fito da safe babu Wanda bai fahimci Bata hayyacintaba duk ta firgice gashi tanason ganin amed suyi magana Kamar me ba halin fita Dan idan Bata samu magana dashiba komai lalacewa zaiyi.

Da maraice saiga manyan bayin delah kusan guda goma sha biyu sunkawo tarin kayan wankan Madara daza'a fara Mata washe gari tana ganin hakan hankalinta yasake tashi jama'ar gari kuwa suna gani suka tabbatar aka fara zarya gidan tayasu ammy murnar samun yancin abal da murnar shigar 'yarsu delah.

Kwanaki goma sun shude da fara gyaran Negestati padima Amma Sam hankalinta a hargitse take takai yanxu ko rintsawa Bata iyayi tun abin na wasa tadawo ko abinci Bata iyaci take tafara wata irin rama da duhun tashin hankali daganan sai kukan dare Wanda yayi masifar daga hankalin NURU da duk duniya taqi jinin ganin damuwa akan fuskar iyayenta da 'yan uwanta ta tashi cikin tsakiyar dare tareda lalubar qaramar fitila ta kunna taga padima zaune hannunta riqeda wuqa tana faman wani irin kuka da sauri ta qaraso ta fixge wuqar cikin tashin hankali da tsoro jikinta yadau rawa sbd ita qaramin abu ke firgitata tace"

Padima me Zakiyi da wannan tafada ta wurgi da wuqar cikin tsananin tsoro.

Sabon kuka padima tasake tana qwacewa tace"

Mutuwa zanyi tunda ko ban kashe kaina yanxuba naje delah mutuwa zanyi.

#MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

SAFIYYAH HUGUMA

BILLYN ABDULL

MISS XOXO

HAFSAT RANO

MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN K xxAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899[9/6, 6:12 PM] Anty Rabi'at: *_UBAYD MALEEK_*

(Royalty versus love)

*_Mamuhgee_*

4

Cikin tsoro da rawar murya NURU tace"

Padima kidena cewa mutuwa kina bani tsoro sosai kidaina kuka menene Dan Allah ki dena kina bani tsoro.

Ganin yanda NURU duk ta firgice cikin tsananin tsoro yasa tadan sassauta tayi tunanin amfani da tsoron NURU sbd dama can ita abu kadan yake Bata tsoro saita sake marairaice fuska tana faso wani kukan tace"

NURU idan Banga amed mukai magana ba akwai babbar matsala wlh komai zai lalace zamu rasa komai da iyayenmu duk mutuwa zamuyi.

Zaro manyan fararen idanuwanta NURU tayi jikinta na daukar rawa tana sake padiman takasa magana tana neman yin baya ta fita a rude padima ta riqota da qarfi tana cewa"

NURU wlh dagaske nake idan bangansa munyi magana ba komai zaifaru Dan Allah kimin hanya naganshi idan nadawo zan fada Miki komai Amma wlh rayuwata na cikin hadari danasu abal ma..

Kasa fahimtarta NURU tayi sbd firgici sai rawa da jikinta keyi ganin hakan yasa padiman taja wani qaramin tsakin takaici tareda girgizata da qarfi ta jawota ta direta zaune tafara shafa bayanta tana hura Mata iska tana kiranta ahankali ahankali hartafara nutsuwa tana dawowa hayyacinta saidata rarrasheta tadawo hankalinta tsaf tukuna ta janyota ta kwantarda kanta kan cinyarta tafara Sabin hawayen samun yaddar NURUn tasake fada Mata abinda tafada Mata da farko NURUn daketa ajiyar zuciyar ta qanqame padima cikin tausaya Mata murya amatuqar sanyaye tace"

Padima idan kikaga amed din shine zesa bazaki kashe kanki ba ko?

Eh NURU bazan kashe kainaba Ni sbd ma kune nakeson ganinsa na nema mafita.

Haka ta lallaba NURU taringa marairaice Mata da kuka hartayi nasarar cika tunanin NURU da tausayinta akan alamarin shiyasa washe gari da za'aje wankan ruwan Madara saita lullube fuskarta taje amaimakon padima bayan tayi Mata hanya sunyi sauyin kaya ta fitar da ita gidan masu wankan dasuka ganta saisuka tambaya tace ai yanzu ita za'a ringawa ba padima ba dayake bayin qasane gabaki daya saisuka yarda sbd manyan bayi basa fitowa delah bare akawo musu irin wannan.

Dama Shima NURU taje ta sanar dashi padima zata fito tanason ganinsa shiyasa yaje inda suke haduwa Yana jiranta danshima a mugun qage yake da ganinta Dan

wlh Shima be shirya mutuwaba tunda yasamu labarin ita aka bayar yasan qaryarsa taqare kashesa zaayi duk ranarda akaji shine yafara kwanciya da ita.

Kamar munafuka haka take tafiya tana waiwaye tana boye fuska harta iso Yana ganinta da gudu ya qaraso yakama hannunta suka nufi can nesa da gidajensu cikin wani lambu bayan bishiyar ayaba ya rungumeta Yana cewa"

Ya Allah Padima nafekushi

(Ya Allah padima Nayi kewarki sosai)

Kuka tafashe dashi tana turesa daga jikinta tace"

Amed duk mutuwa zamuyi

Banason mutuwa guduwa zanyi da qasarnan zanshiga duniya bazan tsaya akasheni ba...

Riqota yayi da sauri Shima cikin firgicin yake yace"

Padima ki nutsu musamo mafita Nima angaya Miki na shirya karban wannan hukuncin ne?

Bazan iyaba nikaina mafitar nake nema.

Zamewa tayi qasa tayi zaman dirshan tana cewa"

Amed kayi gaggawar samo mafita kokuma kawai mu gudu.

Mu gudu muje Ina padima?

Idan muka gudu burirrikanmu fa damuka Dade muna....

Cikin masifar tashin hankali ta katsesa da cewa"

Burin banza tunda Saida rayuwa zamu cika burin,

Ni kaga kawai musan abinyi wlh na cikin masifa wannan wane irin balai ne nasaka kaina aciki amed ka cuceni...

Kinga yi hakuri kidaina kukan yanxu mafitarmu dayace ajanye badake abada NURU.

Wani kallon takaici da baqin ciki tai Masa tana cewa"

Sun San da NURUn suka badani sbd tunanin ita wawuyace batada wayo Ni bansan inda zansaka kainaba zuciyata fashewa zatayi....

Da sauri ya durqusa gabanta cikin Dan samun sa'ida yace"

Muyi amfani da sanyin halinta kiyi Mata wayo ki gurbata Mata tunani da tsananin tausayinki ki Bata tsoro da rayuwar iyayenku da kanta zata bada kanta.

Dakatawa tayi da kukan datake ta dago idanuwanta dasuka gama kunbura sukai jajir ta kallesa tana qoqarin karban abinda yafada din cikin nazarin maganar tace"

Kumafa hakane..

Batada wayo zan iya sata ta bada kanta da kanta.

Zabura tayi ta miqe tsaye tana share hawayenta cikin farin ciki tace"

Meyasa banyi tunanin hakanba tun farko?

Meyasa na tsaya Bata lokacina cikin tsoro da tunanin zan mutu bayan inada NURU.

Riqosa tayi da sauri cikin tsananin farin ciki tace"

Amed kashirya komai zai tafi yanda mukeso zanji da NURU sauran aikin idan mukazo tareda ita saikayi naka.

Rungumeta yayi Yana cewa"

Karki damu tunda munada wadda zata shiga tarkon mukuma mu fita kuka yaqare sai Dadi da rayuwar delah gizah dake jiranmu.

Shafarta yashiga yi Yana lallashinta da qara Bata shawarwarin yanda zasuyi hardai suka samu suka sake biyan buqatarsu agurin Saida duhu yadan yi yarakota har bayan gidansu ta zagaya tashige yakoma cikin farin ciki.

Itama cikin farin cikin tadawo gidan ta tararda NURU a daki tana jiranta cikin firgici da tsoron rashin ganin dawowarta kan lokaci tana ganinta ta taso da sauri cikin tsoro ta rungumeta tana sauke ajiyar zuciyar ganinta tace"

Padima kinbani tsoron rashin dawowarki kan lokaci.

Murmushin jin Dadi padiman tasaki tana rungume NURUn tace"

Wallahi Bet'ami afek'irihalewi NURU.

(Wallahi Ina tsananin sonki NURU)

Ajiyar zuciya kawai NURU ta sauke suka qarasa komawa ciki suka zauna ta marairaice fuska tana Shirin fara hawaye NURU ta katseta da cewa"

Padima karkiyi kuka Dan Allah tunda kingansa kinsamo mafitar matsalarki ko?

Girgiza Mata Kai padima tayi tana tsoyayo hawaye tace"

NURU banason mutuwa,

Banason abal da ammi suma su tafi su barku dagake se meryam qilama duka tafiya zamuyi mubar DUNIYAR bansan yazanyiba duk nice na janyo shiyasa nakeson na kashe kaina nahuta kowama ya huta.

Da sauri NURU ta girgiza Mata Kai tana cewa"

Padima bazan iya Bari ki kashe kankiba gwara mu mutu gabaki dayan koma menene yafi Mana sauqi bazamu iya juran rashin 'daya daga cikin ahalinmu ba kidaina fadar hakan muna tsananin sonki bazaki mutuba yanzu inshallah.

Jan numfashin kuka tayi murya na fita daqyar tace"

NURU kinsan menene yake faruwa ga duk negestati dinda aka Kai aka tararda batada budurci tabawa wani??

Ras Ras qirjin NURUn yayi wani mummunan bugawa harsaida jikinta ya nuna hakan sbd rawar daya Dan dauka ta kalli padima da fararen idanuwanta cikin rashin fahimta tace"

Meya kawo wannan tambayar padima?

Sunkuyar dakai tayi tana tsoyayo hawaye tace"

NURU nida amed mun.....

Wani mummunan tarine ya qware NURU idanuwanta suka firfito tafara tarin cikin azaba da tashin hankali tun tana shafa Mata baya hardai dole suka fito daidai fitowar amminsu Nan sukai kanta akaita Bata ruwa Ana fesa amata Amma sosai ta sarqu idanuwanta sunyi jajir sbd azaba cikin fada ammi tace"

Menene ya sarketa padima?

Ammi kawai zaune take saita fara tari shikenan ne kawai.

Fitowa abal yayi daukeda sabuwar madarar raqumi yabata yakuma fesa Mata take abin yafada Mata tafara fidda numfashi daqyar tana rufe idanuwanta cikin galabaituwa.

Padima ta tayata ta watsa ruwa takaita daki itama tadawo tayi wankan tazo tayi sallah saikuma takejin kunyar NURU din Amma Kuma tunda dai amfani takeson yi da ita dole zata fada Mata hakan.

Kwanciya dukkaninsu sukayi babu ko me dogon motsi sbd tunanin da kowa keyi musamman NURU dake cikin tashin hankalin jin masifar dazata samu ahalinsu.

Washe gari ma NURU ce taje wankan ruwan madaran haka zalika takasa sake tankawa padima maganar dasukai din sbd har lokacin shock din maganar Bata saketaba.

Padima ganin ankwana biyu NURU taki cewa komai gashi zuwa lokacin kowa ya shaida NURUn Bata cikin hayyacinta tana cikin tsananin tsoro da tashin hankali saidai anyi tambayar duniya taqi fada sai kuka.

Hankalin iyayensu yatashi sosai musamman da itama padima suka lura duk a firgice take ta bangare daya wankan haryanxu basuda masaniyar idan anzo NURU akewa sai gidan yakoma Kamar gidan da akai muguwar mutuwa sbd gabaki daya kowa

baya cikin nutsuwa anyi anyi NURU tafada abindake damunta taqi fada sbd gabaki daya tsoro da firgicin abinda zaisamesu yasa ta kasa dawowa hayyacinta tsoron fadama takeji.

Yau dai padima da takaici da baqin ciki ya isheta sbd saura kwana goma sha biyu cikar wa'adin cikin tsakar dare ta tashi ta sake dauko wuqa yauma tadawo ta zauna tsakar dakin tareda fashewa da kuka yanda NURU zataji Dan dama tasan ba bacci takeba saigashi tana bude ido taga padiman ta daga wuqa zata sokawa kanta da gudu ta zaburo ta riqeta cikin tashin hankali tace"

Padima.

Qwace wuqar ta hau Yi padiman ta riqe cikin tsananin kuka take cewa"

Kibarni NURU gwara na mutu sai kowa ya huta matsalarmu da tsoronmu zai qare idan na kashe kaina shikenan Babu Wanda zaisan abinda nayi bare rayuwar abal da ammi tashiga hadari duk laifinane Dana Bari harnazo yanxu ban Kai qarshen matsalarba gashinan kema nasaki a damuwa bazan iya ganinki cikin damuwa da qunciba NURU sbd Ina tsananin sonki 'yar uwata.

Cikin hawaye NURU tace"

Bazaki iya ganinaba cikin qunci kike tunanin Ni zan iya ganin kin kashe kanki.

Zamewa tayi ta zube qasa tana rusa wani sabon kuka tace"

NURU komai ya lalace a rayuwata

Mutuwata itace salama agareku sbd matsalar ta wuce yanda kike tunani NURU cikine Dani yanxu haka...

Neman zubewa NURU keyi padiman tayi saurin riqota tana cewa"

Kingani ko gashinan kina neman sumewa sbd jin wannan muguwar masifa gwara na mutu kowa ya huta NURU kibarni kawai....

Kokuwa suka hau Yi akan saita dauki wuqar NURU na riqeta cikin tashin hankali take gabaki daya hankalinta yakasa dauka wai padima harta San bawa wani kanta,mutuncin,qimarta hadda ciki.

Zubewa tayi qasa tareda rushewa da wani irin kuka Wanda yasa padiman itama zubewa tana sakin nata kukan.

Kwana sukayi kuka Koda gari ya waye kowacce fuskarta da idanuwanta sunyi suntum ai Nan hankalin abal da ammi yatashi musamman dasukai tambayar duniya kowacce tayi shiru har Saida abal din ya harzuka yace aqyalesu koma menene idan sunji uwar Bari sunzo dakansu sufada itadai ammi hankalinta bai kwantaba taringa lallabarsu Amma ba wata mgn saima Kamar zurfafa da NURU keyi da tunani.

Jan padima NURU keyi Kamar wata qaramar yarinya harsuka isa inda tacewa amed su hadu suna zuwa kuwa Yana gurin NURU ta jefesa da kallon qyanqyami da baqin ciki take zuciyarta ta gaurayu da tsanarsa saidai Babu yanda ta iya tunda dole cikin biyu daya za'ayi dole shine zataji idan zai auri 'yar uwarta daya lalatawa rayuwa.

Wani abu ta hadiye me Kama da dutsi ta zuba Masa manyan fararen idanuwanta dasuka kusa gigitashi ya dauke Kai da sauri sbd wlh kallon cikin qwayar idanuwanta kawai na iya sumar dashi da duk wani ma'abocin begenta.

Ka yadda da Kaine kawai kasan padima amatsayin 'ya mace?

Da sauri ya gyada Kai Yana satar kallon padiman dake Masa wani kallo.

Sake jeho Masa qata tambayar tayi da cewa"

Kasan cewa tanada juna biyu yanzu haka a jikinta Wanda yake nakane?

Nasani Kuma ashirye nake da aurenta kafinma kowa yasan da akwai cikin Amma Kuma sbd zata zama negestati wannan al'amari yazama mafi hadari ga rayuwarmu mu duka hadda ta iyayenmu,

Wlh inason padima sosai itama tana Sona NURU Amma yanzu tsautsayi daya gitta mukai wannan abin yasa yazama Kamar wata mummunar qaddararmu da iyayenmu da basujib Basu ganiba..

Rintse ido NURU tayi wani nauyi na ziyartar zuciyarta idanuwanta sukai jajir tace"

Idan harka aminta zaka aureta shikenan kaje kashirya kawai.

Juyawa tayi tabar gurin idanuwanta na sake rinewa da tashin hankali ta nufi gida ko gabanta Bata gani sosai ta fada dakinsu ammi dake zaune tsakar gida tana gyarawa meryam gashi tabita da kallo zata miqe tabita saiga padima tashigo itama tafada dakin.

Rungume NURU tayi cikin tsananin farin ciki ba kunya tahau yimata kukan godiya NURU da baqin cikin al'amarin ya danne Mata zuciya tace"

Padima menene ribar wannan masifar dakika saka kanki damu aciki?

Shin bakiyi tunanin abinda zai faru da iyayenmu ba lokacinda Zaki bawa wani kanki?

Shin bakiyi tunanin wace rayuwace makomar nida meryam ba idan hukunci yahau kanki keda iyayenmu?

Menene laifin su abal dabasujiba Basu ganiba idan anhukuntasu akan laifin da Kika aikata bayan dawainiyar dasukai akanmu suka bamu tarbiya.

Riqota padima tayi cikin marairaicewa tace"

NURU nayi nadama nayi Dana Dani Kuma tunda kin amince da rufa min asiri ki sauyeni ai matsalar ta wuce.....

Ta wuce?

Ta wuce fa kikace padima?

Cikine fa ajikinki na namijinda ba mijinki kike cewa shikenan yawuce.....

Qarar sakin kofin silba sukaje daga bakin qofa take suka juya da sauri cikin firgici ganin ammi hadda abal tsaye yasa padima fara rawar jiki cikin tsananin tashin hankali NURU kuwa zamewa tayi ta zaune al'amarin na isarta Sam kanta baya iya daukan doguwar pressure.

****

Jericho new York

Setin akwatinanta guda biyar cif aka jera Mata cikin mota guda qirar Mercedes Benz beymach 10/2607 2021 ta fito daga bedroom dinta sanye cikin wata doguwar turkian royalle satin gown red me kyau wadda ta fidda kyanta da kyan jikinta hannunta riqeda handbag din arkins irin qamshin datake fitarwa me yawa zaisa kasake tabbatarda ta aje auren tun daga cikin dakinta Dan Vail din rigarma rolling dinsa tayi iya wuyanta tafara saukowa cikin yanayinta na yanga da aji kamar ko yaushe.

AFIA dake zaune Palo riqeda hannun farhat daketa kuka kamar ranta zai futa tana ganin fitowar mum din tasu ta miqe tsaye itama idanuwanta na fara tsiyayar hawaye tafara girgizawa mum din tasu Kai tana cewa"

Please no mum,

Mum please please no.

Itama lailar tanason 'yayanta tanason kasancewa dasu saidai tasan ko zatayi mushe ubayd maleek bazai barmata 'yayansaba Dan haka tunda tasan zasu samu kyakkyawar rayuwa tareda dad dinsu bazata wani damuba ta qaraso ta rungumesu suka qanqameta suna kuka sosai suna roqonta sai Basu hkr takeyi tana cewa"

Zakuyi alfahari da mum dinki idan kukaga tazama cikin top 20s Inshallah.

Zamewa tayi zata wuce farhat ta maqalqaleta tana sakin sabon kuka cikin firgici tana Kiran sunanta.

Ganin haka hankalin afia yatashi taga mum din dagaske tafiya zatayi batasan yazatayi ta hanata tafiya ba batada zabin daya wuce takira _NEGES MUHAMMAD KALEEB DELAH_ asalin kakan dad dinta, tsohon NEGES(sarki) Wanda shine mafi soyuwa da shaquwa agurin dad dinsu sbd shine ya riqesa tun yarinyarsa sbd mahaifinsa dashine yakama yazama sarkin yanxu ya rasu sai qaninsa ya hau bayan an aura Masa mahaifiyarsa Wanda haryanxu shine asalin sarkin delah gizah na yanxu mahaifiyarsa Kuma sarauniyar delah gizah hakan yasa kakansa shine mafi kusanci dashi arayuwarsa danma shine ya tsaya Masa aka taka dokar mulki yabari ya auri LAILAH OMAR masoyiyarsa dasukai karatu tare 'yar asalin ghana dasuka hadu a San Francisco.

Duk da ba wani yabawa KALEEB yayi da LAILAH ba Amma sbd farin cikin ubayd yasashi amincewa yakuma rufe idonsa ya taka doka Dan haka yakeda burin qarawa ubayd maleek Mata Amma ubayd Yana qaidojin rayuwarsa Dan haka abin be yiyuba.

Akwai lokutan da ba'a Kiran KALEEB kaman dad dinta dashima akwai lokacinda ba'a kiransa Amma yau dole zata kirasa sbd shikadaine zai Hana wannan rabuwar sbd iyayen nata Babu Wanda ya tsaya ya saurareta.

Cikin sa'a Kira biyu a na uku aka daga cikin sauri tayi bayanin ita wacece tanason mgn da KALEEB sanin matsayin UBAYD da iyalansa agurin KALEEB yasa aka Kai

Masa wayar cikin girmamawa aka miqa Masa ya karba sbd sanin ba'a kawo Masa waya sai me mahimmanci idan bashi yace akawoba.

Tanajin nutsatsiyar muryar Kaleb ta nutsu jikinta na rawa zata fara Masa bayani taji durin motar dad dinta yadawo Wanda yasa gabanta faduwa.

A nutse ya zuro dogayen qafafuwansa dake sanye cikin black brian Atwood brand loafers kafin yafito gabaki dayansa cikin Ralph Lauren brown suit data fiddo da dukkanin hasken fatarsa ta asalin amhara ethopiano.

Kallo daya zakai Masa kasan shine ya haifi AFIA sbd Kamar dasukeyi tayi yawa duk da Kamar yanda bazakace LAILAH ce ta haifi budurwa kamar afia ba haka Kai tsaye Shima bazakace shine ya aje budurwar 'ya ba sbd kyawun jikinsa da dukda yafara girma bai rabu da geamin ba ma'ana motsa jiki uwa uba ajinsa da asalin kyawunsa tareda izzarsa datake cikin jininsa da har gobe fresh take zamar masa Dan ko ita lailar har gobe duk gayunta da kyanta da Jan ajinta Rena kanta take agabansa shiyasa har gobe take kishin tazama wadda zata tsayu da kanta duniya tasanta da sunanta bada sunan waniba.

Ciki ya nufo qanshinsa na sauya atmosphere din gidan afia na ganin hakan tafara fadawa Kaleb abinda yake faruwa cikin nutsuwa da sauri....

Daidai shigowarsa farhat tasaki Laila tayo kansa da gudu ta fada jikinsa tana sakin sabon kuka Wanda yasashi sake tsuke fuskarsa tsaf wadda tasa Laila dauke Kai daga kallonsa ta nufi qofa zata fita baice Mata qala ba hakama AFIA qafafun lailan dasuka fita ta qurawa ido daidai Kaleb yagama jin komai zaiyi mgn sukaji daddadar muryar dad dinta data ratsa har cikin wayar zuwa kunnen Kaleb yace"

Na datse igiyan aurena dake kanki na sake ki you're free to go MSS LAILAH OMAR.

Dif afia ta dauke wuta cikin tsananin tashin hankalin jin abinda dad dinta yafada Kamar daga sama taji muryar Kaleb cikin ikonsa na tsohon sarki yace"

Ki dakatar da ita injini.

Muryarta na rawa idanuwanta na dishi dishi tace"

Mum Kaleb yace ki tsaya karki tafi Injishi.

Qin juyowa tayi bayan Sarai taji me afia tace saidai bazata iyaba ta daga qafafunta ta isa bakin mota aka bude Mata tashige suna kallo ta tafiyarta idanuwanta na cikowa da hawaye ta maida tana qoqarin kawarda abinda yake taso Mata saidai takasa Saida ta fashe da qaramin kuka tana rufe fuskarta da hannuwanta har suka fice daga qatuwar harabar gidan.

Murya na rawa cikeda firgici afia tace"

Kaleb Ta fita,ta tafi tabarmu.

Wani numfashi Kaleb ya sauke akaro na farko a tarihin rayuwarsa da wani ya bijire Masa Kai tsaye Kamar agaban idonsa Wanda shikansa ubayd hakan yasa dukkanin wata sauran kaunar Laila yaqarasa fice Masa daga zuciya har abada.

Cikin wata irin murya me babban sauti Kaleb yace"

Ki sanarwa da mahaifinki Ina buqatar ganinsa cikin gaggawa zuwa delah.

#MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

SAFIYYAH HUGUMA

BILLYN ABDULL

MISS XOXO

HAFSAT RANO

MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/6, 6:12 PM] Anty Rabi'at: *_UBAYD MALEEK_*

(Royalty versus love)

*_Mamuhgee_*

5

Zubewa AFIA tayi kan kujera tana sake wani irin kuka tana cusa kanta cikin tafukan hannayenta dasuke rawa.

Kamar zai wuce saikuma yaji afian na buqatarsa ayanxun sbd yasan tana cikin radadi.

Cikin takunsa na zallar nutsuwa ta asalin jinin sarauta yatako ya iso gabanta tareda miqa mata hannu batareda yayi mgna ba ta dago jajayen idanuwanta dake tsiyayar hawaye ba kakkautawa ta damqe hannunsa tana Kiran sunansa ahankali cikin kuka mara sauti.

Janta yayi farhat na jikinsa ya haye sama dasu zuwa ainihin babban bangarensa dake daukeda qaton palon farko Dana biyu Wanda baiyi girman na farko ba acikin palon na biyu Nan qofar qaton master bedroom dinsa yake ita Kuma lailah qofar bedroom dinta na tun a palon farko sukuma su afia din sukeda manyan bedrooms dinsu guda biya ata cikin Palo na biyu dake qasa ita daya farhat daya Amma a dakin AFIA din take kwana da farhat sbd tazama tamkar itace uwar farhat din duk da akwai tarin Nanny's da masu aikin dake kula dasu duk su duka din sbd Sam tun tashinta kafinma haihuwar farhat mum dinsu tabarwa masu renonsu dawainiyarsu Sam batada lokacin kantama bare na 'yayanta shi koyaushe tana gurin aikinda zata Gina sunanta duniya tasan da ita shiyasa acikin kadaici afia ta taso harsai bayan uwan farhat duniya tasamu sauqi sbd duk da akwai masu kula da farhat itakam Bata barmusu ragamar farhat din dukaba musamman da watanta goma cif aduniya lailah ta yayeta daga Bata nono tun afia Bata iya dawainiyar farhat ba harta iya shiyasa farhat din duk duniya tafi shaquwa da afia da dad dinta duk da tanason

mum dinta Amma tafison dad dinta da afia itama afian sbd sanin mum ba lokacinsu takedashiba yasa girman dole yahau kanta duk da qananun shekarunta tazama itace madam din gidan dole masu aikin gidan kaf umarninta kawai suke jira sbd ita suka gani Matar gidan ko lokacin jininta tayi baresu masu aikin shiyasa basa Sonta bakuma su tsanetaba tunda batai lokacinsu bama bare musgunawa ko wulaqantawa da tozartawa 'yayanta dai Kam suna tsananin sonsu da qaunarsu tareda tausayinsu duk sbd mahaifinsu UBAYD MALEEK Wanda suke tsananin jin dadin aiki a qarqashinsa duk da tsananin miskilancinsa da ikonsa mulki dake jininsa Amma baida tsanani ko tsauri ko kadan.

Table din lunch aka gama gyarawa yaja 'yayansa suka isa dining room din farhat Kam harta sakewarta ganin ga dad dinta ga afia to itakam batada damuwa tunda dama haka suke rayuwa mum batanan koyaushe.

AFIA ce dai Saida qyar ta iya tuttura abincin Shima yacine kawai saidai Babu Wanda ya isa yace ya karanto kokuma ya fahimci halinda zuciyarsa da tunaninsa suke ciki cikin nutsuwarsa kaman koyaushe yaci abincinsa.

Ranar baisake fita ba yini yayi da yaransa cikin tsananin kulawa da qauna har dare sukai dinner sukaje sukai sallah da wanka suka kwanta AFIA na rungume farhat cikin jikinta sabbin hawaye masu zafi suna gangaro Mata.

Washe gari ma tare sukai breakfast da dad dinsu su suka fara wuce school da driver dinsu kafin shi daga baya ya fice.

Ahankali kwanakin suka fara tafiya damuwa tashigi afia sosai sbd yanda ta Sanya rabuwar iyayenta cikin ranta har abin ya tabata yafara taba karatunta komai Bata ganewa a makaranta tun Ana Mata mgn har Saida school din suka nema dad dinta sukai Masa bayanin kwata kwata Bata gane komai na karatu ko exams dinta gabaki daya Babu Wanda taci hakan yasa ya ragewa kansa aiki sosai sbd samun lokacin zama da yaransa Dan afia idan akai wasa zata iya samun matsalar qwaqwalwama.

Kullum takan Kira mum dinta Amma Bata wani Bata lokacin mgn she's always busy with aiki aiki aiki hakan yafara Sanya afian jin haushi musamman da ita mum din Bata taba kiraba saidai ita takira ta bangare daya ga dad dinsu Yana iya kokarinsa duk kasancewarsa me tarin abubuwan Yi Amma duk ya taqaita sbd su 'yayansa sai hakan yasa tafara dawowa hankalinta taji inama dad zaisamu farin ciki Kamar kowane mijin aure.

Ahankali ahankali trauma din rabuwar iyayenta yasaketa sbd watanni da aka 'diba tuni ta sakewarta yanzu suna rayuwarsu cikin walwala musamman Mum Sarah dake kulawa dasu sosai yanzu kamar itace ta haifesu matarda tun haihuwar AFIA Amman UBAYD ta Aiko musu da ita daga delah gizah gashinan haryanxu tana taredasu tana musu aiki danma ta zama Kamar kakarsu Amma Mum Sarah suke ce da ita sbd tun afia na qarama da farko ma ta dauka itace ta haifeta saidatai wayo tasan lailah ce ta haifeta Amma duk da haka qaunar kamr uwa da 'yace tsakanin afia din da mum Sarah,

Yanzu gidan rayuwarsu suke Kamar dama haka suke Basu taba rashin waniba agidan hakan yasaka hankalin dad dinsu kwantawa ya maida hankali kan harkokinsa musamman idan Yana dubin shekarun sauka mulkin NEGES ABDUL-SAMAD MUH'D KALEEB wato sarki na yanzu qanin mahaifinsa Kuma mijin mahaifiyarsa Wanda sbd Yana yarone mahaifinsa yarasu shiyasa akabada mulkin wa qaninsa kafin shi dansa ubayd ya girma Wanda Sam shi yanzu ba wani mulki dayakeso ko yake gabansa shiyasa bai taba sha'awar zama kusada mulkin ba yayi nesa dasu sbd ma kada son abin yasamu damar shigarsa Amma gashi lokaci na son qaratowa.

Ana cikin hakan kaleeb yaga lokaci nata ja zaman maleek guda baiyi Masa ba Babu mace ataredashi ma'ana Babu gurin sauke buqatarsa Sam Sam ubayd shine jika mafi soyuwa a rayuwarsa Kuma Wanda yakeji cikin ransa fiyeda 'yayan daya Haifa Dan haka bazaiso wata mishkila ta bangarensaba ko kadan zai Masa shirin negestati yatafi da ita inda yake kafin yafara nazari da duban inda zai samo Masa matarda duniya zata shaida UBAYD MALEEK yayi matarda ko indatake akace matarsa lailah data watsa Masa qasa a ido ta kalla tasan tayi babban kuskurenda har abada bazai gyaruba.

A jiya 'daya daga cikin amintaccin bayinsa da tun iayayensu nada rai sukai Masa bauta yai tunanin yonas Wanda cikin wainda aka bawa sauyin 'yanci shikadai ne me 'ya mace wadda zataso amatsayin negestati.....

wani irin numfashi ya sauke ahankali Yana gyara kishingidarsa akan qatuwar shimfidar babbar dardduma me tsananin laushi dayayi sallah bai tashiba Yana adhkar ya numfasa tareda daukar wayarsa dake gefensa ya Kira numbern daza'ayo Masa Kiran tsohuwar jakadiyar marigayiyar matarsa.

Cikin qanqanin lokaci saigata ta iso akai Mata iso tana shigowa ta zube qasa tana kwasar gaisuwa batareda ya dagoba cikin wani irin iko na tsohon sarki yace"

Akwai sabuwar sauyin 'yancin bawai ta negestati 'ya daga wajen bawa yonas 'dan tsohon amintaccen bawana ilyas gasasshiyar tabbarwa nakeso Kuma a sirrance zancen zaizama kije kidubota da kanki ki tabbatarda igancinta idan ta isa ta zamo wadda UBAYD MALEEK zai iya hada shimfida da ita wadda zai iya tafiya da ita can qasar dayake kafin asamo wadda zata maye gurbin igiyoyin aurensa idan yarinyar Bata kaiba atara bayi Mata azabi wadda tafi tsohuwar matarsa komai a killaceta anan cikin delah afara kulawa da ita Ana Bata gyara kafin zuwansa yatafi da ita kokuma kafin na aika Masa da ita.

Angama Kaleeb me delah me gizah.

Juyawa tayi da hanzari Dan zuwa cika umarninsa cikin sauti me amo taji yace"

Babu Wanda zaisan ubayd maleek ya rabu da matarsa hakama babu Wanda zaisan negestatin ta ubayd maleek ce.

Da saurin ta zube qasa cikin girmamawa da tabbarwa tace"

Duk ranarda wannan zancen yafita ta hanyata na bada kaina acire fansar cin amanar danayi.

Jinjina Mata Kai yayi ta miqe tafice tana sake basa gaisuwa.

****

Zaune suke jigum jigum fuskokinsu cikeda damuwa da baqin ciki Babu me iya mgn se sautin kukan padima dake fita ahankali ahankali tana roqon abal da ummi dasu yafe Mata tsautsayi ne.

Cikin nauyin zuciya abal ya dago ya kalleta da idanuwansa dasukai jajir kafin ya kalli ummin da ita shita kalla da idanuwanta dake cikowa da hawaye tana maidawa sbd batason zubarwada padima hawaye kada Allah ya kamata da laifin sakasu zubda hawaye abin yamata yawa,

Fahimtar abinda abal ke nufi da kallon dayai Mata yasa ta bude Baki daqyar cikin nauyin nurya data toshe da baqin ciki tace"

Padima mune iyayenki da bazamu taba zabar Miki abinda zai cutatar dake Dan haka kiji tsoron Allah kifada gskiar abinda yake faruwa,

Nice na haifeku duk ku duka Kuma nasan halin kowannenku fiyeda ku kanku tun ranarda akai maganar badake delah zuciyarki Bata amintaba Kuma shine dalilin dayasa Kika Hana kanki sukuni koba haka ba???

Tsit tayi tana Dan share hawayenta cikin jin tsoron anfara ganota takasa dago Kai ta kalli kowa cikin tsananin fushi da baqin ciki abal yace"

Hakane koba haka ba?

A kidime cikin tsoro tace"

Eh Hakane.

Dukkaninsu wani sabon baqin cikine ya turniqesu musamman NURU da hawayenta suka fara gangarowa.

A qyamace ummi tasake jefa Mata kallon baqin ciki tace"

Sbd baqyason abadake delah shiyasa jika bawa wani kanki yayi Miki ciki sbd ki nuna bamu isa dakeba duniyar dakikeso ita Kika saka gaba....

Da sauri ta girgiza Kai tana fashewa da kuka tace"

Ummi kuyi hakuri wlh banda ciki Amma..Amma...Amma tsoron hukuncin kasheku danima idan naje delah aka....aka..aka gano...yasa nace inada ciki sbd NURU ta yarda taje ta yanda Babu abinda zaisamu kowa wlh ummi sharrin shedan ne Kuma....

Wani wawan gigitaccen Mari abal ya sauke Mata guda biyu Wanda yasata zubewa kwance tana hadiye sauran maganar cikin tsananin tashin hankali sbd yaune karo na farko da aka taba lafiyar jikinta.

Kasa mgn ummi tayi sai hawaye sbd sunkasa riquwa yanxu Kam,

Cikin baqin ciki abal yace"

Sbd son ranki Kika siyarda mutuncinki,

Kika ringa wasa da amfani da qaunarda 'yar uwarki ke Miki harkina qarya da zance me girma na cewar kinada ciki Dan kawai bakyaso.

Kinyiwa kanki padima,

Kinyiwa rayuwarki,

Ban Miki bakiba Amma wannan abinda kikai shine babban kuskure mafi girma dazakiyi danasani akansa Amma tunda ke Kika zaba hakan 'yar uwarki zataje delah kekuma idan kingama tsare tsaren burikan naki amed din yafito zanmuku aure dashi Allah yabawa kowa alkhairinda yake fata.

Miqewa yayi Rai bace ya fice yabar gidan ummi ma qala batace Mata ba ta miqewarta meryam na riqeda hannunta.

Ba kunya padima ta tashi zaune tana share hawaye duk fushinda za'ayi tasan kowa zai sauko itadai tunda buqata tabiya angama me wahalar.

Kallon NURU tayi zatai mgn NURUn ta miqe batareda ta kalletaba zuciyarta na Mata zafi da radadin abinda padima tai Mata baqin ciki goma da ashirin ga tafiya delah ga abinda padima tayi ita rayuwartama ta ruguje gabaki dayanta sbd shikenan ta

tabbata batada rabon zama acikin igiyoyin aure idan taje delah tariga tazama negestati idan ba Allah ne yayi Mata raboba tasamu damar shiga inuwar aure.

Gabaki daya gidan rikicewa yayi Babu me farin ciki bare walwala tundaga ranar sai padima data bushe ido tasakewarta da walwalarta da komai tunda buqatarta tabiya kowama yayita baqin cikinsa duk zasu dawo daidai idan komai yasake wucewa.

NURU ta sauya sosai gabaki daya yanxu batada walwala kullum cikin damuwa da tunani take idanuwanta harsum bushe da kukan tayi tayi tagaji harta daina saidai ido.

Ranarda jekadiyar Kaleb tazo duba NURUn tayi Mata kallo harna qurulla take tagama tabbatarda NURUn itace mafi cancantuwa Nan take takaiwa Kaleb rahoto yabada umarnin afara gyaranta tun agidansu kafin kwanakin daukota su cika.

Al'amari yadawo sabo sbd irin zarya da matakan tsaro da bayin da aka kawo aka zuba a gidan yasa al'amarin yafara bawa kowa tsoro da mamaki itadai padima ko ajikinta matsuwartama ayi ayi agama NURUn ta tafi sbd tsoron karma wani abu ya gitta aqara dawoda abun kanta.

Hankalin iyayensu yafara tashine sbd tunanin wannan tsananta tsaron da matakan dasukai yawa da wuya idanba gizah za'a Kai NURU ba sbd sai 'da mafi kusanci da sarauta akewa irin wannan taka tsantsan din Amma dai Babu iko ko hurumin tambaya.

Cikin kwana goma sha daya dukkanin Wanda yayiwa NURU kallo daya baya sakewa a qaidance idan ba hakaba hukunci zai hau kansa sbd wani irin sauyi me yawa datayi,

Fatarta ta sauya fiyeda tsammani,

Haskenta ya ninku komai nata santsi yake musamman gashinta dako dankwali baya zama sbd tsantsi ga sutura ta alfarma da aka kawo daga Kaleb Kai tsaye a sirrance.

Ayau tun safiyar jiya take kuka har idanuwanta basa iya gani sosai sbd yaune ranar tarewarta/ma'ana tafiyarta,

Ammi da abal kwana sukai Bata nasihu da rarrashinta ita ammin ma Kamar yanda NURUn ke kuka hake takeyi Daren farko lafiyayyun motaci biyar sukazo daukeda dukiya da abinci tareda sitiru na alfarma wa iyayen negestatin kafin aka dauketa a sirrance tareda mahaifinta yakarata yakaita har gaban Kaleb Wanda yasake narkawa abal din dukiyar tukaici rakiya aka nufi wani kebantattcen sashe na musamman daya gama hada jin dadin duniya da NURUn tareda sabbin masu kula da ita su shida cif cif ha'di da jekadiyar Kaleb Wanda ke sake yaba zabinsu na NURUn.

##MAMUH#

Last free page

ZAFAFA BIYAR□□□

SAFIYYAH HUGUMA

BILLYN ABDULL

MISS XOXO

HAFSAT RANO

MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Daya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899[9/6, 6:12 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 6_*

Gyara kwanciya tayi ahankali cikin sanyin jiki da rashin kuzarin daya mamayeta na kukan datun jiya da aka kawota ta kwana tanayinsa.

Juyar dakai tayi daga kallon makeken dakin baccin ma'ana bedroom dinda take Wanda ita kaf rayuwarta da tunaninta dama irin labare labaren da padima ke fada Mata akan akwai daula da jin dadin rayuwa tareda qyale qyalin rayuwa Bata taba ayyano tunanin ganinsu Kamar hakaba abin ya shallake tunaninta musamman da tun jiyan sanyin AC ke shigarta a hankali Saida 'dayar me aikinta data shigo dubata cikin dare taga yanda ta qudundune ta bude Mata qaton duvet me tsananin laushi da Sanya nutsuwa ta lulluba Mata batamasan lokacinda tasake shigewa cikinsaba tana gyara kwanciya sbd sanyin yayi Mata yawa ga tsoron baqunta na kwanciya daki ita daya.

Jin akaro na biyu ansake kwankwasa Mata qofa Ana sake sanar da ita anagama shirya Mata abinci yasa ta tashi zaune tareda miqewa ta nufi qofar qafafunta na rawa murya na rawa cikin sanyi tace"

Ganinan zuwa.

Bayi Takoma akaro na babu adadi tana sake kakkala ko Ina batasan Yaya zatai tayi wanka ba gabaki daya a firgice take ita yanzu ta daina kallon wasu abubuwan na masu daula amatsayin Jin dadin rayuwa sai abun tsoro.

Jin shiru da yawa yasa jekadiyar Kaleb shigowa bedroom din Kai tsaye ta duba makeken gadon Wanda yake zagaye da wani irin transparent labule fari tas taga Bata hango daga ciki kan gadon saita juya tana kallon qofar toilet ta qaraso ahankali takira sunanta.

Jin jekadi ce yasata fitowa a sanyaye tana kallon qasa ta tsaya daga bakin qofar bayin.

Kai tsaye jekadiyar ta fahimci komai dama Kuma daga yau ne za'a fara kokkoyawa NURUn komai hatta kwanciya sai ankoya Mata.

Shiga bayin tayi tana cewa"

Biyoni kigani.

Shiga sukayi bayin tafara nunnuna Mata komai daya bayan daya tareda fidda sabbin setin brush masu tsadar gaske da toothpaste Suma kala kala sai towels da aka jere Suma kusan sunfi guda biyar bangaren kayan wanka kuwa su sabulu da turaren wanka ba'ama magana Nan dai ta tayata komai har kusan wankanma ita tayi Mata Saida suka gama tafito NURUn tasake dauraye jikinta tafito daureda towel dinda yafi kowanne girma shima kusan daqyar ta daurosa kallo daya jekadi tai Mata ta dauke Kai tana sake yabawa da jinjinawa tunanin kaleeb na karbanwa UBAYD MALEEK yarinya 'danya sharaf sa'ar 'yarsa Kamar wannan tabbas za'aga 'yaya masu manyan idanuwa da hanci Dan kuwa NURUn tubarkallah uwa uba UBAYD din da shikam idan shima 'yayan zasu dauko angama magana.

Da kanta ta tsaya tana sake nunnunawa NURUn wasu abubuwan na dangane da shafa da qamshi da sauransu hardai ta shiryata cikin doguwar Bahrain gown blue wadda tasake haskota ta nada Mata gyalen take tayi fes kamar ba NURUn abal ba suka fito tana biyeda jekadi Kamar jela suka fito babban matsakaicin palonta suka nufa inda aka jere Mata abincin sai alokacin hanjinta sukai wani qugin yunwa Dan rabonta da abinci dama tun jiya da a gida ammi tai Mata dole ya Dan ci sbd cushewar ciki da damuwa.

Zama tayi Nan daya daga cikin bayinta tazo ta zuzzuba Mata komai nanma Saida jekadi ta nuna Mata amfanin kowane cokali duk da Bata iyaci dacokali ba tanada nutsuwar cin abinci tun agida kowa yasanta a natse take gudanarda komai na rayuwarta Wanda zaisa Kai tsaye bazaka gane batasan komaiba na wayayyi ko wayayyiyar rayuwa.

Ba laifi taci abincin sosai sbd tana jin matauqar yunwa gashi Kuma bazatace ta taba cin abinci irin wannan ba.

Bayan tagama cin abincin janta jekadi tayi aka sake kimtsata suka nufi gurin Kaleb Dan Kai gaisuwar safe dakuma Kai godiya da zaben dayayiwa NURUn Wanda jekadi a hanya take fada Mata yanda zatayi da yanda zatace.

Suna Isa Saida sukai tsayuwar kusan mintuna talatin kafin akai musu iso suka shiga bangaren tun daga qofar farko NURU ke kallon aljannar duniya danma ba halin bude ido sosai tayi sbd dokace babu Wanda ake Bari yakalli fuskar negestati batareda NEGES dinta yafara ganinta ba bare ita datake ta MALEEK guda shiyasa kusan fiyeda Rabin fuskarta rufe yake cikin burka(hular doguwar rigar dake jikinta)

Duk tarin qofofin Palo palon dasuka wuce akwai masu tsaronsu harsuka Kai wadda tafi kowacce zama babba da tsaro

Nanma Saida akai musu iso tukuna aka bude musu suka shiga aka rufo.

Zubewa jekadi tayi tana kwasar gaisuwa cikin tsananin girmamawa da ladabi.

A natse itama NURUn ta durqusa qasa kanta na qasa ta yaye fuskarta cikin sanyin da nutsuwarta ta gaidashi batareda tayi Masa kirarin dataji jekadi nata jerowaba sbd Bata iyaba.

Kallo 'daya yayiwa NURUn ya tabbatarda nutsuwarta ya dauke Kai Yana amsa gaisuwarsu tareda Basu izinin miqewa.

Basu wani jimaba suka fito zuwa sashe sashe na cikin delah din Wanda wani sashen a mota suka jejje sbd nisa da girman DELAH din,

Ayau ta tabbatarda arziki ma Ashe na wani sunane Dan kuwa taga inda arziki yake magana,

Tabbas delah wani Depot ne na arziki Dan idanuwanta da tunaninta sunkasa daukar wasu abubuwan data gani ahakanma akecewa gizah ta dame delah tabbas idan mutum beyi da gaskeba a irin Nan tsaf imaninsa zai barsa sbd kwadayin dawwama acikin irin wannan daula ta mulki.

Sai magriba suka samu damar dawowa sashenta duk da haka bawai koina suka samu zuwaba Kai gaisuwa saidai duk inda sukaje babu Wanda yaga fuskarta andai tabbarmusu da sabuwar negestati ce.

Tarin tukuicin dukiyar data samu ayau din Bata bayyanuwa danma asalin tukuicin na tafe ne ranarda za'a tabbatarda budurcinta delah ta sheda.

Kallon uban dukiyar zinarai da situru tayi tana rintse idanuwanta cikin tsananin azabar gajiya Dan qafafuwanta har wani numfashin azaba sukeyi daqyar ta miqe ta daddafa tashiga toilet tayi wanka ta gasa qafafuwanta tana tsiyayar hawayen tausayin kanta da kewar iyayenta itafa shikenan yanxu haka zataita rayuwa daga ita sai bayi sai idan neges dinda take tasa ya buqaci ganinta a turakarsa.

Tunanin hakan yasa kukanta tsananta tafara kuka sosai cikin bayin tana cusa kana cikin qafafunta Dan zaune take cikin bathtub.

Da kanta ta rarrashi kanta tasake dauraye jikinta tayi alwala tafito tazo daqyar ta tsaya akan qafafunta tayi sallolin da duk basuyiba yau din tana idarwa da kanta ta sidado ta fito cin abinci da yunwama Kamar ta kusa kasheta.

Tana zama dakanta ta zuba abincin sbd duk basanan suna gurin sallah Suma Dan Suma Kam sun gaji hannu tasaka Bata tsaya saka wani cokaliba kadanma taci sbd cikinta daya qulle tasha lemun sabuwar abarba ta miqe ta nufi daki tana shiga ta kwanta kife take baccin wahala yayi gaba da ita.

Washe gari ma yini tayi daki kwance abinci kawai ke fiddo da ita Palo har dare bataga jekadi ba sai washe gari da yamma tazo bayan ta tabbatarda NURUn ta huta daga wahalar shekaran jiyan kafin suka fara gudanarda aikin dake gabansu.

Sannu ahankali jekadi take koyarda ita komai na al'amuran rayuwar gidan sarautarsu ta delah,

Duk wani abu dayakamata NURUn ta sani Kuma ta iya Ana kan koya matashi Kuma tana 'dan ganewa duk da hankalinta tashi yake idan Ana fada Mata wasu abubuwan ko koya Mata sbd batasan ta Yaya zata gudanar da rayuwarta ahakan ba,

Ta bangaren iyayenta kuwa tuni ta aika musu da dukkanin tarin dukiyar tukuicin data samu.

Ga kaleeb ta bangare daya kullum saita je takai Masa gaisuwa Wanda jekadi ce ta 'dorata akan hakan bawai Dan al'ada bace kawai tanason Gina qauna me qarfi ne tsakanin NURUn da kaleeb sbd sanin irin tsananin qauna dake tsakanin Kaleb da UBAYD MALEEK.

Sannu ahankali tafara sabawa da rayuwar delah ga jekadi ma data Dan shaqu da ita sbd tana Mata kallon uwa kokuma tacema Kaka musamman sbd itama jekadin tsakani da Allah taji tana qaunar NURUn sbd nutsuwa da biyayyarta ga rashin son hayaniya sai hakan kesake saka Mata nutsuwa da shigar NURUn rayuwar UBAYD koba komai UBAYD Kamar 'dane agareta sbd agabanta aka haifesa yagirma.

Tsawon watanta biyu a delah Amma haryanxu ko a zance bataji maganar waye aka bada ita gurinsaba,yaushe za'a kaita,Ina yake haryanxu shiru duk bataji komaiba Abu daya tasani shine jekadi ta fada Mata wata me kamawa za'a kaita wani guri.

Da farko hankalinta ya tashi Jin tafiya wani guri Amma sai jekadi tafara kwantar mata da hankali da cewar zasu dawo bawai zaman dindin bane itadai Sam hankalinta yakasa kwanciya ko bacci yanzu kasawa takeyi saitajin Kamar rabuwa zatai da gida har abada.

Ganin kwana biyu har wata rama ta sakota gaba da tunani da damuwa yasa jekadi takwai Kaleb zancen sai tunani ya shegesa yace anfasa Kiran zuwan UBAYD sbd

idan yazoma kowa zai San shi keda negestatin Kuma Kamar yanda akasan MALEEK da ikonsa bazai taba karban negestati ba matuqar ba baya tareda matarsaba hakan zaisa afara tunanin sun rabu Wanda za'a iya amfani da wannan gurin muguwar manaqisar mulki akawo suka ga karban mulkinsa Wanda keleb bazai taba Bari hakan tafaru ba yafison koda za'a San ubayd da matarsa sun rabu zuwa lokacin sun samu wata Matar aure kawai za'a daura idanba hakaba da matsala babba Dan haka yasa aka matso da tafiyar NURUn tareda Bata damar izinin zuwa ganin iyayenta da daddaren yau.

Qatuwar baqar Mercedes Benz beymach ta ajiyeta gefen gidansu da qarfe goma sha biyu na dare Wanda shine lokacin barinsu fita delah tana kallon qofar gidansu jikinta yayi mugun sanyi taji idanuwanta sun ciko da hawaye ta ziro qafarta waje ahankali tareda fitowa.

Kai tsaye itace agaba jekadi na gefenta tana cewa"

Karkiyi kuka gaban iyayenki Zaki daga musu hankali Kuma laifine babba yin kuka was umarnin masarauta Dan haka ki kula.

Batace komaiba itadai burinta ta Isa cikin gidan taga ahalinta cikin sa'a kuwa har lokacin abal dinta da ammi na zaune tsakar gidan kan shimfida suna Shan iska sbd tsananin zafin da akeyi yau din meryam ma na kwance gefen ammi tayi bacci ammin na Mata fitar sauro.

Da budaddiyar murya jekadi ta rangado sallamar da har maqota anaji sbd asan da zuwan NEGESTATI ne.

Da ammin da abal lokaci daya suka miqe suna kallon qofar dasu NURUn ke shigowa wadda qamshinta tuni yafara cika tsakar gidan da hanzari ta qaraso ta fada jikin ammi tana riqo hannun abal duk alokaci daya tana sake hawayen farin cikin ganinsu batareda ta iya cewa komaiba.

Cikin tsananin farin ciki ammi ke Mata yare tana cewa"

Ya Allah NURU munyi kewarki matuqa.

Murmushin farin ciki kawai abal ke saki Yana kallonta ta cikin hasken farin wata Yana sake godewa Allah daya bashi ikon ganin 'yarsa 'daya tasamu gidan zamanta na rayuwa saura daya itama Yana fatan Allah yabasa ikon ganin yayi Mata aure ta tafi nata gidan.

Zama sukai tana tsakiyar iyayenta Meryam ma tuni NURUn ta tayarda ita sbd bazata iya tafiya basui mgn ba tana ganin NURUnta tafada jikinta da qarfi tana ihun murna Wanda ya tado da gimbiyar gidan wato padima ta fito cikin wani irin laushi tana jujjuya ido ta bude da kyau tana kallon mutanen idanuwanta suka sauka kan NURU tasake dubawa dakyau taga NURU ce da sauri ta qaraso tana cewa"

NURU????

Kece yanxu?

Dagowa NURUn tayi fuskarta daukeda murmushin kewar padiman ta taso suka rungume juna tana cewa"

Nayi kewar dukkaninku padima.

Zaman sukayi padiman nabinta da wani kallon kurulla da zallar mamaki tanson yin tunanin fahimatar wani abu kanta Yana toshewa da mamaki dakuma tausayi tausayin NURUn da rayuwarta ta lalace.

Shagala sukai sosai harsaida lokaci yaja jekadi tashigo da cewar zasu tafi Nan jikinsu duka yayi sanyi Amma hakanan suka bawa NURU qwarin gwiwa abal yabita da wasu irin adduoin Sanya albarka masu zafi wainda suka Sanya jikin kowa yin sanyi suna amsawa da Amin.

Har mota suka rakota tashiga padima sai kallon komai take cikin mamaki tana qaryata abinda idanuwanta ke gane Mata sbd tasan ba komai bane duk wannan akan irin rayuwar da ita zatayi a Nan gaba.

NURU kuwa Har suka Isa delah tunaninta bai daina zurfafaba gabaki daya yanzu kanta a toshe yake sai yanda akai da ita yanzu kenan.

Tana Isa sashenta daki ta wuce Kai tsaye ko tubewa bataiba ta kwanta tareda rintse ido.

Washe gari haka akai fita da ita zuwa gurin passport Wanda tun kafin su Isa aka tanadi komai babu Wanda yasamu damar ganin fuskarta sai Wanda ya dauka hotonta dagacan Kai tsaye delah suka dawo washe garima saida aka futa da ita zuwa wani gurin wanda acanma tasake tabbatarda mulki wani abune na daban sbd irin girman da ake Basu ko cikin ansan cewar bama daya daga cikin jinin sarautaceba ita din.

Ranarda ta cika kwana shida da zuwa gidansu ranar aka gama Shirin tafiyarta tsaf a washe gari itada jekadi jirginsu yabar Ethiopia zuwa qasar France.

****

Breakfast sukeyi zaune su uku akan dining din Wanda suka kwana biyu Basu samu damar cin abinci tareda dad din nasuba sbd rashin zamansa a kwanakin sai yau,

Kallonsa AFIA tayi taga yanda yayi wani irin fresh fatarsa sai wani glowing takeyi tsabar hutu da arzikin dukiya duk da manyancinsa Amma Sam fatarsa taqi bayyana hakan idanma batai kuskure ba saitaga kamar bayan rabuwarsa da mum dinta wani nutsuwa yasamu.

Sake kallonsa tayi wannan karon suka hada ido ya zuba Mata manyan fararen idanuwansa cikin muryarsa me iko yace"

AFIA akwai wani abu ne?

Aje spoon din hannunta tayi ahankali tareda kallonsa gabaki daya cikin taushin murya da 'yar sakuwa tace"

Dad please for how long zamuyita zama haka mum Sarah kwanakin Nan batajin Dadi qafafunta sunfara gazawa Ina tsoron zamu koma rayuwa mu kadai dagani sai farhat sauran maids din babu wani kusanci ko shaquwa tsakaninmu dasu.

Ciki wani irin Isa ya kurba ruwan Black coffee dake cikin farin teacup din hannunsa ya ajiye tareda daukan tissue yakai bakinsa ya goge ahankali ya ajiye tukuna ya dago ya kalleta yaji zancenta ya taba zuciyarsa tabbas suna buqatan abokin zama kada kadaici yayi musu illah gasu yara qananu,

Sam baida sha'awar maidasu zama gizah gurin mahaifiyarsa sbd kada giyar sarauta da mulki ya shigesu Dan kuwa tabbas zai shigesu sbd girma da irin bauta musun daza'aitayi zai gurbata tunaninsu sarauta zatai musu muguwar shiga bazai taba son hakanba Dan haka a yanzu dai baida wani zabi bayan karban negestatin Kaleb Amma bazai taba Bari Susan da hakanba sbd bai karbetaba bakuma zai taba karbantaba zaidai kawo musu itane amatsayin abokiyar debe kewa.

Kallon afian yasake Yi tareda Dan sassauta fuskarsa batareda murmushin yafito dukaba yace"

Akwai abokiyar zama da debe kewa da Kaleb zai Aiko muku da ita ta musamman Dan haka karku damu damuwa ya qare ok??""yafada Yana shafa kan farhat dake kusa dashi tana cin pancakes da Zuma.

Cikin tsananin murna afia tace"

Dad daga delah ne za'a kawo Mana ita?

Gyada Mata Kai yayi cikin Jin dadin ganin farin ciki akan fuskarsu yace"

Yes my angels Dan haka kunada baquwa yanzu Dan haka no worries no sad face no complains.

Yes dady" farhat ta fada tana riqe hannunsa suka miqe tare suna barin dining din Dan yanzu haka yauma tafiya zaiyi zai Kwana biyu acan.

Har mota suka rakasa ya tafi dayake yau weekends ne ba school Yana wucewa suka dawo ciki cikin farin ciki sukaje suna fadawa mum Sarah sunada baquwa tananan zuwa.

Yana barin gida direct airport aka nufa dashi ya Jima Yana tunani kafin ya dauki wayarsa dake gefensa ajiye ya lalubo numbern jekadin kakarsa wadda yasan itace maganar negestati take gurinta Kira daya tana ganin me Kira ta daga cikin tsananin girmamawa hadda durqusawa duk da ba agabansa takeba tahau jero gaisuwa Yana sauraronta kafin ya dakatar da ita ta hanyar amsawa a gajerance cikin nauyin murya kai tsaye yace tanason bayani akan negestatin Nan tahau jero Masa asalin NURU da sunanta dakomai akanta cikin gajiya da zancen ya katse Kai tsaye yace"

Kada su afia su taba sanin waccece ita da matsayin datazo dashi.

Angama MALEEK ubayd sarki me kujerar delah gizah.

Yana kashe wayar ya kasheta gabaki daya tareda ajiyewa Yana daukar iPad karanta wani saqo.

Suna Isa airport ba Bata lokaci yashiga jet suka daga.

Sukuma a washe garin aranar jirginsu ya sauka qasar Kai tsaye babbar mota tazo daga gidan daukarsu daga ita sai jekadi ne Dan haka suna isowa makeken gidan na UBAYD MALEEK aptrmt dukkanin masu aiki suka fito suna musu barka da zuwa akai ciki dasu suna shigowa babban palon gidan dayasa NURU Shan jinin jikinta sukai kicibis dasu afia dasuka fito tarbonsu afia na ganin NURU ta tsaya cak tana kallonta cikin yanayi na Jin dadin wannan ai qawace ma aka kawo Mata tasaki fuska sosai tana cewa"

Jekadi wannan ce wadda zata tayamu zaman?

Da sauri cikin girmamawa jekadi tace"

Eh ranki ya dade itace.

Jin haka farhat ta riqo hannun NURU tana cewa"

AFIA tanada kyau sosai kaman Barbie Dina ko???

NURU bayan zare ido Babu abinda takeyi tana kallonsu hankalinta nakan gidan Wanda yasa taji tsoron duniyama gabaki daya na shigarta.

Dakin mum Sarah jekadi tasauka itakuma NURU dakin AFIA afian tajata tana sake tambayar sunanta duk Dadi ya isheta sbd take taji tanason NURUn.

##MAMUH*

HASKE WRITERS.

ZAFAFA BIYAR□□□

SAFIYYAH HUGUMA

BILLYN ABDULL

MISS XOXO

HAFSAT RANO

MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU

0903 234 5899

[9/6, 6:12 PM] Anty Rabi'at: _*Mamuhgee 7*_

Bin bayan afian take da kallo cikeda mamaki da 'dan Jin shakka shakka tareda tsoron binta zuwa dakinta sbd ko daga dirowar tasu ta fahimta tareda shedar da irin tsananin girman dasuke dashi na iko Dan duk Wanda jekadi ta russunawa Kai ba qarami bane me cikakken ikone na sarautar delah.

Suna Isa qofar makeken bedroom din afia ta bude qofar tareda fara shigewa tana juyowa fuska asake tace"

Welcome to my world beauty.

Tsayawa NURU tayi tana kallon dakin daga bakin qofa jikinta nasake yin sanyi da mutuwa sbd a wannan gabar takai qarshen shiga rikicitaccen tunanin inane wannan duniyar da aka kawota?.

Ganin kamar tashiga tunani da wasi wasi yasa AFIA kamo hannunta ahankali ta janyo hannun tana janyota cikin dakin ta tura qofa ta saketa ta nufi kan couch din dake dakin ta zauna ahankali tana waiwayowa inda NURUn ke tsaye har lokacin tace"

Kishigo karki tsaya anan Zaki gaji da tsayuwa.

Dan cika umarnin AFIA din ne kawai yasa NURU fara takowa tana qarasowa cikintsakiyar dakin fuskarta a qasa sbd yanzu Kam tafara tunanin bauta aka kawota tayi anan ba wai maganar negestati ba.

AFIA batason maimaita zance shiyasa ta miqe tareda fitowa dakin tasaka aka kirawo Mata jekadi tace tabiyota zuwa dakinta suna zuwa ta kalli NURUn kafin ta kalli jekadi Kai tsaye tace"

kiyi Mata bayanin banason wannan kakkamewan datake idan batada sakewa kokuma bazata iya sakewa damuba kawota baida amfani tunda sbd mu aka kawota anan Dan debe Mana kewa.

NURU dake sunkuye da Kai da sauri ta Dan dago ta kalli bakin afia din Jin ba maganar negestati ne yasa aka kawota ananba kenen Reno zatace kokuma aikatau kokuwa bauta zatace duk da taga afia din bazata wuce tsaranta ba Amma dai tana fatan koma tsaran meryam dinsu zataiwa bauta ba kamar afia datake tsaranta ba yafi mata tsari da nutsuwa akan zamowa abokiyar kwanciyar kokuma abokiyar nishadi neges dinta.

Kamar daga sama taji jekadi takira sunanta tana cewa"

Biyoni muje.

Sanyi jikinta yasakeyi ta juya anatse tabi bayanta tana sake sunkuyar da kanta harsun Kai qofa zasu fice afia tasauke ajiyar zuciya ta nufi kujera zata zauna tace"

Jekadi kibarta kawai kun gaji sbd doguwan tafiyan da kukai kuje da ita can ku huta kuci abinci da sauran abubuwan tukuna.

Yanda kikace haka za'ayi li'iliti(princess/gimbiya/'yar sarki)

Wucewa sukayi suka qarasa ficewa suka nufi can dakin da aka sauke jekadin.

Abinci suka fara ci Wanda NURU takasa ci sbd damuwa da tsananin tunanin Ina shin Ina rayuwarta ta dosa ne tare Kuma da fargaba haddama tsoro ta yanda za'ace anan za'a barta to tayaya zata iya rayuwa acikin wainda Bata saniba bama ta taba ganiba.

Ganin ta shiga damuwa da firgici sosai yasa jekadi Dan daka tawa tareda kallonta ta dauki cup din danyar madarar turawa me sanyi ta miqa Mata cikin kulawa tace"

Karba wannan Kisha zakiji dama daman damuwa sbd wata damuwar yunwa na shigowa cikinta.

Ba musu ta karba ahankali cikin sanyin murya tace"

Ameseginalehu(thank you/nagode)

Tana shanyewa ta miqe tashiga toilet din dakin tayo alwala tareda wankan da jekadi tace tayo Dan anan so biyu ko uku zata ringa wanka sbd ko masu aikin gidan tsaftarsu abin koyi da burgewace bare ta masu gidan.

Bayan fitowarta jekadi da kanta ta nuna Mata inda abin sallah ke shimfide Yana kallon gabas ta qarasa bayan ta Sanya doguwar jallabiya fara da lullubin sallah ta tada sallar.

Bayan ta idar duk sallolin da ake Binsu ta gyara zama jiki amace cikin damuwa.

Saida jekadi tayi sallolin itama kafin ta fuskanci NURUn tafara jero Mata bayaninda maleek ya buqaci datai na boye matsayin NURUn na negestati a zaman dazatai agidan kasancewar lefine zatayi nayiwa negestatin UBAYD MALEEK guda yasata Dan dauke kallonta daga NURUn tace"

Kicire damuwar komai ki kwantar da hankalinki sbd rayuwarki zata inganta zamanki anan din,

Kinzo Nan ne sbd Yaya 'yayan MALEEK UBAYD zama badan komaiba haka zalika maganar negestati gabaki daya anbarta inaga saikin dawo delah

Kwanciyan hankalinki shine na iyayenki dan haka yanxu Kam ma Kamar umarnin li'iliti AFIA ne ki sake acikinsu wata babbar sa'ar rayuwace Kika samu wadda kowace mace dake daular ethio ke marmarin samu Amma bazaki gane hakan ba wata qila sai gaban idan kinada rabo kenan Dan haka aikinki ayanxu kawai shine kulawa da

'yayansa cikin kulawa me kyau duk da li'iliti AFIA tsaranki ce bazaki iya Bata kulawaba Kamar farhat Dan haka farhat yanzu a qarqashin kulawanki take.

Tana gama fada ta miqe ta fice Dan komawa gurin AFIA ta sanar da ita inda NURUn zata zauna duk da Babu Wanda yasani ita tasan babban laifine Kuma bazai yiyuba tabari negestatin maleek ta kwana acikin masu aiki ko bayan shekaru dari ne idan har tana raye tasan wata ran saita fuskanci hukuncin hakan.

Cikin girmamawa Kai aqasa tayiwa AFIA bayanin inshallah zasuji dadin zama da NURU Kuma tana bada hkr amaimakon NURUn.

Murmushi me qayatarwa kawai afia tayi tareda cewa"

Ba damuwa ki dawo da ita dakina takwana.

Angama.

Wannan karon da sanyi tashigo dakin bayan tayi knocking ance tashigo.

Qarasowa ciki tayi ahankali ta iso har inda afia din ke zaune kan kujera tana karatu a iPad dinta batareda ta dagoba tacewa NURUn"

Ki zauna kokuma daima ki kwanta tunda agajiye kuke.

Gyada Kai kawai NURUn tayi tareda zaunawa a qasan kujera afia na ganinta batace Mata komaiba ta qyaleta sbd ganin kamar zata takurata da yawane idan tace yasake dasu lokaci daya duba da irin matsayin dasuke dashi dayasa kowa ke Basu tsananin girma dama mutum take buqata akusa da ita akoda yaushe so ko Babu sakewa atsakaninsu ba laifi tunda dai akwai mutum din.

A kan kujera NURU ta kwana AFIA da farhat dake kwana a dakinta suka kwana cikin makeken lafiyayyan gadon dakin lullube cikin bargo me taushi.

Farhat na zuwa makaranta da wuri shiyasa kusan gidan kowa yatashi da wuri sbd shirinta wannan yayi wannan wancan yayi wancan haka Shirin nata yake.

Bacci ne a idon afia sosai sbd ta Dade da daddare tana karatu Dan haka Bata tashiba NURU ce dake zaune jungum taga farhat din nata yaqin saka uniform ta taso tazo ta durqusa gabanta tareda karban uniform din tana Dan sake siririn murmushin tunowa da meryam dinta wadda Allah yasanya mata tsananin kaunar qanwar Tata shiyasa so da dama takeda son yara duk yaron data gani meryam dinta takeji cikin ranta musamman farhat datake kusan tsara da meryam din.

Ahankali tafara Sanya Mata kayan tana cewa"

Kintashi lafiya?

Kallon fuskanta farhat keyi tareda Kai hannu ta latso kumatun fuskar NURUn dakeda taushi sosai cikin murna tace"

you have a very beautiful face like my Barbie.

Duk da batasan me farhat din tafada ba yanda take kallonta da yanda ta taba fuskanta yasata sakin siririn murmushi tana shafa fuskan farhat din tace"

Lewa (you're beautiful too/kema kinada kyau/kyakkyawa)

Duk da basa wani Jin Amharic sbd mum dinsu Bata musu dad dinsu Kuma turanci ne mafi yaren dayake musu mgn dashi shiyasa Basu wani ji kakarsu ce kawai mahaifiyar dad dinsu ke musu yarensu na amheric Amma dai duk da haka tasan me ake nufi da lewa cikin murnar tasan menene NURUn ta fada tace"

Lewa means beautiful right?

Ido NURU ta zuba Mata sbd batasan me tace ba.

Kamo hannunta farhat tayi tajata tana cewa suje ta rakata cin abinci batason ci ita daya a dining.

Kamar jela haka tabita zuwa dining din saidai Bata zauna ba ta tsaya har me aikin abincin gidan dake tsaye ta zubawa farhat din abinda tasan shi takeci itadai tana tsaye tana kallon ikon Allah dayake jekadi ta Tara masu aikin gidan kaf tayi musu bayanin NURU itama daga delah take su girmamata Kamar yanda suke girmama su AFIA shiyasa me aikin me suna Fana tana gama zubawa farhat komai ta jawa NURU kujera Dan ta zauna cikin girmamawa tace"

Me za'a kawo Miki?

Kallon kujerar dining din dake zuba qyallin adon zaiba tayi tana kallon bakin Fana din kafin ta kalli farhat data kamo hannunta tana cewa"

Zanyi latti fa ki zauna.

Zama tayi a dosane tareda girgizawa Fana Kai alaman aa Bata buqatan komai.

Ahankali take taya farhat cin abinci ta hanyar Bata ruwan tea ahankali ahankali sbd zafinsa harsuka gama ta goge Mata Baki da tissue suka taso farhat har lokacin tana riqeda hannunta sbd Babu Wanda yataba zaunawa da ita tunda tafara wayo yabata abinci abaki sai yau sai hakan yamata Dadi sosai itakuwa NURU sbd tasabane da bawa meryam abinci abaki duk da tafara girma shiyasa ko yanzu tabawa farhat din musamman dataga gatan da farhat takedashi ko kwatan rabinshi Meryam batada to ai Bata abinci abaki kaman dolene ma.

Bayan tafiyan farhat makaranta saita koma daki ta zauna zaman zugum tareda fadawa tunanin rayuwarta,

Ko atunani da mafarki Bata taba kawo rayuwarta zata juya kaman haka ba daga negestati yanzu Kuma Ana maganar bauta kokuma tace Reno har wata qasa.

Ajiyar zuciya ta sauke tareda miqewa ta nufa toilet din afia din wanda badan 'yan watan nin data diba a delah ba kafin zuwanta Nan da Babu ta yanda zata iya amfani

da wasu abubuwan wanka takeson Yi Amma takasa Yi sbd kada tafara jiqa toilet din AFIA Bata tashi tayi wanka ba wata qila batason wani yafara jiqa Mata toilet Dan itama a gidansu kusan haka take batajin dadin wanka idan wani yafara shiga ya jiqa bayi shiyasa kullum itake rigan kowa wanka a gidansu.

Dawowa tayi ta zauna daga Nan zaune wani baccin ya Dan dauketa sai guraren goma da rabi da AFIA ta tashi motsin shirinta yasata tashi itama tana bude ido ta tashi zaune ahankali tareda bude Baki cikin sanyin muryarta tacewa afia"

Aderiki (barka da tashi/good morning)

Kallonta AFIA ta juyo tayi tareda sakin murmushi tana qarasa Sanya dogon blue jean ajikinta tace"

Morning lewa(beautiful/kyakkyawa)

Shiru NURUn tayi tareda sakin murmushin yaqen dole sbd lewa din kawai tasani batasan meye dayar kalmar ba.

Gane batada ilimin turanci ko kadan yasa AFIA murmusawa cikin Yar hausar amhara da Bata gwanewa ba tacewa NURUn tayi wanka ta shirya suje cin abinci a dining.

Dama jira take ta miqe ta nufi toilet din tashige tareda rufowa tana sauke ajiyar zuciya.

Tana jimawa a wanka Amma dai yau ta taqaita kokuma tace daga yanzu zata ringa taqaitawa sbd yanxu ba Kamar gidansu bane datake cikin gatanta agaban iyayenta Nan Kuma a qarqashin ikon yara ma take sai abinda aka cemata tayi.

Doguwar riga purple tasaka sai qyallin sequence take ta nade gashinta da gyalen rigar ta daurasa kaman dankwali sbd cikar gashinta yasa tafi son daura gyale akan yafawa sosai tayi kyawunta duk da Bata kwalliya Sam batama taba yiba suka fito dining tana gefen afia din suka zauna Koda Fana tasake tamabayarta abinda zataci

batasan mezatace ba afia ce tace kawai akawo Mata boiled veggies da kwai sai ruwan tea dinsu na gado wato bitter lemon tea me condensed milk da Zuma.

Babu Wanda yasamu damar cin abinci agidan Saida sukaci tukuna kowa yakeda damar karyawa Dan haka suna gamawa afia tayiwa NURU bankwana ta wuce school.

Yini NURU tayi adaki a kwance daga juyi sai tunani sai bacci har lokacin dawowarsu yayi farhat tafara dawowa Wanda yasa kadaicin NURU rayuwa ta jata dakinta acan ta tayata tubewa tayi wanka ta tayata shiryawa suna fitowa daga dakin AFIA na dawowa ganinsu tare yasata Dan Jin dadin ganin walwalar farhat Dan haka tace su jirata itama tayo wanka suci abinci.

Tare sukaci abinci farhat na zaune gefen NURU kusan ko yanzu abaki take Bata abincin Koda suka gama janta farhat tayi zuwa dakinta sbd tanada drowings dazatayi tana neman abokin dazai tayata iccen mangwaro akace ta zano Nan suka baje NURU na tayata cikin nutsuwa.

Sunfara Jan kwanaki da zuwansu jekadi tasaka ido sosai akan zaman NURU duk da dama ta yarda da NURUn nada natsuwar da kowa zaiso zama da ita musamman yanda su afian suka jata ajiki sosai Dan kuwa afia Jin take kaman tasamu babban aminiya yanzu qarin qaunarta da NURU shine yanda take tsananin qaunar farhat take kulawa da ita Dan kuwa yanzu kusan itace ke Shirin farhat na zuwa makaranta.

Ta bangare daya ita kanta AFIA yanzu kusan komai fadawa NURUn takeyi Bata iya riqe bakinta idan suna zaune Jin takeyi kaman ta amayo Mata dukkanin damuwar data shiga da yanda iyayenta suka rabu Amma tana riqe kanta sbd sirrin iyayentane saidai kusan duk wani abu yanzu NURU tasani akansu musamman labarin dad dinsu da tsawon lokacin Nan bai dawoba saidai kullum suna waya dashi bama Kamar farhat da yagama haddace sunan lewa abakinta Dan qiri qiri suka maida sunanta lewa.

Abu dayane matsalarsu da ita gurin fira rigima sukesha sbd batajin turanci ko kadan sukuma yaren bai kamasu ba shiyasa idan suna fira sukeshan dariya sbd wani abin kafin tagane kwatancen kurame sukeyi da ita.

Ganin komai inshallah yayi yasa jekadi tattarawa Takoma tabar NURU da kewa saidai tayi Mata alqawarin ringa zuwa dubo Mata iyayenta akai akai tana bugowa tafada Mata.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Daya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huďu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899[9/6, 6:12 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 9_*

Sun Dade a can Saida afia taduba agogo taga lokacin fitowan dad dinsu yayi yasata aje karatun tana kallon NURU data dage tana kallon dabbobin duniya wainda wasu batama taba sanin akwaiba bare ganinsu sai take kallon abin cikeda mamaki da burgewa fuskarta ma ta nuna hakan

Afia ta dafa littafin tana cewa"

Ma'am Muje saikuma gobe mudawo ki Dora daga inda Kika tsaya.

Murmushi NURU tasake tana cewa"

Inason sanin sunayensu duka.

Karki damu ko farhat zata koya wannan yanxu dai muje inajin yunwa.

Fitowa sukayi NURU nasake wanyewa da qaton gidan sbd saiyau tun zuwanta ta fito ta zagaya cikinsa AFIA kuwa sai sake Mata bayanin komai takeyi tana nunnuna Mata.

Suna shigowa MALEEK UBAYD na gab da shigewa dining room tareda farhat dake gefensa cikin sauri AFIA tace"

Dad NURU na gaidasheka.

Jin haka yasa NURU saurin durqusawa muryarta na rawa tace"

Barka da fitowa cikin yarensu sbd a rikice take batasanma wane kalar yare shi yakejiba ko yake amfani dashi.

Batareda ya juyoba ko ya tsaya ya daga Kai tareda qarasa shigewa yana fiddo hannuwansa dake zube cikin alhijun qananan kayan dake jikinsa na _Stuart weitzman_ dark blue dasuka fiddo hasken fatarsa da asalinsa.

Miqewa NURU tayi kanta aqasa ta nufi hanyar qarmin Palo dazata Kai dakinsu ta shigewarta Dan tasan bama abune me yiyuwa cin abincinta dasu afia ayau.

Itama afian bayan wucewan NURU Bata damu da cewan tazo cin abinci ba sbd ba abune me yiyuwaba cin abinci a table daya da maleek ubayd idanba su 'yayansaba to saidai matarsa ko iyayensa ko 'yan uwansa akwai wainda baya yiyuwa cin abinci table daya dashi Dan haka ta wuce dining room din tareda kallon Fana tace idan tagama serving dinsu ta hada abinci a tray akaiwa NURU daki.

Sunci abinci sungama yakoma sama inda suka bisa suka zauna palonshi Dan Basu lokacinsa na magana Jin idan da akwai wani abin saidai duk Rabin zancensu na NURU ne Wanda yasashi mamakin irin shaquwan qanqanin lokaci dasukai da qaunan dasuke Mata Wanda yasashi Jin ai shikenan tunda sunsamu wadda suke so

yanxu yasamu Daman kansa tunda inshallah hakan ya nuna ba damuwa yanxu ataredasu musamman AFIA dama ita farhat tuni Bata damu da tafiyan mum dinsuba sbd batasan me hakan ke nufi takamaimaiba.

Koda afia tashigo daki NURU na sallan la'asar itama toilet ta wuce Dan alwala.

Ahankali ahankali Afia tafara saka NURU sakewa dasu sosai tana dariya yanxu acikinsu,tana iya kwanciya akan akan gado daya da afia tareda farhat a tsakiyansu wadda itama shaquwanta da NURUn ya ninku fiyeda farko.

Duk wani aikin gidan ahankali tafara sabawa da saka hannunta musamman bangaren girki da sosai take tayasu Dan tana son iyawa hardai bangaren baking hakama gyaran dakinsu Dana farhat tuni ta karbe itakeyi sai hakan yasake janyo Mata qauna da masu aikin,

Duk wannan hidimar datakeyi a gidan bata sake hada hanya dako inuwar dadynsu ba bare ganinsa dama idan Yana Nan masu aiki basa wilgewa to dama ita tasan Babu wani banbanci matsayi tsakaninta da masu aiki shiyasa itama idan Yana gida tana daki ko library gurin karatun da afia ke koya Mata Wanda ba laifi tana Dan fahimta.

Ahaka lokacin yaqara cigaba da ja sosai tuni sauyi yashigo rayuwarta ta sauyin jiki da lafiya tareda fara ilmantuwa Dan kuwa turanci yanzu kaman yaqi haka take gwamadawa suna dariya ita dasu musamman idan tanason bada labarin Abu to ko Yaya yazo watsoshi takeyi ganin hakan yasa AFIA yanke shawaran yiwa dad dinta maganar son asaka NURU makaranta Dan ita dake koya Mata yanzu karatunta yafara daukan zafi tana buqatan maida hankali.

Lokacinda tayiwa dad din maganar Kai tsaye yace tafadawa Omar babban amintaccen yaronsa.

Aikuwa tana yiwa Omar waya Babu Bata lokaci aka nemawa NURUn admission a wata school dake kusa datasu farhat inda zata fara daga farko.

Da farko taso zamewa zuwa makarantar sbd ganin kaman samun damar yayi yawa saida afia ta takura Mata tareda Bata qwarin gwiwan yin karatun tareda kwadaita Mata future me kyau na masu ilimi.

Ranar farko data fara zuwa daqyar ta iya bawa kanta qwarin fahimtar kalmar da ake fada Amma haka tadawo Bata wani fahimci komaiba shiyasa a salube tadawo driver na ajeta tana shigowa daki ta wuce ta zube kan gado kife tana sauke ajiyar zuciya tace"

Afia zakuyi hasaran kudi ne kawai banasaka ran kaina zai iya daukan karatu irin wannan.

Koda aka dauko farhat daga makaranta tana dawowa taga NURUn da gudu tayo kanta tana cewa"

My Lewa 'yan makaranta.

Dariya kalman tabawa NURU ta jawota tana zare Mata school bag daga bayanta tana cewa"

Farhat lewanki kanta a toshe yake kidaina murna ma tun wuri.

Kumatun NURUn dakeda laushi suke burge farhat ko yaushe su farhat din ta matsa tana cewa"

Lewa bazatayi kyan banza ba zata zama me qoqari nasan wata Rana lewa zata zama abin mamaki.

Murmushi tayi tareda kissing goshin farhat din tana cewa"

Kinada yadda sosai haka akan zan iya?

Yes beauty Zaki iya daddy ma zai jinjina Miki sbd qoqarinki zai siya Miki duk abinda kikeso sbd daddy nason me kokari a school sosai.

Murmushi kawai tayi tareda Jan hannunta zuwa daki Dan tubewa ayi wanka.

Suna dining taba bawa farhat abinci Afia tadawo da sauri ta aje jaka ta qaraso tana cewa"

Fana ki kawo mun cheese cream zanci abinci dashi.

Cikin kulawa take kallonsu bayan ta shanye cup daya da juice tace"

NURU ya school da Dadi ko?""taqarasa cikin tsokana sbd Babu wani alamun school yayi Dadi atareda NURUn.

Kallon afian tayi tareda 'Bata kyakkyawar fuskarta tace"

Kiyi dariyanki kawai afili.

Dariya afia tayi tana fara cin pasta salad tace"

Sorry babe Zaki sabane ahankali.

Suna gama cin abincin suka koma daki farhat na Taya NURU fahimtar karatun da akayo Mata afia na dariyansu har lokacin sallan la'asar yayi sukai sallah me karatun addinsu yazo Maheer asim suka fito zuwa libry inda acan yake musu karatun.

Sai dare bayan tagama komai ta kwanta tafara tunanin gobe ya zata Kaya Mata a makarantar Kuma da haka bacci ya dauketa asuba nayi ta farka tayi sallah ta tadasu sukai sallah itakuma tahau ayyukan data Saba tareda Shirin abincin farhat qarfe bakwai tayi wanka tazo tasake tadasu bacci sukai dakin farhat akai wanka ta shiryata cikin school wear itama tadawo daki tashirya qarfe takwas suka gama Shirin suka zauna cin abinci 8:10 driver yadaukesu yakai kowacce makarantarta ya ajiye.

Yauma kusan abin da wuya Amma dai sbd saka Rai sai Bata damuba Kamar jiyan data dawo gidama haka afia ta ajeta tana sake maimaita Mata karatun tun Bata ganewa har abin yafara warware Mata tana ganewa har a school dinma sbd kusan tafi kowa girma acikin makarantar Dan kaman primary ce afia kuwa kaman a secondary take ita.

Tun karatu nabata wahala sbd rashin sabo da nauyin da yake Mata hartazo tafara ganewa ta maida himma sosai tareda nacewa karatu saigashi yanzu batajin wahalarsa Sam ahaka har lokacin exams yayi cikin ikon Allah kuwa taci exams din suka Bata Daman wucewa makarantarsu afia Amma aji daya maimakon aji uku da afia take wato last year dinta wadda daga ita sai University.

Dan hutun dasuka samu yabata Daman waya da iyayenta a waya ta hanyar jekadi Wanda yasake faranta rayuwarta tareda sake kwantar Mata da hankali musamman dataji meryam da padima wadda yanzu ruwan soyayyarsu da amed yafara neman qafewa sbd wasu abubuwan.

A 'yan kwanakin dad dinsu afia na gida Dan haka yanzu ta daina fitowa iyakacin hayaniyarsu a dakinsu ne kokuma a dakin farhat dasuke Zane zanen drowings sbd farhat na tsananin son Zane.

Wanka tafito bataga afia data Bari tana waya da mahaifiyar dad dinsuba ta nufi gaban mirror tana goge jikinta da ruwa ke gangarowa sbd tsantsin fatarta tana duba lokaci tasan suna can sama gurin dad dinsu ta shirya cikin doguwar riga straight designer ta _Alexender McQueen_ wadda taje straight ajikinta ta dauro wata hula Mara nauyi da Bata rufe kanta dukaba sbd tai Mata kadan ta fito ta nufi kicin Dan kamawasu Fana aikin abincin dare.

Sanin suna palon sama tareda dad dinsu yasa tabiyo ta babban Palo sbd hango kaman mum Sarah a palon.

Shigowa tayi gabaki daya palon hankalinta na kan hanyar shigowa da aka bude wani kyakkyawa yashigo sanye da suits farare tsayawa tayi cak tsakiyar palon tana dauke Kai daga kallonsa shikuwa cikin wani irin kyakkyawan murmushi yake kallonta cikeda mamakin wacece wanna agidan yabude Baki zaiyi magana sukaji taku abayansu cikin nutsuwa da Kamala

Da sauri ta juyo daidai Yana isowa daf saura kadan kirjinta ya daki nasa tayi saurin durqusawa qasa zuciyar ta harba da qarfi

Shikuwa kanta dake qasa ya kalla kadan da fararen idanuwansa kafin ya raba ya wuce Jin muryan farhat daga bayansu tana ihun ganin _IMRAN_ NURU na ganin hakan ta miqe da sauri tabar gurin numfashin na kasa daidaituwa dole daki Takoma Dan bazata iya zuwa kicin ahakaba zuciyarta na irin wannan harbawan sbd tsoro

Shikuwa Imran bayan NURUn yabi da kallo cikin basarwa da ya kamo farhat dake tsallan murnar ganinsa tana cewa"

Uncle Imran yaushe kadawo?

MALEEK ya kalla cikin shiga nutsuwa da wani irin kwaijininsa daya cika idanuwansa yace"

Barka da yamma MALEEK.

Zama yayi a kujeransa da Babu me zama Yana amsawa ahankali tareda miqa Masa hannu ya miqo Masa takardun dasukai maganar zai kawo Masa gida.

Karban file din yayi tareda dakatawa daga budewa ya saurara sbd Jin wani qamshi dake fita kadan kadan daga file dinne kokuwa daga jikinsa?

##MAMUH##

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/6, 6:12 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 8_*

Zaune suke a dakin farhat kan kujera tana gyara Mata gashinta da aka gama wankewa farhat din na kwance jikinta tana Mata surutnda fiyeda rabi Bata gane

komai saidai kawai ta murmusawa wata kalmar turancin Idan tajita banbarakwai itama farhat wani lokacin ganin turanci bawa NURU daria yasa idan suna tare turancin take Mata Kuma so take ta iya saboda tanason NURU taringa Bata labari Amma sbd rashin turancin sai ba dama.

Afia ce tashigo tana neman NURU ta qaraso ciki tana kallonsu tace"

Zamu fitan shine Kika jawo aikin gyarawa farhat gashi,

Ki aje idan mundawo a qarasa inason mu biya wani gurin ne daga can.

Riqe hannun NURU farhat tayi tana marairaice fuska tace"

Lewa zanbiku.

Kallonta NURU tayi tareda sakin murmushi tana daure Mata gashin guri daya tace"

Ki tambayi AFIA idan zataje dake to Nima Kinga rakiya zanyi.

Kallon afian sukai duk su dukan atare da sigar roka tayi saurin girgiza Kai tana cewa"

No.

Please AFIA zanje.

Girgiza Kai tayi tana kallonta cikin kulawa tace"

Farhat zamuyi yamma acan sanyi zai sauka kinsan Kuma bakyason sanyi da yawa so ki zauna gida muje mudawo.

NURU Jin tayi kaman tace zata zauna da farhat din ta janyota tana shafa gaban gashinta tace"

Zamu dawo da wuri Inshallah kinji kadaki Bata fuska.

Daki NURU Takoma ta sanya doguwar rigar datafi ta jikinta budewa da daura gyalen rigar akanta sbd su daura sukeyi suka fito afia na sanye da dogon jean da riga me tsayi har qasa saidai gefenta a tsake yake inda ake ganin dogon jean din.

Har jikin mota farhat ta rakosu tana riqeda hannun NURU har suka shiga mota suka fice.

Sai dare suka dawo lokacin farhat harta fara bacci jikin mum Sarah tana jinsu tataso da gudu ta fada jikin afia tareda riqo hannun NURU dake gajiye sbd yawon dasukai na gurare neman wasu text book na afian Kuma sukaje saloon akaiwa afian gyaran qafa itama hadda ita kanta.

Direct daki suka nufa afia tafara shiga bayi alwala kafin tafito itama tashiga tayo wanka tareda alwala tazo kusan atare sukai sallah suna gamawa afia tafara wucewa cin abinci kafin NURUn tabiyota abaya tareda farhat dataketa tambayan Ina da Ina sukaje.

Kamar ko yaushe ita tafara gamawa Amma sbd afia Bata gamaba Bata miqe ba Dan ganin kamar rashin girmamawa ne wa afian datake kamar shugabarta na matsayi.

Saida afia tagama suka miqe dukkaninsu sukai daki afia dakinta ta wuce ita Kuma NURU farhat ta raka dakinta ta sauyo Kayan bacci takaita tayo brush suka dawo dakinsu ta kwantar da ita gefen afia kan gado kafin itama tadawo kujera ta kwanta tana rufe idanuwanta sbd afia tuni tafara bacci Dan agajiye suke.

Washe gari dad dinsu zai dawo Dan haka gidan a natse yake anata gyara da girkin ire iren abincin da akasan su yakeci Dan shi mutum ne da bai cika cin abinci me maiqo ba ma'ana soyayyan Abu bai damesaba kodai dafaffe ko Wanda aka gasa.

Cikin farin ciki farhat take da dawowan dadynta hakama afian Dan haka da wuri tadawo school yau sbd tasan tareda dad din zasuci lunch Dan baya tafiyan dare yawanci da wuri yake dawowa idan yayi tafiya musamman irin wannan daya Dade.

Qarfe biyu da rabi da mintuna hudu jirginsa ya sauka suna zaune a babban Palo suna kallon wani film da NURU afia ce ke fassara Mata me suke cewa tana gyada Kai ahankali sbd kallonma kaman na dolene takeyi afiance ta sakata zaman dole Amma ita tafi Jin dadin zaman daki.

Sunajin diran motan isowanshi da sauri suka miqe farhat da gudu tayi kansa tana Kiran sunansa tana Isa yayi sama da ita Yana sake Mata wani irin murmushin daya kusa sumar da NURU data Dan waiwayo setin qofar idanuwanta suka sauka kanshi da sauri ta dauke kanta daga gurin tana sauke Kai tayi saurin miqewa tana barin palon tsoro na mamaye zuciyarta Dan tabbas laifine yiwa jinin sarautar delah kallon quri bareshi dayake maleek guda na delah gizah Dan haka hanyar daki ta Kama har qafafunta na Dan hardewa sbd tsoron kallon datai Masa Wanda takasa gane laifin ne ya tsoratata kokuwa.

Tana shiga daki toilet ta wuce tana shigewa ta rufo.

Afia ma riqo hannunsa tayi tareda dorawa a goshinta tace"

Dehina metahi ya abal(barka/sannu da dawowa mahaifina)

Kallonta yayi da fararen idanuwansa masu maiqo aciki wani boyayyan annurin ganinta cikin nutsuwa data samu na bayyanuwa cikin ransa ya bude Baki cikin muryarsa me Dadi da sirkin mulki da iko na Koda yaushe yace"

Da akwai wani sirrin wannan boyayyan farin cikin danake gani akan fuskan AFIA UBAYD MALEEK ne?

Wani murmushin farin ciki tasaki suna yowa cikin Palo tace"

Sirrin na farin cikin dawowan abal din afia ne.

Daddy bana dawowankane ba kawai AFIA tasamu best friend yanzu tana surutu da NURU acikin gidan Nan Amma daddy nidai NURU tawace sbd tanada girma irin na AFIA ne suke friends.

Kallon bakin farhat din yayi Yana sauketa cikin palon yace"

Hmmm farhat inaga you are the talkative anan.

Masu aikin gidan ne suka jero mum Sarah ce agaba suka rurrusana suna Masa barka da dawowa cikin tsananin girmamawa batareda kowannensu ya dago Kai ba ya daga musu Kai kawai suka juya suka bar palon Wanda idan ba aiki suka shigoba Babu me shigowa sai mum Sarah.

Har sama farhat tabishi ita Kuma afia ta ja luggage dinsa tabishi dasu iyakacinsu Palo qaida Babu me shiga master bedroom dinsa sai matarsa lailah Dan haka kosu 'yayansa Basu taba shigaba bare Susan Yaya yake.

Suna saukowa daki afia ta nufa inda tasamu NURU zaune tana kallon window inda take hangen library din karatun su AFIA sai datazo Nan takejin tabbas Ashe ilimin boko me yawa yanada amfani tunda gashi yanxu acikinsu Takoma tamkar wani kurman dabba da magana saidai a kwatanta Mata sbd duhun rashin ilimin bokon.

Dafata AFIA tayi tana cewa"

NURU Baki zo kinyiwa dad barka da dawowaba gashi harya shige se yafito cikin abinci Kuma.

Waiwayowa tayi ta kalli afian tareda dauke kai tace"

Darajana bekai naje gabansa harna tsaya na gaishesa.

Murmushi kawai afia tayi tana nufar mirror tace"

NURU kinason dakusar da darajanki anan gidan meyasa haryanxu kinkasa sakin jiki damu ki kulamu da qaunarmu yanda muke jinki?

Farhat na Miki kallon 'yar uwa Kamar ta jini Amma koyaushe kina Mata abubuwan dakesata tuna akwai banbanci me girma a tsakaninku,

Nayi iya duk yanda zanyi Nima ba nuna Miki irin qaunar damuke Miki mundaukeki 'yar uwa Amma Sam kinkasa sakewa Dani Nima meyasa?

Ko bakyajin dadin zama damu ne?

Rayuwanmu be Miki bane?

Tsoro NURU taji na shigarta na maganganun afia din ta juyo ta kalleta tana girgiza Kai tace"

Wlh ko daya Babu wannan sabo ne kawai matsalata inada wuyan sabawa da waje Amma wlh inajin farhat kaman meryam Babu wani abu dabaiminba anan hasalima wani irin girmane kukedashi aguna Wanda yasa bazan iya sakewaba sbd tamkar rashin girmamawa ne.

Ahankali Afia ta dawo takama hannunta tana cewa"

Karna sakejin wannan zoki rakani gurin karatu daganan zanfara koya Miki turanci.

Binta tayi zuwa libry dinsu dakeda wani irin girma da tsari da kyau ga littafai ko wani shagon Saida shagon littafan albarka.

Zama sukayi akan wasu kujeru masu kyau da taushi AFIA ta dauko wani littafi tana ajiyewa gaban NURU tace"

Kiyi kallon zanen dake cikin wannan littafin kafin nagama karanta wani abu cikin wannan littafin na hannuna idan nagama zanfara koya miki.

Karba tayi boyayyan murmushi na bayyana kan fuskarta Jin Wai tayi kallon Zane tsabar toshewar kanta kenan kaman wata yarinya kamansu meryam.

Budewa tafarayi tana kallo aikuwa zanen ne aciki na dabbobi da sunayensu irin su biri,doki,Kare,mage,zomo hardasu bera abin saiyaso Bata dariya ta murmusa harsaida haqoranta suka bayyana AFIA na lure da ita itama sai yanayin NURUn yasata boyayyar dariya.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899[9/8, 4:31 PM] Ummuanwar□: *_MG 10_*

File din hannunsa yasake rufewa ya dan kalli bayan file din tareda yamutsa fuska ahankali cikin yanayi na kamshin zai damesa ya bude Kai tsaye yayi signing inda zaiyi ya rufe tareda miqawa Imran din batareda yace komai ba cikin girmamawa Imran ya karba Yana sake Masa bayanin sauran paparworks din dasuke pending.

Sauraronsa kawai yakeyi idanuwansa akan makekiyar TVn data kusa cike Rabin bangon palon Yana Jin dukkanin abinda Imran din yake bayani akai saidai kaman hankalinsa nason kasuwa gida biyu Dan zuwa yanzu Kam yafara tunanin sauyin qamshin dayake shaqa a hancinsa daga inda yake zaune ne kokuma daga kayan jikinsa Dan yanzu ya tabbata ba file din daya miqawa Imran bane wani abin ne dabam shidaima koma menene qamshin na damunsa sbd qamshin na kaman turaren matane sbd lailah ta taba amfani da irinsa.....

Cak ya tsaya da tunaninsa guri daya tunowa da kusan karon dasukai da mace a palon hakan na nufin suturar jikinsu ta hadu data juna Dan idan ba hakaba Babu yanda zaayi qamshin ya maqalu a kayan jikinsa.

Miqewa yayi yabar palon Yana dagawa Imran Kai alamar amsawa daga gaisuwan a huta lafiya maleek dayayi masa ya shige Palo na biyu yakamata hanyar hayewa samansa.

Daidai fitan dad din daidai shigowan Afia data baro daga dakinsu tana ganin Imran ta saki wani qayataccen murmushin farin ciki tana qarasowa ta zauna tana cewa"

Barr uncle Imran yaushe kashigo?shine ko atambayi Ina afia.

Kallonta yayi da milky idanuwansa Yana sake murmushin daya sata qara kallonsa tana sake kyakkyawar fuskarta cikin muryansa me class kaman Koda yaushe yace"

AFIA MALEEK kinyi saurin tambayane Amma kinsan bazanzo nafitaba batareda naganki ba Dan haka ma nemanki dole ne.

Hmmm that sounds like a bribe.

Dariya yaso saki ya daure Yana miqewa tsaye riqeda hannun farhat Yana cewa"

Ina sauri zantafi zan dawo zuwa weekend zamu fitama inshallah Amma dagani sai farhat.

Tsalle farhat ta buga tana murna da cewa"

Amma zamuje da my lewa?

Kallon tambaya yayi wa afia data tsuke fuska tace"

Don't give me that look bazan fada maka wa take nufi ba tunda ku kadai zakuje kuje muma zamuje inda mukeda buqata.

Juyawa tayi zata tafiyanta yayo gurinta zai hanata tayi gaba da gudu tana cewa"

Kowa yaje da Wanda yakeso bazan fada ba.

Wata 'kayataccitar dariya yabita dashi cikin ransa Yana cewa"

Naga wadda kike nufi kawai inason sanin wacece ita din.

Juyowa yayi gurin farhat tareda shafa kanta Yana cewa"

Sainazo weekend din ko Uncle's princess.

Bayan tafiyansa zamanta tayi apalon tana kallon cartoon sama sama sukuma suna can daki NURU na kwance idanuwanta arufe baccin dole nason daukarta.

Har dare a kame take da kanta acikin daki hakanan idan abin yadawo Mata sai tsoro yasake shigarta sbd tasan da a delah ne hakan yafaru Allah ne kawai yasan hukuncin dazata fuskanta akan ko hada hanya da MALEEK bare kusan karo Wanda taji lokacinda jikinsu ya 'dan shafu sbd itace me tudun qirji.

Afia taso fahimtan akwai wani abu atareda da sanyin NURUn Amma Kuma sanin halin NURUn na yau shiru gobe sakewa yasata sharewa Bata tsaya tambaya ba har sukai bacci.

Washe gari ma ko breakfast a kicin tayisa kafin suka wuce school tanaji afia na maganar dad dinta tafiya zaiyi yau itadai Bata iya cewa qala ba sbd duk lokacinda

su afia da farhat suka dauko maganar dad dinsu Bata taba Koda kuskuren saka Baki ba sbd sanin matsayinta be Kai na saka Baki a zancensaba.

Weekend nayi Barr IMRAN JALALUDDEEN 'dan babban yayan lailah dake qasar ta France shima wato babban tsohon chief minister na esthern ambassador Wanda bayan manyancinsa yakoma gida Amma shi 'dansa IMRAN na zaune anan qasar haryanxu sbd anan yake karatu tareda aikin gamayyar wani sashen kamfanin MALEEK dake qasar yazo gidan da maraice cikin lafiyayyar motarsa white jaguar Yana sanye da designers qananun Kaya dark blue na _Jimmy choo_ wainda suka fito da asalin kyawunsa na Dan Africa sai qamshin Mara hayaniya dayake fitarwa kallo daya afia tayi Masa kaman koyaushe data Saba tace"

Hmm Uncle u look great.

Murmushi yasaki Yana kallon NURU dake gefenta zaune kan kujera tana qoqarin hada wasu kalmomin English a iPad tana sanye da riga da wandon Palazzo me Fadi sosai rigarce kawai takeda shape itama Bata roba bace chiffon ce sai gashin kanta dake dunqule cikin Dan qaramin scarf da turkian gabaki daya hankalinta nakan abinda takeyi dan Monday zatayiwa malamarsu Mrs Edward presenting karatun shiyasa hankalinta baya kansu tunda ta Masa Ina wuni bayan shigowarsa.

Dauke kallonsa yayi daga kan NURU cikin basarwa yasaki wani boyayyan murmushi yana cewa idan sun shirya su taso suje a Kai farhat garden datakeson zuwa.

NURU bataso zuwa ba sbd karatun daya gama daddaure kanta da tunaninta Amma farhat ta takura akan ita da ita takeson aje dole badan tasoba tashiga ciki ta sauyo dankwalin kanta zuwa veil Mara datayi Rollin sai takalmi data sanyo loafers sabanin Afia datai ado bame yawaba itama kusan irin kayan NURU ne ajikinta suka fito suka wuce afian ce Agaba sai farhat da ita NURUn a baya wadda Sam ko kallon sosai bataiwa Imran ba bare ta lura da Yana Dan kallonta akai akai sbd gabaki daya ita bataso fitanba taso tsayawa tayi karatunta Dan yanzu data fara sanin kanshi da wayar karatun batada babban burin daya wuce samun ilimi me zurfi domin tsayuwa da kanta da iyayenta shiyasa yanzu kwata kwata batada lokacin batawa sbd karatu.

Duk wani yawo da tarin siyayyan da akayo a fitar basa kanta gida tamatsu su koma Dan haka harsuka gama yawon suka dawo bazatace ga takamaimai na kamannin

Imran jalal ba Amma shikam yagama karanceta tsaf kaman yanda yake buqata musamman dayayi fira da farhat Sosai yagama fahimtar babban burin NURUn yanzu karatu ne sai hakan yasakashi farin ciki sbd dukkanin wannan na daya daga cikin abinda yake tsananin so ga irin matarda yake ra'ayi.

Ko kafin Monday karatunta tagama fahimatarsa sbd takuran data saka kanta ta saka afia Saida ta tayata bayani harta fahimta dakyau dakyau shiyasa Monday din harsuka je suka dawo cikin annashuwa take musamman data fara da samun yabo gurin Mrs Edward.

Imran jalal kuwa da zuciyarsa takasa hkr da rashin bawa kasa dama agurin NURU yasashi dawo da ziyarar daya Dade da daina kawowa gidan ahankali ahankali tun Bata wani bi takan sha'aninsa dasu afia harta fara sabawa dashin musamman akan karatun dayake dorata akai sosai Dan hakan sai sabo yashiga tsakaninsu duk da baitaba nuna wata alamar so atareda Shiba sbd yasan Basu Isa fara soyayyaba ayanzu tunda karatu ne agabansu sai sunshiga University Koda zasu fara bawa wata soyayya dama.

A bangare makaranta kuwa karatu tuni yadau hanyar nisa Dan kuwa yanzu tana farkon shiga aji uku ita kuwa Afia tana shirye shiryen zuwa _Las Vegas_ karatun shekara daya kafin tadawo tashiga University anan Paris dan haka sai suka Dan shiga damuwa sbd sunrigada sunyi wata irin shaquwa yanzu wadda Sam basa iya ko yini batareda junaba gashi zasuyi rabuwan shekara daya duk da zata ringa zuwa hutu.

Ranar dazata wuce tareda dad dinsu zata tafi Dan haka rakiyar NURU iyakacinta palon ciki Bata fito babban ba har suka wuce cikeda kewar juna.

Bayan tafiyan AFIA sai Kamar wani babban nauyi yahau kan NURU sbd yanzu itace shugabar gidan ita ke bada umarnin komai ta bangare daya ga karatunta ga kula da farhat wadda itama kewar afia ta tabata Amma kasancewar yanzu tamkar ma uwa take ganin NURU sai Bata wani jimaba cikin damuwan tafiyan AFIA din takomawarta Kiriniyarta.

Yau Kam amatuqar gajiye take sbd Suma sunfara shirye shiryen fara midterm exams Dan haka karatu take Babu sauqi ta Dan hakan tana dawowa daga school

wanka tayi bayan ta tabbatarda farhat tayi baccin Rana sai itama Takoma daki tayi Mata wankan ta Sanya riga fara mara nauyi da dogon pencil jeans Wanda yakama siraran cinyoyinta tareda bayyana fadin hips dinta ta sanyo hular dabata rufe kanta dukaba ta fito taje kicin tasamu fresh milk me sanyi sosai Tasha tareda lumshe fararen idanuwanta dasuka gama galabaituwa da gajiya ta fito riqeda sauran madaran tazo Palo ta zauna tana daukan wayan afia data kirata suka fara waya tun tana sawa har bacci me Dadi yafara Dan fizgarta Dole sukabar wayar ko motsawa batai daga gurinba bacci me nauyi yayi gaba da ita a palon.

Farhat data tashi nata baccin tana fitowa palon taga NURU tayi bacci kan kujera ta kalla kyakkyawar fuskarta datai fresh sbd samun hutu da gyara saita saki murmushi tareda qarasowa zata gyara Mata kwanciya ganin kaman zata fado tana Dora hannunta akanta taji dirin motocin dad dinta yadawo cikeda farin ciki ta miqe ta nufo qofa da sauri ko ta bude tareda rumgumesa cikin qasa qasa da murya tace"

Welcome dady.

Kallonta yayi cikin kulawa da mamakin meya samu muryanta take magana ahankali

Duk da qarancin shekarunta ta dade da sanin dad dinsu ba komai yake budewa Baki yayi magana ba da kallo ma kawai suna gane maganarsa Dan haka ta fahimci mamakinsa tasakeyin qasa da murya cikin rada tace"

Dady Lewa na Palo and she's sleeping tagaji sosai da yawa koyaushe batada time din hutawa yanzu tasamu tayi bacci please dady kadamu tasheta.

Kallonta yayi suna qarasowa tsakiyar palon dan dama yasan tsawon shekarun Nan farhat Bata mgnar daya biyu saita lewa,my Lewa,my beauty kunnuwansa harsun gaji dajin sunan abakin farhat.

Dan juyi tayi daga kwancen ta sulmoyi zata fado da sauri farhat tayi kanta ta tareta Amma sbd NURUn tafita girma da nauyi saita kasa tareda saima danneta da NURUn tayi batasaniba sbd baccin yayi Mata nauyi sosai Dan tajima Bata baccin kirki Koda daddare.

Da sauri farhat ta kalli inda yake tsaye cak Yana kallon qanqanuwar yarinyar dabatafi AFIA shekaru da girman jiki da komaima.

Cikin wuya farhat tace"

Dady hannuna zai karye aunt NURU nada nauyi sosai.

Cikin wani irin taku da izzar data gama kame jininsa ya iso gurin batareda ya kalli NURUn ba ya Dan ranqwafo yakai dogayen hannuwansa masu siffar qarfi tareda tsananin taushi ya zura qarqashin bayan NURUn farhat tasamu damar janye hannunta tana yarfewa tayi dakinta da gudu tana cewa hannuna zai kumbura Bari nashafa ointment da sauri kada ya kumbura aunt NURU nada nauyi sosai.

Idanuwansa dake raunana kuzarin Wanda duk ya zubawa su ya waiwayo ya zubawa fuskar NURU wadda take wani glowing na zallar asalin kyawun da Allah yayi Mata.

Gangarowa yayi da kallonsa kadan zuwa jikinta a qirjinta ya dakatar da kallon tareda dauke fuska Yana zare hannuwansa daga qarqashinta yabar gurin sai ayau yasan babban shirmen da Kaleb ya tafka da jekadi kenan tsarar 'yar cikinsa suka kawo Masa amatsayin negestati,

Ta Yaya suke tunanin wannan yarinyar tsarar afia zai iya hada shimfida da ita?Tama Yaya zata iya daukan nauyinsa ko ciki baya tunanin kwsmkesonta zai iya dauka bare haihuwa... unbelievable" yafada cikin zuciyarsa a 'dan takaice sbd tunano 'yarsa afia dake tsararta baya tunanin ko Nanda shekara biyar zai aurar da ita Dan ganin kaman tayi mugun qanqanta amma shi ba saurayiba ko 'dan samari akawo Masa wannan.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/8, 4:31 PM] Ummuanwar□: *_MG 11_*

Sai magrib ta farka ta bude idanuwanta dasukai nauyi sosai tana kallon inda take ta lumshe idanu tana sake tabbatarda tabbas ta gaji matuqa gabaki daya rayuwarta yanzu hutu takeso Dan hakan zata sassautawa kanta tunda dai karatun yanzu yazaunu a kanta.

Tashi tayi zaune tana shafa wuyanta dayayi Mata sakayau sbd yanayin yanda tayi kwanciyar.

A kasale ta miqe tayi ciki tana duba qaton agogon dake bangon palon ta shige palon ciki ta doshi hanyar bedroom dinsu tashige.

Saidayi sallah kafin tayi wanka ta Sanya doguwar riga Mara nauyi black me dogon hannun Kuma har qasa take komaima Bata sanyo akantaba ta fito ta nufi dakin farhat tana Kiran sunanta.

Zaune take tana homework NURUn ta shigo taqaraso kusa da ita ta zauna farhat din ta haye cinyarta tana cewa"

My Lewa dubamin kigani yayi daidai kuwa?

Murmushi NURU tayi tana karba tafara dubawa tana cewa"

Ni danasan farhat Dina nada kokari Babu homework da bazata iyayi daidai ba Amma dai yanzu kinajiye muje kici abinci tukuna daga baya a qarasa lokacin cin abinci yayi.

Kwantawa tayi jikin NURUn tana cewa"

Ni yau banason cin abinci cupcakes and pancakes nakeso cin zakimin ai ko my Lewa?

Kumatunta taja tana sake gyara Mata kwanciya ajikinta cikin tsananin qaunar farhat din tace"

Yes of course sweetie duk abinda kikeso shi zakici.

Ahankali ta sake lafewa jikin NURUn tana cewa"

I love you my Aunt NURU.

I love you too baby.

Tashi sukai NURU na cewa"

Muje cikin yanzu bada dadewaba chief NURU zatayiwa princess pan and cup cakes dinta duka.

Kicin suka nufa cikin murna farhat ke taya NURU aikin da surutu sbd Babu kowa yanxu acikin gidan Dan dama da angama abincin yamma tun 7 na yamma kowanne me aiki na gidan ke barin shashen sukoma sashen masu aiki musamman idan MALEEK na Nan to ita yau batamasan MALEEK din yadawoba Yana gidan.

Saidata gama hada cake din tasaka a oven tafara gasa pancakes din lokacin tuni tacewa farhat taje dining ta zauna gatanan kawowa yanzu.

Cikin farin ciki takeyin aikin daga can cikin kicin din ta Dan dago muryarta me sanyin dadin sauraro tace"

Sweetie kinajin qamshin cake din Nan kuwa daga Nan inda kike sbd I just added your favorite inib yanzu akai inason kina fara cinsa kunnuwanki suyita tsalle Suna gudu sbd Dadi.

Dariya farhat tasaki tana toshe Baki idanuwanta akan fuskan dad dinta daya Dade da samunta a dining din Dan lokacin dinner dinsa yayi.

Ahankali ya dan kallin hanyar qofan dazaikaika kitchen din saikuma ya dauke Kai tareda saka spoon akan lafiyayyan abincin dake gabansa Wanda yanzu Fana tagama serving dinsa ta fice daga sashen gabaki daya.

Kasa kasa da murya farhat tace"

Daddy ai zakaci pancakes dina sbd cakes din aunt NURU are the best

Idan kaci wannan kullum zakaso ka qara kaji Kuma tasaka inib oh oh daddy na matsu akawo.

Dan kallon farhat din yayi da fararen idanuwansa Yana iya ganin farin ciki me tarin yawa da nutsuwar rayuwa gashinan bayyane ko Ina atareda farhat din Wanda hakan yasa yaji wata nutsuwa tashigesa tabbas yaransa deserve the best life,

Yaran MALEEK guda na delah gizah sun cancanci kowane irin farin ciki na duniya dai sbd sune keda matsayinda kusan yafi na kowa a gizah sbd mahaifinsu shine asalin maleek na kujerar sarautar delah gizah Amma rashin dacen uwa Kamar Laila yabarsu da qarewa tamkar marayu gashi shikuma schedules dinsa na rayuwa sun hanashi lokacin zama tareda yaransa.

Amma koma dai menene tunda sunsamu kulawa daga wannan din hakan yamasa Dan kuwa yaransa na cikin walwala da farin ciki Kamar Basu taba shiga damuwan kewan iyayeba musamman AFIA tasamu 'yar uwar dataketa yiwa kanta mafarki da fatan asamu hakama farhat tasamu dukkanin soyayya da kulawan datafi buqata daga iyaye sbd qarancin shekarunta.

Dauke da kyakkyawan tray ta fito kitchen din ta nufo dining room tana

Cewa"

Sweetie are you ready??

Yessss ""farhat tafada da Dan qarfi cikin Jin Dadi da qaguwa.

Ok baby I'm coming ki tabbatarda yau kin rufe qofa da windows dinda kunnuwanki zasu gudu Dan kuwa yau hmmm.

Tana shigowa cikin dining room din tace"

Tadaaa.....cak ta dauke wuta ganin dadynsu farhat din a zaune da 'dan guntun mamakinsu akan fuskanshi sbd su biyun kawai sun cika gidan da hayaniyar datafi ta mutum goma..

Rawa qafafunta suka dauka sbd tsananin tsoro da firgicin data shiga saura kadan tasaki tray din farhat ta karba da sauri tana cewa"

Zaki zubar muyi wahalan banza fa.

Batama San me farhat ke cewa ba gabaki daya ta rude ta tsorota batasan abinyi ba sai kawai ta durqusa cikin rawar murya tace"

Barka da dawowa da fitowa.

Tsit gurin yayi sbd kallo daya yayi Mata ya dauke Kai sbd kayan dake jikinta da kanta dake bude

Itakuma tunda yau ta ritsu Babu damar wucewa batareda izininsa ba Dan hakan ta sauke Kai durqushe agurin.

Farhat ce ganin shiru shiru dad din nacin abincinsa hankali kwance yasata sauka kan dining din tazo gaban NURU ta kamo hannunta tana janta tashi tace"

Lewa Daddy ya amsa gaisuwanki kitaso muci cakes din kibani abaki na matsu nafara ci.

Dan zare hannunta tayi daga na farhat din tana sake saukar da Kai qasa Dan bada tsananin girmamawa ga zaman maleek dake gurin.

Tissue ya dauka ya goge bakinsa tareda Miqewa cikin nutsuwa da kamewarsa ya bar gurin sbd yagama cin abincin dakuma hayaniyar dazata iya basa ciwon Kai tasu.

Yana barin gurin ta zube zaune gabaki daya tareda sauke ajiyar zuciya me sanyi tana dagowa ahankali ta dan saci kallon bayansa ta sauke Kai da sauri tana dawo da kallonta kan fuskar farhat dake Jan hannunta,

Kyakkyawan hancin farhat ta zubawa ido Wanda yake tsaf tsaf na dadynta ne ta debo ta gangara da idonta kan idanuwan farhat din take kirjinta ya buga da qarfi ta dauke idonta akai tana miqewa Kamar wadda kwai yafashewa aciki.

Kasa zama tayi sbd sanyin qamshin turaren dadyn daya cika gurin Kamar har lokacin kaman Yana gurin Dan haka saitakejin bazatama iya sakewaba Dan Jin take kaman Yana Nan Dan haka a tsaye tabawa farhat din abaki harta qoshi itama biyu kawai taci suka tattare gurin suka nufi daki sukai brush tareda wanka sukai sallar Isha sukai Shirin bacci suka koma dakin farhat din acan suka kwana.

Washe gari datasan Yana Nan batai gigin ko kallon hanyar dining room ba sbd dama acan ne kawai ake haduwa dashi acikin gidan Dan koyaushe Yana samansa Dan ko acan saman Palo biyune dashi kafin akai Master bedroom dinsa.

A kicin tayi breakfast bayan antafi Kai farhat school Dan haka itama tana gamawa driver ya wuce da ita.

Kwana biyu tana kame Bata wani fitowa sai yaunema da farhat ta tashi da zazzabin sanyi me qarfi na asthman datake dashi Wanda kaman agurin dadynta ta dauka Dan shima yanada asthma Amma ba'a taba ganewa sbd kiyayewa.

Kayan sanyi masu kauri ta Sanya Mata da socks da wulan sanyi tareda dumama dakin yadauki dumi takawo Mata tea me zafi tabata ahankali hartashanye tana gama Sha ta koma kicin ta maida kayan tadawo kenan tun daga bakin qofa take jiyo kukan farhat din da sauri taqaraso cikin rufewa ganin amai farhat din keyi sosai take hankalinta yatashi ta dauketa tayi toilet da ita yarinyar tafara galabaita sosai Dan kuwa ko zama Bata iyayi da kanta sbd galabaita.

Wanka tayi Mata tasake Sanya Mata wasu kayan masu nauyi bayan ta shafe Mata jiki da mai me Dan zafi ta sake gyare dakin tsaf ta sauya bedsheet da duvet ta kunna turaren daki dake fita ahankali ahankali Yana gauraye dakin da qamshi sai dakin yayi Dadi sbd ga dumi ga qamshi me Dadi.

Fitowa tayi daga dakin Bata cikin nutsuwarta sbd ciwon na farhat yafara Bata tsoro sbd numfashinta dayake wani daukewa yana dawowa gashi tun safe take Kiran Afia Bata samu gasu mum Sarah ma duk sunyi iya dubarunsu Babu sauqi Dole dadynsu afia din akeson sanarwa sbd anema likita cikin gaggawa Amma shima tun safe bai saukoba hakan yasa hankalinta mummunan tashi tashiga tsoro da firgicin halinda take ganin farhat Dan tana tsananin buqatan ganin likita.

Palo tadawo ta tsaya idanuwanta na cikowa da hawaye tarasa abinyi sai kawai ta zauna kan kujera tareda fashewa da kuka ahankali tana cewa"

Yaya zanyi Ni?

Mum Sarah ce da itama take cikin tashin hankalin tace"

Ki Kira IMRAN kifada Masa saiya Kira MALEEK yafada Masa.

Dago idanuwanta dasukai ja sbd kuka tayi ta kalli mum Sarah cikin sake shiga damuwa me qarfi tace"

Bayan afia Dana kasa samu IMRAN ne na biyun danayita Kira Amma shima wayarsa Bata zuwa.

Ki rubuta Masa text zaigani inshallah.

Hawayen cikin idanuwanta suka gangaro batareda ta damu da shafewaba ta daga wayarta tahau rubuta Masa massage tana turawa ta miqe jiki amatuqar sanyaye ta rurrufe ko Ina Takoma daki gurin farhat din.

Zama tayi bakin gadon tareda zubawa yarinyar idanuwanta dasukai luhu luhu sbd kukan tausayin farhat data zabge cikin yini daya sbd azabar ciwo.

Cikin kuka Mara sauti tace"

Farhat Allah yabaki lafiya

Bazan iya cigaba da ganinki hakaba.

Kuka takeyi sosai kafin daqyar ta iya miqewa ta rage kayan jikinta sbd zafin da dakin ya dauka yayi Mata yawa ita ta Sanya riga da wandon bacci qananu rigar Mara hannu ce sai wandon gajere ne iya cinya ta hau gadon tareda rungumo farhat ajikinta ta lullubesu bayan tayi musu addua har lokacin tsiyayar hawaye takeyi ahaka bacci ya dauketa tana qanqame da farhat din.

IMRAN lokacinda text din NURU yashigo wayarsa ya duba agogo qarfe dayan dare da minti arbain da uku sai hankalinsa yayi mummunan tashi sbd yasan ciwon farhat din zabura yayi ya miqe tsaye Amma Kuma bazai iya zuwa gidanba yanzu Amma Kuma tsoronsa idan har lokacin ciwon bai lafaba kumaba,

Numbern MALEEK ya lalubo a rikice ya Danna Masa Kira

Amma kaman yanda yayi tunani bai dagaba Kuma yasan ba dagawan zaiyiba sai kawai ya rubuta Masa massage cewan farhat na cikin mawuyacin hali tasamu attack na asthman datake dashi Yana turawa yakoma ya zauna Yana dafe kansa cikin rashin nutsuwa Dan yasan NURU ma nacan cikin mawuyacin halin damuwa da firgicin ganin farhat acikin halina ciwo.

Kwance yake idanuwansa ne kawai a rufe ba bacci yakeba sbd yanayin sanyi da ake yau me tsanani dashima yakeson Dan dago Masa da ciwonsa sai qaramin ciwon Kai dake damunsa na rashin bacci shiyasa yau ko fitowa baiyiba ruwan energy drink na powerhorse kawai yakesha sai yaga wayarsa na haske alamar shigowar Kira batareda ya dubaba ya share wayar Dan ba dauka zaiyiba.

Ganin anata Kira yasashi dauka Dan kashe wayar duka saiga text din Imran jalal yashigo bai budeba ta gaban lockscreen din yafara ganin abinda ke rubuce cikin massage din ya tashi zaune ahankali Yana qarasa karantawa ya ajiye wayar tareda Miqewa tsaye cikin nutsuwa ya sauko gadon tareda zura slippers din _Berluti_ masu tsananin tsada da rashin nauyi yafito zuwa qasan sanye cikin sleep wears na _prada_ black colour ya sauko direct bayan wasu shekaru yau ya nufi dakin farhat Kai tsaye.

Murda qofar dakin yayi ya tura wani dumi da qamshin English rosalle oud ya daki fuskansa zuwa cikin hancinsa ya sauke boyayyan numfashi ahankali sbd best mist dinsa kenan na daki ya shigo dakin tareda tura qofa sbd akwai Dan duhu a dakin cikin takunsa na nutsuwa da kamewa ya isa bakin gadon farhat din ya zauna tareda kallon 'yar qaramar fuskarta data fada lokacin daya wani irin tausayin 'yarsa da qaunarta me qarfi na ratsashi yakai hannunsa akan fuskarta ya shafa yanajin kaman yakasa amatsayinsa na mahaifi yakasa Basu rayuwarda suke buqata ta kulawan uwa da uba.

Bedside light ya kunna 'dan haske ya bayyana yasake Kai hannu kan wuyanta zai taba yaji temperature dinta hannunsa ya sauka kan hannun NURU dake rungume da ita kaman zata maidata ciki sai alokacin ya lurada NURUn wadda gabaki daya jikinta ke bayyane farar fatarta dake tas wani irin qyalli takeyi musamman dogayen cinyoyinta dake wani haskawa afili ya dauke kansa Yana Dan yamutsa fuska ya zuwa fuskarta da idanuwanta suka bayyanarda kumburinsu na alaman kukan datasha sai sauke ajiyar zuciyar kukan datai takeyi akai akai cikin baccin ya gangaro da kallonsa kan irin rungumar dataiwa farhat cikeda qauna da alamun dake nuna Jin take kaman ciwon yadawo jikinta.

Ya rintse idanu Yana jinginar dakansa jikin kan gadon hannunsa har lokacin nakan nata batareda yatuna ya daukeba sbd tausayinsu duk su duka wato itada 'yayansa daya shigesa.

Rufe idanuwansa yayi ahakan yanajin numfashin farhat me dumin zafi na sauka ajikinsa itakuma Kuma dumin zafin jikinta na zazzabin wuya daya fara shigarta na shiga ahankali nasa jikin ta hannunsu dasuka hadu.

##MAMUH##

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899[9/8, 4:31 PM] Ummuanwar□: *_Mamuhgee 12_*

Qarfe shida da wasu mintuna ya bude idanuwansa dasukai nauyin baccin daya daukesa daga Nan jinginen kan gadon.

Tashi zaune yayi ahankali yana kallonsu sbd har lokacin bacci sukeyi sosai musamman da alamu ya nuna farhat din ta samu sauki sauki sbd numfashinta daya 'dan daidaita.

Hannunsa dake sarqe cikin na NURU data qanqame ya kalla ahankali tareda dago manyan fararen idanuwansa da bacci ya Dan sauyasu ya zubawa fuskarta datake Kama data 'yan babies kaman farhat dinsa saiya maida kallonsa kan farhat da itama innocent face dinta tayi haske ya saka dayan hannunsa yakama hannunta ya zare hannunsa Yana kallon fararen yatsun hannunta dasuke farare fes kaman Bata aikin komai dasu ya miqe yaja bargo ya rufe musu jikinsu musamman NURUn da cinyoyinta suka gama Shan sanyi duk da Babu wani sanyi ko kadan a dakin shiyasa ma shima baccin yadan daukesa.

Ficewa yayi dakin ya rufo musu qofa yayi samansa Dan yin sallah da yau yayi latti.

Bayan fitarsa ba jimawa NURU ta farka ta tashi jikinta amatuqar mace da Dan nauyin jiki da sauran ciwon kan dabai gama sakinta ba ta zauna tareda kallon farhat tana tabata tareda duddubata ta tabbatarda tasamu sauqin dannewan numfashin saitaji hankalinta yadan kwanta ta sauko gadon ta nufi toilet din dakin tashiga tayi duk abinda zatayi tazo alwala tana Kai ruwa bakinta zatayi shaqar hanci taji wani irin qamshi a tafin hannunta ta Kai hannun hancinta ta sake shaqa taji wani irin qamshi dayaso kashe Mata jiki Amma Kuma takasa tuna na menene tunda tasan last abinda ta taba kafin baccin was kayan baccin data Sanya ta kwanta.

Cigaba tayi da alwalarta tagama tafito Takoma dakinsu acan tayi sallar tana idarwa tadawo ta duba taga farhat Bata farkaba har lokacin bacci takeyi ta gyra Mata lullubinta tareda gyara Mata kanta Takoma daki ta cire kayan baccin ta Sanya dogon wando da rigar sanyi da hula ta nufi kicin Dan hadawa farhat din pancakes

da tea din sabuwar Madara datasan farhat na tsananin so ko zata samu taci Dan duk jiyan bata iyacin komaiba sbd tsanani da azabar ciwo.

Tana cikin aikin mum Sarah da itama baccin rabi da rabi tayi sbd damuwar ciwon na farhat tashigo tana Taya NURU aikin bangare daya Kuma ga Fana na aikin hada breakfast na MALEEK.

Sauri tayi tagama sbd kada farhat din tatashi Bata kusa tana gamawa ta aje jere komai a dining ta nufi dakin farhat din tana waya da Afia data Kira a rude sbd Imran yafada Mata saita kwantarwa afian hankali tana cewa farhat din tasamu sauki inshallah.

Turo dakin tayi tashigo Kai tsaye tana ganin farhat din zaune kan gado ta qaraso da sauri cikin farin ciki idanuwanta na cikowa da hawaye cikeda qaunar farhat din me girma tace"

Finally Sweetie kin tashi""rungumeta tayi tana cewa"

I miss you so very much baby

Kinabani tsoro jiya sosai harbansan tunanin me zanyiba.....

Idanuwanta ne suka sauka akan MALEEK dake tsaye gefen gadon daga dayan gefen fuskarsa nakan waya dayake dubawa na Kiran dayayiwa Dr Damien.

Wani irin mummunan firgici da tsoro ne yashigeta tayi Saurin gayara hularta data zame tana tashi daga kan gadon tana gyara wuyan rigarta ta sauke Kai qasa tareda zubewa qasa cikin tsananin girmamawa da sanyin murya tace"

Barka da fitowa.

Bai jita bane kokuwa ya akai itadai dataji shiru ta dago sai taga baya gurin saitaji jikinta yasake yin sanyi sbd wani lokacin mantawa takeda matsayinta na baiwa sai irin hakan ta faru take tunowa da ita din bakowa bace face baiwa 'yar bawa jikar bawa gadon bauta,

Allah ne yahada qauna me qarfi da tsafta tsakaninta dasu afia da farhat Wanda ta dauka hakan tamkar wata rahamace ga rayuwarta shiyasa dorewa da dawamammiyar qauna atsakaninta dasu afia yazama cikin adduarta tacikin sujjadarta.

Kamo hannunta taji farhat tayi ta juyo kanta tareda zama kusada ita tana kawar da tunanin damuwa tasaki fuska cikin kulawa tace"

Yaya kikeji yanxu sweetie?

Kwantawa tayi jikin NURUn tana gyada Mata Kai alamar da sauqi.

Shafa kanta NURU tayi tana cewa"

Baby muje ayi brush nahada Miki pancakes dinki kici ko kadan ne zakiji Dadi Dr ma Kuma Yana zuwa hakama uncle Imran na zuwa haddama AFIA nason Jin muryan princess farhat.

Kallonta kawai farhat din keyi sbd Bata iya ko dariya haka ta dauketa takaita toilet tayi Mata wanka da ruwa me zafi tayi Mata brush suka fito ta shafa Mata Mai da duk abinda yakamata ta shiryata cikin Kaya masu kauri sosai tareda hular sanyi da socks ta hannun da qafa suka fito Palo tana daukeda ita suna fitowa babban Palo Ana budewa Imran kofa Yana shigowa cikin kayan sanyi shima sbd yau gari akwai sanyi sosai tana ganinsa taji wani irin sanyi aranta sbd dama Wanda zaiyi magana da dadynsu farhat din take neman mafita.

Qarasowa yayi Yana karban farhat din ya kalleta lokacinda ta lafe ajikinsa cikin kulawa yace"

Sorry farhat baby.

Kallon NURU datai Dan zuru zuru yayi yaji jikinsa na mutuwa da wata sabuwar qaunarta me qarfi ya sassauta kallonsa Yana Mata kallon kulawa yace"

How are you?

Numfashi ta sauke tana kallonsa tareda tana nufar dining room tace"

Am gud,ya sanyin yau?

Munsaka tasowa da safe haka.

Zama yayi da farhat daidai tana dawowa daukeda tray din tea da pancakes tazo ta zauna kusa dashi tana daukan cup din tafara bawa farhat dake jikinsa zaune tana sake Masa bayanin Yan jikin farhat din yake jiya shikuwa sai binta yake da ido cikin kulawa Yana sauraronta yanaji acikin ransa kaman itada farhat din iyalinsa ne duk da dai Bata Isa haihuwan farhat dinba Amma sai yaji inama ace acikin gidansu suke da ita amatsayin matarsa da hadasu zaiyi su biyun ya ciyar dasu breakfast din.

Ahankali qamshin dataji da safe a hannunta hakama a kayanta kwanaki data rasa Ina tasamu taji Yana doso hancinta Yana shiga cikin sanyi Bata kawo komai akaiba taci gaba da bawa farhat din daidai tana gama Bata Imran yace"

Ok tunda farhat ta qoshi saura lewanta yanzu.

Murmushi ta 'dan sake zatai magana qamshin yashiga hancinta sosai ta waiwayo ahankali idanuwanta ayau cikin babbar rashin sa'a suka sauka cikin NASA daidai shigowarsa palon gabaki daya cikin wasu Armani's dark blue best color dinshi sbd kalar na fidda kalar fatarsa sosai,

Gabaki daya shekarunsa na dattijanka sun boye cikin hutu da izzarsa tareda kamewarsa dake yawo cikin jininsa na sarautar asali,

Babu Wanda zai kallesa Kai tsaye yace shine ya haifi zuqeqiyar budurwa kamar AFIA UBAYD MALEEK ba.

Inda suke bai kalla ba dukkaninsu suka miqe tsaye musamman NURU da tuni tayi ciki daukeda tray Imran yabita da 'dan satar kallo gashi jeans ne ajikinta Wanda yasa MALEEK qara muryan tv kadan tadawo da Imran din hankalinsa.

Dr Damien yazo tareda nurse yaduba farhat Sosai tareda Bata duk wani kulawan likita datake buqata kafin yatafi yabar nurse dazata cigaba da kulawa da ita harta warke tukuna.

Duk yanda yaso sake ganin NURU harya gama yininsa ya tafi Bata Kuma fitowaba saidai suka rage firan a waya sbd maleek na gida Kuma a palon farkon yake zaune yau Wanda yasa kaf gidan tsayawa iyakarsu sbd ba'a wilgewa idan Yananan.

Saida zai tafi NURUn ta rakosa har mota sbd maleek na sama sai lokacin Imran yaji bayason tafiya musamman yanda NURUn duk ta sukurkurce akan ciwon farhat din Amma haka ya tafi yabarta.

Da daddrema haka batareda sun saniba bayan sunyi bacci yashigo dakin wannan karon NURU kayan baccinta masu Dan tsayine Dan wandon kayan yakai gwiwowinta hakama rigar nada hannu Amma duk Rabin Samanta abude Dan haka ko zama baiyiba ya dubasu ya gyara musu lullubinsu yafice daga dakin.

Kwana biyu tana kulawa da farhat Sosai hartaji sauqi ta warware Takoma kiriniyarta sai alokacin hankalin NURU ya kwanta tasamu walwala itama sbd dama ita tafi zamowa kaman farhat din da dabiun yarinta akan afia data dauki girman Dole ta dorawa kanta na zama babba acikinsu.

Imran kuwa sai zuwansa na yanzu ya ninka na da Dan yanzu Sam yafara saka danne feelings dinsa NURU Dan kusan kowa yafara fahimtar hakan gashi karatunta na tafiya daidai shaquwanta da Imran yasa ta dauki burin zama lawyer itama sai hakan yasake bashi kwarin gwiwan soyayyanta.

**AFIA tagamo karatunta na shekara daya Wanda yayi daidai da gama na NURUn itama Dan haka itama saitaje Las Vegas tayi shekara daya kafin suje University Dan Afia tafadawa dad dinta zata jira NURU tagama tadawo kafin suje University tare

Sanin irin shaquwan dake tsakaninsu musamman yanzu daya sanyata jerinsu ma'ana tamkar 'yarshi sai bai musa da hakanba ya amince Mata aka fara yiwa NURUn Shirin tafiya Las Vegas itama musamman gashi Imran yadan shiga damuwa na tafiyan Tata sbd tun ba'ayi nisaba NURU tafara cike dukkanin wasu matakanda cikakkiyar budurwa me daukan hankali zata cike to inaga taje tayi zaman kanta idanuwanta da kanta sun bude sbd rayuwace ta wayewa Dan gidan MALEEK ne dake Vegas din zata zauna itama kaman yanda Afia tayi zama itama.

NURU da farhat sunshiga damuwan kewan juna dazasuyi musamman farhat da komai NURU ke Mata ko dadynta Saida yayi aikin rarrashin kewar NURU da farhat dinsa zatayi.

##MAMUH##

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/8, 4:31 PM] Ummuanwar□: *_Mamuhgee 13_*

Las Vegas

Sabuwar rayuwarsa NURU Bata taba koda mafarkin samun yiba Koda kwatance itace take gudanarwa a Vegas sbd wani yalwataccen 'yanci da gata datake samu ta bangare biyu wato Imran da Kuma su afia da mahaifinsu Wanda shine ya dauki nauyin komai nata sbd 'yayansa.

Wata irin tsadaddiyar rayuwa takeyi a Vegas acikin lafiyayyan qaramin flat din maleek dake cikin wani babban building na masu Vegas da kanta.

2 bedrooms ne manya sosai agidan kowanne da toilet dinsa shima babba sai Palo 'daya da kitchen sai dining area shikenan,

Komai na gidan farine sai Yan abubuwa qalilan daba farare ba Dan kasancewar gidan Dan kuf kuf yasa bayada wani kadaici ko tsoron zama Kai daya saidai uban zallar dukiya da aka narka gurin gyaran gidan.

Tunda tazo bus takebi Bata taba amfani da motar da aka Bari Dan fitarsuba Dan tuqinta bai wani gama riqewaba Amma dai tsarin tuqin ne anan Bata ra'ayi tafison idan Takoma gida.

A school tunda tafara zuwa Bata samu matsalar karatun da mutanen makarantarba ko daya Dan haka saita maida hankali kawai tana karatun saikuma gyara jiki da harkan fashion da sabuwar qawarta 'yar Morocco take janta suna Dan fadawa ahankali ahankali.

Karatunta yayi nisa tagama gane kan farin Vegas Dan haka saita saje Takoma tamkar wata baturiyar qasar danma banbancin ita haryanxu kusan fiyeda Rabin suturarta sunanan jallabiyane saidai mafi yawanci na Turkish da Kuwait ne tafisonsu sbd mayafansu daurawa takeyi kaman scarf bata yafawa sai jeans da riguna masu har qasa Amma masu tsaga Suma da scarf take sanyasu sai handbags takarmanta Kuma mafi yawansu loafers ne masu tsada saidai Kuma yanxu tana Sanya heels musamman idan tasaka Kuwait gown.

Yau a gajiye tadawo gida tana waya da Afia taqarasa shiga cikin palon tareda rufo qofa ta wuce bedroom dinda yake nasu Dan dayan ko key dinsa Babu a gidan sbd ba'a shigarsa shiyasa ko bakin gurin qofar Bata taba zuwaba.

Ajiye Jakarta tayi tareda waya ta tube tafada toilet tayi wanka da ruwa me zafi Sosai jikinta ya saki ta fito tanajin wata irin yunwa Kuma.

Neutrogena oil kawai tashafa ajikinta sai body mist ta Sanya straight English riga Mara nauyi wadda ta zaune daidai fadin jikinta daga sama har qasa ta Sanya qaramar hula bayan tayi sallolinda bataiba tana gamawa ta miqe tareda zaran wayarta ta fito Palo ta aje wayar kan kujera ta nufi fridge Dan dauko drink da biscuits koshi tafara ci kafin ta Dan dafa ko noodles taci Dan batada qarfi ko kadan tana buqatan qarfin dahuwar noodles din Dan tun safe bataci komaiba.

A kujera tazo ta zauna tareda daukan remote ta kunna tv ta Nemo tashar cwtv Ana wani American series the arrow.

Tana fara ci tagyara zama kenan taji doorbell din yayi ringing ta fara kallon agogo kafin ta kalla qofar ta ajiye cup din hannunta tareda Miqewa ta nufi qofar tana tauna sauran biscuit din dake bakinta ta bude qofar Kai tsaye.

Mr Omar ne a tsaye riqeda wata qaramar brief case da wata luggage qarama

Cikeda mamaki ta saki murmushin farin cikin ganinsa Dan bayan Imran Babu Wanda yataba kawo Mata ziyara daga gida cikin muryarta me Dadi da sakewa tace"

Mr Omar you.....Bata qarasaba qamshin da zuwa yanzu tagama sani da tabbarwa Kona wanene taji ya doshi hancinta Yana shiga take ta hadiye sauran maganar tana kallon bayan Mr Omar.

MALEEK ne sanye cikin Louis Vuitton suits dark blue as usual,

Sai waya dake kunnensa Wanda alamu ya nuna da mahaifiyarsa yake mgn sbd yare dayakeyi Wanda sautin muryarsa daya kusa sumar da ita sbd tsoro da nutsuwar dake cikin muryar tareda wata irin kamewa Dan yaune Rana ta farko datake Jin muryarsa Kai tsaye Yana magana.

Daburcewa tayi tareda tsorata tashiga hankalinta sosai tareda rabewa gefe tana kame jikinta musamman kayan dake jikinta hakama kanta duk rabi a bayyane.

Mr Omar yariga yasan wacece ita ma'ana matsayinta na negestatin MALEEK Dan haka ko gangancin dagowa yayi Mata ko kallo daya baiyiba Dan sanin babban laifin aikata hakan musamman a irin yanayin datake damashi ko acan gida baya iya dagowa ya kalleta sbd sanin laifine hakan su sauran tunda Basu saniba nasu me sauqine.

Kai tsaye MALEEK yashigo har lokacin waya yakeyi Dan haka ko lura da ita baiyiba bare yaji gaisuwarta ya wuce ciki Kai tsaye har lokacin itadai kanta na qasa kirjinta na dokawa da qarfi qarfi

Mr Omar ne yamiqa Mata waya batareda ya kalletaba kansa a qasa Yana cewa"

Jekadi ce akan wayar.

Karba tayi jikinta amatuqar sanyaye ta Dora wayan a kunnenta tareda miqawa jekadi da gaisuwar"

Barka da yau jekadi.

Barkanki da yau Allah yaqara Miki lafiya da kyau da Nisan kwana NURULHUDA.

Tsit tayi tana sauraron jekadin sbd zuwa yanzu kusan tasaba da kirari da irin gaishe gaishen da jekadi ke Mata Wanda ta dauka hakan amatsayin 'dan wani girma daya shafeta na 'yayan MALEEK su AFIA datake taredasu musamman dayake itama da sunan ake Mata amfani a makaranta wanda da farko ko a makaranta aka Kira sunan tsoro kamata yakeyi hartazo tadan saba Amma duk da hakan har yau har gobe idan aka kirata da NURU MALEEK sai gabanta ya Fadi.

MALEEK yazo wani mahimman taron dare da zasuyi da wasu abokanan huldansa masu mahimmanci Dan haka kinsa Babu masu hidimarsa anan kece zakiji da komai musamman yanzu da dakinsa ke buqatan gyara kasancewan yadan Kwana biyu bai ziyarci farin ba Dan haka ki gyara komai atsarin yanda yakeson komai kada kiyi kuskure ki kiyaye.

Bakinta yayi nauyinda bazata iya magana ba saidai Kai kawai ta daga tareda miqawa Mr Omar wayarsa ta juya ya biyota abaya ya ajiye kayan hannunsa ya juya ya fice bayan yace Mata idan MALEEK ya nemesa Yana can qasa a mota ya ciro key card na bude master bedroom din maleek yaja qofar ya fice.

MALEEK na balcony din dayake fes fes tsare dawasu lallausan kujeru guda biyu da table a tsakiya sai glass door din dayake Hana iska shigowa ya damesu kullum acan take karatu itama Dan haka gurin agidan ma kaman yafi samun gyara sbd ko Imran yazo anan suke fira harya tafi nada gidan.

Ganin Yana can ta dauki jakukunanda mr Omar ya ajiye ta nufi dakin da sai yanxu ta fahimci nasa ne ta Dora card din budewa akan qofar dakin ta bude.

Ahankali ta tura zuciyarta da qafafunta tareda hannuwanta Babu Wanda baya rawa sbd daburcen datake.

Girman dakin da makeken royal bed din dake ciki me wata irin transparent labule fari tas data zagaye gadon tayanda bazaka baccinsa ba saidai inuwarsa idan Yana ciki.

Mirror dinsa tamaida ido akai girmansa yasata juyowa gaba daya tana kallon kanta aciki ta yanda take firgice.

Komai na dakin fari ne shima Kuma komai tsaf tsaf yake ba wata qura sbd ba gurin shigowarta kamar dai akwai mutum aciki kullum.

Qamshinsa ne dai wadda tafara haddacewa sbd tsoro shine yake tashi takowane lungu da saqo na dakin.

Cikin sauri da gaggawa tahau aikin daya shigo da ita take ta gyare komai tsaf tareda wanke toilet ta goge ta kunna AC da turaren daki dake fita ahankali sbd Bata budeshi duka ba kadan ta bude ta yanda kamshin zaifi bada nutsuwa sbd kadan kadan yake fita Kuma saiya Jima kafin ya feso kadan din.

Gadonsa ne kawai batayi gangancin ko tabawa ba sbd sanin hukuncin laifin hakan Dan ko yau da a delah ne ko gizah Allah ne kawai yasani idan zataga safiyar gobe sbd mugun babban laifine ganin makwancin asalin jinin DELAH bare MALEEK guda matuqar ba negestatinsu ba ko matayensu Suma sbd sune abokanan kwanciyar tasu Dan haka kallo daya tayiwa gefen gadon Bata kumaba harta gama ta fice dakin zuciyarta na sake shiga rudu.

Tana fitowa palon tahau tattare kayan biscuits da drink dinda takeci tayi kicin dasu tasake tattara palon ta gyara hakama cikin take tahau gyaransa takuma Dora Masa abincin daren dazaici.

Sanin kalolin abincin dayakeci yasata hada Masa gasashen flat bread da boiled veggies aciki sai ruwan lemon tea masu zafi da qamshin lemon leafs da ginger takawo dining ta jera ta bar palon gabaki daya ta shige daki ta rufo Dan batasaka ran zata sake dogon motsiba a gidan har gari ya waye yatafi.

Yakai mintuna talatin Yana wayar dayake Yi kafin ya kammala tareda kashe wayar gabaki daya ya nufi hanyar master bedroom dinsa dinsa yashige Kai tsaye tareda rufowa.

Wayar hannunsa ya ajiye gaban mirror ya nufi closet dinsa ya rage kayan jikinsa duka ya daura brown towel a qugunsa lafiyayyan fatarsa da hutu da kulawa yagama bayyana atareda ita Kamar ta sabon saurayi me sabon jini ajika.

Babban toilet dinsa daya kusa girman dakuna biyu yashige.

Bayan fitowarsa yayi duk abinda zaiyi ya Sanya fararen kayan bacci masu Dan kauri na _roughbay_ da socks din sanyi a qafafuwansa yazuro slippers yafito dining tea din kawai yasha sai rolled flat bread din guda daya yasha ruwa kadan ya koma daki yayi brush ya kwanta tareda Jan duvet cover take qura ta Dan tashi sbd Bata taba komaiba na gadon bare kakkabewa da sauya su bedcovers.

Muguwar shaqa yayiwa kurar wadda zai iya cewa tun Yana yaro rabonsa da shaqar Kura irin hakan sbd mummunan attack din datake basa take yafara tari ahankali ahankali Yana rufe hancinsa da bakinsa ya yaye bargon gaba daya Wanda yasa qurar sake tashi take tarinsa yafara qarfi idanuwansa na fara sauyawa ya sauko da qyar numfashinsa na sauyawa da sassarqewa ya isa gaban mirror ya lalubo wayarsa ya kunna zuwa lokacin yafara samun attack Dan kuwa numfashi yafara dauke Masa Kiran Mr Omar ya Danna daqyar ya iya furta"

My inhaler.....

Yana fadar hakan ya saki wayar Yana durqushewa agurin cikin tsananin azabar toshewar numfashi da wani irin zufan wahala daya jiqasa cikin qanqanin lokaci.

Mr Omar najin muryar MALEEK da abinda yafada yasan attack ne zai samu a rikice yabude inda ake aje inhalers dinsa cikin duka motocin dayake hawa ya ciro jikinsa har wani rawa yakeyi da gudu ya nufo ciki tsabar sauri da rikicewa ko lift kasa tsayawa shiga yayi ta staircase yabiyo Yana hada stairs uku uku gurin hayewa.

Danna doorbell yake ba kakkautawa Wanda yasa NURU dake waya da Imran akewa ba shiri ta fito sbd gudun 'karar ta damu MALEEK.

Kayan bacci ne ajikinta qaramin guntun wando da rigarsa Mara hannu Dan haka saita sanyo doguwar kimono akai ta riqe gaban ta fito da sauri ta bude tana cewa"

Please stop ringing the bell Ina zuwa.

Tana budewa taga mr Omar ciki mamaki take kallonsa kafin tayi mgn ya dunguro Mata inhaler din cikin gaggawa yace"

MALEEK yasamu attack na asthma kiyi sauri ki Kai Masa idan yayi nisa ki shaqa Masa please go go go fast.

Karba tayi ta juya arude sbd ita duk Mr Omar dinne ya rudata ta yanda yake maganar dukkanin jikinsa na wani irin rawa ga tsoron shiga dakin na MALEEK Yana ciki Amma haka ta Isa arikice ta bude tashige qofar na rufewa shima Mr Omar Jan qofar yayi yakoma gefen qofar shiga palon ya dasa sabon zama.

Tana shiga yana qoqarin zubewa kwance batasan lokacinda ta qarasa da sauri ba cikin tsoro da rudewa ta tarosa dayake batada kauri sosai da qarfinda zata iya taresa musamman da jikinsa yariga yasaki sai takasa suka zube kan gadonsa gabaki daya.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU

0903 234 5899

[9/8, 4:31 PM] Ummuanwar: *_Mamuhgee 14_*

Kokuwar tashi takeyi daga kan gadon dukkanin jikinta rawa yake sosai sbd tsananin tsoro da tashin hankali tareda ma firgici duk ta gama rudewa Amma sbd jikinsa yasaki gabaki daya ko kadan takasa motsashi daga jikinta sai numfashinsa dake qoqarin barin qirjinsa da sauri ta lalubo inhaler din dake hannunta ta dago kansa daga qirjinta dake harbawa ta Dora cikin bakinsa ta Danna harso biyu zuwa uku taga kaman Yana responding saita sake daddannawa tana shafa bayansa ahankali kaman yanda takewa farhat tana dan hura Masa iskan bakinta a fuska har lokacin jikinta rawa yake sosai sbd fadar tsoron datake ciki baya misaltuwa ganinta kwance kan gadon da za'a iya raba gangar jikinta da kanta akan laifin hakan.

Wata irin rawa jikinsa ya dauka kamar Yana fizga sosai Sosai take hankalinta yayi mummunan tashi ta turesa gefe daqyar daga kanta ta tashi zaune tana gyara Masa kwanciya hannuwanta na rawa ta fara Kiran sunansa da DADDY cikin masifaffen tashin hankali ganin Yana jijjiga da qarfi.

Da gudu ta sauko gadon tana wurgi da kimonon jikinta ta fita da mugun gudu ta dauko wayarta hannunta na rawa daqyar ta iya riqe wayar ta Nemo sunan Dr Damien ta Danna Masa Kira tana dawowa dakin da gudu cikin firgici take koro Masa bayani muryanta na rawa tuni zufa yayi Mata sharkaf.

Cikin son Samar Mata nutsuwa Dan ta fahimci bayaninsa yace"

Ki kwantar da hankalinki please ki fahimci abinda zanfada miki.

Jijjiga Kai tayi tana saurarensa cikin qaguwa tana sake hada zufan tashin hankali ko qarasa sauran bayanin baigama yiba tayi cilli da wayar ta nufi gaban madubi tafara dudduba allaurar da Dr Damien din yace

Bata ganiba tahau bubbude drowers cikin tashin hankali take na rashin ganin allaurar

Tayo gurin luggage dinsa ta bude tahau yamutsawa cikin sauri da tashin hankali cikin sa'a kuwa ta ganta da sauri tayo kansa tana zuwa kaman yanda Dr yace tayi ta Zuqa Masa allurar take yasaki wani wahalalle numfashi dukkanin jikinsa na sakewa numfashinsa ya tsaya cak ya daina motsi.

Dauke wuta tayi itama ganin baya numfashi baya motsi a kidime ta haura gadon ta taba kirjinsa taji baya bugawa ta Dora kunnenta kan kirjin nanma taji tsit a haukace ta daga qafafunsa ta Dora kan cinyarta ta zare Masa safunan qafan tasaka tafin hannunta tana gogawa da qarfi tanayi tana kallonsa adduo a bakinta har batasan wainda takeyiba

Ahankali ahankali taga numfashinsa yafara dawowa ahankali

Wata irin wahalalliyar ajiyar Zuciya tasake sai alokacin hawaye suka gangaro Mata har batasan lokacinda ta qanqame qafafuwansa dake kan cinyartaba tana sake kukan tsananin tsoro da ace wani abu yasamesa Yaya zatayi?

Me za'ace?

Me 'yayansa zasuce?

Ta Jima ahaka tana kukan kubuta daga muguwar masifar data tashi afkowa zuriarta gabaki daya kafin ta Dan dago ta kallesa da jajayen idanuwanta taga yanzu Kam numfashinsa yagama daidaituwa Amma bai tashiba sai hakan yasakata Jin shakka ta gyarawa dogayen qafafuwansa zama akan cinyoyinta dake filin Allah,

Jikinta daya gama daukan dumin tashin hankali yafara shiga qafafunsa gakuma tafin qafafunsa datake gogawa da tafin hannunta 'Dan dumi yaringa shigar qafafunsa yasashi motsawa ahankali a wahalce batareda ya bude idanuwansa ba

Itakuma taci gaba da gogawa Wanda Dole yasashi bude idanuwansa dasukai ja a wahalce ya kalleta daqyar ya maida idonuwan ya rufe Yana sauke wani numfashin me fitarda siririn sauti.

Bata ankara daya Dan farfado ba taci gaba da goga Masa tafin qafafun

Ya sake bude idanuwansa a wahalce yanason cewa ta daina ya kasa sbd hakan datake Yana Masa wani iri temperature dinsa tana hayewa sama Amma yakasa mgn sai kawai ya maida idonuwan ya rufe bacci ya daukesa me qarfi a wahalce.

Qarfe bakwai na safe yabude idanuwansa ahankali Yana furta sunayen Allah da adduar tashi bacci cikin zuciyarsa,

Motsawa yayi ahankali tareda yunqurawa zai tashi zaune yaji qafafuwansa a riqe ya Kai idanuwansa zuwa gabansa yaganta kwance rungume da qafafuwansa baccin wahala ya dauketa.

Kallo daya yayi Mata ya dauke idanuwansa daga gurin Yana zame qafafuwansa ya zuro qasa tareda yaye labulen makeken gadon ya fito Yana tafiya ahankali duk da garau yake Jin kansa ba damuwar ciwo ko daya Amma akwai rashin qarfin jiki ya nufi toilet yashige.

Harya fito tana baccin Bata farkaba Dan haka Kai tsaye ya shirya cikin Ash Armani's ya fesa turarensa na imperial majesty rosalle ya saka takalmin _manolo blahnik_ ya fice Kai tsaye Yana kunna wayarsa ya Kira mr Omar daya kwana zaune zaman jiran yazata Kaya yana ganin Kiran maleek yayi wuf ya dauki Kiran a qage yace"

Good morning MALEEK.

Ka kunna mota ganinan fitowa.

Da gudu mr Omar ya sauko ya nufi mota yashiga ya kunna da sauri tareda gyara parking yayi saiti daidai kofarda maleek din zai fito

MALEEK din nafitowa ya bude Masa yashiga ya rufe ya zagaya da sauri yashiga suka wuce.

Qarfe Tara da mintuna ta bude idanuwanta dasukai mugun nauyi sbd kukan datasha dakuma bacci

Tafara jujjuya idanuwan taga inda take a zabure ta miqe jikinta na rawa ta wuntsulo qasa tana kallon gadon taga bayanan da sauri ta fito cikin gadon har tana tuntube ta fice ko ganin gabanta batayi Takoma dakinta jikinta na rawa.

Daqyar ta nutsar da kanta Dan yin sallah tayo alwala tazo tayi sallah zuciyarta na harbawa da qarfi

Kallo daya zakai Mata kasan a firgice take takasa samun nutsuwa tana zaune a daki tana tunane tunane har kusan 12 tayi Dole ta fito Takoma dakin ta dauko wayarta sai alokacin taga misscals din Imran da text din Mr Omar na cewan sun wuce komawa Paris MALEEK zaiga likita.

Ajiyar zuciya ta sauke duk da bawai tasamu nutsuwa bane dajin hakan sbd ita yanzu qaddarorinta yawane dasu yanzu dame zata Kira qaddarar datakaita hawa gadon MALEEK na DELAH Giza Wanda ko 'yayan sarauta bila adadin ba kowane yaga ko gurin zaman Shan iskansaba gata tsautsayi da qaddara yasata ganin makwancinsa dako 'yayan cikinsa Basu taba ganiba Dan daga afia har Farhat Babu Wanda yataba shiga bedroom dinsa nako Ina Bare suka shimfidar kwanciyarsa.

Kiran Imran ne ya katse damuwarta da tunaninta sbd rashin daukan wayanta tun jiyan yasashi shiga damuwa Dole ta Dan sake suka hau magana sama sama qarshe dai Dole hakura yayi da wayar akan tayi bacci ta huta zai kirata zuwa anjima danma Bata fada Masa abinda yafaru ba bakuma tajin zata taba iya fadawa kowa har abada.

Wanka tayi sai alokacin yunwar dake cikinta tun ta jiyan ta taso Mata ta nufa kicin ta dumama sauran abincin dabaiciba jiyan taci Tasha orange juice Takoma daki sai alokacin takira Afia suka hau fira itama sama sama harsaida afian tagane tace"

NURU are you sure you're okay???

Numfashi ta sauke kafin tace"

Eh kawai ciwon Kai ne ke 'dan damuna shima sbd I didn't sleep well last night ne.

Ok tom kiyi bacci yanzu Koda na 1 hour ne you'll feel good inshallah.

Aje wayar sukai ta kwanta Dan tasamu tayi baccin Amma Sam takasa har lokacin zuciyarta Bata cikin Dadi qarshe jekadi ta Kira taji lafiyan iyayenta tukuna ma tasamu ta 'dan rintsa baccin ya dauketa.

Bata farka ba sai yamma tana tashi wanka tayi tayi sallolinta ta Sanya riga da guntun wandon jeans baqi ta fito ta dafa kwai da farar noodles taci Tasha ruwa ta dauko ledar crunchy chips chops tazo ta zauna kallo tana ci saiga Kiran Afia ta dauka Nan suka hau waya yanzu cikin sakewa Dan baccin ya taimaketa sosai.

Karatunta yadau zafi sbd tafara exams din kammalawa shiyasa yanzu batada wani lokaci sosai karatu ne a kanta ko lokacin fira ta waya batadashi Dan wani lokacin wayar a kashe take yini saitazo kwanciya ta kunna da afia kawai take waya kafin takuma maidawa ta kashe ahaka ta gama exams dinta kwana uku ta qara akai ta tattaro tadawo gida ranar murna da farin cikin farhat Bata misaltuwa hakama afia datai tsananin kewan NURUn kusan daima kowa yayi kewarta shiyasa ranar gidan kaf acikin walwala suke Dan Jin suke kamar rayuwar gidan tadawo sbd AFIA ko yaushe tana library gurin karatun batada lokacin kowa na gidan

Farhat ma haka take turata daki tace taje tayi karatu itakuma NURU tana shiga cikinsu tayi aiki harma tayi Wasa da dariya dasu uwa uba idan ta biyewa farhat gurin wasan yara na guje guje ko qasa a playground na gidan Wanda ka zuba komai na wasan yara domin farhat Wanda ita kanta farhat yanzu take morewa playground din data samu abokiyar dake tayata shiriritarta shiyasa yanzu batada kaman NURUnta.

Hutun sati biyu kawai NURU tayi Mr Omar ya kammala komai na karatunsu dazasu fara yanzu na cikan burirrikansu,

NURU lawyer itakuma AFIA likitanci.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

_Mabudin zuciya--HAFSAT

RANO_

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899*_Mamuhgee 15_*

Mg's skincare

Hi my people♀

Ina gaisuwa

Toh albishirinku□ku karkade kunnuwanku kuji inamai sanarmaku cewa set dinmu ayanzu yazama available maiso yarugo aguje karya tsaya Sanya ayi babushi☺ kundaisan kayan *mg's* dabanne ba karya indai tafannin gyaran jikine kunsan yanda sabulun mg's herbal whitening black soap kemaida fata tazama Babu kuraje, pimples, acne,eczema, stretch mark, knuckles,black head,spot,dama duk wani matsala daya danganci fata duk wnd yayi anfani dashi yasan yanda yake maida jiki yazama abun burgewa abun kwatance, fata tadinga haskawa tana walwali duk inda kikashiga sai anyaba😍 toh Inaga wannan zazzafan set Mai maida tsohuwa yarinya ☺Uwargida Takoma amarya😁 amarya Takoma tamkar yanmata❤yanmata Kuma sudawo Yan Sha shida fata tadinga walwali tana daukan Ido ☺ wani abun ba'a magana shiru akeyi sai Wanda yajaraba shine zai karas😘bama cika Baki duk wnd yagwada shine zaifadi ynd product din mg's yake❤Kuma munakara Fadi cewa kayanmu organic ne bana bleaching ba suna tsagwaran gyaranjiki ne fiye da tunaninku kuyi kokari kushigo Kuma adama daku Wanda bayada halin siyan set toh sabulun mg's kadai kukarike kankat ne insha Allah□

Set dinmu yakunshi

Soap,body cream,face cream,body nd face scrub, cleanser,

Price:13k

Kaman ynd nafadi Wanda bazasu iyasiya set ba sabulun kadai zaibaku mamaki shikadai kukayi anfanidashi zaigoge duk wn prblm na skin living the skin fresh,smooth nd make the skin to glow set din kawai zaikara murje fatane buh ko soap mutum yake anfani dashi ba'a magana□

Soap price:3k

Mai bukatan Kaya should chat:08062991549

Call:08064532391

To plc ur order

Munada komai available now so hurry nd grb urs before you hear sold out

Karkubari abarku abaya ko abaku lbr domin kynm yanagyara ko fatan d Mai yabata komutum bashida komai zai iya using kayan zaisa jikin k yafidda wn kyau medaukan hnkl duk inda kikayi se ankalla,show ur skin some luv domin mata da gyara akasanmu😉just gv it a try nd ur skin will definitely/forever thank you❤

Mn Kaya kowani gari buh delivery is not free

Team glow♀

****

Sunfara karatunsu hankali kwance saidai NURU da hidima takeson Mata yawa yanxu Dan karatun nasu duk me zafi ne Amma ita ga hidimar kula da farhat da lalurorinta gakuma na gidan Dan yanxu tasaba sosai take saka hannu a aikin kigan musamman ma abinci sbd ko su afia da farhat sunfi Jin dadin cin nata hakama dad dinsu duk da kaman canke ne sukayi kaman yafi ci sosai idan tayi din saiya kasance kobatayi kullum idan Yana gari ita keyi.

Ta bangaren Imran jalal kuwa yanzu soyayya suke gudanarwa afili cikin kwanciyar hankali musamman yanzu daya tabbatarda yagama dasa soyayyarsa a zuciyarta Dan haka yake biyeda ita kaman jela Dan kusan koyaushe Yana gurin daukota daga makaranta kokuma Yana gidan firar yamma,

Yan gidan kaf yanzu kowa yasan menene a tsakaninsa da NURU musamman daya fara kawo Mata maganar aure Dan shi Sam Jin yake kaman soyayyarsu na buqatan kiyayewan tsaro bayason wasa wani Abu ya gitta so yake kawai suyi aure tazama tashi daganan ne kawai zaijisa hankali kwance shiyasa ya takura Mata da maganar auren.

Juyowa yayi daga tuqin dayake ya 'dan kalleta da fararen idanuwansa cikin sauti me bayyanarda Sonta dake mamaye dashi yace"

Beauty yau MALEEK zai Paris gobe da safe zanshigo zamuyi maganar wasu takardun contract dinmu idan mungama zanmasa maganar zuwa neman aurenki gaskia bazan iya cigaba da jira ba is high time ace komai namu yazama dahir ma'ana samun tabbacin zamowanki matata shine agabana komai baya gabana yanzu kamar wannan.

Tunda yayi maganar zai fadawa MALEEK zancen neman aurenta gabanta yayi mummunan faduwa ta dago da sauri ta zuba Masa manyan fararen idanuwanta tareda fadawa cikin tunani me qarfi da firgici.

Wane irin sarkakiya rayuwarta take cikine?

Menene matsayar rayuwarta gabaki daya yanzu sbd batasan menene sunan dazata alaqanta kanta dashiba adaidai yanzu.

Har suka Isa gida batasaniba sbd tunani da tsoro me qarfi da zancen Imran din ya tado Mata.

Kiran sunanta yayi Yana kallonta gabaki daya sbd tayi nisa a tunani batasan sunfi mintuna biyar zuwa shida da isowa gidanba.

Sake Kiran sunanta yayi Yana cewa"

Are you ok?

Waiwayowa tayi dukkanin jikinta a matuqar sanyaye ta kallesa ta gyada Masa Kai batareda ta iya bude Baki tayi maganaba

Zai sake mgna ta bude kofar motar ta fice daukeda handbag dinta da wayarta a hannu.

Bin bayanta yayi da kallo cikin 'yar damuwar sauyawarta atake cikin motar.

Baishigoba sbd a yanda take dinnan bazai samu damar ta kulashiba yanda yakamata sai kawai ya tada motar ya juya ya fice daga gate din gidan ya wuce.

A palon ciki ta tararda farhat na kallon cartoon ta taso da gudu ta fado jikinta tana Mata sannu da zuwa

Qaqalo murmushi tayi ta shafa kanta tana cewa"

Sweetie Aunt NURU batajin Dadi kanta na ciwo zanje na huta ko.

O o sorry aunt.

Gyada Kai tayi tareda sake shafa fuskan farhat din tana wucewa zuwa daki sbd AFIA Bata dawoba sai zuwa yamma.

Tana zuwa daki ta zube kan kujera tareda watsarda Jakarta da wayarta kan daya kujeran tana dafe goshinta tareda rintse ido tana.

Ta Jima ahakan cikin tunani me zurfi har wani wahalallen bacci ya dauketa Bata farkaba sai yamma da Afia tashigo.

Tashi zaune tayi kanta na tsananin sarawa ta miqe tsaye ta nufi closet ta tube ta shige toilet.

Wanka tayi tareda alwala ta fito ta shirya cikin doguwar Bahrain gown mara adon komai Mara nauyima kwata kwata,ta nada mayafi ta tada sallah.

Bayan tagama sallolinta miqewa tayi ta nufi kicin Dan aikin abincin dare sbd Imran yace yau dad dinsu afia zai dawo.

Acikin sanyi takeyin komai sbd rashin walwalar datake ciki na dawo da ita tunaninta da Imran yayi Dan kuwa Dole wata Rana duk cigaban rayuwar dazata samu saita dawo inda asalin rayuwarta take tsaye wato baiwa Kuma negestati.

Meyasa ta shagala hartaso manta wacece ita?

Ta Yaya zatai aure bayan batada wannan damar ko ikon,

Shin ita ayanzu ma menene matsayinta a masarautar delah?

Menene sunanta anan gidan? Yar aiki kokuwa me Reno kokuwa me debewa 'yan gida kewa.

Tayaya Imran zai mallaketa amatsayin matarsa bayan ita din negestatin wani ce Wanda haryanzu batamasan ko wayeba.

Ta Yaya zata Bari Imran yayi maganar aurenta gurin maleek bayan tasan hakan bame yiyuwa bane.

Kammala komai tayi ta diba nata ta jera a tray ta fice daga kicin din tabarwa Fana ta jeresu a dining.

Koda taje daki ta aje abincin tafaraci tana amsawa afia firarta sama sama

Dataga ma ba iyacin abincin zatayiba saita shanye drink din kawai ta bar abincin.

bayan sallar magriba motar data dauko MALEEK daga airport tana shigowa gidan su Kuma lokacin sun gama sallolinsu suna zaune a Palo na biyu farhat na kwance jikinta tana kallon cartoon AFIA Kuma na gefensu itama riqeda wani hardcover t book tana karantawa ita Kuma NURUn tayi nisa sosai a tunanin abinda yake damunta hankalinta gabaki daya yabar jikinta zaune kawai take.

Karan doorbell yasa AFIA kallon farhat sbd sanin Babu masu aiki ko daya yanzu a part din lokacin shigewarsu yayi sun koma part din masu aiki saikuma gobe tace"

Farhat kije ki bude kofa I think Imran ne yazo yanzu.

Sunan Imran din da AFIA ta fada yasata dawowa hankalinta ta juya a hankali ta kalli afia murya a Sanyaye tace"

Kina magana ne?

Batareda ta juyoba hankalinta na kan littafin datake karatu ita afian tace"

Eh inaga Imran Yana bakin qofane doorbell Yana qara.

Kallon hanyar fita palon zuwa palon farko NURU tayi cikin nazari saidai Kuma dama tasan zaiyi wuya Imran din yaqi dawowa yau din sbd sauyin daya gani tattareda ita dakuma nacinsa akan maganar aurensu.

Zame farhat tayi daga jikinta tareda Miqewa tsaye ta nufi daki ta doro qaramin mayafin doguwar riga akan kayan jikinta ta fito ta nufi qofa ta budu Kai tsaye tareda bude Baki zatai mgnar idanuwanta suka sauka kan Mr Omar dake Danna doorbell din gabanta yayi mummunan faduwa ta saci kallon bayansa daidai isowar MALEEK din sai Imran a bayansa Wanda da gani shima isowarsa kenen mr Omar ya juya da sauri yabar gurin ganin MALEEK ya qaraso,

Take taji qafafunta na neman Gaza daukarta tayi saurin kaucewa daga bakin qofar tana sauke kanta sbd wani irin kwarjini da cika Mata idanuwa dayayi saikuma shedan dake dawo Mata da tunanin abinda yafaru dasu a Vegas sai kunyar al'amarin na bayyanuwa atareda ita Wanda yasata dagowa ahankali ta sake kallonsa daidai kawowarsa daf da ita idanuwanta suka hadu da nasa idanuwan dasuka kusa sata zubewa agurin batasan lokacinda ta bude bakiba da siririyar muryarta tace"

Barka da dawowa.

Akaron farko daya bude Baki ya amsa Mata da"

Yawwa.

Gabaki daya Jin tayi tana neman rikicewa har batasan lokacinda ta rufe qofa da qarfiba Wanda ta daki hancin Imran daya fara shigowaba da qarfi har baisan sanda ya saki qara me qarfiba wadda tasata dawowa hayyacinta da sauri ta bude qofar cikin damuwa da kulawa tayi kansa tana cewa"

Oh my God, I'm so sorry Im banluraba na manta kana baya, please let me take a look"" tafada tana duba hancinsa da harya fara ja abinka da farin mutum ga idanuwansa tuni suka cicciko da ruwa sbd hancin daya bugu sosai.

Rufe hancin yayi Yana cewa"

No karki damu ba wani matsala bane buguwane kawai.

Im dan Allah kayi hakuri bansan meyake damunaba bansan tunanin me nakeba.

Shihhhh ya isa haka just relax sweetheart am fine

Duba kiga hancinma ya sauka.

Fuskar tausayi tayi tana sake kallonsa da alamar ban hkr tace"

Shigo ciki na dauko ointment sai a shafa agurin.

Ki barshi zanje gida zanshafa idan naje gidan kishiga gobe zandawo da safe dama nazo Naga ko kina lafiyane kishiga ciki Saida safe.

Im you sure you're ok??tafada tana kallonsa.

Murmushi yasakar Mata Yana cewa"

See you tomorrow.""ya wuce.

Saidataga tashin motarsa kafin ta sauke numfashi Mara sauti ta juyo ciki ta rufe kofa tanajin ba Dadi cikin ranta.

Hanyar kicin ta nufa Dan daukan ruwa tana kaiwa dining room ga tarin dibbin mamakinta saitaga maleek zaune akan dining da kayan daya shigo dasu Wanda ke nuni da kaman tunda yashigo Yana gurin bai qarasa samanshi ba kenan ko su afia Basu San da dawowarshiba.

Fatar wuyansa dake sheqi take kallo har zuwa hannayensa data tuno tsananin laushin dasukedashi da sauri ta Kori shedan tareda juyawa zatabar gurin kamar daga sama taji muryarsa me kamewa yace"

Serve me.

Tsayawa tayi cak daga inda take tsaye sbd Bata taba tunanin yasan da tsayuwarta a gurinba,

saidata sauke numfashi ta daidaita nustuwarta kafin ta juyo cikin nutsuwa ta qaraso gabansa a ladabce tasake bude Baki tace"

Barka da fitowa.

Bai amsaba sbd fuskarsa dake kame

Ta matso sosai tareda fara bubbude abincin ta zuba Masa Kamar yanda ta kwatanci zaici ta juya zuwa kicin ta bude fridge ta dauko qaton royal silver jug na fresh fruit juice ta kawo daidai fitowar farhat data biyo bayan NURUn ganin ta dade Bata dawoba daga bude kofar sbd matuqar NURU na gida Bata iya dadewa ba ajikintaba.

Ta kofar Palo ta hango dad dinsu a dining zaune cikin tsananin farin ciki ta qaraso da gudu tana cewa"

AFIA Daddy is back.

Qarasowanta da gudu yayi daidai da tsayuwan NURU a gefensa Dan zuba Masa juice ta fada jikin NURUn da qarfi wadda dama ita kuma ta fada jikinsa gabaki

dayanta har ita har jug din juice din daya zube ajikinsu duk su biyun da sauri ta dago ta kalli fuskarsa da idanuwansa suka sauya launi ta kalli kanta datake zaune dare dare kan cinyoyinsa fuskarta da tashi na tsiyayan ruwan juice a rude batama saniba tsaban firgici ta zame qaramin gyalen kanta takai fuskarsa zata goge ya kauce fuskan sai hankalinta yayi mummunan tashi ta sakata tafin hannuwanta masu wani irin taushi ta Dora kan fuskarsa tahau gogewa arude jikinta na rawa Kuma har lokacin tana kan cinyarta.

Ahankali ya bude idanuwansa masu sake rudata ya zubawa hannayenta ya dauke Kai tareda sake kame fuskarsa ya dago hannayensa duka biyun zai janye jikinsa kamar daga sama muryar AFIA ta sauka da cewa"

What's going on here????

Kallon tsananin mamaki da tsoro tareda firgici da rudewa take musu musamman NURUn dake zaune kan cinyar dad din.

A zabure NURU ta miqe jikinta har Yana rawa ta kalli afia batasan lokacinda ta qaraso gabanta ba tana cewa"

Juice ne farhat ta turo ya zube.

Kota kansu baibiba ya miqe yabar gurin gabaki daya Yana zare agogon hannunsa daya jiqe shima.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899*_Mamuhgee 17_*

*_Turare by awwaba_*

*Assalamu alaikum warahmatullah, shin kinaba amfani da turaren gashi a matsayinki na mace data amsa sunanta idan amsarki aa toga dama tasamu *awwaba scent* *tazomaku* *da turaren fesawa a gashi natural 100% organic *wanda akahada rose water da essential oils tripped action gashi yy kamshi yay kyali kuma moisturiser at *the same time ba anan abun yatsayaba duk wanda yy order zaahada masa da freshener kala hudu ta daki *ta bandaki ta Mopping da turaren wanka a kan kudi 3,000 kacal indai q cikin watan September dinnna ne daganan kuma zasukoma *normal price dinsu, hakanan turarukqn wuta da humra dinmu anyi masu ragi duk me bukata se nememu a 08034236800 ta what's app kokuma ya ziyarci shafinmu a instagram *@turare_by_awwaba mungode*

****

Washe gari tunda safe yasake dawowa gidan Dan ganawa da maleek Amma sbd rashin sa'a Koda yazo maleek din yafita haka ya juya jiki amace yakoma gida da niyar ya dawo anjima Dan Dole Dole tsakanin yau zuwa gobene damarsa ta qarshe ta ganawa da maleek sbd jibi Ana fara aikin Santiago Babu ranarda zai samu kansa harya samu damar magana dashi.

Ta bangaren NURU itama gabaki daya ta rasa sukuni da walwalarta akan zancen Dan ko abincin kirki tadaina ci kullum saidai tea sbd fargaba da tsoron abinda zai iya kaiwa ya komo

Duk yanda Afia tayi tayi da ita akan abinda yake faruwa takasa Mata bayani dataga kaman ran afian ya baci ne saita fada Mata da Imran nason turowane ita Kuma tana tsoron karatuntane kawai da haka afia ta zaunar da ita tabata wani qwarin gwiwan barin Imran din yayi zancen tahakane zataji idan abin me yiyuwa ne.

Hakan yasa tadan rage damuwar abin cikin ranta tafara jiran tsammani.

IMRAN kuwa Kai yayi mugun daukan zafi sbd duk wata hanyar dazai gana da maleek ta toshe har abin yafara bashi tsoro sai kawai ya yanke shawaran fadawa mahaifinsa Dan shi dakansa ya nema MALEEK din.

Zaune suke a dining suna dinner Kiran FORMER M.AMB JALALUDDEEN yashigo wayarsa yayiwa wayar kallo daya yaci gaba dacin abincinsa a natse harsaida yagama zuwa lokacin yayi Masa Kira kusan hudu sai Ana biyar din ya daga cikin kamewa da ikon sarauta dake yawo cikin jikinsa ya amsa sallamar M JALALUDDEEN suka gaisa a mutunce gaisuwa irinta dattijai manyan mutane kafin M JALALUDDEEN yafara da cewa"

MALEEK nayi kirane akan maganar aure da Imran yakeson yarinyar gurinka wadda yace sunriga sunfahimci juna sosai da ita to.....

Wata nutsatsiyar gyaran murya MALEEK yayi a natse wadda duk wanda yasan mulki da sarauta yasan dakatarwane ga zancen da ake Dan haka M JALALUDDEEN ya dakatar da abinda yake fada

Kai tsaye MALEEK cikin kamewar muryarsa me nuna isarsa yace"

Wannan maganar ba'ayin irinsa a waya.

Hakane tabbas Bata waya bace MALEEK to kabada lokacinda zamuzo sai ayi maganar akai qarshe Inshallah.

Kallon agogo yayi alamar zancen na shiga lokacinsa Dan haka Kai tsaye yace inada tafiya gizah agabana banida lokacin bayarwa idan nasamu time zangani Inshallah.

Daga haka sukai sallama Yana aje wayar AFIA dataji ya ambaci tafiya gizah hankalinta yayi mummunan tashi ta kallesa cikin son tabbatarwa tace"

Dad zakaje delah gizah??

Yana miqewa yace"

Eh Anneti tasamu attack na zuciya yau da safe.

Yana fadar hakan ya wuce gabaki daya.

Bin bayansa tayi da kallo zuciyarta na bugawa tana nanata zancen tafiyar.

Kasa yadda da tafiyar dad dinta zuciyarta tayi dari bisa dari sbd zuwansa zai iya kawo komai na lalacewan faranta da adduar datai shekaru tanayi na ganin dawowar iyayenta tare,

Shin Tata dad zaije delah gizah yanzu bayan zuwansa batareda matarsaba zai bayyanawa duniya cewan sun rabu Wanda hakan daidai yakeda rasa qimarsa da darajarsa hakama Kuma hakan zai jawo kokuma bada damar shigowar wata cikin rayuwar mahaifinsu ko Mata ko negestati.

Dafe kanta dake neman tarwatsewa sbd tsananin tarin damuwa data sawa kanta akan wani irin zazzafan kishi datake jiwa mahaifiyarta Dan haka bazata iya Bari dad yayi tafiyar Nan gizah ba sbd sanin tsananin qarfin iko da dokoki tareda al'adun mulkin irin na delah gizah.

NURU dake cikin Tata damuwar me nauyi tana zaune gefen AFIA din taji yanda takeda sauke ajiyar zuciya alaman Bata cikin kwanciyar hankali ko daya ta bude Baki ahankali cikin kulawa tace"

AFIA kinada damuwan wani abune?kimata sauke ajiyan zuciya.

Kasa waiwayowa tayi takalli NURUn sbd idanuwanta dasukai zuru zuru sbd masifar data sakawa ranta ta kishin mahaifinta ga wata mace

Batareda ta juyoba tace"

Bakomai kawai kaina na ciwo ne shima inaga sbd rashin bacci ne da bansamu nayiba jiyan.

Kafin NURU tayi magana ta miqe ta nufi toilet tashige ta rufo qofa.

Hawaye takeson Yi Amma ta daure tana kallon fuskarta cikin mirror ta rintse ido tana Jin shin mum dinta ta cancanci wannan fadan datake tare Mata kuwa?

Shin idan ta dage ta Hana dad dinta rayuwa da wata mace akan Taya mum dinta kishi tayi adalci a tsakaninsu kuwa bayan mum din itace ta lalata komai tayi watsi dasu ta tafi neman duniya wadda idan ba Allah yasoba har abada bazata samu duniya irinta dad dinsu ba.

Share hawayenta tayi tareda wanke fuskarta ta dauro alwalar azahar datai ta fito tana qoqarin sakewa Dan kawarda tambayoyin NURU akanta.

NURU dake binta da ido ganin babu damuwar komai a kan fuskan AFIA din sai tabar tamabayarta tana sauke numfashi Dan harta fara shiga tunanin kodai maganartane da Imran tazama matsala tunda tasanma kila zuwa yanzu yagama fadawa MALEEK komai.

Farhat ce tashigo daukeda littafi a hannunta tayo gurin NURU ta zauna kan cinyarta tana cewa"

Lewa nakasa gama wannan dubamin kigani.

Sallah Afia ta tayar tana dauke tunaninta daga kansu sbd Sam Babu Wanda zai gane abinda takeji.

Tana idar da sallar tadawo cikinsu suka cigaba da abinda sukeyi da ita Dan tasamu ta fitarda tunani da damuwardake azalzalar ranta.

Har dare tana sintirin yawo tsakanin Palo da 'dakinsu akai akai sbd tanason ganin dad dinta akan ko tafiyarsa delah gizah na Nan.

Har suka kwanta Bata samu ganin dad dinba sbd bai dawoba koya dawo ya wuce sama ya shige Bata saniba gashi tana Kiran Mr Omar Amma wayan Bata shiga haka ta hakura ta kwanta badan taso ba.

Washe gari da safe daga NURU har Farhat sun wuce makaranta ita kadaice Bata tafiba sbd ta sakawa ranta zata zauna harsai tasamu yin magana da dad dinta.

Guraren 11 na safe kuwa saigashi ya sauko qamshinsa na gauraya palon ahankali ahankali sai kyakkyawar fuskarsa dake kame kamar koyaushe

Tai Masa kallon qaunarsa amatsayinsa na mahaifinta datake tsananin kauna da alfahari dashi ta miqe tsaye tana aje laptop din dake kan cinyarta tana amfani da ita ta saki wani siririn murmushi tana qarasawa gurinsa tace"

Good morning dad,barka da fitowa.

Kallon kyakkyawar fuskarta dake yanayi da tasa yayi Yana alfahari da ita sbd juriyarta da iliminta tareda hakurinta ya bude Baki da muryarsa me amon iko yace"

Morning li'iliti(princess)

Murmushi tasake saki tana kallon dining din dayake qoqarin zama tace"

Dad can I join you?

Batareda ya dagoba yace"

Sure princess.

Janyo kujeran dining din tayi ta zauna tana cewa" thank you abal.

Tsit gurin ya dauka suna cin abinci Babu me mgnar sai ita dake cin abincin ahankali sbd son fara kawo zancen tagaji da wasi wasin yin zancen ko kartayi kawai saita kasa dannewan ta aje spoon din hannunta a natse ta kallesa da taushin murya tace"

Dad Yaya jikin Anneti(sarauniyar mahaifiya/mahaifiyarsa)

Zaka tafi tafi gizah kenan dad?

Dan kallonta yayi tareda sassauta fuskarsa ya gyada Mata Kai.

Sake gyara zama tayi cikin tausasa harshenta da bayyanarda damuwar data Dade da dannewa cikin ranta da biyayyarta ga dad din nata tace"

Dad maganarku da mum zai fito fili idan kaje....shiru ta Dan Yi tana kallon kamewar fuskarsa ta daure taci gaba da cewa"

Idan zancen ya bayyana cewan mum ta tafiyarta tabar..... kallo daya yayi Mata da fararen idanuwansa takasa qarasa sauran zancen ta marairaice fuska tace"

Dad please ko zaka duba kagani kodan sunan mum da naka dazai iya baci.

Tissue ya dauka ya goge bakinsa tareda Miqewa tsaye ya kalleta yace"

Take care princess"ya wuce.

Kasa motsawa tayi kanta na toshewa sbd hakan na nufi zancenta be karbu ba agurin dad dinta sbd hakan da yayi shine rashin amintarsa ga zance idan ankawo Masa.

Miqewa itama tayi tabar gurin Takoma daki ta zauna ta jawo waya ta Nemo numbern mum dinta tafara tunanin takira ko karta Kira,

Fasa Kira tayi tai wurgi da wayar tareda Miqewa tsaye ta sauya Kaya ta fito tashiga mota ta fice daga gidan Dan zuwa dauko NURU datasan yanzu ta Isa gamawa tunda ita yau Bata samu zuwaba.

Tunda suka dawo taketa qoqarin cire damuwarta sbd kada NURU tagane saidai NURUn tana lure da ita saidai batason takura Mata da tambaya sbd batasaniba ko matsalar ta sirrice.

Kwana sukayi ahaka suka Kuma yini ahakan har akai kwana biyu

cikin kwana biyun duk ta Hana kanta sukuni da tunanin al'amarin Wanda take ganin rushewa familynta zaiyi idan wata tashigo cikinsu amatsayin matar dad dinsu ko negestati

Itadaima tafi son iyayenta su shirya koma menene hakan yafi shigowar wata cikinsu.

Ganin dai dagaske AFIA na cikin damuwa me qarfi boye kawai take yasa NURU kallonta bayan sun kwanta tace"

Afia koma menene abindake damunki please ki rage idan bazaki iya ciresaba ko hakura dashiba sbd wannan damuwan naki bamajin dadin ganinki ahaka ko farhat dake qaraman yarinya tafara cewa menene akaiwa AFIA.

Please AFIA kicire koma menene kibarwa Allah a rayuwa dama akwai hakan duk da nasan ke koma menene damuwan ba wani babba bane sbd Babu wani abu najin dadin duniya da Kika rasa Dan Allah ki cire damuwan please baby.

Tunda tafara magana afia ke kallonta sbd wani tunani daya shigota na sha'awar bin dad dinsu gizah Dan koma menene tafison tanacan zatafi samun saukin hanawa kokuma handling maganar rabuwar iyayenta taqi barin ta fita Dan kuwa tasan daga lokacinda maganar ta fita MALEEK na gizah bazai qara awa ashirin da huduba

Batareda Matar aure ko negestati ba Dan haka zasu bishi Dan toshe yiyuwar hakan Dan kuwa idan hakan tafaru dad dinta bazai karbi mum dintaba har abada Wanda ita Kuma akan hakan ko kamawa tayi tayi amfani da NURU zatayi Dan Hana wata shigowa rayuwar dad din daidai NURU tayi hkr but she'll have to use her innocence.

Wani numfashi mara karfi ta saki tareda kallon NURUn cikin kauna da kulawa ta riqo hannunta ta rungume tace"

Thank you my NURU" ta rufe idanuwanta ahankali bacci na daukanta.

Washe gari haka ta tashi cikin walwalarta da sakewarta har hakan yasanya NURU da farhat farin ciki sosai har wasan ruwa da basketball sukai yau da yamma a playground Wanda duk abinda sukeyi dad dinsu na gidan dan haka Koda daddare yau taredashi sukai dinner Banda NURU dataqi fitowa tea kawaima Tasha sbd karatun data duqufa dayi Dan gobe tanada zuwa wani court yin wani aikin 4hours dake cikin karatunta.

Acan dining kuwa AFIA ta sanarwa dad dinta sunason binsa Dan Suma su dubo Anneti.

Kallonta yayi kadan tareda maida kallonsa kan farhat dake cewa"

Yes daddy Nima zanje Kuma zamuje da Aunt NURU ma ko AFIA?

Kallon bakin farhat din dako yaushe yake furta sunan NURU ko lewa yayi tareda dauke Kai Yana goge bakinsa yace su zama ready jibi ne tafiyar.

Cikin murna dukkaninsu sukace thank you dad.

Bayan fitarsa NURU tafara wucewa court kafin afia ita Farhat yau Babu zuwa school dinsu.

Sai yamma sosai suka dawo duk su dukansu Koda ta shigo tana waya da Imran da duk yabi ya sukurkurce Mata da cewan amatse yake da MALEEK yabawa su dad dinsa lokacin zuwa.

Murmushi kawai tayi sbd Bata taba tunanin maleek daya Bata ingantacciyar rayuwa tareda 'yayansa zai Bata ingantacciyar rayuwa ta har abada ba ta hanyar bada damar azo neman aurenta Dan tunda haryace idan yadawo zai Basu Daman zuwa ayi magana kenan da yiyuwar barinta tayi aure da rayuwar aure kaman kowaba babban mamakinta data kasa yadda dashi shine yau itace tasamu damar ace MALEEK na Delah gizah guda shine da kansa zai bada aurenta tabbas wannan tunanin idan yafado Mata kanta da tunaninta kasa dauka suke.

Ga tarin dibbin mamakinta tana shigowa Palo Imran suka tarar zaune Yana sako Mata murmushi da wani irin kallon Sonta daya gama yiwa tunaninsa da zuciyarsa mugun kamu saiyakejin kamar bazai iya rayuwa Babu itaba Dan kuwa komai zai iya faruwa dashi idan bai samu NURU ba amatsayin matarsa uwar 'yayan dazai Haifa.

Afia na ganin hakan ta wuce ciki tana Masa dariya da cewa"

Uncle Imran take it easy fa kada ka rasa 6sense dunka akan soyayya mu shiga uku barr IMRAN jalal ya zauce.

Da wata Yar dariyar qarfin hali yabi afia da zancenta idanuwansa suna Jan NURU dake tahowa cikin dogon wando da farar riga sai black scarf daure kanta duk da agajiye take sosai kyawunta ke bayyane tana qarasowa gap dashi ya miqa Mata cup din drink me sanyi da aka kawo Masa Yana cewa"

Have this my love kingaji ko?

Murmushi tasakar Masa takai hannu takarba takai bakinta ta kurba kenan idanuwanta suka sauka cikin na MALEEK dake tsaye da waya a kunnensa yanayi daga Palon ciki take ta qware da qarfi tana sakin tari ta miqawa Imran cup din tarinta na tsananta sosai

Cikin sauri da kulawa ya miqe Yana qoqarin Kai Mata cup din ruwa bakinta Tasha kozata ji sauki sauki sai kawai yaji anriqe cup din ya juyo da sauri sukai ido biyu da Mr Omar dake kallonsa cikin ido Ras ya Dan sake fuskar wata gantalalliyar murmushi tafito Masa yayiwa mum Sarah dayazo da ita kallo daya tayi saurin kallon NURU tana riqota tana Mata sannu tajata sukai ciki

Saida suka shige ya dago ya kalli Imran cikin girmamawar data so kularda Imran yace"

Barr IMRAN idan Babu damuwa zamu iya zuwa palon baqi dake gefen wannan sashen sbd dokokin gidan sun Dan qara tsauri yanzu Babu me sake shigowa sashen MALEEK dagashi sai 'yayansa.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*[9/14, 10:00 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 18_*

Oumahmad collection's

07014488636

Kitchen utensils

Fabrics

Shoes nd bag

Phones

Veils

Children's wears

Furnitures

Dubai,china,India,turkey,Malaysia

Kano hotoro

Fcbk Maryam muhd.

****

Shiru Imran yayi yana bin Mr Omar da ido baice komaiba sbd Kamar bai gama fahimtar me Mr Omar dinba yace Kuma baiyi abinda yace mishi yayin ba, kamar zaiyi magana sai kuma ya fasa ya juya ya fice daga Palon Yana fita harabar gidan ya shiga motarshi ya fice Dan Yana buqatan samun iska me kyau Dan yayi refreshing kwakwalsa dayakejin kaman ta toshe baya gane komai.

Mr Omar mabayanshi yabi da wani irin kallo mai ma'anoni da dama, ciki kuwa harda na tausayawa dan ya hango tsantsar soyayyar Nuru a cikin kwayar idonshi wadda yasan abin kamar da wuya Dan kuwa zancen me girma ne dayafi qarfinsu su 'yan qasa qasa Dan kuwa yana da tabbacin aure tsakanin Nuru da Imran ba abune me yiwa ba duk da dai fadan hakan ba huruminsa bane.

Dan

A bangaren Nuru kuwa karfin hali kawai take har lokacin gashi AFIA ta nace Mata akan tafiyar da zasuyi sai anje da ita Wanda takega kaman ta wuce huruminta Binsu delah gizah ziyartar kakarsu uwa sukutum ta MALEEK,

Amma ganin batada zabi na kanta ko ikon kanta Dole ta shirya 'yan kayanta da basuda wani yawa yawancima dogayen riguna ne Dan Bata dauki me wando ko dayaba da zai nuna tasamu dama da sake da yawa.

Tana zaune jikinta a matukar mace tana qarasa hadawa Farhat kayanta cikin nata pink akwatin me hoton frozen sisters saiga Farhat din ta shigo da gudu ta zauna kan jikinta tana cewa"

My Lewa please kumana pancakes me Honey and chocolate.

Kallon bakinta NURU tayi tareda sake murmushi tana kamo fuskanta tayi kissing goshinta tana cewa"

Kome farhat din aunt NURU takeso za'a Mata.

Muje cikin din yanzu bada dadewaba zakici pancakes sweetie.

Kicin suka nufa tana riqeda hannunta suna shiga ta dorata kan kitchen island ta zauna ita Kuma tafara hadawa farhat din na tayata fira.

Bayan sun gama a kitchen din suka ci nasu saidai na AFIA suka aje Mata a dining.

dakinsu ta nufa ta tararda Afia a kan doguwar kujera rigingine idanuwanta a lumshe ta kifa littafi saman cikinta da alama karatu take bacci ya dauketa batare data sani ba.

Murmushi Nuru tayi ta gyara mata kwanciya ta lullube bargo me taushi kafin tayiwa Farhat wanka ta shiryata cikin kayan bacci marasa nauyi ta kwantar da ita anan dakinsu itama ta nufi toilet din tayo wanka tareda dauro alwala tayi sallar ishai kafin ta Sanya kayan bacci irin na farhat din riga da wando dogo saidai rigar batada hannu sai siriri hakama kayan nada roba ajiki sai suka kwanta jikinta sbd kusan kayan baccinsu su duka ukun duk za'a siyo iri daya ake siyowa saidai banbancin size.

Ta hau gadon zata kwanta farhat ta motsa cikin bacci tace"

Aunt NURU water please.

Kallonta tayi da idanuwanta dasuke Jin bacci tace"

Ruwa farhat??

Yes aunt.

Numfashi ta sauke tareda zuro qafafunta qasa ta saka slippers din dasuke yawo dashi cikin gida ta miqe tsaye tareda daukar qaramar hula ta saka akanta dabai rufe dukaba ta fito.

Al'adarshi ce fitowa cikin dare ya duba inda ya kamata saboda tsaro da fita hakk'in na k'asa dashi, yana kula da ransu da lafiyarsu, dan duk da Maleek ya kasance mutum mai izza da mulki hakan bai sashi ya manta dokokin Allah dake kanshi ba, yana k'ok'arin sosai wajen kaucewa hakk'in mutane, dan haka lokuta da dama yana fitowa cikin dare ya duba lafiyar iyalinshi da sauran mutanen gida.

Ba ruwanshi da lek'awa d'akin kowa dan yasan muhimmancin Privacy sosai iyakacinshi kawai ya duba inda ya kamata.

Ganin haske a cikin yasashi kallon hanyar tareda nufowa cikin nutsuwa saidai bai qarasaba sbd tunda take rayuwarsa nai taba shiga cikinba tun girmansa a iya saninsa Dan haka sai ya tsaya iya dining musamman dayaji kaman motsi a kicin din.

Itakuma daukeda robar ruwa biyu a hannunta ta fito batama lura da komaiba tabi ta gabansa ta wuce saidai taku daya ta qara ta tsaya cak zuciyarta na sauya bugawa sbd idan hancinta yajiyo Mata daidai qamshin MALEEK taji agurin.

Juyowa tayi ahankali Wanda yayi daidai da qarasowarsa zaibar gurin jikinsu ya hadu da sauri tayi baya tana sauke kanta kafafunta na son daukar rawa yayi Mata kallo daya ya wuce yabarta tsaye jikinta na neman yin sanyi sbd Tama rasa halin me tashiga a tsakanin tsoro da firgita.

Daqyar takai kanta daki ta tayarda farhat din zaune tana Bata ruwan abaki tana cikin Sha AFIA ta farka ta tashi zaune tana 'yar guntuwar hamma ta miqe ta nufi toilet.

Farhat data gama Shan ruwan da NURUn ke Bata ta daga Kai ta kalli NURUn tana sake shaqar jikinta tace"

Aunt NURU kina qamshin irin turaren daddy.

Cak Afia dake gaf da shiga toilet ta tsaya batareda ta waiwayo ba ta Kira Jin amsarda NURUn zata fadawa farhat din.

Kasa cewa komai NURU tayi sbd batasan mezata fada ba saidai jin alamar AFIA ta tsaya yasata bude Baki daqyar a Sanyaye tana kamo abinda zata samu cewa tace"

No sweetie hancin kine sbd kila kinyi mafarkin daddy yanzu da kikai bacci.

Kwantar da ita tayi tana cewa"

Koma bacci kinsan gobe akwai zuwa school da wuri gakuma tafiya gizah.

Ajiyar zuciya kusan suka sauke tareda AFIA ta zame ta kwanta gefen farhat din tana rufe idanu ba shiri itama Afian toilet din tashige tana sake sauke numfashi me sanyi.

Washe gari tun 8 ta fice zuwa school bayan tagama breakfast da Shirin farhat data wuce school itama ta wuce sbd Kira da massages dinda Imran keta danno Mata gabaki daya hankalinsa a tashe yake musamman data fada Masa cewan daita za'aje gizah din saiyakejin kaman ya bisu Dan har zuciyarsa tafara bashi shawarar aje contact din Nan daya riqesa Wanda ya Hana rayuwarsa shaqat bare sukuni.

Tana Isa makaranta a can ya tarar dashi harya rigata Isa da kallon mamaki daga ita har afia suke binsa musamman ganin duk yayi wani iri idanuwansa sunyi laushi kaman ma kwana yayi bai rintsa ba.

Cikeda tausayinsa suke kallonsa duk su dukan hardai ita NURUn da idanuwanta sukai rau rau hawaye na neman cikowa cikinsu sonsa na qara shigarta ta tsaya daf dashi tana kallonsa cikin kulawa me tsanani da taushin murya tace"

Im lafiyanka kuwa?

Kana lafiya?

Bakayi bacci ba ko?

Kasa Bata amsa yayi sai kallonta dayakeyi kaman zai hadiyeta afia na ganin hakan ta wuce tabarsu anan tana yar dariyarsu.

Motarsa suka koma suka jingina anan yafara zayyane Mata shawarar dayakeson yankewa ta ajiye aiki sai bayan aurensu tukuna ta girgiza Masa Kai tana cewa"

Karkayi haka im idan muka saka gaggawa a al'amarin zai iya zuwa da tangarda,

Dan Allah kabi komai a hankali.

Murmushi kawai yayi Yana kallonta Yana cewa"

Idan kuka tafi zanyi missing dinki my love.

I will miss you too im Amma fa ka ajiye maganar aje aikin Nan please.

Gyada Mata Kai yayi kaman qaramin yaro sai hakan yabata dariya ta murmusa tana Dan juyar da kanta gefe daganan ya suka fara fira yanata sake langwabe Mata.

Ranar ko wani karatun kirki batasamu yiba sai yamma dasuka dawo Wanda shine dakansa ya dawo da ita tun a gate yana ajeta ya juya ya wuce.

Batajin yunwa Dan taci abinci a makaranta Dan haka wanka tayi tai salloli tana idarwa tasake hada sauran kayansu na tafiya Dan yau da daddaren zasu bi jirgin Daren zuwa gizah.

Kasa zaune tayi takasa tsaye gabaki daya batajin nutsuwar zuciya data gangar jiki daurewa kawai takeyi Amma wlh tana cikin wani hali na tsoro da shakka na zuwanta can din sbd sanin matsayinta Kuma idan taje can Dole tayi bauta kaman sauran bayi matuqar ba maganar zamtowanta negestati zai fito fili ba kuma idan hakan ta fito fili Dole amiqata ga NEGES dinta Wanda duk wannan cigaban rayuwar data samu zai tashi a banza.

Daga ita har afia qarfin haline kawai sukeyi suna sakewa Kamar suna cikin farin cikin tafiyar Wanda kowaccensu cikin ranta a matuqar tsorace take kaman zuciyoyinsu zasuyi tsalle su fada kowa da bikin zuciyarsa.

Qarfe Tara na dare jirginsu zai tashi Dan haka suna sallame sallar ishai suka fito masu aiki na janye da akwatinansu dasuke kaman set Dan duk iri dayane,

Ita doguwar rigace purple ajikinta sai gyale light purple data daura sai handbag da wayarta da sauran Yan abubuwanta qananu dasuke ciki

Qafartama flats Versace ne black a sanye sai face mask data Sanya Dan kaman iska iska takejin yamata yawa.

Mota daya suka shiga su biyu itada afia farhat Kuma motar daddynta tabi.

Har aka Isa airport Babu me doguwar magana acikinsu sai yaqen Dole dasuke zabgawa.

Kai tsaye angama komai nasu suna zuwa ta baya qofar 'yan first class aka bi dasu suka shige duk da hakan maleek nata inda basa ganinsa Amma shi Yana ganinsu da haka jirginsu ya daga massage din Imran na shigowa ko budewa batayiba tasaka wayar flight mode ta saka cikin jaka.

Doguwar tafiya sukayi me nisa ta tsawon awanni masu Dan yawa kafin suka Isa lokacin har qarfe bakwai yayi na safiya.

Airport din cike yake da wasu irin matakan tsaro na musamman da aka baza koina sbd saukowar MALEEK da familynsa.

Motocin daukarsu guda hudune sukazo daukarsu wainda suke na musamman ne Dan kuwa dama Dan maleek aka siyesu zamansa suke duk lokacinda yazo Kuma duk shekara ake sauya Masa su ko ya zo kobai zoba.

Cikin motocin alfarma aka daukesu daga airport din motocin tsaro suna gabansu da bayansu aka nufi babbar masarautar delah gizah dake daukeda babban tarihin arzikinda ko Ina aka sani musamman sbd qarfi da girman mulkinsu.

Duk yanda ake fadar delah ta gizah NURU hankalinta yayi mummunan tashi sbd yau idanuwanta sun gane Mata Dan kuwa duk yanda take tunanin gizah ta wuce Nan,

Tsorone da kamewa suke shigarta dataga tsagwaron dukiyarda idanuwa basa iya gama kalla Dan kuwa ita ayau taga abinda Bata taba ganiba arayuwarta,

Delah dinsu ta can dasuke ganinta aljannar duniya sbd tarin dukiya da zallar mulki Ashe ba komai bace akan Nan asalin delah gizah.

Matakan tsaro ne tako Ina da askarawa da bayi kowanne akan tsari sbd mulkin na wayayyun Kaine mulkine na masu ilimin turai da addini,

Rayuwar masarautar delah gizah tafi tsauri da matakan mulki da zuba zallar ikon sarauta shiyasa duk inda ta kalla saita sauke Kai taji jikinta yayi sanyi musamman dataga yanda ake bawasu afia girma Kamar za'a musu sujjada sbd girmamawa hakama duk Wanda ka kalla ko a kuskurence Babu Wasa ko Sanya ga dukkanin wani Wanda yake qarqashin masarautar Dan kuwa ko doguwar sakin fuska babu tsakanin jinin sarautar 'yan delah gizah din da bayinsu kokuma masu aikinsu basusan komaiba sai rayuwar mulki da iko cikin wadata da arzikinda basusan Yaya zasuyi dashiba.

Babbar masarautace datayi hudu zuwa biyar din delah ta garinsu wadda wannan komai nata ma basai anfadaba kana shigowa zaka kame kanka da kanka sbd Wasa ko laifi kadan saiyayi sanadinka ashafe labarinka.

Komawa tayi ita abiye kawai take dasu afiyan dandai duk tagama Shan jinin jikinta ta kame kanta farhat ce riqeda hannunta Taki saki sbd ita duk Bata wani Saba da kowaba Anan din sai Anneti AFIA ce kawai tasan kowa ta Saba da kowa harma da rayuwar mulkin itama ta iya tsaf Ashe akwai a jininta Dan kuwa take itama ta rikide Takoma li'iliti AFIA UBAYD MALEEK dinta Wanda yasa NURU sake Kama kanta.

Shi maleek ma sunsan ganinsa ayanzu ko su dasuke 'yayansa abune me tsananin wuya agaresu Dan kuwa ayanzu MALEEK yafi komai tsada da wuyar gani a gizah Dan kuwa tsaron dake hanyar zuwa sashensa ko asalin sashen NEGES (sarki) bai samu tsatsauran tsaro ba Kamar nasa sbd shine asalin MALEEK na kujerar kowa yasan shine sarki kawai dai mulkin baya hannunsane Wanda shine yaso Kuma bai tashi karba bane Dan hakane yasa matuqar MALEEK na gizah to kowane irin tsaro da matakai sun ninku.

Babban sashen dake maqale Dana Anneti mahaifiyar MALEEK anan ne masaukinsu dama Wanda yagama Jin gyaran Jin dadin duniya.

Bayine da masu hidimarsu birjik a qaton babban daki guda dake gefen part din Wanda aka zuba musu gadaje irin na Yan makaranta masu hawa bibbiyu su anan suke rayuwa aikinsu kawai shine duk ranarda iyalin maleek sukazo sune masu hidimarsu.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/14, 10:00 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 19_*

Assalamu alaikum, ina masu son su iya baking da decoration na birthday cake wanda idan aka kalla sai an kara kalla😇

toh ga dama ta samu er uwa kiyi maza kiyi rigista, sannan zaki koyi ydda ake hada whip cream din da yke daukar awanni ba tare da ya narke ba□□

zaki koyi ydda akeyin vanilla cup cake mai dadin gaske😊 er uwa ba'a iya nan muka tsaya ba zamu koya miki ydda akeyin chocolate bar cookie domin farantawa mai gida da baki

kuma duk akan kudi naira 3500 kacal

Online class neh full vedios kamar a gabanku akeyi, tare da note da voice note ydda zaku fahimci komai cikin sauki😇

kada kubari wannan dama ta wuceku

Domin neman karin bayani ki kira: 07089621678

I.G handle: Umsad cakes nd more😍

****

Zama NURU tayi a makeken royal bed dinda yafi Kama Dana kwanciyar mutum hudu zuwa biyar sbd girmansa ga wani irin ado da komai na dakin yasamu kana shigowa komai na masarautar ma kana gani kasan kana cikin palace.

Sake wani marayan numfashi tayi zazzabin daya kamata Yana sake qarfafa ajikinta Dan kuwa itadai batamasan menene matsayin dazata dauka anan din ba,

Shin me Reno?

Kokuwa baiwa?

Kokuwa negestati?to idan negestatin ne to ta wa?

Dafata AFIA tayi tana zare dankwalin kanta dake nade da dogon gashinta ta zauna tana miqar da hannuwanta a gajiye tace"

NURU Yaya dai?

All okay right???

Dan dagowa tayi jiki ba qwari ta kalli afia din saita sauke kanta tanajin kallon afian ido cikin ido yanzu ba nata bane kila kozasu koma yanda suke sai sun koma gida.

Cikin sanyin harshe tace"

Headache ke damuna Amma inaga na gajiyane zai saki idan na huta.

Cikin kulawa afia tace"

Sorry.

Gyada Kai kawai tayi tana sake dauke kallonta daga kan afia din.

Wanka sukai sauya cikin wasu irin dogayen rigunan alfarma wainda aikene na musamman daga sashen Anneti.

Babban makeken palon suka fito har zuwa dining Wanda yake shaqe taf da kalolin abinci da abin Sha tareda snacks da fruits kowanne sai daukan ido yake yanda aka jeresu kaman mutum goma ne zasuci abincin.

Zama suka farhat na gefen NURU sbd wata irin maqalewa data sameta tun zuwansu sbd farhat din nata rashin son shiga mutane masu yawa irin hakan shiyasa ma ko acan dad dinsu ya Hana bayi ko masu aiki da yawa sbd ko bayan farhat shima bayason guri da mutane da yawa komai girman gurin kuwa.

Cikin nustuwa da kwanciyar hankali sukaci abinci suka koshi suka koma Palo suka zauna aka aika da asanarwa da Anneti zasu zo gurinta kawo gaisuwa Nan da mintuna kadan.

Tunda saqon gasunan zuwa sashenta ya iso Mata farin cikinta ya Dada bayyanuwa sbd a duniya idan abinda tafi so da qauna shine MALEEK dinta da 'yayansa duk da kullum adduarta Allah yaqarowa UBAYD 'yaya masu albarka sbd tanason ganin zuriar UBAYD MALEEK ta yadadu Amma ga dukkan alamu kila hakan bamai yiyuwa bane sbd matarsa kowa ya lura Kuma ya fahimci batason yawan haihuwa.....Dan faduwa gabanta yayi da tunanin wani zancen binciken NEGES yabayar daya fada Mata yana ganin kaman UBAYD MALEEK Bata tareda matarsa.

Saurin rufe fararen idanuwanta da maleek duk su ya sauko tayi cikin wani irin hali na damuwa me tsanani tace"

Ya Allah ya kabar da wannan zancen akan MALEEK dinta Dan kuwa har abada ko amafarki Bata fatan ace hakan yazama gaskia Dan kuwa sbd wannan zancen da NEGES ya fada matane ciwon zuciyarta ya tashi Wanda tasa aka bugawa MALEEK Dan kawai yazo ta tabbatarda abinda hankalinta ya dagu da jinsa.

Saida afia ta tabbatarda zuwa yanzu saqon zuwansu ya isa gurin Anneti kafin suka dungumo zuwa gurin nata.

Tun a hanya NURU ke sake shiga taitayinta tana sake Kama kanta farhat dai na maqale da ita bayi uku na bayansu.

Fadar tsari da kyawun sashen mahaifiyar MALEEK bamai faduwa bane saidai kawai ace Masha Allah da wannan daula.

A babban palonta na kurya suka taddata suna shiga da sallama dauke a bakunansu Banda farhat data saki hannun NURU tayi gurin Anneti da gudu ta fada jikinta cikin tsananin farin ciki.

Farin cikin ganinsu ya Hana Anneti rufe Baki ta budewa afia hannuwanta ta qaraso da sauri ta rumgumeta tana cewa"

Kemiri nafik'akelewi ya Anneti (I miss you so very much Anneti/nayi kewarki sosai Anneti)

Murmushin farin ciki Anneti tasaki itama cikin yare da muryarta me tsananin taushi da dattako tace"

Masha Allah li'iliti takusa zama Mata agurin me gagaruman sa'a

Ya Allah ya albarki rayuwanku ku duka.

Amin sukace dukkaninsu har NURU dake tsaye Dana farko ta kasa qarasowa.

Idanuwa ta zubawa NURU dake tsaye tana kallonsu cikin burgewa suna hada ido tayi saurin sauke kanta tareda zubewa qasa ta durqusa tana cewa"

Barka da hutawa Anneti.

Har lokacin kallonta Anneti keyi sbd kyawun NURU da yanayin kyan fatarta dake haskota yasa take Mata kallon 'yar sarautar delah ce ta bude Baki cikin kulawa ta amsa mata tana maido kallonta kan Afia tace"

Wannan wacece??

Cikin sauri farhat tace"

Aunt NURU ce ta Dade agidanmu taredamu she's family.

Da mamaki tasake kallon NURU tana kallon afia data share zancen Dan batason fadar matsayin NURU na 'yar Taya zama da aka kawo musu ita wadda su tuni suka dauketa 'yar uwa ta jini wadda takewa kallon wani bangare na rayuwarta Dan kuwa qaunace me qarfi a tsakaninsu.

Jawo wani zance afia tayi ta hanyar cewa Nuru ta qaraso ta zauna acikinsu.

A Dan kakkame ta qaraso Amma Bata zaunaba saita zauna a qasa Yana cewa hakanma she's ok.

Ganin NURU da farhat yasa Anneti bataiwa afia maganar mahaifiyarsuba Wanda afia ta lura da hakan hankalinta yatashi sosai matuqa musamman batason ayi tambayar gaban farhat Dan zata fada cewar mum dinsu ta Dade da tafiya tabarsu.

Basu bar sashenba sai dare suna zuwa wanka sukai suka kwanta Banda NURU data fara waya da Imran.

Kasa bacci afia tayi tana saqa da warwara,

Babban abin tsoronta anan shine Dole ita Anneti zata tambaya mum dinsu Dan kuwa MALEEK ko sunyi mgnar da Anneti bazai taba fada Mata komai akaiba ita Kuma duk qaryar dazatayi na kawo wani excuse dazatace ya Hana mum zuwa bazai shigaba Dan kuwa Anneti zata gane komai Daren dadewa Dan haka take buqatan lokaci Wanda zatai amfani dashi ta shirya iyayenta kafin agano.

Da wannan tunanin tayi bacci takuma farka,

Washe gari ma agurin Anneti suka wuni saidai Banda NURU wadda ta Kama kanta ta zauna guri daya sbd yawo ba nata bane acikin masarautar gizah ta yayan masu masarautar ne

Sai washe gari dazasu yawon ziyara cikin masarautar zuwa sashe sashe na 'yayaye da sarauniyoyin gizah shine tabisu saidai tayi danasanin Binsu Dan kuwa sake tabbatarda rashin darajarta tayi shiyasa Bata Kuma gigin binsu ba idan zasu fita acikin gizah din ta Kama kanta ta zauna guri daya sai tunanin gida da iyayenta yadawo Mata Kamar sabo.

Duk yanda Afia ke zamewa Anneti sbd kada tasamu damar yimata maganar mahaifiyarsu yau da kanta taje gurinta Dan tabbatarwa da kaman jita jitan da kaman yakeson fita na rabuwar iyayenta din sbd shekaran jiya da jiya duk sashen dasukaje sai anyi tambayar matar maleek guda ace bataxo duba Anneti ba wane irin uzurine wannan.

Hakan yasa hankalinta tashi matuqa sbd tabbas Kam kowa zaiyi nasa tunanin daban daban ace Annetin delah gizah mahaifiyar MALEEK guda ace matarsa batazo dubata ba tabbas zance yafara bayyana take ta aika sako na musamman ga mahaifinta na cewa akwai karatu me mahimmanci a makaranta sunada buqatan komawa Kuma tana roqonsa daya koma taredasu sbd shine jigonsu bazaso komawaba bataredashiba.

Hakan datayi saiya sake saka Anneti cikin shakka da mamaki sbd sakon MALEEK saiya biyota gurinta yake Isa gurin maleek Dan haka ta aika aje akawo Mata farhat batareda sanin afia din ba.

Agurinta ranar farhat ta kwana da daddare bayan sunyi Shirin kwanciya ta kalli farhat din tana shafa Mata Kai cikin kulawa tace"

Farhat mamanki meyasa bata biyoku ba bayan ga abal dinku dayafita ayyuka yazo dubani??.

Kai tsaye farhat tace"

Mum ta Dade da tafiyanta munata kuka nida afia

Daddy ma da kansa yace idan ta tafi kada tasake dawowa yabata da ita koyaushe.

Wani mummunan bugawa zuciyar Anneti tayi har Saida ta dafe Dan kuwa kiris ne yahana ciwon zuciyarta tashi duk da hakan wani radadin tashin hankali takeji,

Idan dagaske MALEEK yarabu da lailah zancen yafito Babu ta yanda zai karbi mulkinsa Dan kuwa kaf a tarihinsu sarakuna basa sakin matansu wannan wace irin masifa ce.

Cikin tashin hankali tasake sanyaya harshenta tace"

Tun yaushe ne ta tafi?

Tun kafin aunt NURU tazo ne ta tafiyan munata kuka hadda Afia Amma tunda aunt NURU tazo daga delah jekadi takawo Mana ita shikenan muka daina kuka sbd Aunt NURU tana Sona sosai tunda tazo AFIA tadaina damuwa suka zama Best friends tanamun pancakes da komai nakeso Kuma daddy ma tana Masa abinci fa yafi nasu mum Sarah Dadi aunt NURU tafi mum sbd ita Bata barina Ina kuka Kuma tace bazata tafi tabarniba kaman yanda mum tayi idan sunyi aure da uncle Imran ma Dani zata tafi.

Wuta Anneti ta dauke gabaki daya

Numfashinta yafara yankewa tana dannewa,zufa kuwa kaman tana cikin dakin gashin biredi.

Daqyar ta iya daidaita numfashinta ta kalli farhat tana nazartan zantuttukanta daya bayan daya tana fahimtarsu tana kawowa inda farhat tace jekadi takawo musu NURU daga delah sai kawai ta tsaya anan ta shafa kan farhat din tareda kwantar da ita tana Mata addua har tayi bacci.

Palon hutawarta ta Isa ta zauna tareda daukar wayarta ta Nemo numbern jekadi ta Danna Mata Kira.

Cikin girmamawa me girma jekadi ta dauki wayar tareda zubewa qasa tana jerowa Anneti gaisuwa cikin tsananin girma.

Shiru Anneti tayi na mintuna biyu kafin tace"

Jekadi bayanin komai nakeso na NURU yarinyar dake zaune agidan MALEEK.

Tsit jekadi tayi tana juya zancen zufa na karyo Mata cikin tsananin ladabi da girmamawa tayi kasa da Kai kaman agaban Anneti din tace"

Allah ya taimaki Anneti kimun afuwa nafara tambayo izinin fadar wannan magana agurin KALEEB.

KALEEB?" Anneti ta fada ahankali cikin mamaki duk da tasan dama Dole Saida sanin Kaleeb jekadi ke komai.

Katse wayar tayi ta Nemo numbern kaleeb da kanta takirasa.

Kira uku tayi se Ana hudu ya daga cikin muryar girma da mulki take itama tayi qasa da murya tahau gaisuwa cikin tsananin girmamawa tana sake tambayarsa manyanci.

Shiru tayi bayan gaisuwar tarasa ta inda zata faro har Saida yayi gyaran murya a kame yace"

Kiyi maganarki kada ki damu kaleeb zai duba koma menene.

Cikin sanyin murya tace"

Allah ya taimaki kaleeb idan banyi shishigiba inason sanin wacece yarinyar da jekadi takai gidan MALEEK.

Murmushin manya yayi Kai tsaye yace"

Negestatinsa ce sbd ya rabu da matarsa.

Hawaye ne suka ciko Mata ido tace"

Allah ya taimaki kaleeb nagode Allah yaqara girma ina fatan ban dameka ba da Kiran dare danayi.

Bakomai Anneti Allah ya taimakemu duka.

Maganar rabuwar MALEEK da matarsa kuwa kinsan meya dace kiyi qato shiru sbd fitar hakan barazanace ga maleek.

Inshallah kaleeb ngd ahuta lafiya.

Kasa daurewa tayi Saida wasu irin hawaye me zafi suka gangaro Mata sbd wannan masiface agurinta babba.

Ta Yaya zata Hana fitar maganar rabuwar MALEEK da matarsa.

Jekadi takira anan jekadi ta fayyace Mata komai na yanda rabuwar take Wanda yasa ran Anneti baci sai yanzu ne tagano dalilin qin barin ayi maganar da afia keyi sbd Kare mahaifiyarta kada mutuncinta ya zube.

Ko so daya adaren Anneti Bata rintsaba Dan kuwa ki NEGES bazata Bari yaji zancenba tunda zargi kawai yake zata barshi yayita zargin kawai batareda ya tabbatarba.

Washe gari tun qarfe Tara ta aika cewa tana gayyatar su AFIA cin abincin safe a sashenta tareda ita.

Da farko AFIA taji wani Abu na kwanan da farhat tayi acan gurin Anneti Amma da bataji bayani ko ganin sauyi afuskan Anneti ba saita sake abinta Dan ma kada asamu damar yin maganar saita saka NURU shiryawa Dole suka taho tare.

Tunda suka zauna cin abinci Anneti tayiwa NURU kallon sakanni ta dauke kanta ta maida kan Afia dake cin abinci ba damuwar komai aranta.

Suna gamawa NURU ta fice daga sashen gaba daya sbd kallon da Anneti ke Mata yasa hankalinta tashi matuqa tashiga wani irin matsanancin tsoro.

Kai tsaye Anneti ta kalli afia bayan fitar NURUn tace"

Maleek da lailah sun rabu gaskia ne kokuwa???

Wani irin mummunan tarine ya kufcewa afia ta dago da jajayen idanuwanta ta kalli Annetin cikin tsananin firgici da tashin hankali tace"

Aa Basu rabu ba sunanan tare.

Meya hanata zuwa ita?

Sake dagowa tayi dukkanin idanuwanta na qarasa sauyawa cikin dakewa da qarfin hali tace"

Ayyukane sukai Mata yawa tayi tafiya.

Murmushin takaici na manya Anneti ta sake tana kallon zallar kuruciyar afia da yarintarta tace"

Idan har hakane kuna buqatar uwar dazata kula daku da mahaifinku sbd....

Cikin tsananin tashin hankali da firgici afia ta miqe tsaye jikinta har 'yar rawa yakeyi ta zube gaban Anneti cikin rawar murya da Bata girmanta na uwar MALEEK tace"

Anneti Ina roqanki da kadaki kawo Mana kowa bama buqatar wata uwa sbd munada me kula damu wadda take tamkar uwa.

Kallon tsaf Anneti ta Mata saidai tasan zallar kuruciya kecin afia Amma tace"

Wacece ita?

NURU tafada Kai tsaye.

NURU ba mata bace Matar uba ake magana wadda zata zauna daku har abada.

Rintse ido tayi sbd fadar abinda zata cutatar da NURU saidai Dole zatai hakan Dan kawai abar zancen su samu su taciyarsu batareda wani maganar aure aure ba wa dad dinsu.

Bude idanuwanta dasukai jajir tayi ta sauke Kai muryarta na rawa tace"

NURU da dad zasuyi aure idan munkoma.....

Wani razanannan kallo Anneti tai Mata cikin tsananin mamakin mahaikaciyar kuruciya irin tata,

Wace irin zuciyane da afia dazata yiwa mahaifinta qarya Dan Kare mahaifiyarta?.

Ji tayi zuciyarta ta sosu da abinda afian tayi saidai ta danne bacin ranta sbd gudun shedan yashigo cikin lamarin sbd afia ta dauko wata mummunar sabia me qarfi qararda zance irin wanan akan MALEEK guda idan har Bata dauka matsayinsa na mahaifi agaretaba.

Tabbas yau zata nunawa afia yaro man kaza ne,

Ta dauko magana me girma Dan Kare darajar wadda batasan daraja ba Dan haka yau zatasan ba'a Wasa da magana irin wannan.

Kitashi kije zancenki ya karbu.

Ajiyar zuciya boyayya afia ta sauke duk ganin takashe maganar qara auren mahaifinta duk da zuciyarta bata daina bugawaba kamar zata faso ta miqe ta fice tana istigfarin na neman yafiyar ubangiji.

Bayan fitarta waya Anneti ta daga ta Danna Kiran jekadi Kai tsaye cikeda bada umarnin me qarfi tace"

A isarwa kaleeb saqo daga Anneti cewan muna roqon alfarmar auren NURU daga negestati zuwa Mata ga MALEEK na Delah gizah UBAYD MALEEK.

Da qarfi jekadi ta zube qasa tana yiwa Anneti wani irin kirarin tsananin farin ciki da girmamawa.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/15, 6:23 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 20_*

Assalamu alaikum, ina masu son su iya baking da decoration na birthday cake wanda idan aka kalla sai an kara kalla😇

toh ga dama ta samu er uwa kiyi maza kiyi rigista, sannan zaki koyi ydda ake hada whip cream din da yke daukar awanni ba tare da ya narke ba□□

zaki koyi ydda akeyin vanilla cup cake mai dadin gaske😋 er uwa ba'a iya nan muka tsaya ba zamu koya miki ydda akeyin chocolate bar cookie domin farantawa mai gida da baki□

kuma duk akan kudi naira 3500 kacal□□

Online class neh full vedios kamar a gabanku akeyi, tare da note da voice note ydda zaku fahimci komai cikin sauki😇

kada kubari wannan dama ta wuceku□

Domin neman karin bayani ki kira: 07089621678

I.G handle: Umsad cakes nd more😍

****

Tana aje wayar miqewa tayi Takoma dakinta tareda dafe kanta da tuni yadauki wani irin ciwo sbd tarin mamakinda afia ta Bata Wanda take sake Dora hakan akan rashin uwane tareda ita tarbiyarta tafara yin qaranci tana sauyawa Dan kuwa ita din Bata saniba Amma abinda tayi laifine me girma da Muni yiwa mahaifinta qarya irin wannan da zata iya zubda mutuncinsa da awani gurin ta fada hakan Dan hakanma ta yanke shawaran Babu Wanda zaisan abinda afia din tayi zata bar zancen akan MALEEK aure kawai zai qara basai kowa yasanda rabuwarsa da matarsaba bare qaryar da afian ta shata Dan Kare mahaifiyarta.

Afia kuwa tana Isa sashensu a palo ta tadda NURU da farhat na zaune Kamar ko yaushe farhat na jikin NURUn suna kallon cartoon din SpongeBob ta tsaya cak tana kallonsu hawaye nason ciko idanuwanta Amma ta danne sbd tanajin zuciyarta na karyewa na abinda tayi din sbd ta Kara NURU Dan biyan buqatarta Wanda idan daga baya bayan sun koma akaji auren NURU da Imran za'a iya daukan hakan amatsayin cin amanar MALEEK datayi tunda yanzu Anneti taji cewar MALEEK zata aura..

Cikin yanayi na sanyi NURU ta dago Jin mutum a tsaye akansu ta kalleta da idanuwanta dasukai laushi sbd ciwon Kai datake ji kadan kadan ta bude baki ahankali tace da sanyin murya tace"

Afia lafiyanki k.....Bata qarasa maganar taba afian ta qaraso hawayen cikin idanuwanta na gangaro ta rungume NURUn tana rintse ido batareda tace komaiba.

Shiru NURUn tayi itama dukkanin jikinta na sake yin sanyi Jin saukan hawayen afia akan bayanta dake bayyane ta cikin doguwar riga Mara hannu.

Sun Jima ahaka kafin NURUn ta dago afia tana kallon idanuwanta dasukai jajir ta saki wani sanyayyan numfashi tace"

Menene yafaru??

Kasa kallonta afia tayi ta juyar da Kai gefe tana hawayen cikin idon suka sake gangarowa kafin ta dago ta zubawa NURU idanuwanta cikin sanyin murya da nadama tace"

NURU idan Baki saniba ayau inason kisani ke din wata babbar bangarene na rayuwata nida farhat,

Ina Jin araina tamkar yanda nakejin farhat sbd na dade da Baki matsayi na 'yar uwar uwa daya uba daya,

NURU wlh kisani duk duniya banajin zanyi Abu Dan kawo cutatarwa gareki Dan haka nake roqonki dakimun uzuri karki zargeni da komai idan har kikaji wata magana ta bullo Miki daga Anneti duk da nasan sirrine da bazata futarba ita kanta saidai koma yayane Ina roqon alfarmarki da kadakice komai duk tsanani kada kifada komai duk abinda akace kice eh sbd hakan shine zai bani lokacin kawo gyara tsakanin dad da mum Dina Wanda kinfi kowa sanin wannan shine burina a duniya and you promise to support me akan hakan right??

Tsit NURU tayi tana kallon afia din kaman wata sokuwa sbd ita anan Bata gane komaiba sbd zancen duk a baibai yake bayan hakan ita menene nata wane matsayi take dashi da afia zatace tashigo cikin zancen komai akace tace eh,to menene zata cewa eh din??

NURU Zaki taimakemu mu dawo da mahaifiyarmu nida farhat??

Cikin tsoro da mamakin shiga huruminda ba nataba ta kalli afian da idanuwanta sukai jajir ta gyada Kai ahankali batareda ta iya bude Baki tayi maganaba sbd Jin abin take yayi Mata nauyi kaman bazata iyaba sbd Jin kamar ba zancenda zata shiga bane.

Zamewa tayi gefen NURUn data shiga tunani haka kawai ta kwanta tareda Dora kanta kan jikin farhat dake jikin NURUn itakuma da hakan duk su duka biyun suka shiga tunani.

****

Tsaf kaleeb yaga sauraron saqo me girma da jekadi tazo dashi idanuwansa nakan makekiyar TVn data kusa cike Rabin bangon palonsa zaka dauka baya sauraronta Amma tsaf yagama Jin komai ya jinjina Kai Yana sake juya zancen cikin ransa da tunaninsa.

Jekadi menene halaye munana da kyawawa na NURULHUDA??

Ya qarfin nutsuwarta da biyayyarta?

Ya qarfi da girman son duniyarta take?

Sake zubewa qasa jekadi tayi cikin girma da tabbacin abinda zata fada Kai tsaye tace"

Allah ya qarawa Kaleeb Nisan kwana da lafiya.

NURU negestati ce wadda zance komai nata da yardar Allah yayi abisaga tsarin da kake son Matar MALEEK ta kasance,

NURU jikace Kuma 'yar asalin amintaccin bayinka da kakanta da mahaifinta,

NURU baiwace me biyayya tareda da'a wadda takaita ga samun ribar zaman rayuwa,

Anneti ce da kanta tayi zabin NURU tazaman Matar aure ga MALEEK wadda zan bada rayuwata akan Anneti Bata yanke komai akan garaje Wanda wannan halin na zurfi da tsaftataccen tunanin daukarsa tayi daga cikin halayen girmanka da adalcinka ya kaleeb.

Jinjina Kai yakuma Yi tareda kallonta wannan karon ya bude Baki cikin gamsuwa da zallar cikar ikonsa yace"

Ahada dukiyar neman auren MALEEK UBAYD zuwaga mahaifinta tareda saqon 'yantawa ga dukkanin zuriarsu tareda tukuicin zuwa gizah ga dukkanin ahalin Dan halartar auren 'yarsu.

Sake zubewa jekadi tayi tana miqa tsagwaron godia da kirari tareda fatan nasara da tarin aduoi ga wannan aure harta fice tanayi cikin tsananin farin take da wannan aure sbd har cikin ranta Allah yasanya Mata kaunar NURU take Kuma fatar cigabanta Wanda tun zuwanta ta yaba takuma Yi tunanin kyawu da halaye na gari irin na NURU matuqar ta zama negestatin MALEEK to ko Bai auretaba wata Rana to tabbas saita zamana negestatinsa datafi matansa daraja a zuciyarsa saigashi abin yazo alokacinda Babu zato ba tsammani Dan haka ko minti biyu Bata qaraba aka fitarda saqon kaleeb take aka fara hada dibbin dukiya da tarin zinarai masu nauyi da daukar ido Wanda yasa take maganar ta fito filin Allah zancen auren ya bazu Kamar wutar daji wasu Basu tabbatarba Saida aka Kai dukiyar gidansu NURU yakasa dauka take aka sauya musu muhalli acikin qanqanin lokaci gari kuwa ya dauka tako Ina zancen akeyi wasu na qaryatawa wasu kuwa mamaki da firgici ya hanasu yadda.

Padima dake zaune bakin kofar dakin da aka jere dukiyar neman auren NURU dakuma Wai MALEEK UBAYD Wanda sunansa kawai sukeji kaf delah din Nan kila idan ba kakansaba sai wasu qalilan ance Babu Wanda ya taba ganinsa koda cikin sa'a ne.,

Sam Bata yardaba da wannan zancen tafi yarda da cewan wani dai acan gizah zai auri NURUn Amma badai MALEEK ba Dan kuwa har abada ko ita datake gaban NURU akomai Bata taba kawosa cikin rantaba bare NURU sokuwa wannna masarautar delah ta boyewa su abal ne amma tasan tsohon da take negestatinsace zai aureta Kuma a iya saninta ba ace musu maleek ba da akazo daukarsu negestati.

Kallonta amminsu tayi lokacinda ta fito dayan dakin riqeda hannun meryam daketa tsalle tsalle da farin ciki me tsanani tun jiya da akace Mata zasuje inda zasuga NURUnta.

Da mamaki ammin tace"

Padima tun jiya kin kasa dogon motsi kin kasa kin tsare kofar dakin Nan bayan kinsan Babu Wanda zai shigo gidan Nan idanma sata kike gudu ki kwantar da hankalinki Mana idanma tambaba kike na waye NURUn zata aura ai zamuje saimu tabbatar sbd muma munkasa yadda da abin al'amarin yazo mana a wani irin girmame saidai koma wane munsan wannan babban cigabe da abin farin ciki ga NURU sbd aure abune me girma dazai tabbatarda darajarta.

Qala padima Bata samu cewaba dan kalma daya acikin zancen ammin Bata fahimta ba babban burinta da damuwarta yanzu shine su tafi gizah din tasamu ganin NURU taji komai daga bakinta shine kawai zai Bata kwanciyar hankali tanaji meryam na fada Mata amed na kiranta waje harso shida tayi kamar batajitaba qarshe korata tayi da wani mugun kallo dayasa meryam din tafiya gurin ammi tana waiwayen padiman sbd ganin yau ko gyaran dogon gashinta batayiba Wanda kullum sai tayi gyaransa Kamar wani sarki.

Daga waje Kuma amed ganin Bata fitoba harya gaji da tsayuwa ya juya ya wuce Yana cewa"

Kome Zakiyi wlh sai anci dukiyar Nan Dani sbd rabona ya koka aciki Dan kuwa nasan yanzu tunda Zaki tafi gurin NURU a gizah dukkanin burinkanki kinsamu damar cikasu wlh maqalewa yanzu nafara Miki mutu ka raba komai Zaki samu taredani zamu cisa.

****

Zaune yake cikin makeken palonsa na quryar sashensa Wanda bayan masu gyarawa Babu Wanda yataba shigarsa ciki Koda kuwa mahaifiyarsace.,

Kyawu da tsarin palon kawai ya isa sanyaka lissafinda bazaka iya kaiwaba musamman sbd komai na sassansa na daban ne Dan zamowarsa MALEEK.

Akaro na biyu ya sake wani boyayyan numfashi Yana sake lumshe fararen idanuwansa dasuka Dan sauya sbd ciwon Kai me qarfi daya damqesa lokaci daya da kaleeb yakirasa ya sanar Masa da aure za'a daura Masa da negestatinsa abisaga umarni dakuma roqon alfarma da neman cika biyayya daga mahaifiyarsa da Bata taba neman wata alfarma daga garesaba ataqaice wannan ne Karo na farko data yanke hukuncin wani Abu akansa tun bayan rasuwar mahaifinsa Yana qarami.

Kaleeb ya sanar dashi an aika komai ankai qarshen komai jibi za'a daura auren Wanda har zancen ya fita shin tayaya zai musa wannan auren da yarinyar datake tamkar 'yar cikinsa Dan kuwa idanma lissafin yaje daidai afia zata girmeta Koda da shekara biyune ko daya.

Ta Yaya aure zai shiga tsakaninsa da wadda yakewa kallo daya da farhat qanqanuwar yarinyar da batafi shekara gomaba.

Wayarsace tayi haske tana vibrating ahankali ya bude idanuwansa ya kalla wayar ahankali yaga sunan Mr Omar akai dauke Kai yayi tareda mayarwa ya rufe tsawon lokaci ahakan kafin ya bude idanuwan daidai Mr Omar nasake Kira sbd sanin MALEEK dakyau da yayi yasa yake iya kwatanta mintunan sake Kira na biyu idan yayi na farko cikin sa'a kuwa ya daga batareda yace komaiba.

Da sauri cikin girmamawa da kaucewa dogon bayani da MALEEK bayaso yace"

Barka da hutawa MALEEK.

Dama 'yan media ne sukeson yada zancen...um..um..maganar auren ko za'a sirrantane?duk Wanda ya fitar Kuma mu dauka mataki akansa.

Kai tsaye yace"

Aure Yana boyune???

Jin haka yasa mr Omar cewa"

Allah ya huci zuciyar MALEEK.

Kashe wayarsa yayi ya ajiye tareda Miqewa yayi ciki Dan kuwa kila Babu me sake ganinsa sai gobe idan kaleeb ya iso daura auren Dan yasan zancen yanzu cikin awanni kadan zai bazu koina musamman NEGES da tun jiya yake son ganinsa Amma baya cikin mode dinda zai iya ganin kowa.

Yana daf da shigewa breaking news din auren THE KING OF DELAH GIZAH MALEEK UBAYD ya sauka acikin cikin qatuwar TVn dake palon ya juyarda idanuwansa ahankali zuwa kan time sai kawai yashige sbd Dama yasan media jira kawai suke abasu tabbacin zancen gashinan mintuna uku da zancen harsun sake breaking news.

****

Qarfe shida na yamma daidai lokacinda zancen auren ya fita adaidai lokacin Anneti tayo aike me qarfi na daukar NURU zuwa wani kebantaccen sashe dake cikin sashenta Wanda Babu Wanda yasan inda aka Kai NURUn har afia kuwa Dan Koda aka tafi da ita afian na bacci Dan ko daki ba'a Bari Takoma ba daga Palo Dan haka Koda afia ta tashi da mummunan labari biyu daya Bata mummunan shock taci Karo na farko tun a waya tasamu labarin auren mahaifinta ta fito a rude saikuma tasamu labarin kebe NURU Wanda kowa yace baisan inane aka kebetaba.

Wayar dad dinta ta nema arikice tafara Danna Masa Kira Bata shiga hannuwanta dukkaninsu rawa suke da qafafunta tana sake Danna Kiran dad dinta Kiran Imran sai shigowa wayarta yakeyi na kakkautawa tana kashewa Dan ayanzu batasan ma a Ina kanta yakeba ta zari takalmi tayi sashen Anneti saidai tana shiga bata samu ganinta ba sbd Wai tana hutawa Bata fitowa lokacin dawowa tayi a haukace ta nema numbern kaleeb ta Danna Masa Kira shima Bata samu damar magana dashiba Yana cikin dakin hutawarsa.

Ji take kamar ta Ari hauka sbd so take tasamu bayanin abinda tagani take kumaji idan zancen datayine aka dauka da gaske take ake Shirin auren tun anan.

Palo tadawo ta zaune tana neman rusa kuka sbd idanuwanta dasuka kada sukai jajir ta dafe kanta dake neman tarwatsewa.

Wayartace tayi ringing a zabure ta wawuro wayar tana dubawa sai jikinta yayi wani irin daskarewa sbd tsananin sabon firgici da mamakin data shiga sbd ganin sunan""

MUM" baro baro akan screen dinta sai kawai jikinta ya saki tana kallo wayar na ringing harta tsinke Bata iya dagawa Dan kuwa rabon data ji mum dinsu shekarunma batasaniba tun bayana tafiyarta sai yau Wanda tasan dalilin Kiran baya wuce labarin auren dad dinsu data gani a duniya.

Zubewa tayi kan kujera tareda sake kuka Mara sauti tanajin wani zafin mum dinta da duk itace silar watsewar farin cikinsu" i hate you mum"takeson cewa Amma zuciyarta na hanata saidai wani irin zafin mum din takeji,

Babban baqin cikinta biyu ta rusa rayuwar NURU bayan tasan yanda sukeson juna da Imran hakama Imran ta rusa Masa farin ciki uwa uba me gaba daya bazata iya yadda ta karbi wata ba mum dinsuba amatsayin matar dad dinsu Dan haka Dole zatasan yanda zatayi ta Raba wannan auren ko an hadashi sbd kowa yasamu abinda yakeso.

***

Duk wani gyara da shiri na musamman anfara yiwa NURU shi atake da aka zo da ita Wanda Kuma kala Babu Wanda yake cewa ga duk tambayoyin datake musu sbd ita tsoro da firgici abin yake Bata Dan batasan meyake faruwa duk ta daga hankalinta musamman dataga ire iren gyara na musamman da ake Mata tamkar wata sarauniya Wanda Kuma ta tabbatarda wannan Shirin na aurene kokuma na Shirin kaiwane ga NEGES,to kenen gurin NEGES dinta datake negestatinsa za'a kaita..wasu irin hawayene masu matuqar zafi suka ciko idanuwanta tuno komai ya ruguje kenan daga yanzu a rayuwarta.

DELAH GIZAH ta dauki babban amo na jama'a manyan qasashe da dauloli dabam dabam hadda turawa da larabawa na nesa Dana kusa sun cika gizah damqam shiyasa tsaro da matakai harsunyi yawanda ko matso na Wasa basayi sbd atake

zakayi ta bakin ranka sbd matakan tsaron ba dama musamman idan washe gari tayi ranar daurin auren kenan matakan saisunfi tsananta dan kuwa ko yanxu bashiga ba fita a gizah idanba na manyan baqinsuba na daurin aure.

Anneti duk wani farin ciki tana cikinsa musamman datai ido biyu da kyakkyawar fuskar NURU wadda cikin kwana biyu kacal ta sauya sbd tsananin gyara daya maidata tamkar asalin sarauniyar gizah musamman har wani sheqi fatarta keyi tuni tasake bada odar dasa sabon gyaran ciki Wanda zaibadu damar janyo zuciyar MALEEK gareta daga sun kusantu.

Washe gari jekadi na isowa tareda iyayen NURU dasu padima acikin tawaga ta musamman ta kaleeb Wanda Yana shigowa gizah aka rufeta gabaki daya ba shiga ba fita sai bayan daurin aure da qarfe biyun Rana.

Guri na musamman aka sauke iyayen NURU wainda suketa fama da padima da zazzabi me qarfi ya rafketa reras Banda some some Babu abinda takeyi daqyar suka samu tayi bacci kafin sukaci abincin alfarma fiyeda kala goma suka koshi aka kawo kayan Shirin abal dinsu ya shirya masu tafiya dashi suna jira yafito suka nufi can bangarenda za'ayi daurin aure yabar amminsu da sallar nafila tana zuba adduaoin a daura auren Nan lafiya yasa idan akai auren sai mutuwa NURUnta.

Meryam Kuma a zaqe take dataga NURU wadda Babu me ganinta kaf sai mijinta idan tafara fitowa daga maboyarta Wanda wannan al'adarsu ce.

Qarfe biyu aka daura auren UBAYD MALEEK M KALEEB da NURULHUDA ABAL YONAS akan sadakin darhaman zinare Wanda dubban daruruwan hamshaqan duniya suka shaida a masarautar delah gizah dakeda kafaffen tarihin.

Daurin auren yasamu 'yan farin ciki da Yan sabanin hakan da masu burika daban daban akansa Dana alkhairi Dana sharri.

Maganar aurensa ita ta batarda maganar rabuwarsa da matarsa data fara bulla.

Har yamma tayi lis afia Bata cikin cikakkiyar nutsuwarta Dan haka tanajin saqon fitowa da MUSHRAH(bride/sabuwar Matar sarki/amarya)yagama bazuwa a cikin delah gizah ta shirya cikin qarfin hali da danne damuwarta ta shirya tsaf cikin shigar alfarma ta li'ilitinta tafito Dan zuwa miqa gaisuwarta datake al'ada dakuma Dole

Dole ga duk wani Wanda ke cikin masarautar delah gizah fitowa Kai gaisuwa ga duk MUSHRAn NEGES wato amaryar sarki.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899*_Mamuhgee 21_*

Tunda aka fito da ita taga sauyi me matuqar girma da mamaki sbd tsaro da girman da ake Bata kamar za'a bauta Mata yasa taji hankalinta ya ninku gurin tashi da firgici saidai sbd a rufe take Babu me iya ganin hakan gashi takasa Jin komai daga bakin kowa bare ta tabbatarda abinda yake faruwa Abu daya data tabbatar shi shine tabbas yau gurin NEGES dinta za'a miqata Wanda hakan yasa idanuwanta masifar cikowa da hawayen tausayin kanta dana im harma Dana afia da farhat dinta da zasu rabu gashi har abada Bata ikon sauya wannan ikon akanta.

Kai tsaye babban sassan MALEEK UBAYD aka nufa da ita Wanda shine yakeda ikon fara ganinta kafin tafito kowa yaganta Dan haka suna Isa tangamemiyar kofar gurinsa masu tsaro suka bude musu sbd tsananin tsaro da securities din gurin masu Kama da samudawa anan kowa ya tsaya daga ita sai jekadi suka shige aka rufo har lokacin Babu kala jekadi Bata ce ba shiyasa batama San da ita ake tareba bare tasan inda suka shigo.

A kofar palonsa na karshe Wanda dagashi saina hutawarsa sai master bedroom dinsa Dan haka daganan jekadi taja gefe ta tsaya cikin bawa NURUn girma tace"

NURU gaki a kofar shiga gurin uban gidanki Kuma mijinki na halak malak Wanda shine zai budeki kafin kifito al'ummar gizah nason sheda ganinki wato mace me sa'a.

Da haka tayi baya ta fice daganan Takoma can farkon shigowa jiran fitowar NURU din.

Kasa motsi tayi daga inda take tsaye sbd firgicinta daya koma zallar mamaki Dan kaman Bata fahimci me jekadin tagama fadaba ta wuce.

Saitaji kaman tace aure?

Girgiza Kai tayi ahankali tareda sauke Numfashi sbd sanin ba hakan bane itada samun arzikin daukar igiyoyin auren wani sai Allah tunda harta rasa igiyoyin auren im tasan aure gareta sai rabo me qarfi Dan tuni take cikin radadin hakan har lokaci da rayuwar data samu a Paris ya mantar da ita komai yanzu Kuma qaddararta tadawo gareta Dan haka ba gudu bare tsira.

Ahankali ta tura tareda saka Kai cikin qofar da jekadi ta 'dan bude Mata ba dukaba sbd takaitawa NURU aikin bude qofar Wanda badan kofar MALEEK bace itace zata bude Mata ita har qarshe.

Wani irin sanyin AC ne Dana wani qamshi data sani suka fara tarbanta ta maida kofar ta rufe ahankali har lokacin fuskarta arufe take.

Tunda ta iso tsakiyar palon ta tsaya cak batareda ta qara taku ba sbd bugun zuciyarta daya qaru Yana fita da qarfi Dan zuwa yanzu tagama tabbatarda qamshin datake ji musamman data iso tsakiyar palon taji yasake gauraya gurin.

So take ta yaye fuskarta taga inda take sbd firginta daya sake dawowa Amma ba hali sai kawai qafafuwanta suka hau rawa da dukkanin jikinta dama gashi ko abincin kirki tadaina ci kwana biyun sbd tsoro da shakkun datake ciki na abinda yake faruwa

Hannunta dake tsananin rawa ta daga ahankali ta shafo fuskarta dake lullube taji zufan tashin hankalin turaren MALEEK datakeji tako Ina na shiga hancinta take ta lalubo kujera ba shiri sbd jirin dayake Shirin dibarta ta ta zauna akan kejeran cikin rudewan rasa abin,

Dauke wuta tayi atake sbd Jin kusada mutum ta zauna batareda tasaniba rintse ido tayi cikin tsananin tashin hankalin rashin sanin meyene Wai yake faruwa da ita ta yunqura da sauri zata tashi taji anriqe hannunta ta tsaya cak tareda saurara abinda takeji na qamshin MALEEK zuciyarta na harbawa da qarfi kaman zata faso kirjinta.

Lullubinta taji an yaye ahankali Wanda yasata yin qasa da kanta tareda rufe idanuwanta sbd koma wanene bazata iya kallonsa Kai tsaye ba tunda shugabantane.

Tsit gurin yayi Babu wani motsi Babu wata magana tsawon mintuna shida ahakan kafin ya miqe ahankali har lokacin kayan daurin auren ne ajikinsa dasukai Masa matuqar kyau suka sake boye manyancinsa tareda bayyanarda asalin kyawunsa abun Kamar almara Amma har wani kyalli yakeyi Wanda ake cewa na anganci.

Ciki ya wucewarsa batareda yace komaiba,

Har lokacin Bata dagoba saidataji shigewarsa ta bude fararen idanuwanta ahankali ta dago Amma takasa bin inda yabi Koda kallo ne,

Hannunta daya Kama ta dago ahankali takai hancinta gabanta yasake wani irin faduwa,

Duk Wanda ya yaye fuskarka daga fitowarka wankan boyo shine yakeda Kai da ikonka Kona aure Kona negestati,

MALEEK???

MALEEK???

Toshewa kanta yayi gabaki daya Bata fahimci komaiba ta miqe har lokacin qafafunta na rawa ta fito dama wannan al'adace Kuma ancikata tunda ya yayeta.

Tana fitowa kallo daya jekadi Tai Mata ta hangi tsagwaron rudu da firgicewa atareda ita da hanzari ta qaraso gurinta cikin kulawa da girma tayi qasa da murya tace"

Ki nutsu kada ki daga hankalinki taron mutane ne keson ganin MUSHRAn MALEEK.

Cak ta tsaya tareda waiwayowa ta kalli jekadi da idanuwanta da zuwa lokacin tuni hawaye suka fara gangaro musu kenen dai ta tabbata maleek ne hancinta da wasi wasinta yazama gaskia.

Da sauri jekadi ta Kara gabanta ta boyeta tana cewa"

Allah ya taimaki mushrah wannan ba girmanki bane bayyanarda hawayenki agabanmu Dan Allah ki kwantarda hankalinki

Allah kuma ya huci zuciyarki da salama idan bazaki iya ganin kowaba ayanzu ko zamu rakaki gurin iyayenki dasuka zo kifara mgana dasu wannan sakone daga Kaleeb Kuma Yana Tayaki murnar tareda sanyawa aure albarka.

Ita gabaki daya batasan lokacinda kuka yazo mataba ba shiri jekadi ta nufi sashen Anneti da ita Wanda yafi kusa daga Nan din suna zuwa Anneti tace akaita kuryar dakinta abarta ta huta tukuna dama zataji abin wani iri tunda batada masaniyar komai.

Take aka sanar kowa ya tafi NURU tana hutawa bazata samu damar fitowaba yanzu Wanda hakan yasa kowa yafara mamakin irin sa'a da gata tareda daurewa da NURUn ta samu na take al'ada tun aranar farko.

Afia ma Bata datazo yau da mamaki Takoma sashensu sbd Bata samu damar ganin NURU ba sbd dolen Dole abarta ta huta tasamu nutsuwa Wanda itakuma tasan NURU na buqatarta yanzu sbd tayi Mata bayanin kada ta tayarda hankalinta idan sun bar Nan komai zai koma daidai zata samu Imran dinta.

Kuka tayi sosai batareda tasan Kona meneneba itadai yanzu iyayenta dataji suna kusa takeson gani Dan sune zasu Mata bayanin komai ta fahimta.

Sai dare lis ta fito cikin wasu kayan dabam da aka kawo Mata akasa tayi wanka ta sauya ta fito dukkanin abindake jikinta qyalli yakeyi tundaga kayan dake jikin nata har zuwa wata siririyar diamond necklace dake wuyanta ta daqyar ta iya cin abinci tareda Anneti suna gamawa Ana kawo Mata farhat data rikice musu kwana biyu na rashin ganin NURU din tana ganin NURU ta fallo da gudu itama NURU sai lokacin taji Dan damar abinda takeji ta rungume farhat din cikin samun nutsuwa tace"

I miss you sweetie.

I miss you more my Lewa ohhh Anneti tace ke mamanace yanzu bazaki taba tafiya kibarniba kaman mum ko??

Wani dum NURUn taji takasa dagowa ta kalli Anneti dake jinsu hakama takasa bawa farhat amsa ita Tama rasa kunyace ta kamata kome?

Riqeda hannun farhat din suka fito daga sashen Anneti jekadi da sauran mabiyanta uku na bayansu suka nufi gurin iyayenta farhat nata yaba kyawu da sauyawar datayi itadai gabaki daya tafiyar kawai take hankalinta baya tareda ita abubuwa da yawane suke yawo cikin kanta wainda suka girmi tunaninta.

Suna Isa dukkaninsu jekadi daga waje suka tsaya daga ita sai farhat suka shiga bayan an wangale Mata kofar tana shiga aka rufe abal da amminsu dake zaune a Palo suka kallo qofar atare fuskokinsu na bayyanarda wani yalwataccen farin cikinsu daya kasa boyuwa itama kasa motsawa tayi sbd kasa gasgata mafarki take kokuwa gata ga iyayenta bayan wasu shekaru take idanuwanta suka ciko da hawaye suna Shirin gangarowa meryam data fito daga gurin padima tana ganin kyakkyawar halitta a tsaye cikin palon ta tsaya cak taqare Mata kallo ta tabbatarda NURUntace a guje tayo kanta tana Kiran sunanta NURU ta ware Mata hannu tareda dauketa cak suka qanqame juna tana jero Mata yarensu Wanda farhat ce kawai batasan me take cewa NURUn ba.

Daqyar suka saki juna kowanne farin cikinsa yakasa raguwa ta qaraso gurin amminta ta rungumeta tareda riqo hannun abal dinta cikin yare da muryarta me sanyi tace"

Abal ubana nagari nayi kewarku fiyeda komai da kowa nayi farin cikin ganinku cikin lafiya da wadata.

Murmushin farin ciki me sauti abal yasaki Yana dafa kanta yace"

NURU 'yata tagari munyi farin cikin ganinki cikin koshin lafiya da nustuwar rayuwa,

Bamu taba farin rayuwaba irin Wanda Kika bamu ayanzu na aurenki da muka gani cikin ahali me girma da daraja.

Amminsu kuwa sbd farin ciki takasa cewa komai sai kallon 'yarta takeyi cikin tsananin so da kauna tareda alfahari Wanda yasa NURUn Jin nauyin iyayenta musamman da abal ya dauko maganar auren yana Mata nasihar hakuri da nutsuwa tareda tawakalli daya santa dasu Kuma yake qara Jan hankalinta dasu akan ta rungumi wannan aure da hannu bibbiyu.

Cikin mamaki ta kalli ammi tace"

Ammi Ina padima?

Ajiyar zuciya ammin tasaki tareda Dan satar kallon abal din kafin ta kalli kofar dakin da padiman ke ciki tace"

Tana can akwance batada lafiya sosai gobema inshallah zamu koma gida sbd aje can abal dinku yasamu maganin Bata Wanda zaiyi Mata tunda ciwon na jiri ne.

Subhanallh"NURU tace cikin damuwa da kulawa kafin ta miqe ta nufi hanyar dakin bayan ta kalli farhat dake maqale da ita tacewa ammi ga farhat Nan su gaisa

Ammin tajawota ta Dora kan cinyarta tana tambayarta tana lafiya?

Tana Isa dakin tashiga Kai tsaye padima dataji zuwan NURUn tasake sassake jiki tana maqale murya tareda qaro nishin ciwonda babusa hadda hawayen da tun safe suka kasa tsaya Mata na abinda ya tsaya ya danne zuciyarta.

Da sauri NURU ta qaraso bakin gadon tana kamo padiman tana Kiran sunanta cikin tsananin kulawa Tama dungumota gabaki daya tana cewa"

Padima meya sameki bayan yau Ina cikin tsananin farin cikin ganinku ku duka.

Marairaicewa padima tayi itama tana rungumo NURUn cikin muryar datayi laushi ta ciwo tace"

NURU nayi tsananin kewarki wadda bantaba sanin haka nake kaunarkiba Saida Kika tafi nakasa nutsuwar zuciya,

Wlh NURU nayi kewarki fiyeda zato ga amed ya yaudareni yace yafasa aurena Amma tsoro yahani fadawasu abal Wanda hakan yasa suka tsangwameni"""kuka tasake Mara karfi sosai tana sake shigewa jikin NURUn tace"

Nidai NURU bansan ya zanyiba mutuwa kawai nakeson Yi sbd itace daidaini,

Dan Allah NURU ki yafemun abinda nayi Miki wlh nayi nadama tunda gashinan Naga ishara irin wadda bantaba tsammani ba.

Cikin mamaki NURU ta share Mata hawayenta tana cewa"

Kidaina kuka padima duk wannan yariga ya wuce Kuma shi amed kansa yayiwa sbd Allah zaibaki Wanda yafisa Inshallah idan har kin tsarkake zuciyarki.

Wasu sabbin hawaye tasaki tana satar kallon kofa tace"

NURU bazan taba daina kukaba sbd kuka yaganni.

Da tausayawa NURU tace"

Kidaina fadar hakan padima.

Padiman zatayi mgn saiga amminsu tashigo wadda takasa zama Jin sun Dade aciki tsaf hankalinsu Bai kwanta da kebewar NURU da padima ba Dan haka Bata Bari padima tasake mgn ba ta janye NURU suka fito inda ta zauna tsakiyar iyayenta suna sake zantawa Kamar kadasu tafi goben jintake Kamar tabisu kosu bita musamman Meryam wadda takeda burin dauka duk tayi aure Amma yanzu Kam ko ita Bata gama tantance matsayintaba bare harta dauko wani ya zauna a qarqashinta.

Saida jekadi taga lokacin kaita gurin maleek yayi tashigo ciki ta sanar musu tayi bankwana da iyayenta bayan anshigo da tarin kayan arziki anjere musu daga Kaleeb da Anneti sai babbar kyautar MALEEK wadda ko ciki baa shigo da itaba saidai idan sun Isa gida akai musu.

Dazata fice harda hawayenta padima ta riqo hannunta tana hawaye qasa qasa tace"

NURU ki taimakeni Banda lafiya mutuwa zanyi idan Ba'a nemamin magani ba ciwon zuciya me qarfi nake fama dashi tunda dadewa kullum bana iya bacci ki taimakeni ki tafi Dani ki nemamin magani NURU.

Kallonta NURU tayi a Dan tsorace tace"

Tun yaushe padima shine Baki fadaba idan yayi tsanani wani Abu yasameki fa?

Kallon abal tayi cikin damuwa da kulawa tace"

Abal meyasa ba'a fadamunba ko a wayane da anfadawa jekadi ta fadamun ta waya wannan ciwon ba abun Wasa bane zantambaya afia Inshallah zamu tafi da padima.

Wani mugun kallo ammi tayiwa padiman data bushe idonta ba wani alamar qarya ko yaudara atareda ita abal ya hade fuska tsaf yace"

Kije NURU Allah ya albarkaci rayuwar aurenki ya Hana duk wani Wanda beda fatan alkhairi sa'ar rabarki,

Padima bazata bikiba kowane irin ciwone zamu nema Mata magani Inshallah.

Kallon padima NURU tayi tana Bata hakuri ta ido da cewa tayi hkr Inshallah ta Mata alqawarin dawo da ita hannunta ta nema Mata lafiya idan nasu abal din baiyiba.

Da haka aka wuce da ita tabarsu suna binta da addua suka wuce ciki Babu Wanda yaceda padima dake tsaye idanuwanta sunyi jajir zuciyarta na wani irin zafi da harbawa.

Kai tsaye sashensu datake dasu afia aka maidata sbd saqon maleek daya Isa gurin jekadi ta hanyar Anneti cewar basai ankar NURU gurinsaba yau din gobe zasu koma,

Tana Isa ta tarar da Afia zaune tagama hada musu kayansu tsaf sbd suma dad ya sanar cewa gobe zasu koma dama amatse take dasu bar Nan din sukoma Kota samu kanta tayi tunanin abinda yakamata.

Tsayawa tayi daga bakin kofa tana kallon afia da duk damuwa da sanyin jiki ya bayyana atareda ita taji tausayinsu su duka ya dawo Mata sbd tafi kowa sanin burin afia akan dawo da mahaifiyarta gidan MALEEK gashi yanxu su duka qaddara ta bullo musu ta inda basa zato.

Qamshin NURUn daya cika gurin yasata dagowa sukai ido biyu kowa yakasa motsawa suka tsurawa juna ido kafin Afia ta taso ahankali ta qaraso gaban NURUn ga mamakinta saitaji afia din ta rumgumeta tana cewa"

Thank God you're back NURU nayi kewarki.

Mamaki yasata daskarewa batareda tace komaiba ko motsawa.

Afia kuwa tarigada tasan zaman aure ko rayuwar aure tsakanin NURU da dad dinta bamai yiyuwa bane har abada Dan haka Bata sawa ranta damuwaba Dan duk duniya Babu Wadda dad dinta zaiso idan ba mum dintaba Dan haka tasan shima idan har aka koma Babu wani maganar aure dazaibi hakama NURU tana komawa Imran yadawo bazata yarda ba Imran zataso komawa Dan haka ta daure tacire damuwar komai aranta.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN qNUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899*_Mamuhgee 22_*

Washe gari tunda safe sakon Anneti na gayyatarsu cin abincin safe tareda ita ya iso musu suka shirya dukkaninsu itadai jekadi dama tunda safe tazo da kayanda NURU zata saka tana Palo takasa ta tsare Dan kuwa komai daya danganci NURU yanxu saiya biyo ta gurinta kafin ya isa gun NURUn.

Da kanta tashirya farhat kafin itama ta shirya cikin doguwar royal gown dinsu me adon golden stones da sequence rigar ta tafine straight shiyasa ta fidda shape din tudun qirjinta zuwa shafaffen cikin har fadin hips dinta saidai adon sequence ne ya 'dan boye bayyanar shape din nata Sosai Sosai Amma duk da hakan yafito sai wuyan rigar dakeda Fadi sosai ta Sanya qaramar siririyar sarkar gold ta doro gyalen rigar akanta ta rufe gashinta dake daure Yana qamshin turaren hayaqin da akai Masa ta fito afia nabinta da kallon yaba kyawun datai Wanda duk be daga Mata hankaliba tunda dai duk abanxane suka fito jekadi na bayan NURU sai sauran masu Binsu suna bayansu kawunansu duk a soke kasa.

Afia ce ke kokarin janta da firar karatunsu da tun shekaran jiya yakamata su koma Amma Basu komaba itama NURUn abin sai lokacin yafado Mata musamman da tafara zuwa Court itama afian tana zuwa asibiti sama sama sbd karatun nasu.

Tun kan su qaraso aka sanarda zuwansu suna isowa suka tararda askarawan maleek kusan guda shida a sassan Anneti din afia na gani tasan dad dinsu na ciki ita Kam NURU batasaniba tunda Babu abinda tasani anan din Dan haka Babu tunanin komai dayazo Mata suna isowa aka wangale musu qofa Ana yiwa NURU gaisuwa ta musamman kafin aka juyo akaiwa AFIA da farhat suka shige.

Suna shiga palon farko duka sauran Yan rakiyarsu suka tsaya anan dagasu se jekadi suka wuce har cikin asalin palon hutawar Anneti suna shiga jekadi ta zube qasa cikin bada girma tace"

Allah yaqara MALEEK kyakkyawar zuciya data fuska,barka da fitowa.

Da hannu kawai ya amsa tareda juyowa Jin muryar AFIA na gaishesa cikin girmamawa itama.

Farhat kuwa kusadashi ta zauna tareda riqe hannunsa tana cewa"

Good morning Daddy.

Da sauri jekadi ta Raba gefen NURU data kusan sanqamewa a tsaye sbd shammatarta da abin yayi Sam ko kadan ko qamshinsa batajiba batama taba saka ran zata ganshi ananba.

Kallon afia yayi da idanuwansa masu haske cikin sautinsa na kamewa ya amsa Mata tareda cewa"

Kuna lafiya?

Gyada Kai tayi tana cewa"

Yes Inshallah.

Ahankali NURU ta tako ta qaraso ciki ta tsaya ta gefen NURU cikin sanyin murya batareda ta kallesa ba kanta na 'dan qasa tace"

Barka da fitowa.

Tsit gurin yayi kafin ya dago ahankali itama ya kalleta Wanda yayi daidai da fitowar Anneti tasaki murmushin ganinsu ta nufi hanyar dining room tana cewa"

Farhat zo ahau table cin abinci Afia zokiyi serving Dina.

Dan kallon NURU afia tayi ta sauke idanuwanta akan budaddiyar gaban rigarta daya bude sosai Dan idan har ba shedan ne yake Mata gixoba tana hango saman nonuwar NURUn kadan ta juya ta wuce tana Dan waiwayowa harta shige dama farhat ita tuni tashige.

Dauke idonsa yayi daga kanta tareda Miqewa baice komaiba ya wuce ciki.

Ajiyar zuciya ta sauke a boye sbd idan har akwai abinda yafi takura da firgici tashiga sbd taji idanuwa akanta saidai Babu tabbacin nasane Kona afia.

Kokarin zama takeyi taji Anneti takira sunanta tafasa ta nufi hanyar dining room din a sukwane tana Dan sauke Kai tana shiga Anneti ta nuna Mata kusada ita ta qaraso ta zauna kirjinta na bugawa sosai sbd duk wannan abin wani iri takejinsa Yana Mata nauyi sbd zuwan komai lokaci daya.

Afia ce tayi serving kowa Nan suka hau cin abincin Babu me mgn musamman itadai gabaki daya bataci abinda ya wuce Loma hudu ba sbd amatuqar takure take.

Maleek ne yafara tashi ya fice kafin Anneti saisu daga baya suna fitowa tuni aka fitarda komai na tafiyarsu suka dunguma zuwa ainihin fadar NEGES inda yayiwa NURU kallon tsaf kafin ya kalli MALEEK Dan kuwa yatabbatarda NURU bazatayima sa'ar afia ba Amma maleek ya aureta.

Yanaga Dole akwai dalilin dayasa MALEEK auren wannan yarinyar wadda akace asalinta ma 'yar bawan kaleeb ne,

Idan har da akwai dalili saiya bincika yaji Dan kuwa wannan karon bazai dagawa MALEEK qafaba Dan Bai shirya sauka mulkiba ya bawa MALEEK kujerarsa Dan haka zai binciki asalin ita yarinyar da zuriarta dole baza'a rasa abinda zaiyi amfani dashiba daga ciki ya rusa maleek gaba daya saiya mallaki kejeran da hujja.

Kyauta me girma yayiwa NURU tareda su afia kafin aka fito da NURU sai alokacin kowa yaganta 'yan jaridu kuwa sukaita dauka wasuma a sace suke daukar hotunan hadda maleek batareda sun saniba.

Kayan aure da aka bawa NURU Dole saidai aka barsu anan a hannun jekadi data riga yanxu tadawo gizah sbd sassan NURU daza'a fitar a tsara itace zata zauna Dan duk lokacinda NURU zataxo tananan Dan haka kayan acan sassan NURUn za'a ajesu.

Har airport jekadi ta rakasu tana sake jaddadawa NURUn wasu bayanan na cewa wannan aure ba saki ba warwarewa,aurene daya qullu har abada Dan haka ta nutsu ta rungumi abinda Allah yabata ta riqe da kyau tareda kiyayewa Banda Kuma yarda da kowa sbd za'a iya biyowa ta gurinki a cutatar da maleek.

Itadai saurare take kawai Dan batamasan wane turn rayuwarta zata daukaba daga yanzu Kuma.

Harsuka shiga jirgi suka miqa tana cikin tunanin yanda zatai rayuwa agidan amatsayin matar dadynsu afia gashi haryanxu bataga wani Alama daya nuna afia bataji dadin abinba ta bangare daya ga Imran datasan yanacan Yana jiran dawowarsu batasan me zatace masaba ya fahimta.

Sai dare sosai suka sauka motocin daukarsu suna airport jiransu Mr Omar sai wani rawar jiki yakeyiwa NURU Wanda yasa MALEEK yimasa kallo daya ya nutsu ya daina aka barta cikinsu afia kamardai yanda suka Saba tun ada.

Suna isowa gida su mum Sarah suka tarbesu suna zubewa yiwa MALEEK barka da dawowa Kai tsaye ya wuce samansa bayan ya amsa musu da hannuwa.

NURU suka jiyo sunawa barka da dawowa taredasu afia wadda tayi gaba sbd sai yanxu taji tasamu nutsuwa harwani ajiyar zuciyar nutsuwa take sakewa farhat mum Sarah takama hannunta suka nufi dakinta Dan wanka da hutawa.

Koda NURU tashigo daki afia harta shiga wanka Dan haka itama a qage ta cire kayan jikinta ta dauko towel ta daura tana warware gashinta afia ta fito tana gama warwarewa ta nufi toilet din tashige ta sakarwa kanta ruwan zafi tana rufe ido itamadai kusan dawowa gidan yabata nustuwa.

Tana fitowa ta Sanya kayan bacci ta saka jallabiya akai tayi sallolinta tana gamawa ko ruwa Bata nemaba ta cire jallabiyar ta haye gado ta shige bargo sai bacci Wanda afia tuni tayi nata baccin.

Washe gari sai guraren 11 dukkaninsu suka fito kowanne a shirye Banda farhat da har ankaita school sukuma sai zuwa gobe zasu fara zuwa.

Kai tsaye dining suka nufa suka zauna breakfast afia na fadawa nuru suna buqatan zuwa shopping sbd kusan turarukansu da mayukansu dasu shower creams dinsu duk sunyi qasa gashi ita tana buqatan wasu books na karatunta data siya tun last month sun iso ankirata tazo ta karba.

Ruwa NURU Tasha ta aje cup din tana cewa"

I also need some books zanbincika idan munje.

Miqewa tayi ta nufi daki tana shiga wayarta na ringing ta qarasa ta dauka cikeda mamaki da tsoro ganin Imran ne me Kiran ta ajiye wayar tareda kifewa hankalinta na neman tashi,

Me Imran keyine dazai kirani bayan nasan yariga yasan abinda yafaru.

A musulunce a al'adance duk laifine me girma Amma duk da hakan zatai magana dashi tafada Masa Dole hakuri zasu dauka haka Allah yaso Babu aure atsakainsu.

Tana daukan wayar tana tsinkewa sai kawai ta ajiye tareda kashe wayar gaba daya ta nufi closet dinsu ta janyo dogon pencil jeans da riga doguwa har qasa saidai daga qasan a tsage take har cinyoyi Wanda yasa ake Dan ganin jeans din idan tana tafiya ta janyo veil ta daura harta dauki wayarta sai ta fasa ta ajiye ta juya ta wuce.

Afia Dama a shirye take suka fito afia da kanta zataja motar yau suna sako qafafuwansu waje NURU ta tsaya cak wani tunani Yana fado Mata na sanin yanzu fa ita Matar aurece batada ikon fita kona kanta.

Waiwayowa afia tayi ta kalleta tana cewa" lafiya Kika tsaya?

Numfashi NURU ta sauke tana basarwa kada afia tagano dalilinta saita riqe gefen cikinta tana Dan yamutsa fuska kadan tace"

Marata tana ciwo inaga period Dina zaizo kije Bari nakoma na kimtsa najira zuwansa Dan kowane lokaci zaizo.

Da wani irin kallon mamaki afia tace"

Amma ai ba lokacin period dinki bane.

Sake yamutsa fuska tayi tace"

Eh ba lokacinsa bane Amma inaga abubuwan da akaita banine a gizah dama tun can sunata sani ciwon ciki.

Kallon mamaki da tsoro afia Tai Mata takasa cewa komai sai kawai ta juya tana cewa"

Shikenan ki koma Ni zanje nadawo.

Juyawa tayi Takoma ciki tana shiga Palo tana ta sauke ajiyar zuciya ta nufi daki ta cire rigar ta sauyo da qarama Mara kauri tabar wandon ta nufi kicin direct Dan aikin abincin Rana Kota samu abinyi dazai hanata zaman tunani.

Tanayi su Fana da mum Sarah na tayata harta gama tafito ta jera a dining tana baro dining din saiga farhat andaukota daga school tun daga Palo tana shigowa tace"

Aunt NURU yau akwai drwing dazamuyi babba na _Eiffel tower_ competition ne inason nazama 1st.

Yes yes sweetie Inshallah zamuyi shi babba me kyau Wanda zaisa ki cinye afterall who's gonna help you drw????

Da qarfi tana tsalle tace"

Our beautiful Aunt NURU.

Hmmn that sounds like a bribe sbd bantaba Jin kince our NURU ba saidai kice your NURU to yau kenan kinyadda keda afia.

Suna qarasawa kofar shiga palon kurya farhat na cewa"

No not afia,Ina nufin me and my dad since you are his wife now.

Tsit NURU tayi sakamakon hada ido datayi da maleek dayake saukowa tayi saurin dauke kanta tana riqo hannun farhat wadda ta kwace tayi gurinsa tana cewa"

Daddy barka da fitowa.

Kama hannunta yayi Yana nufar hanyar dining Yana cewa"

Hw is daddy's little princess?

alhmdlh dad but today I have.....kallonta yayi cikin nustuwa yace"

Go and freshen up first kafin kizo naji menene.

Da gudu tayi ciki tabarsu tsaye sai alokacin NURU tadan gyara tsayuwa tana rage murya qasa qasa tace"

Barka da fitowa.

Kai kawai ya gyada Mata ya nufi dining Wanda yasata Dole binsa Dan serving tunda dai Babu kowa agurin.

Zama yayi taqaraso cikin Jin nauyin kayan dake jikinta musamman dayake kujeransa tana seti da inda take tahowa tamafi Jin kunyar rigar dake jikinta din sbd Ana ganin yanayin kalar bra dinta fara ta ciki sbd transparent ce Amma ba sosaiba Dan Bata tana tunanin har lokacin Yana gidaba.

Tana qarasowa tafara serving dinsa cikin nutsuwar Dolen data tattarowa kanta.

Tana gama zuzzuba Masa ta nufi kicin ta hado drink dinda tasan yanasha tareda ruwa masu sanyi Amma ba sosaiba takawo ta aje tareda zuba Masa drink din a cup ta Dan dago kadan ta kallesa zatai magana ta rude ta kasa sbd kallon dayayi Mata yasata neman rudewa hartana neman fada Masa Bata saniba Saida ya tareta da hannunsa daya Wanda ya ba tsammani ya sauka daidai kan shafaffen cikinta daga ita harshi da saida suka kalli juna ya dauke Kai Yana kamewa tareda janye hannunsa tayi saurin juyawa tabar gurin jikinta na neman sakewa sbd duk duniya Babu Wanda yataba taba mararta sai yau gashi abin kamar na tsautsayi batasan yaushe rigarta tadan dagaba Dan kuwa direct taji saukan dumin hannunsa akan skin dinta da gudu taqarasa daki ta nufi toilet da gudu sbd har wani fitsari fitsari takeji na shiga rudu.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899*_Mamuhgee 23_*

Abdul-rahman (sudais) is a young boy who's so passionate about putting the Holy Qur'an into memory. Please help this little boy grow his YouTube channel *ABDUL-RAHMAAN* you got nothing to lose in sha Allah thank you and Jazakumullah khair□□

https://youtu.be/WWIGq5Jbtb0

Do subscribe please

****

Kodata fito kasa zuwa dakin farhat tayi sbd gabaki daya kafafunta sunyi sanyi toilet dinma tana fitowa ta zube kan gado a kife tana sauke ajiyar zuciya a jejjere Dan Kamar har lokacin tanajin dumi da softness na hannunsa akan mararta.

Bude kofar da akaine yasata Dan juyowa ahankali taga afia ce ta tashi zaune da sauri tana cewa"

Princess tadawo.

Dariya afia tayi tana qarasowa ta aje shopping bags din dake hannunta tace"

Harkinji sauki kenan?

Waskewa NURU tayi da cewa"

Eh" tajawo kayan tana budewa Dan mantar da kanta tunanin abinda yafaru din.

Duk abinda take buqata afian tasiyo Mata ta tashi ta tattara kayan tasa musu su a inda suke aje kowanne tayi sallah tazo ta zauna suna duba wani sabon Francie's program na likitoci da lawyers tareda engineers a laptop.

Sai la'asar lis tayi wanka ta sauya cikin White three quarter da farar top me laushi ta fita tayi dakin farhat afia tabi bayanta da kallo sbd kusan kome NURU tasaka kyau yake Mata inama ace Imran dinta tafara aura dashine zata more rayuwa sbd yanda yake Sonta Amma dad dinta bazata taba samun so agaresaba har abada sbd mum ce kawai a zuciyarsa.

NURU na shiga dakin farhat ta taddata itama sanye da fararen qananun Kaya tana jiranta har ta fidda kayan drwing din Nan suka baje suka fara.

Sai bayan magriba suka gama

Farhat ta dauka da gudu taje nunawa dadynta ya duba Masu idan sunyi daidai Amma bayanan kusan so uku tana komawa bayanan ta karba wayar NURU ta saka numbernsa dake cikin kanta ta Kira Bai dagaba tukuna ta hakura anan dakin sukai sallarsu suka kunna cartoon suka baje abinsu adakin suna kallo Saida lokacin cin abincinsu na dare yayi suka fito zuwa dining suka zazzauna sukaci suka koshi suka shige anan dakin farhat NURU tayi barci Bata koma nasu ba Dan dama hakan takeyi wani lokacin.

Qarfe goma Sha biyu da mintuna ya nufo dakin farhat din wadda kusan kullum idan haryana gida saiyazo ya dubata da daddare sbd qarancin shekarunta musamman yau dayasan saitayi nemansa sbd zanenta yaduba Mata Dan haka ya nufa dakin Kai tsaye ya bude yashigo tareda rufe kofar har zai kunna wuta gudun kada ya tadata yasa Bai kunna dinbaya qaraso bakin gadonta tareda zaunawa bakin gadon ya Kai hannu yakunna bedside lamp kadan haske ya 'dan bayyana yana waiwayowa yaganta itace kwance abakin gadon farhat na quryar gadon ya sauke sahirtaccen numfashi Yana kallon kayan baccin jikinsu itadai farhat komai iri daya riga da guntun wando royal blue bacci suke duk su duka hankali kwance.

Dan qara rage hasken wutar yayi sbd kaman hasken zai damesu yajanyo musu bargo ya lullubesu ko Gama janye hannunsa baiyiba NURU tasa kada ta yaye lullubin Dan dama Bata cikason rufaba cikin bacci.

Fuskarta yayiwa kallon minti biyu ya dauke Kai tareda Miqewa ya nufi hanyar ficewa harya taba kofa zai fita saiya tsaya tareda Dan rufe ido ya bude tunanin Dole wani

daga cikin masu aiki zasu tadasu da asuba yasashi dawowa yasake Jan bargon ya rufa Mata saidai Yana dauke hannu takai hannu cikin baccin zata yaye yakai hannu zai danne hannuwansu suka sauka atareda nashi akan nata Wanda Kai tsaye yasata bude manyan idanuwanta dake cikeda bacci ta dagosu.

Kasa yadda tayi da abinda tagani tasan mafarkine kawai take Dan haka saita juya hannunta tasanya tafin hannunta tana sake tattaba hannunsa Dan Jin tsananin taushinsu ta lumshe ido baccinta na fizgarta har lokacin tafin hannuwansu na hade.

Dan sarquwa yayi da yawu kadan yasaki Dan qaramin tari Mara dogon sauti Wanda yasata bude idanuwanta duka da qarfi tareda zaburowa daidai motsawar farhat sai yayi saurin dafeta Takoma kwance sbd kada ta tada farhat ga farhat din da surutu zata iya jeho wani zance akan hakan.

Kallonsa takeyi face to face akaro na farko a rayuwarta zuciyarta na harbawa a tsorace yayi Mata kallo daya da idanuwansa da yau suka shiga daidai cikin nata take taji jikinta ya sake gabaki daya sai kawai ta sake a jikinsa ya hadiye wani mugun yawu a maqogaransa Wanda yasata kallon moqoshinsa sbd yanda Adams apple dinsa yayi sama yayi qasa ta maqoshin nasa.

Miqewa yayi tsaye yaraba jikinsu sbd asthma dinsa dayakejin kaman zata tashi ya juya ya fice adakin yabarta kwance Bata iya ko daga hannunta sbd mutuwar jiki saidai ido databisa dashi cikin wani irin yanayi na kunyane ko na menene ta Bata saniba illa dai Abu daya data tabbatar ayau shine kyawun da Allah yabasa Wanda ko rabinsa 'yayansa Basu daukoba cikin yama manyanta kenan...daganan baccinta ya watse har kusan asuba Bata samu baccinba gashi gobe tanada zuwa makaranta Dole ta rintse idanuwanta Dan tayi baccin Kona Dole ne.

Qarfe shida ta farka ta sauko gado tashiga toilet tayo alwala ta tada farhat sukai sallah ta fice.

Tana shiga dakinsu ta tada afia sallah kafin ta fito ita ta fice zuwa kitchen aikin breakfast.

Tana gamawa ta jere a dining takoma daki tayi wanka tashirya cikin black riga da wando ta doro doguwar kimono fara akai ta daura black scarf me kauri tafito sukayi breakfast itadasu afia da farhat suna gamawa kowa yaje ya dauko jakarsa suka fito.

Da Mr Omar suka fara cin Karo tsaye jikin motar dazasu tafi da ita makaranta tareda sabon driver cikin girmamawa yana Dan taudasa harshe cikin sakin fuska yace"

Gud morning Mrs MALEEK.

Gud morning princess.

Kallonsa AFIA tayi Jin abinda yace itadai NURU sidadawa tayi ta wuce Jin kalmar tamata girma ta shige mota tana kunna wayarta da Imran yahanata sakat da kira saigashi tana kunnawar kiransa na shigowa ta dannata silent tana Dan kallon gefen Mr Omar dake tsaye idanuwansa kuwa quru akan wayarta tana juyowa ya dauke Kai Yana cewa"

Adawo lafiya.

Suna barin gidan ta sauke ajiyar zuciya tareda daukar wayar data kusa katsewa cikin sanyi da rawar murya na rasa abin cewa da damuwa tace"

Hello im ka.....da wata gigitacciyar ajiyar zuciya ya katseta yana cewa"

NURU labarin aurenki Bai kasheniba duka ya kashe rayuwata gabaki daya amma rashin daukan wayarki zai kashenine sbd.....

Da siririyar murya tayi saurin katse zancen da cewa"

Kariga kasan komai Im tayaya zan iya daukan wayanka yanzu inajin tsoron hakan.

Kasa danne abinda yakeji yayi cikin wata wahalalliyar murya idanuwansa na cikowa da hawayen zafi da ciwon da zuciyarsa kemasa ya bude Baki dakyar yace"

NURU shin da gaske kin auri MALEEK sbd wlh nakasa ji nakasa yarda da komai inason ji daga bakinki Dan kuwa nasan nikadaine a zuciyarki nakasa yadda da hakan NURU na.....

I'm sorry im bansan mezan iya cewaba Amma dai koma menene gskiyan shine aure dai andaura Wanda Koda bada son Rainaba Dole zan kiyaye dokan aure Dan Allah im kayi hakuri komai yafaru ne kaman daga sama,nasani kana tsananin Sona haka Nima Ina.....shiru tayi Idanuwanta na cikowa da wasu irin hawayen karyewan zuciya sbd Jin sautin kukansa dake fita ahankali cikin karyewa da zuciyarsa keyi taji zuciyarta ta karye itama hawayenta na gangarowa takasa karasa mganar ta kashe wayar sbd kukansa reras dake ji cikin qaramin sauti.

Kasa cewa komai afia tayi tanajinsu sbd tausayinsu datakeji musamman im Wanda tafi kowa shaida irin so me girma dayakewa NURUn.

Farhat kuwa riqo hannun NURUn tayi tana kallon hawayen daya gangaro Mata tace"

Aunt NURU meya samu uncle Imran din Naga kina kuka.

Dauke kanta tayi tana goge hawayenta da tissue ta Dan qaqalo murmushin yaqe tace"

Ba komai kafiyansa kalau he's just missing you princess farhat.

Murmushi tayi tace"

kema Yana missing naki ko??

Shiru sukayi Babu Wanda yasamu damar cewa kalaba har suka Isa aka ajeta suka wuce Dan su sunada Dan nisa.

Suna isa makarantar Kai tsaye ladies washroom ta nufa ta nutsar da kanta tareda bude kanta kwakwalwarta tasamu damar haddace abinda take nanatawa kanta na cewa tanada haqqin auren wani akanta yanzu dokar Allah na kanta.

A dauki mintuna aciki kafin ta samu 'yar nutsuwa ta gyara fusakrta ta fito tana duba wayarta dake ringing ga mamakinta saitaga numbern ta Ethiopia ce Kiran daga gidane kenan da hanzari ta dauka tana tafiya cikin sa'a kuwa padima ce cikin tsananin farin ciki tace"

Hey padima hw are you??

Dif padima tayi sbd batasan abinda NURUn tafada meyake nufiba tana danne baqin cikinta tayi kasa da murya cikin tsananin damuwa tace"

Nuru kina lafiya kuwa?

Ya gida?

Yasu farhat?

Lafiya kalau kowama Yana lafiya,yayasu abal da meryam Ina ammi?

Sake qasa da murya tayi tace"

Lafiyansu kalau nuru.

Kefa padima kina lafiya dai ina?Kuma Yaya jikinki?

Antabo Mata inda take jira sai kawai takasa riqe kukan 'dacin ran datakeji tsawon kwanaki cikin qaramar sheshekar kuka tace"

NURU wlh bansamu saukiba Ni kilama ciwon ajaline abun yamin tsanani Kuma Babu wani magani dasu abal ke bani hasalima haryanxu fushi sukeyi Dani tun kan maganar cikin Nan da Babu nidai Dan Allah NURU kitaimekeni inason gyara rayuwata sbd Nima na faranta ran iyayenmu.

Sanyi jikin NURU yayi ta danyi shiru na seconds kafin ta sauke numfashi me zafi asanyaye tace"

Padima kidaina kuka Inshallah Zaki samu lafiya bazan Bari wani Abu yasamekiba da yardan Allah,

Yanzu Ina makaranta idan nakoma gida zanyi shawaran zuwanki na tambayi AFIA muji idan da hali sai jekadi takawoki Nan anemamiki lafiya.

Da qaramar muryar kuka tace"

Ngd sosai NURU Dan Allah kadaki manta ayi magana da wuri kada abin yayi qarfi fiyeda da.

Tana kashe wayar tafara tunanin Yaya zatayi yanzu da wannan sabuwar damuwar Kuma,da haka ta shiga class.

Qarfe biyar saura suka dawo amatuqar gajiye Dan ko zama batayiba ta aje Jakarta ta tareda zare kimono dinta ta nufi dakin farhat dan wanka take tsananin buqata da fitsari dayake neman matsarta gashi AFIA tarigata shiga toilet bazata iya jiraba.

Tana Shiga dakin farhat bata ciki Kai tsaye ta tube tareda janyo qaramin towel din farhat ta daura tafada toilet.

Ajiyar zuciya ta sauke lokacinda ruwa masu dumi suka sauka jikinta sbd yau Bata zauna sosaiba sbd zuwanta biyu kotu yau ga damuwar padima data Imran Amma yanzu taji sauki komai datayi wankan Nan.

Farhat yau da zazzabi tadawo daga school sbd bayan drwing din da jiya aka bawa kowa yayo yau games sukayi ita tana cikin masu football Wanda yadata haki da yawa Amma sbd ba qura asthmanta be tashiba saidai ta kwaso zazzabi me qarfi Wanda tun a school tayi collapsing aka Kira MALEEK Koda suka Isa ta farfado Amma Kam tanajin jin zazzabi sosai siadai yanzu zazzabin ya sauka gabaki daya saitasamu bacci ya dauketa Dan hakane yasa Koda suka dawo gida da ita ganin su afia basanan yasa yatafi da ita samanshi yanzu ta balcony daya hango dawowarshi saiya daukota ya dawo da ita dakinta danta samu kulawa gurinsu afian sosai.

Fitowa tayi tana gyara zaman towel din farhat dayayi Mata kadan tana sauke ajiyar zuciyar nustuwar data samu tana qarasowa tsakiyar dakin taganshi tsaye bakin gadon da farhat ke bacci wata mummunar razana tayi ta damqi towel din da qarfi Jin zai sabule Mata ta sake dagowa da sauri ta kallesa cikin tsananin tsoro.

Tsabar rudewa rigarta dake gefen gadon ta nufo da sauri zata dauka kafin ta iso yabar gurin batareda yabari ta qaraso gurinba ya fice dakin gaba daya Dan towel din ko Gama rufeta baiyiba sbd qanqantarsa.

Zamewa tayi bakin gadon farhat tana kallon kanta tareda dafe goshinta tanajin wani irin yanayi na damuwa.

Zarar kayanta tayi ta fice da sauri ta fada dakinsu ta Sanya kaya tayi sallah ta zauna gefen afia batareda tace komaiba ta zurfafa tunanin wani Abu dayakasa fita cikin ranta afia na lure da ita Amma batace Mata kalaba.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899[9/21, 9:10 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 24_*

Saida safe dukkaninsu sukasan farhat batada lafiya Koda suka Isa dakinta tana zaune jikin dad dinsu Yana zaune bakin gadonta sanye da black jallabiya ta maza me tsananin taushi sai kyallin maiqo takeyi alamar ta masu abun duniya ce.

Itace agaba ashigowa kafin Afia Amma tana ganinsa tayi slow afia ta wuceta tana qarasa dayan gefen ta farhat din ta zauna tana cewa"

Gud morning dad,

Farhat bakida lafiya bamusaniba mum Sarah ke fada Mana yanzu da safen Nan.

Dago fuskarsa yayi dake fayau dinta sai wani daukan ido take ya kalleta da idanuwansa Wanda itama daidai shi ta sata kallo suka hada ido tayi saurin sauke idonta muryarta da wani irin salon sanyi dabata saniba tace"

Barka da safiya.

Har lokacin kallonta yakeyi

Tasake dagowa ta saci kallonsa suka sake hada ido sai kawai tunanin ganin dayayi Mata jiya da daddare kusan Babu komai a jikinta take wata matsananciyar kunya ta mamayeta batasan lokacinda ta rufe idoba ta fita da gudu Kamar karamar yarinya.

Da mamaki afia ta dago ta kalli kofar kafin ta juyo ta saci kallon dad dinta da bataga alamar ma yasan da NURU tashigo bare tace kofar yake kallo ta maida kallonta kan farhat tana cewa"

Sorry baby aunt NURU taje Sanyo kayane sbd batasan dad na Nanba ta taho da sleeping dress ajikinta shine Takoma ta sauyo nasan kin matsu tazo gurinki ko baby?

Gyada Kai farhat din tayi tana kwantawa jikin afia din tace"

Afia I saw mum yesterday a school dinmu she was there before I fainted.....

Da sauri AFIA ta dago ta kalli farhat din tareda kallon dad dinsu da sauri shima saidai ko Gama juyowa batayiba ya miqe ya fice kamarma baiji me farhat taceba afia tabi bayansa da kallo kafin tadawo da kallonta kan farhat cikin mamaki tace"

Baby dagaske Kinga mum?

Gyada Kai tayi tana kallon afia din tace"

Eh naganta tazo kafin ta iso gurina I fainted daganan shikenan saidai Naga dad kawai.

Wani yawu afia ta hadiye kafin ta ta danne mamakinta da farin cikinta tana miqewa tace"

Ok baby Bari naje naturo Miki NURU tazo tayi Miki wanka da brush saita Baki abinci akwai abinda zanyi yanzu na gaggawa ok baby.

Wucewa tayi ta fice da sauri ta nufi dakinsu ta janyo doguwar riga tasanya akan kayan baccin jikinta ta dauki wayarta da sauri ta fice ta nufa library dinsu Dan Yin waya.

Doguwar kimono NURU ta doro akan kayan jikinta na bacci kafin ta wuce ta nufa kicin ta hadawa farhat Dan guntun breakfast sharp sharp ta dauko a qaramin faranti ta nufa dakin tana adduar Allah yasa ya fice.

Ganin baya dakin yasata qarasowa da wuri ta ajiye tray din tana cewa"

Sweetie kiyi hkr bamu San bakida lfy ba,jiya ma anan nayi wanka Amma banluraba sbd hankalina yatafi wani gurin dabam na.....kasa qarasawa tayi tana sake tunano abinda yafarun sai kawai ta sauya zancen da sakin qaramin murmushi tana cewa"

Ok sweetie muje ayi brush kizo ga breakfast sai asha magani.

Tayar da ita tayi suka nufi toilet din suka shige.

Harsuka gama komai har wanka da Shirin farhat din kafin suka fito zuwa nasu dakin itama NURU tayi wanka ta shirya cikin doguwar riga suka fito Palo ta kunna Mata cartoon takoma ciki tayi Shirin makaranta tazo ta fice har lokacin afia Bata shigowaba tanacan.

Tsaye take cikin libry din idanuwanta sunyi jajir sbd tsananin baqin cikin dake mamaye da zuciyarta ayanxun datake waya da mum dinta cikin tsananin sanyin murya da sarewa tace"

Haryanxu Babu 'yayanki acikin ranki kenan?sbd wani burinki na duniya mum kike fadar haka? Tayaya kike tunanin dad zai iya rayuwa ahaka for how long kikeso yayita jiranki?mum please ki.....

Cikin iko da muryarta me taushi ta katse afia da cewa"

Zandawo wa MALEEK Amma ba yanxuba haryanxu akwai abubuwan dake gabana,afia kinada naci akan zance daya koyaushe bayan nace Miki zandawo Amma ba yanzu ba idan akwai abinda yafi cancanta yanzu dakiyi shine ki raba maleek da yarinyar daya aura Kuma tabar gidan gabaki daya sbd matuqar tananan koya saketa bazan iya dawowaba infact inason sauyin gida tunda harta zauna a wannan gidan koba komai idan haryanzu kunason aikinta zaku iya zama da ita acan Amma dai Ni Kam a sauyamin gida musamman farhat da lalurorinta sunyi yawa yau ciwo gobe lafiya....

Cikin mamaki,takaici da baqin ciki daya Gama kashe afia tabude Baki tace"

Mum shin akan abindake gabanki kika watsar da 'yayanki musamman Yar qanqanuwa Kamar farhat harkina cewa lalurarta yayi yawa?

Ciwone fa atareda ita Wanda Allah ne ya Dora Mata ba ita tadorawa kantaba, badan NURU ba da yanzu dukkanin mu munshiga wani hali and now kina cewa akoreta?a koreta kokuma mubita can mu zauna kenan kin yafemu?

Mum inasonku keda dad duka saidai I'm sorry to say this to you yau nafi son dad ayanzu fiyedake da duk wani tunaninki Dan kuwa koba komai shi yasan haqqinmu 'yayansa akanshi Yana bamu Dan haka mum tunda haryanxu Bakida mijinki da yayanki aranki inaga zaifi idan na karbi hakan na runguma nakuma amince Dan kuwa na tabbatarda dana amince da hakan tuntuni da bazan cutatu hakaba,

Na lalata rayuwar mutum uku sbd hope din Zaki dawo saidai Ashe mafarkinane kawai....hawayen baqin ciki me tsanani ne suka gangaro Mata ta kashe wayar da qarfi tareda wurgi da ita sbd Jin mum din na cewa"

Afia ke yarinyace haryanxu bazaki ganeba Dan haka please don't call again idan Baki shirya daukan abubuwan dazan fada mikiba.

Kuka me qarfi ta sake tareda daukar wayar taqara kwadawa da qasa tana qoqarin sulalewa qasa cikin kuka taji hannuwan dad dinta duka biyu ya riqota Yana kallon kyakkyawar fuskarta ya girgiza Mata Kai ahankali ya bude Baki cikin muryarsa me nutsuwa da dadin sauti yace"

AFIA MALEEK karki manta ke 'yar maleek ce jikar kaleeb our beautiful and brave lioness and you know wat thats means right princess??

Da jajayen idanuwanta ta dago ta kallesa zatayi mgn yace"

Ya Isa haka banason Jin komai all I want from you shine ki maida hankali akan karatunki ki Gina career dinki da kanki.

Sakinta yayi tareda juyawa zai fice saikuma ya dakata batareda ya juyoba ya bude Baki wannan karon cikin cikakken iko da bada umarni cikin sautinsa me daidaita nutsuwarta yace"

Wannan shine Karo na karshe daza'a Kuma maganarta acikin gidan Nan.

Karo na karshe.

Gyada Kai tayi tana sawa ranta batada uwa araye daga yau itama sbd dukkanin inda take tunanin mum dinta yau ta kai limit Dan Bata taba daukar uwa zata iya yafe har yayanta ba datake ikirarin Bata buqatar farhat sbd tacika ciwo, wannan kalmar ta rusa duk wata sauran hope datake dashi akan mahaifiyarsu.

Fitowa tayi tana shigowa Palo ta tararda farhat zaune apalon tana kallon cartoon cikin walwala abinta tana ganin afia din tasake murmushin farin cikin ganinta tana cewa"

Afia bakije makaranta ba kina inane tun dazu?

Aunt NURU ta tafi ta dauka kintafine.

Kasa magana afia tayi tausayin qanwarta me tsanani na shigarta har batasan sanda hawaye suka ciko Mata idoba suna gangarowa ta qaraso ta zauna gefen farhat din tareda rungumeta jikinta tanajin tsananin so da kaunar yarinyar tareda tausayinta,tayaya uwa zatace Bata buqatar 'danta sbd wani ciwo na harbawa da Allah ya sako Masa,

Ta Yaya mum dinsu zatace Bata buqatar farhat?

Kamar farhat din tasani saita lafe jikin afian batace komaiba hawayen afian Bata sauka kan jikinta sun Jima ahaka kafin Afia ta zame tareda Miqewa yayi daki ta rufe kanta tana wani irin kuka me ciwo da baqin cikin rayuwa,

Babu abinda Allah be basuba najin dadin duniya sai rashin uwa tagari da soyayyar uwa da Basu samuba kwata kwata,

Suna cikin ni'imar dukiya me yawa,

Mulki na sarauta me girma,uba nagari da soyayyarsa,ilimi na Boko Dana addini,kyawun jiki Dana fuska taredana zuciya daidai gwargwado Amma uwa Basu samu komai daga garetaba bayan dawainiyar daukan ciki da haihuwa duk cikinsu Babu Wanda yayi shekara yanashan nononta take zaresu tabarwa masu aikisu sune komai nasu tayaya zasu qarar da soyayyar uwa.

Sai yamma NURU tadawo tun apalo ta sake tabbatarda farhat ta warware Dan da gudu ta tarbeta suka fada kan kujera cikin murna take bawa NURU labarin yau dad yafita da ita Amma Basu dadeba suka dawo.

Miqewa NURU tayi tana cewa"

Iyye yau Daddy ya kyauta Mana sweetie taje yawon datake so.

Duk da haka fa aunt NURU alqawarin mu Yananan fa dakikace Zaki kaini yawo har wani qasa daban.

Hanyar daki suka nufa tana cewa"

Eh banmantaba saina gama karatu idan zanje Vegas attaching papers Dina na Gina career Dina dake zanje Inshallah sweetie.

Tsalle tasaki tana cewa"

Yes yes my Lewa

Suna shiga daki afia na zaune tayi wanka sanyeda gajeran wando da shimi tana aiki da laptop tana ganinsu ta sake fuska tana cewa NURU"

Welcome baby.

Thank you princess"NURU tace tana zare kayan jikinta tana fadawa Afia zancen dasuke da farhat suna dariya.

Wanka tayi tazo yayi sallah ta Sanya qananun kayan Shan iska itama tasha coke daya ta Dan kwanta sbd ta Dan gaji Kuma batajin yunwa Dan taji snacks a wani coffee shop.

Tana bacci wayarta tadauki ringing afia dake zaune ta kalli wayar saitaga sunan padima.

Murmushi tasaki sbd tasan padima abakin NURU Amma Basu taba gaisawaba Dan haka ta dauka Kai tsaye tareda cewa"

Assalm alaikm padima ānichī gini inidēti neshi? (ya kike ya gida/hw are you doing and family).

Tsit padima data Kira da Dan qungun kukanta tayi Jin muryar afia wadda takeda tabbacin itace 'yar maleek da ake fada Dan haka saita Dan saita murya cikin girmamawa da kulawa da sautin muryarta daya tabbatarda tayi kuka tace"

Lafiya kalau alhmdlh li'iliti.

Ya karatu da hidima?

Murmushi me sauti afia tayi tace"

Ba hidima saidai karatu shima munatayi inshallah munkusa gamawa, NURU na bacci yanzu saidai ko Zaki sake Kira anjima kokuma idan ta tashi saina fada Mata ok?

Dan kame kame padiman tafara tana cewa"

Eh baza'a tada ita bane yanzu da magana zamuyi me mahimmanci ne?

Kai tsaye afia tace"

Aa baza'a tashetaba yanzu dai lokacinda ta tashi dakanta kokin manta Matar maleek ce?

Koma yayane bazan tashetaba saita tashi da kanta matuqar ba lokacin sallah bane kawai ya isa yasa na tasheta sai idan dad ne dakansa yake nemanta which kuma is not possible for now dai.

Wani Abu padima taji yataso Mata kamar zata ashararo ashar ta danne tana cewa" Sabala ibilis cikin ranta.

Wato NURU har matsayin nata yafara kaiwa haka tun wuri.

Jin shiru yasa afia cewa"

Ko da akwai matsale ne a gida?

Kifadamun zanyi maganan da ita idan ta tashi.

Shiyafi komai sauki 'yar maleek padima tafada cikin ranta tareda sauke wani wahalallen numfashi tana karye murya zuwa rawa rawar son kuka tace"

Dama nafada Mata maganar rashin lafiyan danake fama dashine abin yafara tsanani anyi magani anan gida baiyiba shine tace zata kaini Inga likita anan ko za'a dace.

Da mamaki a bayyane afia tace"

Anan Kuma?

Tun yaushe ne ciwon?

Tsawon shekara"padima tafada tana hawaye.

Gyara zama afia tayi tana cewa"

Shekara daya ciwo ajiki shine NURU Bata taba fadaba.?

Menene matsalar?

Ciwon zuciyane yanzu nakai Ina amai da tarin jini wani lokacin.

Innalillahi padima meyasa bakuje ko English hospital na can ba.

Shiru padima tayi tana hawaye da shehekar data sake bawa afia tsoro tafara Mata tambayoyin akan yanda takeji da kalar jinin datake gani tana nazartawa da 'dan nata ilimin na likita da Bata qarasa zamaba.

Girgiza Kai tayi cikin jimami da tausayawa tareda tsoro tace"

Padima this is serious yakamata kiga likita cikin gaggawa gaskia.

Kuka padiman tasake fashewa dashi tana cewa"

Bansan Yaya zanga likitaba Dan Allah li'iliti ki taimakeni NURU takasa taimakona banason na mutu yanzu.

Ki taimakeni ki kawoni gurinki ki kaini gurin likita Dan Allah.

Shiru afia tayi ciki rasa sanin abinyi Nan take Sadai koma menene batada ikon kawo padima Nan take Dole saidai NURUn ce zatace akawota tukuna akawota din sbd kawo mutum Kai tsaye gidan MALEEK wani aikine Dan kuwa sai ankaita gizah an tantance kafin akawota gidan MALEEK Wanda yanzu Kam NURU ce kawai takeda ikon kira gizah tafada tanason akawo Mata padiman.

Ajiyar zuciya ta sauke tareda nutsuwa cikin son fahimtarda padiman tace"

Kiyi hkr padima Inshallah Zaki samu lafiya Amma yanzu dai Ni inshallah zan nema appointment na babban likitan da Zaki gani anan Amma maganar zuwanki zanyiwa NURU magana idan ta tashi saita Kira inda za'a kawo ki anan din.

Nagode sosai Allah yaqara girma ina gaida NURUn idan ta tashi.

Katse wayarta tayi tareda wurgi da ita tana jerowa daga afia din har NURU zagi sbd Sam sunqi hawa yanda takeson suhau su rikice da tausayinta yazama basa tunanin komai saina tausayinta tasamu Isa qasar.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/21, 9:10 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 25_*

Tana aje wayar ta waiwaya ta kalli NURU har lokacin baccinta takeyi hankalinta kwance Kamar wata 'yar baby.

Kyakkyawar fuskarta ta kalla zuwa jikinta ta sauke ajiyar zuciya me qarfi sbd tausayin NURUn da Kamar rayuwarta ta raunane auren sa'ar mahaifinta bayan tanada Wanda takeso daidai ita sabon jini Amma yanzu gashi auren dattijo yahau kanta duk da MALEEK yawuce duk wani tsarin Imran nesa ba kusaba Dan kuwa Kota Ina Babu inda Imran yakamo maleek bayan qananun shekaru dazai nuna Masa Wanda shikansa maleek din kyau da hutu tareda wani irin iko da sarauta dake yawo

a jininsa suna boye manyancinsa matuqa sosai dan kuwa jikinsa kawai masu qananun shekarunma bazasu kaisa kyawun jikiba musamman dayake Yana geamin sosai haryanzu shiyasa jikinsa koyaushe Kamar na yara.

Ajiyar zuciya tasake saukewa tareda cire wannan tunanin aranta Dan kuwa ita yanzu tariga ta cire kanta acikin maganar komaima Dan kuwa ko lokacinda take muradin raba auren nasu bataga ta inda zata faraba dama fatanta idan mum tadawo dad zai sawwaqewa NURUn sbd wadda zuciyarsa keso tadawo to Amma ita ta ina take gano yiyuwar saki arayuwar dad dinsu Wanda ko rabuwarsa da mum haryanxu duniya Bata gama saniba bare yayi wani sakin.

Aje laptop dinta tayi gefe tareda Miqewa ta Sanya slippers ta fita zuwa kitchen Dan yin wani aikin duk da Bata iyaba Dan debewa Kai kewa batason tunanin komai yadawo Mata musamman na mum dinsu datake fatar shafewa ta manta gabaki daya.

Sai gab da magriba NURU ta farka daga baccin miqe tashiga toilet tayi fitsari da brush ta fito ganin bakowa a dakin tasan wani Abu sukeyi ta zame gajeran wandonta ta dauko wani dogo da zo har qasan gwiwanta ta fito riqeda wayarta tana duba wani email da aka turo Mata daga karatun court din dataje jiya tana dariyar mark din data samu ta nufo kicin dan tunda tafito yanayin qamshin datakeji tasan afiace a kitchen din.

Ganin uban aikin da afia din keyi tareda farhat da mum Sarah sai Fana dake tayawa yasata sakin dariya cikeda mamaki ta miqawa farhat wayarta tana cewa"

OMG meyake faruwa anan ne?

Cikin kanne dariya mum Sarah tace"

Princess na aikin abincin dinner ne.

Wani wargazajjen flat bread ta cire daga pan duk ya sauya kala sbd Kwan jikinsa duk ya kone afia tayi tana aje spoon din hannunta tace"

Alhmdlh na Gama waye zaiyi Mana testing?

Shiru kowa yayi NURU ta matsa tana sake kallon girke girken da mamaki da dariya akan fuskanta tace"

Nidai bana cikin 'yar dandanawa.

Farhat kuwa da sauri tayi bayan NURU tana cewa"

Nima bana ciki.

Kallon mum Sarah afia tayi da alamar ke fa??

Wani yawu mum Sarah ta hadiye tareda kallon Fana tace"

Saidai Fana kinsan Ni inada suga ba komai nakeciba musamman yau ya haye da yawa sugan.

Tana gama fadar hakan ta sulale ta fice daga kicin din.

Fana Kam ba damar wani zance ta matso ta diba komai daya bayan daya tana dandanawa harta Gama ta dago idonta na kallon qasa tace"

Komai yayi daidai ranki ya dade.

Da mamaki NURU ta kalli Fana daketa faman danne yunqurun amai dake taso Mata na abincin Amma ahaka sbd gudun batawa afia tace komai yayi.

Afia da kanta tajera komai a dining ta wuce tabarsu NURU ta kamawa Fana suka gyare kitchen din tsaf komai yakoma kaman ba'ayi aiki dashiba Fana ta wuce sashensu na ma'aikata NURU ta rufe koina na cikin ta fito ta nufi dakinsu tayi alwala tayi sallar magriba lokacin afia hartayi wanka ta shirya ta fito taje Tasha black tea kawai Takoma daki sbd karatu takeson yi.

Har akai ishai suna Palo suna kallon wani adventure film a Netflix daganan ta hadowa farhat _Rice Krispies_ har suka Gama suka koma daki sukai sallah sukai Shirin kwanciya Bata Bari dakin farhat ba Saida taga tayi bacci tukuna tabaro tadawo dakinsu har lokacin afia n karatu tazo ta zauna kusada ita itama tana duba wasu hardcover books na lauyoyi na _Michael Connelly THE BRASS VERDICT_

Karkata tunaninta yayi akan abincin da afia din ta dafa dake kan dining Wanda maleek zai iyaci yasa ta aje littafin hannunta tareda kallon afia da bacci bacci yafara fizgarta ta miqe ta fita Dan dauke abincin daga kan dining duk da tasan kilama ya shige zuwa yanzu.

Direct dining ta nufa ta kwashe kayan ta maida kitchen tana qoqarin barin kitchen din taji motsin bude kofar kicin din ta baya tayi saurin waiwayowa cikin sauri da Yar fargaba tace'

Waye??

Muryan mum Sarah taji daga bayanta ta kofar nata dakin tana cewa'

Fana ce zata shigo ta hadawa MALEEK tea yakira Yana buqatarsa yanzune kafin ya sauko.

Jin haka tasake ajiyar zuciya ta matsa jikin kofar tace"

Fana ki koma kawai zanyi masa.

Juyawa Fana tayi ta wuce itakuma ta juyo ta kalli mum Sarah tana cewa"

Tea kawai Koda wani Abu?

Tea kawai yace amma bansaniba ko Zaki hada Masa da wani abun.

Fara hada Masa tayi tareda dauko cake dinda tayi jiya ta jera masasu a plate ta dauko ganyen lemon daga fridge ta wanke tareda zuma ta hada tea din ta zube ta jero a tray ta fito mum Sarah na biyeda ita daukeda sauran kayan suna shiga dining room Yana shigowa itace agaba ta 'dan dago kadan cikin taushin murya tace"

Barka da fitowa.

Akaro na farko ya amsa gaisuwarta da "yawwa" Yana zaunawa kan dining ta ajiye tray din hannunta ta matso kusadashi Dan zuba Masa qamshin turarenta na _Black Opium_ ya bugo Masa cikin hanci ya dago ahankali ya kalleta

Jin idanuwansa akanta yasa ta dakatawa tana Dan juyowa suka hada ido ta sauke nata tana juyowa da sauri ta kalli mum Sarah dake gurin tun kan ta Gama juyowa mum Sarah tayi saurin aje tray din tabar gurin tana soke kai ganin abinda yake neman fun karfin mamakinta.

Mum Sarah na wucewa ta juyo tana qarasa zuba Masa tareda jawo Masa cake din ta koma kitchen ta dauko ruwa ko zaisha ta ajiye tareda budewa ta zuba a cup.

Kasa wucewa tayi saida taga yagama tana daga kicin tana hangensa ya miqe ya wuce ta fito ta kwashe kayan ta maida ta nufi daki tana miqa sbd bacci takeji yanzu Kam.

Saidata shige ya kashe wutar palon farko yashigo ciki ya wuce sama.

Washe gari suna Shirin zuwa makaranta afia ta dauko zancen padima tafadawa NURUn tana qara cewa"

Inaga zaifi idan tazo Nan taga likita gaskia sbd Sam yanda nayi Mata tambayoyi da amsoshinta akwai rikitarwa bangane komaiba gskia sosai so inaga tazo taga likita zaifi.

Kallon bansan ta yayaba NURU tayiwa afia jikinta a sake tace"

Bansan ta inda zanfara bane,

Bansan ta gurinwa zan fara ba.

Kiyiwa jekadi bayanin komai da abinda kikeso ita zata isar Miki da saqonki koina dakomai saidai kawai kiga padima ankawota.

Shiru tayi hakanan tanajin wani iri kamar zata wuce guri idan tayi hakan Amma Kuma ceton 'yar uwartane zatayi tunda tanada damar yin hakan zatayi Inshallah.

Juyowa tayi ta kalli afia tace"

Thank you,zan yiwa jekadi magana idan na Isa makaranta inshallah.

Suna Isa makaranta takira jekadi saidata jira jekadi tagama gaisuwarta ta amsa cikin bawa jekadi nata girman itama kafin ta fadawa jekadi buqatarta tason akawo Mata 'yar uwarta padima tazo Mata ganin gida.

Ba musu jekadi tace"

Angama Inshallah MUSHRA,zanje yanzu na sanarwa Anneti ta sanarwa da MALEEK sai a aika gida ataho da ita Nan daganan sai akawo Miki ita har inda kikeso.

Koda jekadi ta isarda saqon NURU ga Anneti Bata musaba tace jekadi ta isarwa da MALEEK sakon aikuwa Kai tsaye shima ta isarda sakon a waya ta hanyar Mr Omar Wanda yace anbasu dama take washe gari aka aika aka taho da padima wadda Ta taho badan iyayensu sunso ba sai Dan saqon ta hanyar kaleeb ya iso musu.

Abal ya tabbatarwada padima duk yaji wani mugun labari yasamu NURU bashi ba ita har abada hakama ammi Kuma ahaka taji takuma amince saidai ta qudurta bazatayiwa NURU komaiba kodan kalaman iyayensu saidai bazata dawoba saitasamu nata rabon na ingantacciyar rayuwa ta taho tabar amed da mugun mamaki da baqin cikin daya kaisa Shan mugun qudurirrika akan ko zaiyi yawo tsirara bazata jimaba zaimata aikinda ko wata bazata rufaba acan saita dawo saidai Kuma wani tunanin daban yasashi Kiran mahaifinsa dake cikin amintaccin NEGES yafada Masa zuwan padima Wanda shima atake yafadawa NEGES.

Kallon jekadi Anneti tayi lokacinda take miqa Mata saqon NURU na wata sabuwar madarar raqumi da akaiwa Hadi da sinadarun Karin kyan fata Da wasu abubuwan ma tace"

Wannan sakon NURU ne da hannunki kullum Zaki ringa Bata tana shansa harya qare sbd na yanke shawaran kece Zaki Kai Mata 'yar uwarta ki zauna acan sai lokacinda tagama ziyararta kudawo tare sbd dalilai na Kare maleek da iyalansa duk da 'yar uwartane Amma bamusan Yaya halayenta sukeba musamman gashi ziyarar tazo a bazata.

Yanda kikace haka za'ayi Anneti.

Miqewa tayi ta fice Tana sake miqa gaisuwarta.

Tana fitowa duk da darene sosai saitaji tana buqatan zuwa ta duba lafiyar 'yar amanar NURU Dan kuwa tamkar amanartane NURU tabata Dan haka ta nufa sashen Kai tsaye.

Tun daga nesa taga kamar wutar sashen a kashe take sai abin yabata mamaki ta Dan dakata tareda dudduba sauran sassan duk hanyoyinsu wuta a kunne.

Daga can ciki kuwa gyara tsayuwa yakoob yayi Yana kallon padima dakewa tarin darhamai da danyen zinarai daya zube agabanta kallon haramun Kamar zata cinyesu abakinta yace"

Yaya Zaki iya kokuwa??

Hadiye wani yawu tayi tareda danne kwadayinta ta kallesa tsoronta na bayyanuwa tace"

Bazan iya kisaba wlh sbd ban iyaba bantabayiba.

Wani kallon Kai tsaye yayi Mata Yana sake zuba Mata wasu akan wainnan yace"

Ba kisa zakiyiba zuba Masa kawai Zakiyi a abunsha sauran aikin anan zamu qarashi,

Idan Kika cika wannan aikin akwai alqawari me girma na cikar buri da akai Miki alqawari daga shugabana haka zalika Kuma fitar maganar daidai take da bakin rayuwarki.

Wani kallon tsoro biyu tayi Masa kayan cikinta na juyawa sbd duk balainta batakai na kashe wani ba

Waninma maleek datake 'dan yiwa kanta kwadayinsa dukda tasan da wuya ita ko bashiba burinta dai gidan mulki

Yanxu ta Yaya zata iya kisa?.

Kuma aikinma batasan na ainihin wayeba tunda yadaice shugabansa bai fada ko wayeba.

Ciro wani qyalle yayi ya miqa Mata tareda cewa wannan ki warware gashinki ki dauresa aciki idan kinje can so daya kawai akeso ki juye Masa duka a abunsha kawai Banda abinci,

Idan kinzuba kiyi flushing din kyallen.

Miqa Mata yayi ya juya ya fice Yana cewa"

Sauran bayanin idan andawo Nan zakijisha.

Fitowa yayi fuskarsa rufe da kayan bayi Mata ya wuce batareda waiwayeba ya fice gabaki daya daga gurin.

Da mamaki jekadi tabi bayan baiwar data fito daga sassan Dan Haka ta qaraso da sauri tana sake duddubawa kafin ta nufa kofar Kai tsaye tashiga

padima dataji motsi tayi saurin boye darhaman tareda janyo abincinta da bataciba gabanta tareda zaunawa ta kishingida tareda rufe idanu har jekadin tashigo.

Da rashin yarda da mamaki jekadi ke kallon koina kafin ta kalli padima Kai tsaye tace"

Waye yafita yanxu daga Nan?

Bude idanuwa padima tayi tana ganin jekadi tayi saurin miqewa tareda russunawa tace"

Allah ya taimaki jekadin jekadai.

Sake maimaita tambayarta jekadi tayi tana kallon padiman har lokacin.

Cikin girmamawa tace"

Abincine takawo sbd dazu Koda aka kawo banajin dadin cikinq nace amaida zuwa anjima adawo dashi.

Kallon tsaf jekadi Tai Mata kafin tayiwa abincin da aka kawo din ta tako ahankali tana kallon abincin takai hannu ta bude tayi Masa kallon tsaf tareda Dan Kai hannunta a kaikaice taji dumin abincin Wanda baida dumi ko kadan ta dago ta kalli padiman kallon tsaf tasaki wani murmushin bazata dayasa padiman Dan washe Baki itama tace"

Saida safe ki huta lafiya"" ta juya ta fice batareda yiwa padima sauyiba ko alamar komai.

Tana fita padima ta sauke ajiyar zuciya tareda warware gashinta tasake gyarawa kullin zama cikin yalwataccen gashinta.

Ta zaro uwar dukiyar data boye tana tunanin inda zata kaita kafin tadawo.

Zagaye tafara cikin tsananin tsoro da firgici Dan ganinta da wannan darhaman masu tarin yawa zasu iya kaita lahira, gabaki daya tsoro da tashin hankali takeji wace masifar ce wannan daga zuwanta ko Paris din Bata qetaraba ta hadu da wannan balain yanxu idan taqi Yi ance abakin ranta,

Idan tafadawa wanima abakin ranta,hakama idantace zata tona tafada gskia batasan waye ya aikoba Dan aikenma fuskarsa rabi arufe babbar masifar datafisu shine idan ta aikata tayi kisan Kai ga Wanda tasan ko gunduwa gunduwan gawarta Kare suka samuci tayi arziki to ita Kam wane tashin hankali ne wannan.

Tana hada wani mugun zufa ta dauresu waje daya tareda cusawa cikin kayanta na sawa takoma gefe ta zauna har lokacin gumi take hadawa ta Nemo numbern amed sbd sanin shikadaine abokin cin mushenta na rayuwa.

Yana ganin kiranta yasaki ajiyar zuciya sbd abinda yake jira kenan Dan mahaifinsa ya fada Masa komai Dan shine yaje gurin padiman.

Dauka yayi cikin matsewa sbd har lokacin takaice yake da ita yace"

Lafiya dai ko Kira da wannan tsohon daren.

Wani wahalallen numfashi tasaki cikin qasa da murya tace"

Amed inason ganinka a Giza komai tsanani gobe Dan Allah.

Kallon mahaifinsa yayi sbd tun Rana ya iso Giza din yau shima sbd wannan tarkon nasu ya Dan sake Bata murya yace"

Sbd me zanzo kiranki?

Kinga karki rainamun da hankali Mana.

Cikin rawar murya tace"

Dan Allah amed kazo kokuma idan bazaka samu zuwa ba ka hadani da mahaifinka wlh Ina cikin wani mummunan tashin hankali ne na..... shiru tayi tana tuno maganar da Dan Aiken yafada Mata dazu hawayen cikin idonta suka gangaro Mata ta sauya zancen da cewa"

Akwai dukiyar NURU ce a hannuna inason baka ka Adana min harna dawo sbd bazan bataba batamasan da itaba.

Washe Baki yayi Kai tsaye Yana cewa"

Ganinan tafe yanzu kuwa.

Da mamaki tace" yanxu Kuma?

Kana gizah ne dama?

Da sauri yahau gyaran zancen da cewa"

Aa inanufin zan fadawa mahaifina zaishigo ya karba ta sirrance.

Bata yadda dashiba Dan taji gargada a zancensa Amma yanxu tunda tanason kubuta daga wannan saita ciro maganin da aka Bata ta Raba biyu ta bude gaban wata sarqar daham dake cikinsu tasaka dayake qaramine saiya shige ta maida Dan locket din ta rufe tana cewa"

Idan ta 'batarmin acan tareda zamuje qasa Dan ga shaida nan nasaka acikin kayan Kuma bazaka taba ganowaba.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899*_Mamuhgee 26_*

Washe gari sakayau taji ta Dan rage tashin hankalinta sbd ta rabu da dukiyar Dan hakanan taji Kamar jakadi Bata yarda da itaba ita yanxu data tabbatarda mutuwa ba abin Wasa bace data ji tafara Jin kamshinta zuwanta gizah sbd jiya harzuwama yanxu cikin matsanancin tashin hankali takejin kanta gabaki daya kusan Rabin zumudin tafiyar yabarta tsoro da shakkun abinda zai iya faruwa gaba shine yafi

komai cikata yanxu gefe daya gasu abal tana Isa sukaji wani abun yafaru ayanda tasan abal dinsu dakansa zai iya bada shedar kome yafaru itace...

Gyaran muryan jekadi ya dawo da ita zurfin tunanin data shiga ta dago ta kalleta jiki duk amace ta Dan rusuna ta gaidata

Jekadi ta amsa cikin sakewa tace"

Bismillah zamu wuce Inshallah.

Janyo Jakarta tayi suka fito daganan har sassan Anneti aka fara kaita ta gaidata cikin tsananin girmamawa da tsarguwa kafin suka fito bayan sun Isa gate na biyu Dana uku Saida aka bincike kayanta tsaf kafin suka fito main gate inda dakarun tsaro suke sunfi guda ashirin suka fice daga delah gizah zuwa airport manyan motocin tsaro biyu na bayansu har airport.

****

Yau tunda safe suka fice duk su dukansu sbd exams dasuka fara ayau din ga uwa uba ita NURU tana gama da ciwon Mara sama sama dam idan zatayi period kusan kowane wata saitayi ciwon Mara ga uwa uba Imran da kwanakin Nan tunaninsa yakasa barinta Jin cewar bayada lafiya sosai

Tausayinsa takeji har cikin zuciyarta saidai tasan matuqar ba afiace zataje ganinsaba tabita itadashi iyakaci addua.

Suna fitowa yau sbd sammako dasukayi cikin itace agaba tana gyara daurin kanta na scarf fari shikuma Yana fitowa daga geamin dinsa wasu qananun zufa dasuka fiffito Masa suna gangara daga fatarsa da tsantsinta ya hanasu zama ta dago ta kallesa wata irin mummunan kunya ta kamata tayi sauri dauke Kai kasa batasan lokacinda tace"

Gud morning ba.

Kallo daya tayi Mata daga sama zuwa qasa ta dauke kansa ya wuce Kamar bai lura dasuba afia dayake tasan halin dad dinta saitayi gaba sbd sanin jinin mulkin ya motsa akansu su 'yayansa.

NURU ma hakanan tabi bayan afia tana kashe wayarta suka fada mota suka wuce.

Sai yamma lis suka dawo Kai tsaye daki suka nufa kowa yayi wanka ko abincin kirki NURU bataciba sallah kawai tayi ta janyo laptop tareda wasu takardun tahau karatu afia ma libry ta wuce Dan ita tafi ganewa karatu acan.

Daqyar kowaccensu tayi sallar ishai sbd bacci da gajiya suka Dan sake tattaba karatun bacci yayi gaba da kowaccensu a inda take.

Sai cikin tsakiyar dare su padima suka iso Dan haka ko cikin main gidan ba'a Bari sunshigo ba sbd MALEEK na Nan Dan haka part din masu aiki suka sauka akan seda safe zasu Shiga cikin gidan.

Tunda safe sukuma su NURU suka wuce school sbd jiya bacci be barsu sunyi karatunba sosai shiyasa Koda safe dasu padima suka samu shigowa su NURU sun wuce aka sauketa dakin dake kusadana mum Sarah na jekadi ma Yana gefen nata saiya zama sun sanya dakinta tsakiya.

Kallon aljannar duniya takeyi hawaye na silalo Mata a fili tace"

Wannan wane irin masiface take bibiyata,

Amed Kaine ka cutatarda rayuwata wannan rabon ya subuce min.

Kallon dakin da aka sauketa tayi Wanda aka Kira Dana saukan baqi Wanda tasan har abada kila ko a mafarki bazata samu irinsa ba matuqar ba aikin da aka Bata tayiba dasukai Mata alqawarin cikar buri.

Shafa kanta tayi taji maganin na ciki ta sauke ajiyar zuciya tana bawa kanta qwarin gwiwan aikatawa.

Da wannan tunanin tayini tana kallon kanta a madubi sbd ko tsaron dake Nan gidan ba qarami bane tsaf zatayi ta bakin ranta ba duniyar ba lahirar Dan haka Dole Saida taka tsantsan.

Da yamma suna dawowa farhat tafara tarbonsu da gudunta tayi musu oyoyo tana sanardasu isowansu padima Wanda yasa NURU sakin wani qayataccen murmushi tana 'dan wartsakewa daga gajiyarta taqarasa ciki cikin farin ciki.

Jekadi ce tafara fitowa ta russuna cikin girmamawa tace"

Barka da dawowa ikon MALEEK na gizah.

Da murmushi ta matso tareda girmamawa itama tace"

Allah yaqarawa jekadi matsayi

Kun iso lafiya?

Ya kuka baro Anneti.

Murmushin ganinta cikin sabon sauyi jekadi tayi sbd lurada Kamar taqara Dan sakewa fiyeda da tace"

Anneti na miqo gaisuwarta gareki da sauran iyalan MALEEK gabaki daya.

Muna amsawa tace tana kallon kofar da padima ta fito fes hartayi wanka ta Sanya doguwar riga me Fadi sosai ta qarasa da Dan sauri suka rungume juna suna yare tana tambayarta su abal da ammi da meryam.

Duk suna lafiya ta amsa tana yiwa afia barka da dawowa cikin 'yar girmamawa.

Tareda padiman suka qarasa dakinsu sunata yare Wanda yasa afia keta Binsu da murmushin burgeta dasukai musamman NURU daketa nuna kulawa ga 'yar uwarta saitaji NURUn na sake Shiga ranta tace"

Baby am jealous fa.

Murmushi NURU tayi tana cewa"

Karki damu itafa tafiya zatayi tabar Miki NURU.

Padima da batasan me sukace ba farko sai Binsu take da ido kishinsu na sake ciketa musamman NURU da idan ta tuni asalinta.

Wanka sukai kowa ya shirya cikin qananun Kayan Shan iska suka baje karatu suna fira da padiman at the same time.

Har dare tana dakin suna first gida Dana ciwonta Wanda take ce musu ba laifi tanajin kaman tafara Jin sauki sbd wani magani da abal yabata.

Sai dare sosai NURU ta rakata har cikin dakinta suka zauna suna dasa sabuwar zancen gida Wanda duk yasake tadowa NURU kewar gida da iyayenta ita kuwa padima satar kallon tsadaddun kayan baccin dake jikinta takeyi Wanda itama anhadota da daya na sawar yau Amma saitakega kaman na NURUn sunfi kyau da tsada Wanda batasan cewa daga jikin NURUn ne.

Sai after 12 tafito daga dakin Takoma nasu ta kwanta tanajin farin cikin saduwa da 'yar uwarta.

Washe gari ma sammako sukayi sai yamma Amma ba sosaiba suka dawo zuwa lokacin farhat tadan fara sabawa da padima dake kokarin zama kamar yarinya itama tana Taya farhat din Wasa itadai jekadi idanuwanta na bude qyam akan komai dake wakana a gidan.

Kwata kwata su NURU basa zama sbd exams shiyasa Basu ma dauko maganar ciwon padima ba Bari sukai saisun Gama exams sunsamu lokacin kansu isashe tukuna itama padima Bata damuba Dan so take kadama su Gama exams din da wuri Dan kada a tado maganar tasamu ta aikata aikinta ta tattara Takoma Dan ita anan ko gurin zama Bata ganiba dan haryau datake batun cike sati biyu da zuwa Bata taba saka maleek a idontaba Dan haka gwara tayi wannan aikin Takoma can Giza kila nata rabon acan yake tunda anmata alqawari.

Kamar koyaushe yau gidan bakowa sai masu aiki sai ita saisu jekadi da mum Sarah datakewa laqabi da tsofin najadu.

Duk wata damar aikata aikinta Bata samuba tsanani da tsaron da ake bawa abincinsu yayi yawa shiyasa komai yafara cakude Mata musamman dataji jekadi tafara qyanqyasa zance komawarsu tunda sunyi sati biyu cikin na uku gashi ita Tama rasa uban hasarar metake idan Takoma ba wani sakamakon.

Yau da wuri NURU ta dawo sbd sauranta exam daya tagama hakama yau daya tayi Dan haka cikin walwala da gajiya take gashi tanason bawa padima lokaci su futa yawo takaita taga gari da 'yan siye siye duk da kusan so biyu suna futa da afia data samu interval na Wana biyu.

Wanka tayo ta fito sanyeda doguwar riga sukaci abincin cikin nishadi da walwala har akai magriba suka shige ciki Acan sukai sallah dakinsu suna sake fira daganan NURU ta dauko maganar ciwon padiman kafin tabata amsa ta dauko wani zancen ita padiman da haka suka kamo wani zancen har lokacin bacci yayi suka kwanta.

Washe gari NURU batada exams Dan haka suka shirya suka fita yawon shopping itada padima da farhat sai jekadi datake bayan NURU ko Nanda can Wanda yasa NURUn fara Dan tsarguwa Amma sbd kaunarta da jekadi Bata nunaba saima siyayya da akaiwa kowa suka dawo gida da yamma lis.

Kowa daki ya nufa yayi wanka da salloli kafin suka fito cin abincin dare gabaki dayansu.

Suna gamawa NURU tayi daki tasake yin wanka tareda Shirin bacci ta nufi dakin padima harzata Shiga mum Sarah ta qaraso gurinta tana cewa"

MALEEK na buqatan black lemon tea.

Fasa shiga tayi ta nufi kitchen tana cewa"

Ok mum Sarah ki tayani wanke ganyen lemon din Bari na dauko cake dinda nayi dazu da safe.

Padima najin haka ta fito tayo kitchen din tahau Taya NURU aikin suna Dan firantawa.

Saidata hada komai tafara daukan cake ta nufi dining tabar padima a kicin tadawo ta tararda padima na tayata juya tea din kafin ta qaraso ta karba jekadi tashigo kicin din NURU tace"

Yawwa nagode padima bari nadauko guri na juye.

Juye Masa tayi ta dauka takai dining daidai fitowarsa ya qaraso dining din ya zauna ta sulale ta bar gurin sbd kayan dake jikinta Koda ta isa kitchen padima Takoma daki jekadi ce kawai a tsaye tana Shan ruwa.

Bai wani Sha dayawaba sbd yau taste din ba Dadi Dan haka ya miqe yahaye sama.

Yana wucewa NURU tayi daki itama bayan tayiwa jekadi Saida safe.

Saida jekadi ta tabbatarda kowa ya shige tadawo dining room ta dauki cup dinda MALEEK Tasha tea tazuba kadan a hannunta ta shinshin taji bataji wani qamshinba dabann takoma kicin ta dauko wani cup ta zuba shayin takai bakinta tareda rintse ido ta kurba kadan

Take ta bude idanuwanta tana kallon cup din gabanta na Dan faduwa tasake kurba tea din take jikinta yafara sauyawa da yanayi kaman na zafi zafi kaikayi kaikayi tayi kicin da sauri ta Adana tea din ta fito zuwa lokacin yafara Jin kamar ana hura wuta me zafi cikin jikinta ta nufi hanyar dakinsu NURU da qyar tana dafe jikinta ta Isa kofar dakin tayi knocking so biyar ajere NURU dake korarin rufe laptop ta kwanta ta ajiye laptop din tana kallon kofa kafin ta taso sbd kada atada afia datai baccin gajiya.

Ganin jekadi cikin yanayin ba daidaiba yasata fitowa dakin gabaki daya tana rufewa tareda kallon jekadin cikin mamaki tace"

Lafiya kike jekadi?

Bakida lafiya ne?

Girgiza Kai tayi wani irin mummunan gumi dayafi kamada Ana sheka Mata ruwan zafi Dan har tsiyaya take ta bude Baki daqyar a Dan wahalce tace"

MALEEK....kije kidubo MALEEK....guba..gubar qona jini a tea.....

Arude NURU take kallon bakin jekadi kayan cikinta na juyawa tsabar kaduwa tace"

Guba...maleek kuma?....

Turata jekadi tayi tana cewa"

Kije da sauri kidubosa akwai matsala babba.

Juyawa tayi da gudu tana waiwayen jekadi akaro na farko tana hawa Daman MALEEK dukkanin jikinta na rawar tsoro da firgici itakuma jekadi Kai tsaye dakin padima ta Isa ta Sanya mukulli daga waje kafin tafada dakin mum Sarah tana fidda wani gurnani azaba da wahala.

Tana Shiga qaton palonsa na farko taga Kofa biyu daya ta palonsa na biyu daya ta dakin matarsa lailah Bata tsaya komaiba ta nufi wadda qafafunta suka jata zuwa ta bude da sauri ta fada nanma wani palon ne tana hango kofar Master bedroom dinsa ta nufa da gudu ta fada ko ganin gabanta sosai batayi.

Cak ta tsaya tsakiyar dakin sbd fitowarsa wanka kenan dagashi sai towel iya qugunsa dukkanin fatar jikinsa tayi jajir kamar anmasa duka da danqo

Hankalinta take yaqarasa hargitsewa tanabin jikinsa da kallon qafafuwanta na daukar rawar tashin hankalin ganin wannan mummunan al'amarin.

Sbd jininsa nada tsananin karfi yasa yake iya controlling tsananin azaba da radadin dayakeji na juyawa cikin jininsa ya dauke idonsa daga kallonta tareda juya Mata baya sbd rashin kayan jikinsa.

Ganin masifar tafi yawa abayansa yasa batasan lokacinda ta qaraso da guduba ta Dora duka tafin hannuwanta a tsakiyar bayansa Wanda yasa wata ajiyar zuciya me qarfi kufce Masa sbd wani sanyin saukin azabar dayaji

ya juyo gabaki daya Yana kallonta hannuwanta akan jikinsa ya lumshe fararen idanuwansa dasuka koma jajir yabudesu fes akanta.

Ba sha'awar mace yakejiba ko kadan sbd komaima bazai iyaba ayanxun sbd konuwa da tafasar dayakeji acikin jikinsa Amma haduwar jikinta da nasa ya raunana azaba da zafin dayake ji sosai

 yasake ware idanuwansa akanta tareda matsowa cikin jikinta sosai tayi saurin kasa da ido zuciyarta na harbawa haryana iya gani ta saman kirjinta

Hannu 'daya yasa ya zagayota tareda matseta cikin jikinsa yasakejin wani sanyi yasake sauke ajiyar zuciya tareda Dan sassautawa yana kallon fuskarta daidai ta dago zuciyarta na harbawa da tsoro da firgici da komaima ta kallesa idanuwansa suka shiga cikin nata kusan atare suka sauke ajiyar zuciya

Ya dago hannunta ahankali Yana kallon fuskarta ya Dora kan botiran rigar baccinta

Ta maida idonuwanta ahankali ta rufe bugun zuciyarta na tsananin Tues tanaji Yana bude botiran rigar har qarshensu rigar ta zame a tsorace ta rungumesa sbd kirjinta dake bayyane qyam.

Atare suka sauke qaqqarfar ajiyar zuciya musamman shi dayaji sanyi na shigarsa ya rungumeta gabaki daya cikin jikinsa idanuwansa alumshe.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Daya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899[9/22, 9:06 PM] +234 814 307 3081: *_Mamuhgee 28_*

Da asuba Saida afia ta tada ita sbd nannauyan baccin daya dauketa ta bude ido daqyar ta kalli afia kanta na wani irin sarawa sbd nauyi dayayi mata sbd rashin bacci da damuwar abinda yafaru cikin daren.

Tashi tayi daqyar ta nufi toilet tashiga tayo alwala tafito ta tsaya gefen afia ta tada tata sallar.

Suna idarwa afia ta ringa satar kallonta a kaikaice sbd duk wani motsin NURUn qamshin turaren dad dinta takeji ajikinta yana tashi.

Shiru tayi sbd batamasan mezatace ba Amma mamakinta anan Ina NURU ta hadu da qamshin?

Ta Yaya?

Ganin idan tayi magana Kamar ta muzanta NURUn ne yasata yin shiru ta Adana kalamanta tukuna.

Gari nafarayin haske NURU ta fito ta nufi dakin mum Sarah ta dubo jekadi har lokacin bacci takeyi saita fito ta nufi dakin padima ta tura tajisa arufe taga key din ajiki ta waje saita bude dakin tareda shiga har lokacin bacci padiman keyi ta qarasa bakin gadonta ta taba bargonta ahankali zata tasheta

Padiman tasaki wani razanannan ihu tana zabura zaune gumi duk yagama jiqata idanuwanta duk a waje take kallon fuskar NURU jikinta na Dan rawa ta sharce gumi tana saukowa daga gadon.

Da mamaki da tsoro NURU ke kallonta tace"

Lafiya padima?

Mafarki kikayine kike wannan ihun kina hada gumi haka?

Kasa kallonta padima tayi sbd har lokacin gumi takeyi cikin tsananin firgicin mummunan mafarkin datayi batareda ta waiwayo ba ta nufa hanyar toilet tana cewa"

Mafarki nayi sbd banyi addua ba na kwanta.

Bayanta NURU tabi da kallo cikin mamaki sosai kafin ta juya ta fice daga dakin ta nufi kitchen tana Danna Kiran Mr Omar.

Saidata tabbatarda ita kadaice a kicin din tace"

Gud morning Mr Omar.

Barka da tashi ranki ya dade"yafada daga can bangaren cikin girmamawa.

Shiru tayi cikin nazarin abinda zata fada Masa...shikuma Jin hakan sai ya gyara murya cikin nutsuwa da Bata tabbaci yace"

Dr Damien yazo ya duba MALEEK tun six harya wuce ma inshallah komai ya wuce.

Sake yin shiru tayi tana wani nazari kafin ta sauke ajiyar zuciya me sauti tace"

Mr menene wannan ciwon?

Shin kodai wani abun sukaci kokuma ya taba skin dinsu?

Tsit Mr Omar yayi Jin tambayar tata saidai baija shirun da tsayiba Dan kada ya Bata hope na zai amsa tambayar ya Dan sake gyara murya cikin Bata girma yace"

Ranki ya dade Inshallah allergy ne kawai Amma bana saka ran da...

Qin qarasawa yayi tareda dauko zancen itama jekadi kowane lokaci duk zasu farka lafiya Inshallah.

Ajiyar zuciya ta sauke zuciyarta na wasi wasin abinda yace na cewan allergies ne,

Wane irin allergy ne wannan me tsananin azaba.

Daga sama tajisa Yana qara saita murya yace"

Ranki ya dade idan na hali Dan Allah basai 'yayan MALEEK sunsan meya faruba,kowama Dan Allah kada yasani sai maleek ya tashi anji daga garesa shida jekadin.

To" kawai tace tana kashe wayar cikin 'yan tunane tunanen dasuke shigarta.

Kasa yin komai na breakfast tayi tabarwa Fana aikin ta wuce daki tashiga wanka tafito lokacin har afia tagama shirinta itama tahau shiri suna gamawa ko breakfast NURU batayiba afia ce kawai tayi suka wuce makaranta.

Tunda suka Isa NURU batada sukuni tunanin halinda yake ciki ya hadu da karatun exams dinta ya hargitsa Mata Kai har wani jiri jirin ciwon Kai takeji sauqinta dayane daga yau tagama exams dinta hutun gaske zatayi kafin sudawo hutu inshallah sbd tana tsananin buqatar hakan.

****

Qarfe goma Sha 'daya da mintuna shida maleek ya sauko ahankali yake tafiya cikin nutsuwa da kamewa Yana sanyeda jallabiya milk sai daukan ido takeyi sbd maiqo da laushin yadin jallabiyan.

Mr Omar dayake tsaye tuntuni Yana jiransa a palo yayi saurin sake sauke kansa cikin tsananin biyayya ya sake ja baya maleek ya wuce yabi bayansa cikin tsananin girmamawa yace"

Barka da fitowa MALEEK.

Allah yaqara lafiya da Nisan kwana tareda tabbataccen tsari da kariya.

Fitowa sukai suka nufi gym dinsa har lokacin Mr Omar na bayansa suna shiga a Dan qaramin palon dake ciki maleek ya zauna tareda Dan lumshe idanuwansa dasuke Dan nuna yayi rashin lafiya sbd sunyi haske sosai sun 'dan fada sai hakan yayi kaman yaqara Masa kyan fuska.

Cikin nutsuwa Mr Omar ya matso daga bayansa yace"

MALEEK garin meriz ne jekadi ta farka tun dazu nayi magana da ita a dakin littafai ta tabbarminda.....shiru yayi tareda sauke Kai.

Dagowa maleek yayi batareda ya kallesaba yace"

Uhum...

Sake gyara tsayuwa mr Omar yayi Yana Dan gyaran murya a raunane yace"

Jinin mushrah ce tayi wannan aikin.

Alokacin ya dago manyan idanuwansa dasuka koma fararensu tas ya dorawa Mr Omar dayayi saurin yin qasa da Kai Yana cewa"

Afuwa MALEEK Amma tabbacen zancen kenan na duba shayin da jekadin ta gabatarmin tareda tabbacin zancenta na cewa tun a gizah taga abin zargi atattare da jinin mushrah din.

Shiru dakin ya dauka tsit na tsawon lokaci maleek baice komaiba

Mr Omar Kuma jiran damar dazai cigaba da koro bayanin sauran zancen.

Ko motsi maleek yayi Mr Omar yasan manufarsa Dan haka shirun maleek din ya tabbar Masa da abinda zaiyi ya juya a nutse ya fita tsawon mintuna uku saigashi tareda jekadi da itakam ta zurma sosai ba laifi saidai jikinta lafiya kalau takejinsa Mr Omar ya rufe kofar ya qaraso yace"

MALEEK ayanda jekadi tayi bayani Babu sanin mushrah ko wani daga cikin ahalinsu gameda wannan aiki na 'yar uwarta,

Akwai banbancin halaye da ra'ayoyi me girma a tsakaninsu Wanda Kai tsaye zamuce hassada kokuma rashin wayo yasa wani daga cikin gizah yake amfani da ita batareda tasaniba.

Kallon jekadi maleek yayi cikin nutsuwa da kamewar murya yace"

Inawa jekadi ya jiki tareda barka da arzikin samun lafiya.

Cikin girmamawa me girma tace"

Godiya nake maleek hakama jekadi nayi maka sannu da jiki.

Maleek kaman yanda kasani Babu inda wannan aiki yafito sai a gizah Kuma kamar koyaushe dai zarginmu Yana yawone akan mutane da yawa musamman idan mukai la'akari da bincikenmu damuketa fama a dunkule na rasuwar mahaifinka,

Tsawon shekarun Nan Danayi a delah naqi barowa nayi bin duk wani diddiqin sirri Babu wani alamar acan ko wanenen me wannan garin na meriz yake Amma yau bayan shekaru masu tsayi garin yasake bayyana Wanda hakan na nufin garin meriz a cikin delah gizah yake.

A Daren ranar dazamu zo cikin dare Naga abin zargi a sassan baquwar mushrah Amma sbd na tabbatar nashiga najata da wani zancen Kuma tabbas hancina ya shaqi kusan qamshin meriz Amma sbd tabbatarwa naqi magana sbd tasamu damar zuwa dashi anan mu tabbatar da hujja saidai banyi zaton zatayi tsaurin aikata abinda aka aikota dinba ayimin afuwa MALEEK.

Kuma kaman yanda Mr Omar yafada hassadace me qarfi a tsananin padime da mushrah wadda ta samo asali daga cigaban aure da mushrah tasamu na MALEEK Kuma haryanzu mushrah batasan da wannan halayen na 'yar uwartaba Dan kuwa ko wannan zuwan nata inada tabbacin Babu alkhairi acikinsa sbd iyayensu takanas kaleeb yayi magana dasu bayan nayi Masa bayanin komai na ranar danaga mutum yafita daga sassanta Dan haka Ina me roqo da neman afuwan maleek akan kada yayi fushi da mushrah akan laifi mafi Muni da jininta ta aikata.

Tsit suka kumayi gabaki dayansu na tsawon lokaci maleek na nazartar abubuwa da dama acikin kansa wainda ba komai bane sai mutuwar mahaifinsa dayayi wato mutuwar azaba yanaji Yana gani duk da Yana yaro qarami lokacin Amma Yana iya tuno azabar dayaga mahaifinsa aciki,

Tun daga lokacin Basu sake ji ko ganin wani Abu daya danganci garin meriz ba sai yau sama da shekaru arbain kenan.

Tabbas zarginsu ya tabbata cewar a gizah kowanene yake Dan haka yanxu Kam aikinsu na gaske zai fara.

Dagowa yayi ya kalli Mr Omar dake jiran umarni ya maida idonuwansa kan jekadi Kai tsaye cikin kamewa yace"

Baza'a bari kowa yasan da zancenba ciki kuwa harda ita datayi aikin ki maidaita gizah idan tanacan ne za'a San waye shugaban aikin nata sbd na tabbatarda ita kanta nasan wa takewa aikiba sbd al'amarin me girmane bazasuyi saurin bayyanarda kansuba,

Amfanin wannan aikin na meriz da aka sata shine komawata gizah neman magani sbd sunyi tunanin acan ne kawai za'a samu maganin warkar Dani dagacan ne zasu qarasa niyarsu wadda baasantaba.

Gyada Kai jekadi tayi tace"

Kabar komai ahannuna kafin ka iso gizah Inshallah aikin yayi nisa

Inshallah sai Allah yacika nufin kaleeb Dan kuwa alqawarine sai anciyar da dabbobin gizah Naman duk Wanda ko da ido yataba ganin garin meriz bare ya taba.

Mr Omar ne ya matso yace"

Jekadi sai magana ta gaba itace umarnin maleek ne kada mushrah tasan abinda yafaru sai lokaci yayi hakama iyayenta

Duk abinda tayi idan lokaci yayi zatafada musu dakanta aranar qarshe da Babu gyara.

Gyada Kai jekadi tayi tana sake yiwa MALEEK fatar samun lafiya ta miqe ta fice.

Mr Omar kuwa gyara tsayuwa yayi yana sauke Kai yace"

Maleek meye ainihin wannan hukuncin na jinin mushrah da aka sanarwa jekadi.

Jininta ta aikata kuskure babba na cutatar da 'yar uwarta hassadarta tasa tasaka kanta cikin masifarda tun kafin mahaifinta yazama saurayi bare yayi auren haihuwarta.

Wayar kaleeb ya karba da Mr Omar ya miqo Masa bayan yagama yimasa bayanin komai dasuke ciki suka fara magana kowanne cikin kalar nasa ikon da kamewa ta sarautar dake jininsu kafin ya ajiye wayar.

Miqewa yayi tareda nufar kofa sai ya dakata ahankali batareda ya juyoba Kai tsaye yace"

Ka bawa jekadi muriz din damuke ajiya sbd bincike abisaga umarnin kaleeb kullum abata drop daya acikin abinsha ahaka har agama gano ainihin shugabanta duk tsanani kada abari asan muriz ake Bata sbd kaucewa basu alamar ansan dasu.

Cikin jinjina Kai Mr Omar yace"

Yanda kaleeb yace shine daidai.

Fitowa sukayi suka nufo ciki Koda suka shigo direct sama maleek ya wuce kasancewar NURU batanan hakama afia yasa jekadi da kanta ta tsare kitchen harsaida Fana tayiwa maleek din breakfast aka jere Masa Mr Omar Kuma na daga bakin kofar Palo shima ya kafa ya tsare.

Padima datake jiran Jin mugun labari na kuka ya faru agidan taji Babu komai batajin motsin kowa alamun lafiya Amma duk da hakan qin fitowa tayi tanajin hankalinta

Sam be kwantaba gabaki daya gizah takeson komawa ta karbi dukiyarta da tukuicinta na aikin da aka sakata da dasa tata cin sabuwar duniyar.

Sai yamma sosai su NURU suka dawo cikin farin ciki da walwala suke duk su dukan sbd Gama exams dasukai.

Wanka nuru tafarayi ta Sanya blue pencil jeans da farar _Gaultier_ top me hannun shimi ta fito a kicinma taci abinci tanason mgn da jekadi Amma Sam jekadin taqi Bata dama qarshema ce Mata tayi allergy ne Kamar yanda Mr Omar yafada Mata.

Padima Saida NURU tadawo tafito suna fira sama sama Dan takasa sakewa Kai tsaye tacewa NURU gida zata koma.

Da mamaki NURU ta kalleta zatayi mgn jekadi ta qaraso cikin girmamawa ta kalli NURUn tace"

An kammala maganin maleek.

Da wani irin farin ciki me tsanani data danne padima ta juyo ta kalli jekadin tanajin dukkanin damuwarta ta yaye kenan yasha tea din boyewa suke baida lafiya kenan.

Miqewa NURU tayi tabar gurin tana cewa"

Padima Ina zuwa.

Murmushi me Fadi jekadi tasakarwa padime tana cewa"

Ki huta lafiya jinin mushrah.

Cikin farin ciki padime tace"

Yawwa.

Dama tanason sanin halinda yake ciki duk da tasan yanzu ko kallo bazata samu daga maleek dinba Amma tanason tabbatarwada yasamu lafiyar Dan haka ta dauki tray din ta fito kenan ta hadu da farhat tana cewa"

Aunt NURU abincin daddy ne wanna?

Gyada Mata Kai kawai NURU tayi tana cewa'

Bari na aje anan ki jirani na sanyo jallabiya saimu Kai Masa.

Jekadi dake fitowa daga kicin ta matso gaban NURUn a natse tace"

Abincin maleek ba'a barinsa ako Ina shiyasa ko jiya yasamu allergy.

Kallon kanta tayi taga shigar Sam Bata daceba da zuwa gurinsa zatai magana jekadi ta sauke Kai tana cewa"

Afito lafiya.

Numfashi me sanyi ta sauke tareda daukan tray din tana satar kallon hanyar dakunansu tafara hawa saman sbd kada afia ta fito.

Tana shiga palon farko ta tsaya kofar palonsa na kurya tana sauke ajiyar zuciya sbd gabanta dake faduwa ta kalli farhat data bude kofar Kai tsaye ta shige tayi gurinsa

da gudu Yana zaune kan royal kushin yayi crossing fararen qafafuwansa da Babu takalmi sai daukan ido suke kaman baya taka kasa dasu.

Shigowa tayi qafafunta na Dan rawa ta qaraso ta ajiye tray din kan table tana dagowa maleek dinma na waiwayowa yayi Mata kallo daya ya juya sbd kayan dake jikinta.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

SAFIYYAH HUGUMA

BILLYN ABDULL

MISS XOXO

HAFSAT RANO

MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/22, 9:08 PM] +234 814 307 3081: *_Mamuhgee 27_*

Wani irin 'dumi taji Yana yawo cikin jikinta sbd akaro na farko arayuwarta da jikinta ya hadu Dana wani ba kayan komai ajikinta ga jikinsa da zafi Sosai sai qara manne jikinsu yakeyi Yana sassauke ajiyar zuciya ajere batasan lokacinda ta rufe idanuwanta ba tana sake shigewa jikinsa sosai sbd ganin kaman hakan na rage Masa Abinda yakeji,

Ahankali tazagaya da hannuwanta zuwa bayansa ta rungumesa da kyau take wani wawan jiri ya debesu su dukan ba shiri ya xebe kan makeken round royal bed din dake make da tsakiyar dakin shine a qasa itace a samansa ya lumshe idanuwansa tareda budesu daqyar ya kalleta yaga yanda idanuwanta sukai lahu alamar batada zabi sai nasa ya juyar da ita gefe ta kwance tareda sake shigewa jikinta ahankali Yana fidda wani boyayyan wahalallen numfashin tsananin azaba.

Ganin haka yasa hankalinta yatashi tasake rudewa ta qanqamesa cikin jikinta tana shafa bayansa da tafin hannuwanta ahankali ahankali tana karanto addua sbd batasan takamaimai mezatayiba ga jikinsa har lokacin da wani irin zafi.

Zameyi da sauri ta sauko gadon idanuwansa na rufe har lokacin ya dungule guri daya sbd azaba ta Sanya hannu ta zare wandon rigar baccinta tareda pant dinta cikin tashin hankali da sauri ta nufi toilet dinsa ta fada daqyar ta iya gane kan toilet din ta sakarwa kanta ruwan sanyi masu tsananin sanyi harsaida numfashinta yakusa daukewa sbd sanyi haka ta daure ta fito da sauri ta nufo gurinsa

Ya bude idanuwansa daqyar yayi Mata wani irin kallo yanajin 'yarinyar qarasashi kawai zatayi daga kwance kafin ya lumshe ido tashige cikin jikinsa sanyin jikinta na shigarsa yasake qanqameta Yana cusa kansa cikin wuyanta dake zuba qamshin turaren _Byredo_ ya sake Kai fuskarsa kan tata suna shaqar numfashin juna sosai ta bude fararen idanuwanta itama dasukai taushi ta kallesa shima ita yake kalla da nasa jajayen idanuwan tanajin hannuwansa na yawo jikinta Amma Bata iya motsawa sbd har lokacin cikin azabar ciwon yake Saida duk sanyin jikinta yashige nasa jikin itama jikinta yadauki dumin nasa yafara sauke ajiyar zuciya yanajin sauki saukin tsananin zafin dayakeji.

Tsit dakin yayi bayan sanyin AC daketa yawo a dakin Babu me motsi acikinsu musamman ita dake cikin jikinsa a nade numfashi ma ahankali take fitarwa sbd tsananin hali na kunya datakejin kanta aciki yanzu sbd ayanda taji yayi tsit tabbas sauqi yafara zuwar masa.

Tsawon lokaci suna ahaka Babu me motsi ahankali ta zame Yana jinta Amma bai motsaba ta tashi zaune ta gyara Masa rufa ta sauka gadon ahankali ta dauki kayan baccinta ta maida tareda dauke towel dinsa aqasa ta maida toilet tafito tasake taba jikinsa har lokacin da zafi Sosai sauqin kawai shine Yana iya daure ciwon yanzu Dan haka ta juya ta nufi kofa Dan zuwa gurin jekadi Koda akwai maganin daza'a bashi sbd tsananin zafin jikin yayi yawa idan Babu zata Kira Mr Omar yanxu cikin Daren nan yazo anema likita.

Saukowa tayi tana duba qaton agogon dake Palo daya nuna qarfe biyu da mintuna hudu ta nufa dakin jekadi Kai tsaye ta bude tashiga Bata gantaba.

Da mamaki cikin tsoro ta Isa kofar toilet din dakin cikin rashin nutsuwa takira sunanta harso biyar taji shiru a rikice ta bude bayin tana jefa idanuwanta ko Ina Amma bata ciki ko rufe kofofin bataiba ta fito da gudu tayi dakin mum Sarah tana bude kofar tayi saurin zaro ido tareda qarasowa cikin firgici tayo kan jekadi da jikinta haryafi na maleek yin jajir da daukar zafi ta dago arikice tace"

Mum Sarah kikawo ruwan sanyi sosai da towel da sauri.

Hannuwanta har rawa sukeyi tafara ragewa jekadi kayan jikinta tabarta daga ita sai shimi

Ta karbi towel din da mum Sarah ke miqo Mata yadau sanyi sosai sbd ruwan kankarane aka saka Masa ta ya6a Mata ajiki take sanyin yafara shigarta tafara jero ajiyar zuciya a wahalce.

Ganin hakan yasa NURU ta miqe da sauri kafafunta har rawa sukeyi ta nufi dakinsu kota kan afia dake kwance a qasa batabi ba ta zari wayarta ta fito sauri ta nufi dakin mum Sarah tana Nemo numbern Mr Omar dayake shima acikin mansion din yake Yana ganin kiranta ya tashi zaune sbd koyaushe a shirye yake kullum dare Baya wani dogon bacci sbd tsaro.

Cikin girmamawa ya dauka da cewa"

Barka da.....a yamutse ta katsesa da cewa"

Mr Omar maleek da jekadi sunci ko guba kokuma wani Abu daban kaga kawai kazo yanzu yanzu matsalan babbane, maleek... maleek..jikinsa duka yayi wani...

Ko rufe Baki batayiba taji buga kofarsa

Ta dago a tsorace ta kalli kofar palon zuciyarta na bugawa da qarfi sbd tsananin tsoro

Ta cikin wayar dake kunnenta har lokacin taji yace"

Nine abude kofar da sauri.

Da gudu ta qarasa kofar ta bude Masa dukkanin jikinta rawa yakeyi Bai dago ya kalletaba yace"

Zanduba jekadi ta jikinta zamu gano ko menene.

Da sauri tayi gaba tana cewa'

Zo zo zo kaduba suna cikin tsananin azaba,

Maleek ya....shiru tayi tana kaucewa ya qarasa gurin jekadi da sauri

Kallo daya yayi Mata yasan menene

Da sauri ya daga hannunsa daya yakai bakinta saikuma ya kasa tabbatarwa ta hakan ya dakata cikin tsananin tashin hankali yace"

Idan na tabbatar garin asirin Kona jinine Wanda zai.....

Cikin tsawar dabatasan Tai Masa ba tace"

Mekake jira ka tabbatar Mana maleek na can cikin irin halin kayi sauri kafada mana abinda za'ayi kokuma Akira Dr Damien kaduba kaga halinda suke ciki...

Sake sauke Kai yayi cikin Dan Jin nauyin zancen yace"

Bakinsu za'a laso aji idan da daci sosai.

Wani irin kallo Tai Masa itama cikin tsananin Jin zancen wani iri daga sama.

Ganin kallonda mum Sarah Tai Mata ta sauke Kai haka shima Mr Omar din yasata Shan jinin jikinta sbd hakan na nufin itace Dole zataje ta dandano musu na maleek tunda dai Babu me iya Shan na jekadi hakama maleek Dole sai ita Dan dama irin wannan masifar idan ta samu mutum Miji ko Mata ke lasa bakin idan Kuma yarone iyayensu idan tsofine yayansu.

Juyawa tayi da sauri ta fita ta nufi hanyar sama zuciyarta na bugawa a qarfafe sbd tsoro haka ta qarasa dakin har lokacin Yana kwance lullube idanuwansa arufe ganin hakan yasa ta qarasa da sauri ta haye gadon Bata tsaya wata wataba takai fuskarta dap da tasa zuciyarta na harbawa tasa hannuwanta biyu ta tallafo fuskarsa ta rufe idanuwanta ta Dora qaramin bakinta kan nashi ta zura harshenta cikin bakinsa ahankali ta laso sai alokacin ta bude fararen idanuwanta ta kallesa ga mamakinta saitaga idanuwansa a bude hancinta yake kallo.

Da sauri ta zabura tareda zare bakinta tana saukowa gadon dukkanin jikinta na rawa tayi kasa da kanta zatai mgn can qasan maqoshinsa ya bude Baki a wahalce yace"

Idan jekadi ce ko mr Omar kice abinda suke zargine Mr Omar yasan password na inda maganinsa yake

Daga haka ya maida idanuwansa ya rufe sbd azabar abinda yakeji cikin jikinsa

Da sauri ta juya daga dakin ta fice zuwa qasan har tana hada bene uku uku gurin saukowa ta iso dakin da sauri ta kalli Mr Omar muryarta na rawa tace"

Yace shine duk abinda kuke zargi din kayi sauri ka dauko antidote din yace kasan komai please please please hurry Mr Omar...

Cikin sauri sauri shima yace"

Ok ok Amma Dole saimun tabbatarda bakin nasa akwai "daci sbd ta hakan zansan idan yagamabin jininsa..

Rikicewa tayi tana rawar murya tace"

Eh"kawai sbd ita Bata wani gane daci acikin bakinsaba gabaki daya ta rude da wani irin dumi da qamshin _Vedshakti lemon mouth freshner_ data debo abakin nasa Dan haka bazata iya tantance komaiba.

Tashi Mr Omar yayi ya fice daga dakin da sauri haryana tuntube tabarsu cirko cirko a tsaye kowa kayan cikinsa na juyawa sbd fargaba.

Jin shiru shiru yasa NURU fitowa takalli agogo lokacin har qarfe uku da arbain tayi tafito Palo yafiso goma tana komawa dakin mum Sarah Jin take Kamar tayi Ari hauka ta dauko wayarta zata Danna Masa Kira sai gashi yashigo da gudu gudu ya miqa Mata Yana cewa"

Hada da ruwan zafi kikai Masa yasha inshallah zafin zai sauka gabaki daya bayan asuba saina Kira Dr Damien.,

Idan yasha zaiyi amai sosai karki basa komai bayan wannan sai bayan 2 hours.

Karba tayi tayi kicin mum Sarah na bayanta jikinta na wata irin rawa take dafa maganin harsaida mum Sarah ta matso cikin tausayi da damuwa itama tace"

Ki nutsu Inshallah maleek da jekadi Babu abinda zaisamesu.

Gyada Kai tayi kawai tana dauko cup cikin cups din MALEEK dake gurinsu daban ta zuba Masa ko a tray Bata tsaya dorawaba ta dauka ta fice da sauri tana cewa"

Mum Sarah ki zuba kiyi gaggawar bawa jekadi.

Tana Isa dakin ta ajiye cup din saidata qara sanyin AC kafin ta qaraso gadon ta aje cup din kan bedside ta kallesa tanajin nauyin yanda zata bashi sbd tagama fahimtar Dan idanuwansa na rufe bashine ke nufin Yana bacci ba.

Kafin tayi wani yunquri taga ya motsa tareda bude idanuwansa Yana tashi zaune batareda ya kalletaba ya miqa hannu daqyar

Dasauri ta dauko cup din ta matso ta miqa Masa tareda tsayawa akansa Kamar zata fasa kuka sbd Jin yanayin take har cikin ranta.

Kurbi daya yayi ya dakata sbd abinda yakeji ta matsosa sosai cikin kulawa da damuwa tace"

Yace duka za'a shanye.

Ko kallonta Bata samu damar yayiba yasake daga cup din yasha Yana rufe ido tareda shanyewa ya miqa Mata cup din da sauri Yana saukowa gadon ya nufi toilet yafara kelaya wani irin aman azaba Wanda yasata kasa hkr tabisa ciki idanuwanta na cikowa da ruwa musamman ganin Aman hadda jini sosai aciki ta rude tana dafa bayansa da har lokacin yake bayyane ba Kaya ajikinsa Dan abin kamar daurin Rai da dai towel dinsa har lokacin be kunce ba koya kunce akwai qaramin gajeran wando ajikinsa.

Saidayayi mugun amai sosai kafin taji take zafin jikinsa ya sauka gabaki daya ta zuba Masa ruwa ya wanke fuskarsa da bakinsa ta fito tabarsa aciki ta sake gyara Masa gadon da duk suka cukuikuye sbd rudewa ta dauki cup din ta fice daga dakin tun kafin yafito sbd ta lura tun cikin toilet din yadawo MALEEK dinsa.

Gurinsu jekadi ta Isa da sauri itama cikin sa'a ta tararda ta amaye komai gabaki daya ta shigo suka kamata tareda goggge Mata jiki suka kwantar da ita take baccin wuya ya dauketa sai alokacin dukkaninsu suka saki ajiyar zuciya me qarfi abinda takeji tokare a zuciyarta ya fada Mata ta dafe goshinta tana sake sakin jerin ajiyar zuciya kafin ta dago dmta kalli mum Sarah tace"

Menene yafaru bayan shigewata da daddaren?

Ajiyar zuciya mum Sarah tasaki tareda sauke Kai qasa cikin rashin sanin takamaimai na komai tace"

Bansaniba

Kawai dai abinda nasani shine jekadi tashigo dakina acikin wannan halin

Abu daya tace shine na jininta na quna.

Wani sabon numfashin takuma saukewa me zafi kafin ta bude Baki tace"

Shikenan zuwa da safe idan duk sunji sauki zamuji abinda ya samesu

Ki lura da ita Mr Omar zai Kira Dr bayan asuba.

Juyawa tayi ta fice jikinta a matuqar mace sai yanxu takejin tsamin jikin guje gujen dataitayi daga sama zuwa qasa ta nufi dakinsu ta fada kan gado tareda lumshe idanu tana godewa Allah dayasa komai ya tsaya nan Amma Kuma zuciyarta na Bata wani irin yanayi Mara Dadi na afkuwar al'amarin sbd idan har ciwon maleek ne kaman yanda yasaba to ita jekadi fa?

Gabaki dayama wannan ciwon wani babban abune na daban sbd azabar dasuka Shiga sai me qarfin jini ne kawai zai iya dauka dan kuwa taga tsananin azabar dasuka shiga musamman MALEEK.

Bude ido tayi ahankali tasake lumshewa har lokacin tanajin dumin jikinsa daya Shiga jikinta sbd ba qaramin full body contact suka samu ba Dan ita yacire rigarta shikuma dama Babu anasa jikin.

Saurin rintse ido tayi da qarfi tana cire tunanin cikin ranta ta gyara kwanciya Dan tasamu bacci ya Dan dauketa kafin asuba.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899*_Mamuhgee 29_*

*YERWA INCENSE & MORE*

(The scents with diff essence for YOU& your HOME)

(MASARAUTAR KAMSHI)

Ina masu neman kayayyakin kamshi yan nahiyar ketaran chadi da Senegal? Kai harma da ingataccen had’i yan bornu? To ku matso domin nesa tazo kusa...

YERWA INCENSE & MORE: Sun zo muku da kayayyakin turaruka kamar haka:

Khumra kowacce Iri.

Turarukan Wuta

Mopping khumrah

Washing khumrah

Bathing khumrah

body mist

kullaccam

scented hair cream/spray

wardrobe balls

carpet spray

air-fresheners

scented pebbles

body sprays

oil perfumes

Perfumes

kabbasa

burners

coal igniter

tong

kasko

english coal

dilke&halwa set

scented body mist

_kai dama sauran kayayyakin da bamu ambata, YERWA INCENSE AND MORE, Na tura kayayyakin su koina a fadin Nigeria da ketare. Domin tuntubar su. Suna instagram: _@yerwaincense_and_more. Ko Facebook site:YERWA _COLLECTIONs. Ko a duba su ta number su: _*08095215215/09044191709*! _

suna bada kayan su kan sari ko sayi dai-‘dai

****

Harta Gama zuba Masa ta ajiye Bai Bai Kuma waiwayowa ba amfani yake da wayarsa sai farhat dayake tankawa ahankali,

Juyawa tayi zata fice batareda ya kalla inda take ba yace"

Kijira ki tafi da kayan.

Dakatawa tayi tareda sauke ajiyar zuciya boyayya sbd atlas dai yanuna yasan da shigowar mutum ba farhat kadaiba.

Juyowa tayi ahankali tadawo daga gefe ta tsaya tana Dora kallonta kan tv dake aiki Sam bama murya kusan gabaki daya Wanda ta fahimci qaidar iya muryar tv dayake buqatane ahakan.

Ganin tsayuwar Kamar zata damesa saita sulale ahankali Takoma palonsa na farko ta zauna tana kallon tsari da haduwar palon Wanda kusan komai na palon milk ne.

Juya idanuwanta tayi kan wani qaramin hoton LAILAH dake cikin qaramin milk frame tana tareda maleek din dukkaninsu cikin qananun Kaya black shi Yana zaune gabaki daya hankalinsa nakan wayar dake hannunsa itakuma ta rungumosa tana dariya fararen haqoranta tas a bayyane sunyi kyau.

Dokawa taji qirjinta yayi ta dauke kanta daga kallon hoton tareda Dan hadiye yawu tana qoqarin Wasa da yatsun hannunta.

Kasawa tayi tasake juyowa gabaki daya ta qurawa hoton ido tana qarewa LAILAH kallo.

Kyakkyawace da kyanta yake a bayyane,gata da kyawun jiki Kamar ba ita ta haifi afia ba Kamar dai yayarta,

Wayewarta ko acikin hoton a bayyane take sbd yanayin shigarta da yanda take nanuke ajikin MALEEK Wanda son datake Masa yake bayyane afili shima alamunsa da yanda hankalinsa ke kwance qarara a hoton ya bayyanarda soyayyarsa ga matarsa.

Sake dauke kallonta tayi daga hoton jikinta nayin sanyi bugun zuciyarta na qaruwa ta waiwaya gefenda kofar dakin lailah din saitaji jikinta na Gaza Mata ta miqe tabar gurin ta koma cikin palonsa wannan karon sallamarta daqyar ta fito qasan maqoshi sbd shaqewar dataji maqoshinta yayi.

Qarasowa tayi kanta a qasa ta dauki tray din ta fice batareda tabi takan farhat ba dasukazo tareba.

Tana saukowa kitchen takai kayan ta wanke da kanta ta maidasu gurinsu ta fito ta nufi daki batareda Takoma gurin padima ba.

Tana zuwa daki ta fada kan gado takwanta tareda rufe idanuwanta tana sauke ajiyar zuciyarda batasan Kota mececeba.

Har dare Bata sake fitowa daki ba Koda padima tazo ta tambayeta ce Mata kawai tayi kanta na ciwo hutu take buqata.

Padima Bata damu da hutun da NURUn tace tana buqataba ta zauna gefenta tareda kallonta Kai tsaye tace"

NURU inason zankoma gida Kuma cikin gaggawa sbd kwana biyun Nan inata mafarkai marasa Dadi na abal da ammi kaman dai da akwai babbar matsala Dan haka Ni inaga zankoma gurinsa kada ya zamto babuke akusa Babu Ni.

Tashi zaune NURU tayi tana kallonta da yanayi na damuwa tace"

Amma ai nayi waya da abal ko dazu Kuma banji alaman matsala ko wani damuwaba bayan haka meye amfanin zuwanki kema idan Baki ga likita ba akan Taki lafiyan.

Yamutsa fuska tayi tana cewa"

Kibar maganar nawa ciwon sbd bana tunanin zan tsaya ganin likita naji sauqinsa sosai Dan dama kila hadda damuwar rashinki akusa ne yasa abin yayi tsanani yanzu Dana zauna dake naji saukin komaima kawai damuwata anan iyayenmu ne kiyi tunani kema kinsan Koda damuwa abal bazai taba Bari kiganeba barema Koda na baro fa bayajin Dadi kwana biyu Yana fama da ciwon tari...

Da wata sabuwar damuwar NURU ta kalleta tana cewa"

Amma meyasa tun zuwanki Baki fadamun abal bayajin dadiba padima?

Kinga shine ya gargadeni akan kada na fada Miki Kuma ko yanzu kada kiyi Masa maganar Dan zaisan cewa nafada Miki

Nidai gida zankoma jibi kiyi Shirin duk abinda Zaki bani da Wanda Zaki karbomin daga MALEEK,

Ni bana wannan ba NURU meyesa nakeganin kaman ba zaman aureba kike a gidan nan??

Dan Babu wani alamari daya danganci aure danaga Yana faruwa dake.

Shiru NURU tayi tareda dagowa ta kalli padiman tsawon mintuna sbd batasan me zataceba tunda kusan gaskia padiman tafada, ta sauke numfashi tareda Miqewa tana cewa"

Kidaina wannan tambayar padima

Ba lallai komai ake bayyanawaba

Tunda dai akwai auren komaima ahankali za'ayi.

Miqewa padiman itama tayi tana cewa"

To dai iyayenki saisu daina dukan gaban 'yar so tana auren MALEEK na delah gizah Dan kar ayi zaton wuta a maqera ajita a masaqa.

Juyowa NURU tayi ta kalli padiman da manyan idanuwanta ta matso daf da ita harsuna shaqan juna tace"

Ko a kasuwa za'a jita ba ruwanki bane ki Kama bakinki kadaki fadawa su abal abinda zaisasu damuwa sbd padima ba ruwanki da abinda zai kawo musu bacin Rai ko damuwa.

Murmushi padima tasaki cikin isashiyar muryarta tace"

Kiji da matsalar gabanki ta zaman aikin gida da renon mijin wata Ni kibarni zanji dasu abal din naki idanma labarin yakaimusu wata Rana Dan yanxu banjin zanyi lokacin isar musu da wannan labarin inada nawa sabgogin kawai dai kishirya min komai nafada Miki gida zankoma.

Wucewa tayi ta fice daga dakin tabar NURU nabinta da kallon takaici takaici sbd halin padima dai haka yake tun suna yara saidai kwana biyun Nan datazo musu tayi tunanin tafara sauyawane shiyasa taketa kiyayewa sbd kada suyi halinsu agabansu afia subarwa kansu abin takaici.

Zaunawa tayi kan kujera tana furzar da numfashi tace"

Zanyiwa jekadi magana ta maidaki tun kafin mufara halin acikin gidan Nan tunda kinji kingani kinfasa neman lafiyar ai shikenan kije ko Dan lafiyar iyayenmu.

Da daddare har daki tasamu jekadi zata zauna jekadi tayi saurin miqewa tana cewa"

Ba girmanki bane mushrah idan kinason ganinane duk inda kike zan sameki naji bayaninki ko umarninki.

Murmushin yaqe kawai tayi sbd duk ranta a jagule yake yau din daga wannan sai wannan.

Daga tsayen ta kalli jekadi da taushin murya da zallar gajiya da damuwar komai tace"

Jekadi padima zata koma gida jibi nafadawa Mr Omar yayi muku komai na tafiyar,

Idan kunje kibata wadataccen kaso acikin wainnan dukiyar dake can na dukiyar auren.....kasa karasawa tayi sbd Jin nauyin fadar kalmar aurenta

Itakuma jekadi Jin tayi shiru tace"

Yanda kikace haka za'ayi Inshallah"sbd ta fahimci abinda take fada.

Gobe ku shirya saimu fita akaiku kuyi siyayyar abinda kuke buqata.

Godiya jekadi keyi Allah yaqaro girma da kusanci tsakainki da MALEEK tareda tabbaciyar qauna.

Shiru tayi batareda tace komaiba saima sanyi da jikinta yayi ta juya zata fice jekadi tadago takalleta cikin tausayi da kaunarta saitaji bazata iyaba ta gyara tsayuwa tareda aje matsayinta na jekadi takira sunan NURUn cikin tsananin kulawa kaman yanda ta Saba a da.

Tsayawa NURUn tayi tareda waiwayowa ta juyo gaba daya damuwarta na raguwa sbd tasan jekadinta ta Da ce kafin tazama Matar maleek.

Takowa jekadi tayi tazo har gabanta takamo hannunta tajata zuwan kan kujera ta zaunar da ita kafin itama ta zauna ta fuskanceta cikin kulawa a natse tafara cewa"

NURU aure da kike gani Kona soyayyane saika dage da kulawa da naci akan wasu abubuwan sbd kusan a rayuwar aure ke mace kece zakija ragamar Kama hanyar zuwa wani mataki,

NURU kinshigo wata irin baudaddiyar rayuwar aure wadda kike buqatar juriyada kokartawa kafin kisamu matsayinki na Matar gida idan ba hakaba rayuwarki da quruciyarki zasu qare su tsufa cikin tausayi me tsanani,

Aure gidan sarauta musamman irin naki auren dayake da qalubalai da tazarori masu yawa,

Shawara daya anan itace ki maida hankali ki dage karki dage a Gina karatu kawai ki zauna kiyi nazari aurenkima kina buqatan dage Masa Dan bawa kanki suna da matsayi a gidanki sbd karki tsufa agidanki bakisan suna ko matsayinki a gurin Wanda kike aureba Dan kuwa wannan wata rayuwace da Kika shigo ba Babu fita sai

mutuwa hakama akwai qalubalai agabanki Dan haka ki nutsu kiyi abinda yakamata kiyiwa kanki yaqi kema Dan tabbatarda zamanki acikin aurenki sbd auren MALEEK babban rabone agareki ki,

Kibude idanuwanki ki daina yadda da kowa da komai sai abinda zuciyarki ta nutsu dashi NURU.

Sai alokacin ta dago ta kalli jekadin jikinta duk yakuma yin sanyi ta bude baki ahankali tace"

Nagode jekadi.

Gyada Mata Kai jekadi tayi tana miqewa tace"

Ranki ya dade Zaki iya tafiya.

Miqewa tayi ta nufi kofa tana Jin gabaki daya gajiya takeji sbd sanyin da jikinta ketayi ayau din daga wannan sai wannan.

Dakin farhat ta wuce kawai sbd acan zata samu nutsuwa yanzu kawai

Tana shiga ta nufi toilet tayo alwala ta fito daidai shigowan farhat Nan suka shirya sukai sallah tare daganan tacewa farhat baccin awa biyu zasuyi kafin la'asar

Nan suka kwanta.

##MAMUH##

KUYI MANAGE.

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899[9/25, 5:30 AM] +234 706 452 3456: *_Mamuhgee 30_*

*YERWA INCENSE & MORE*

(The scents with diff essence for YOU& your HOME)

(MASARAUTAR KAMSHI)

Ina masu neman kayayyakin kamshi yan nahiyar ketaran chadi da Senegal? Kai harma da ingataccen had'i yan bornu? To ku matso domin nesa tazo kusa...

YERWA INCENSE & MORE: Sun zo muku da kayayyakin turaruka kamar haka:

Khumra kowacce Iri.

Turarukan Wuta

Mopping khumrah

Washing khumrah

Bathing khumrah

body mist

kullaccam

scented hair cream/spray

wardrobe balls

carpet spray

air-fresheners

scented pebbles

body sprays

oil perfumes

Perfumes

kabbasa

burners

coal igniter

tong

kasko

english coal

dilke&halwa set

scented body mist

_kai dama sauran kayayyakin da bamu ambata, YERWA INCENSE AND MORE, Na tura kayayyakin su koina a fadin Nigeria da ketare. Domin tuntubar su. Suna instagram: _@yerwaincense_and_more. Ko Facebook site:YERWA _COLLECTIONs. Ko a duba su ta number su: _08095215215/ 09044191709_

suna bada kayan su kan sari ko sayi dai-‘dai

****

Washe gari tunda safe Kamar kusan dai yanda ta Saba kitchen ta nufa aikin breakfast tayi su Fana da mum Sarah na tayata suka hada abincin safen saina maleek data hada Masa daban ta jera a tray sbd har lokacin Bai fara saukowa qasa cin abincin tareda 'yayansa Kamar yanda ya Saba ba

Ga afia har lokacin batasan yayi rashin lafiyaba ko da safen taje har sama ta gaidashi Amma bataga komaiba lafiya kalau ta gansa.

Tana gamawa tabarwa Fana aikin jera abincin a dining ita ta dauki nasa ta fito saidataga alamamun afia na daki kafin ta haye sama cikin sa'a kuwa baya palon saita ajiye ta juya ta fitowarta.

Tana saukowa dakin Farhat ta nufa Dan har lokacin bacci take itama kusan gidan yau kowa na gida tunda hutu suke.

Zaunarda farhat din tayi tana cewa"

Sweetie kitashi Haka fa ko kinmanta yau zamuje yawo.

Cikin bacci ta bude Yan idanuwanta tace"

Aunt ai ba yanzu zamuba Saida Rana kibari muyi bacci Mana.

Murmushi tayi kawai tareda kyaleta ta wuce toilet dinta anan tayi brush ta fito ta nufi dining Bata jira kowaba ta zauna taci ta koshi ta tashi ta nufi dakin padima dake zaune tana latsa wayarta ta dago suka kalli juna tasaki murmushi tace"

Ranki ya dade ta tashi kenan.

Batajin biyewa padiman Dan haka ta datse zancen da cewa"

Padima idan kinci abinci ki shirya anjima zamu fita ko.

Dan Dadi taji ta qaraso gurin NURUn tana cewa"

Inane zamuje?

Ko amsa Bata bataba ta juya ta fice tana cewa"

Ba takamaimai ko Ina aka samu zuwa za'ayi.

Qaramin tsoki padima taja tana dawowa ta zauna bakin gado tana cewa"

Duk zanyi lokacinkine daga baya indai fara Isa komai yashigo hannuna tukuna.

Dakinsu Takoma ta tararda afia zaune tana waya cikin damuwa take cewa"

Inshallah anjima zamuzo aunt Allah yabashi lafiya yasa kaffarane duk wannan.

Kashe wayar tayi tareda dagowa ta kalli NURU data tsaya tana kallonta cikin son Jin wayene baida lafiya taga duk afian tashiga damuwa.

Numfashi me zafi ta fitar kafin ta zauna bakin gado cikin sanyi tana cewa"

Jikin Imran ne yayi tsanani tana cewa sai anyi Masa aiki,

NURU inaga duk wannan nice sanadi.

Kallonta NURU tayi jikinta amace sosai itama da tausayin Imran din sbd tabbas tasan Imran na Mata so me qarfi Amma ya suka iya Haka qaddara ta taho saidai hakuri.

Muryarta a Sanyaye tace"

Kidaina fadan haka wannan duk yin ubangiji ne haka ya tsaro dama

Shima Inshallah zaiji sauki ahankali zai Saba ya rungumi kaddara da zaran yasamu wadda zata kula dashi.

Kallonta afia tayi da tunanin idan kulawa zatashi mantawa da komai ya dangana ya warke itace tafi kowa kamata tabashi sbd itace sanadin rabasu harya shiga wannan halin Dan haka Inshallah zatai iya kokarinta gurin sauke wannan alhakin dake kanta ko Dan haqqinsu ya sauka daga kanta.

Shiru sukayi dukkaninsu kowa da tunanin daya Dan fada musamman NURU datake ganin gwara Imran din yasan rashinta shine takamaimai matsalarsa idan yaso yaqar matsalar Yana tilastawa kansa mantawa da ita shikenan yayi maganin tasa matsalar

Amma ita haryanzu batasan matsayin kantabama bare tasan meye tata matsalar hartakai ga maganinta

Ita kawai rayuwar take aduk yanda tazo Mata.

Qarfe biyu Sukayi wanka suka shirya

afia ta fita zuwa Taya farhat shiryawa tabar NURU na sauya wasu kayan sbd riga da wando tafara sakawa taga basuyiba ta sauya zuwa riga da skirt Suma taga basuyiba qarshe ta Sanya wasu maroon _Yves Saint Laurent_ riga da wandon Palazzo dasuka fiddo zallar yarintarta na matashiyar wayayyiya musamman kalar ta yiwa fatarta kyau ta Sanya wedges takalmin _CH/HC carolina Herrera_ black tazo gaban mirror zata fesa turarukansu dake jere saita fasa ta dauki _Lady l_ na _Acqua di parma_ ta fesa Wanda ya hadu da kamshin body mist dinta da spray na _ royalle Nina Ricci_ suna bada qamshinda sai ka kusantota sosai zakajishi

Tana daura scarf a kanta afia tashigo ta Isa gaban mirror tasake gyara fuskarta ta juyo tace"

Everyone is waiting for you fa kowa yafito.

Wayarta kawai ta dauka Banda handbag suka fito tareda afia din wadda itakuma heels ne takalmanta kusan Koda yaushe.

Suna fitowa Palo farhat tayi gurin NURU da duk ta cika musu ido musamman padima datake Mata kallon qyashi kafin ta dauke Kai tana sakin boyayyan tsokin da

NURUn taji Amma ta qyale kaman bataji komaiba suka fito dukkaninsu afia ke driving sai ita NURUn a gaba sai padima da farhat sai jekadi a bayan.

Mr Omar yaso NURU tabi motar driver sbd ganin kaman sunyi yawa a motar Amma tace tafi buqatan cikinsu din suka fice Yana musu adawo lafiya.

Gurin wasan farhat suka fara zuwa sukayi kusan 2 hours agurin kafin suka fito suka tafi wani qaton mall

acan suka Bata lokaci sosai Dan sai yamma sbd irin kayan da padima tayita dauka Babu Wanda yace tabari

Dan kanta dataga kayan sunmata nauyi tabari suka fito aka aika duka siyayyan kayan dasukai direct zuwa gida da motar mall din.

Har zasu fito afia ta nufa bakery dinsu akai Mata packaging cupcakes guda shida masu icing na chocolate kadan ta biya ta karbo ta nufosu NURU ta kalleta tana cewa"

Mezakiyi da cupcakes?

Zamu biya dubiyan Imran a hospital so nayi tunanin abinda zamu Kai bansaniba kila wannan zaiyi.

Mum manta duka amma da a gida za'ayo Masa wannan din Amma ko hakan ma inaga yayi.

Mota suka shiga suka nufi hanyar asibitin farhat se murna takeyi zataga Uncle Imran sbd akwai shaquwa da sabo tsakaninta dashi Dan Kam acikin dangin mahaifiyarsu shikadai tasani duk da shima bawai tasan asalin asalin alaqarta dashiba kawai abinda tasani uncle Imran kaman family dinsu ne.

Suna Isa harabar asibitin sukai parking dukkaninsu suka fito NURU da afia ne agaba sauran na biye dasu NURU na riqeda hannun farhat wadda sai tsalle tsalle take tana cewa"

Aunt NURU mu bamu siyawa uncle imran komaiba kaman afia.

Murmushi tayi tana cewa"

Munkawo Masa addua ai muma.

Receptionist suka tambaya room number din Imran jalal tafada musu a third floor room 10.

Suna zuwa kuwa dakin na farko farko afia ce tafara knocking tareda bude kofar ta tura tashiga ahankali da sallama abakinta saidai ganin wadda ke dakinta yasa dukkanin bakinta qafewa saidai gudun wani tashe tashen bacin Rai da bazasu qari kowa da dadiba yasa ta danne ta qarasa shigowa dakin NURU da afia suka shigo hannun farhat har lokacin yana riqe acikin hannun NURU.

Kallo daya NURU tayiwa Matar dake zaune ta dauke wuta zuciyarta na harbawa da qarfi ta dauke Kai ahankali tana kallon afia da yanayinta ya sauya gabaki daya ta maida kallonta kan dad din Imran din dake tsaye da Alama fita zaiyi duk saitaji tana neman shiga wani mummunan hali ta samo nutsuwa daqyar cikin kannewa ta saki fuska ahankali tacewa dad din Imran din"

Ina wuni,ya me jikin?

Alhmdlh Mrs MALEEK

Ya gida?ya maleek?and fmly?

Alhmdlh sir"tafada tana waiwayowa gefen LAILAH dake zaune dukkanin qamshinta na turaren _Calvin klein boss lady_ yacika dakin tana sanye cikin wasu set na byredo ash kala komai nata kana gani kasan manyan kudadene suka siyesa

musamman makeup din dake fuskarta Wanda akoda yaushe LAILAH Bata rabuwa da ita.

Wani abune ya wucewa NURU da kayar tasamu numfashinta ya saki ta bude Baki daqyar tace"

Barka da yini miss.

Wani irin murmushin tausayinsu su duka yaran tasaki sbd sai yau Allah yayi zataga matarda maleek yake aure yanzu,

Afia ta kalla zatayi magana

Afia tarigata da cewa"

Ina wuni mum.

Kin amsawa tayi tana cewa"

Wannan shine sabon manner dinki da farhat?

Da mamaki afia ta kalleta tace"

Sabon manner kuma mum?

Maida kallonta tayi kan farhat dake jikin NURU tana kallon lailah da dukkanin hankalinta sbd tanason zuwa gurinta tana shakkar irin tsawar da lailan ke Mata wani lokacin duk Bata mantaba sbd lailah batason Ana fado Mata ajiki kokuma yaro yace koyaushe Yana cikin jikinta.

Farhat kixo ki gaida mum.

Wani kallo lailah tayiwa NURU wadda gabaki daya Bata sake kallon inda lailan takeba sbd Jin take gabaki daya dakin ya gundureta ga Mr jalal ya fita ta zare hannunta daga na farhat da har lokacin take tsaye bataje gurin mum dinba ta nufi gurin Imran daya bude idanuwansa alokacin ya zuba Mata ta qarasa gurinsa ta zauna kan sofa ta qaqalo murmushi daqyar tace"

Ka tashi kenan Yaya jikin?

Bai dauke kallonsa daga kantaba ya gyada kai Yana miqawa farhat hannu cewa tazo.

Lailah zuwa lokacin ranta yafara baci sbd kowa sai acting dumb yakeyi ta gyara zama ranta nafara baci akan afia tace"

Afia nice na haifeki komai girman dakike ganin kinyi Dan haka you better stop acting dumb with me kafin ranki ya baci kokuma kinason nunamin zama da bayi kin manta girman uwarki,...

Da mamaki afian take kallon mum din cikin rashin sanin abinyi tace"

Mum please idan wani yabata Miki Rai acikinmu daga zuwanmu kiyi hkr Amma wlh Ni bansan me mukayiba anan,

Farhat kije gurin mum ki gaidata nace....

Just shut up afia

before I lose my cool ki fita daga gabana Dan Naga gabaki daya kin rasa tarbiyanki Kamar Ni Ina Miki magana kina cewa Farhat ta gaidani sbd nace Miki gaisuwan ne agabana kawai.

Hawayene suka ciko idanuwan afia sbd gabaki daya batasan metayiba da mum din keta faman wannan janye janyen ta bude Baki cikin rawar murya tace"

Kiyi hkr mum Amma dai kaman kina saukemin fadan da banawa bane.

Sai alokacin NURU da duk takejinsu ta Dan waiwayo afia din takai hannu zata dafata sbd ganin yanda hawaye suka tsinke Mata

Lailah ta aika Mata wani qanqantaccen kallo tana cewa"

Excuse me miss wannan tsakanin uwa da 'ya ne stay within ur limits ok

Bana saka trashes cikin al'amurana

For God's sake ma meyasa haryanxu kikeda auren MALEEK akanki bayan duniyama tasan bazaki tana zama Matar da maleek zai iya zama da itaba

Ke yarinya ce bazaki gane hakan ba Amma nasan Zaki gane kalmar pack and leave sbd ma nafasa komawa San Francisco zandawo gidan sbd afia na wannan little ant din sun dauki wani hali da bazan dauka ba..

Jekadi da padima dake bakin kofa suna Jin komai dadin duniya yagama kashe padima duk da Jin takeyi Kamar tashiga tayiwa lailan mugun duka Amma dai Kuma yanda take nuna isarta akan 'yayanta da NURU ta mallake yasata Jin Dadi taji inama tanada ikon shiga dakin taga yanayin NURU sbd har lokacin NURU Bata juyo ta sake kallon ko gefenda lailah maleek takeba sai lokacinda tace zata dawo rayuwar MALEEK NURU ta waiwayo ta kalleta daidai suka hada ido lailan ta gyara zama zatayi magana aka turo kofar data Sanya NURU kallon kofar da idanuwanta dasukai jajir sukai ido biyu da MALEEK Wanda Mr Omar ya budewa kofa

Shima ita ya kalla dakyau sbd baisan da zasuzo asibitin ba Amma ganin su jekadi a waje yasa yasan suna ciki.

Dauke kanta tayi tareda maidawa kan Imran sbd rashin sanin abinyi Dan gabaki daya dakin jintake numfashinta a toshe yake.

Lailah dake zaune har lokacin ta zubawa maleek fararen idanuwanta tana jiran abinda zai fara fitowa daga bakinsa idan ya idanuwansu suka Shiga cikin na juna.

Da fararen idanuwansa ya kalli Imran dake kokarin tashi Amma Babu me kamasa sbd NURU ce kawai a kusa dashi afia har lokacin tana gaban mum dinsu hawaye take na baqin cikin wannan halin da mum ta nuna.

Cikin kamewar murya Kai tsaye MALEEK yace"

Kana samun sauqi kenan,

Allah yaqara lafiya.

Maida kallonsa yayi kan NURU dataqi waiwayowa ta sake kallon kowa ahankali yace"

Muje.

Dagowa tayi ta kallesa direct cikin ido kafin ta dauke tana miqewa tsaye da wayarta a hannu ta wuce batareda ko sai anjima tayiwa Imran ba sbd a rayuwarta Bata taba yin mummunan danasaniba Kamar zuwanta asibitin Nan yau.

Tana fitowa Jekadi ta taso zata bita Mr Omar yayi saurin Yi Mata hannu Yana nuna Mata MALEEK da ido Takoma ta zauna tana cewa"

Allah ya tsare hanya MALEEK.

Harya fita ko afia alamu Basu nuna yasan dasu a dakinba bare lailah harya fice,

Ita kanta afia tashiga shock

ta dago ta kalli mum dinsu da Bata nuna damuwaba sbd tasan halin MALEEK dama Dole saita fuskanci fushinsa kafin yasan yanda zata sauko dashi dakanta sbd soyayyarta me qarfi dake ransa,

Ganin NURU yanzu datayi yasa taji bazata iya komawaba tana buqatar kasancewa da maleek yanzu Dan kuwa batai tunanin NURUn takai hakanba duk da yarinyace Amma tanada wani irin kwarjini me fizga.

##MAMUH#

[9/25, 5:30 AM] +234 706 452 3456: *_Mamuhgee 31_*

*YERWA INCENSE & MORE**

(The scents with diff essence for YOU& your HOME)

(MASARAUTAR KAMSHI)

Ina masu neman kayayyakin kamshi yan nahiyar ketaran chadi da Senegal? Kai harma da ingataccen had'i yan bornu? To ku matso domin nesa tazo kusa...

YERWA INCENSE & MORE: Sun zo muku da kayayyakin turaruka kamar haka:

Khumra kowacce Iri.

Turarukan Wuta

Mopping khumrah

Washing khumrah

Bathing khumrah

body mist

kullaccam

scented hair cream/spray

wardrobe balls

carpet spray

air-fresheners

scented pebbles

body sprays

oil perfumes

Perfumes

kabbasa

burners

coal igniter

tong

kasko

english coal

dilke&halwa set

scented body mist

_kai dama sauran kayayyakin da bamu ambata, YERWA INCENSE AND MORE, Na tura kayayyakin su koina a fadin Nigeria da ketare. Domin tuntubar su. Suna instagram: _@yerwaincense_and_more. Ko Facebook site:YERWA _COLLECTIONs. Ko a duba su ta number su: ___08095215215 / 09044191709_

suna bada kayan su kan sari ko sayi dai-‘dai

****

Mr Omar ita yafara budewa kofar mota tashige kafin ya zagaya ya budewa MALEEK yashige shima ya zagaya yashige ya tada suka bar asibitin sbd fita irin wannan Mr Omar shine yakejan MALEEK hardai idan zasuyi sirrantacciyar magana sai basa fita da drivern maleek din.

Tafiya suke Babu me magana acikin motar sai numfashinta dake fita ahankali ahankali sbd nauyin da kirjinta yayi.

Dan dagowa yayi ya kalleta ahankali tareda ajiye wayar hannunsa ya maida kallonsa kan wani envelope daya bude da muryar me kamewa yace"

Today shud be the last time.

Ajiyar zuciya ta sauke me dumi kafin ta waiwayo ahankali ta kallesa da idanuwanta dake bayyanarda halinda zuciyarta ke ciki na tsananin tarin damuwa me nauyi sbd Jin guntun zancensa.

Batareda ya kalletaba Yana cigaba da karanta takardar yace"

You deserve it.

Wannan karon cikowa idanuwanta sukai da hawayenda batasan lokacinda suka balle mataba dama kukan take buqata kozataji saukin damuwarta.

Mr Omar guri yasamu gefen hanya Mara mutane sosai da hayaniya yayi parking tareda budewa ya fita ya rufo musu kofar yana matsawa daga gurin.

Ahankali shehekar kukanta yafara fita sbd takasa daurewa kuka takeson yi.

Shiru yayi tareda dungurar da takardar sbd gabaki daya baya gane me yake karantawa ya lumshe ido ya bude ya juyo ya kalleta

Kuka takeyi hawayenta na gudu akan fuskarta ya zuba Mata idanuwansa gaba daya akaro na farko dabaisan mezaiceba.

Zaro tissue yayi ahankali ya miqa Mata cikin muryarsa me kamewa da dadin sauti yace"

Idan kinsan bazaki iya daukaba Meyasa kikaje?.

Wayace kije asibitin tun farko?

Kasa kallonsa tayi sai hawayenta dake qara gudu takasa bude bakinta.

Dauke kansa yayi Yana zaro wani Tissue din yakuma Bata ta karba tana goge hawayenta dasukaqi tsayawa

Ahankali yace"

Daga yau idan ba school ba karkije koina.

Da sauri wannan karon ta dago ta kallesa shima ita ya kalla cikin ido ya daga gira daya alamar yes abinda kikaji nace.

Wani irin mutuwar jikine kallonsa ya sakar Mata Wanda Kuma jikin nata ya nuna hakan sbd sakewa da hannunta me tissue yayi.

Dauke Kai yayi daga kallonta Dan kada sauyin dayaji daga nasa bangaren ya bayyana Kamar yanda nata ya bayyana.

Itama juyar da kanta tayi bayan ta Kuma kallonsa ya waiwayo ya kalleta saitaji Kuma kunyar kallon ta kamata ta sauke Kai tana share fuskarta.

Wayar Mr Omar yakira

Yana ganin Kiran yasan sungama ya dawo motar ya bude yashigo ya tada motar suka wuce.

Koda suka iso gida su afia sun Dade da dawowa

Koda Mr Omar ya budewa NURUn kofa ta fito maleek harya bude da kansa ya fito shiyasa kusan a jere suka shigo

Afia dake palon zaune ta dago tana kallonsu harsuka kawo maleek ya wuce Kai tsaye NURU kuwa Jin tayi nauyin afia ya kamata saidai itama Bata tsayaba sbd samun kanta tayi da rashin bawa afia wani bayanin komai tashige tana cewa"

Afia kundade da dawowa kenan.

Harta shige afia Bata iya waiwayawa ta kalletaba sbd kusan itama dai batasan tunanin mezatayiba

Itama yau dai komai ya kunce Mata daga mum dinta har dad din Kamar suna sauyawa.

Tubewa NURU tayi ta sauya Kaya zuwa free doguwar riga mara nauyi da tsayi tafada toilet tayo alwala tazo ta tayarda sallah.

Tana gamawa ta fito hankalinta kwance sbd tasamu nutsuwa ba laifi Wanda takega kila sbd tasamu tayi kukan ne.

Kitchen ta nufa ta dauko ledar crispy patato chips daya ta bude tun daga can tafara ci harta iso Palo tazauna gefen farhat da duk ta tsorata da rigimar dazu tsoron lailah yasak shigarta tana cewa"

Sweetie inzo mu kalla pj masks cartoon ko.

Kwantawa jikinta farhat tayi tana cewa"

Aunt next time idan mum LAILAH tazo daddy idan zai tafi dake kuje Dani tayita yiwa afia fada afia nata kuka inajin tsoro.

Murmushi kawai NURU tayi tana cewa"

Kidaina Jin tsoro tana sonki bazatayi Miki komaiba mum dinki ce.

Kallonsu suka fara suna zaune mum Sarah tazo zata haye samansa tana tura wringer wheel mop bucket jekadi data fito kitchen takira NURU tana waiwayowa da ido ta nuna Mata mum Sarah ta juya ta kalla mum Sarah din taga abinda yake hannunta ta sauke ajiyar zuciya ahankali tareda Miqewa tsaye tana miqawa farhat ledar crispy 'dinda sukeci tace"

Ina zuwa sweetie.

Gurin mum Sarah ta nufa Kai tsaye tace"

Mum Sarah kawo Bari natayaki kije kawai.

Kallonta mum Sarah tayi sbd wannan shine aikinta agidan tsawon shekaru Babu Wanda aka yarda dashi akan gyaran sama sai ita ko yanzu taso cewa NURUn tabarshi Amma ganin yanzu ita Matar maleek din ce saita miqa Mata tana cewa"

Thank you" ta juya Takoma kitchen.

Afia dake zaune palon tana jinsu saita waiwayo tareda tasowa tana cewa"

Muje na tayaki sbd aikin de yawa karki gaji.

Dan wani kallo NURUn tayiwa afia na mamaki da fara shakku akan afia sbd zuciyarta na Bata kaman afia batason kusancinta da dad din sbd mum dinta idan ta tuna yanda Afia din taqi jinin a danganta dad dinta da auren wata mace ba mum dinsu ba ta sake dubanta tana cewa"

Wannan aikin bazaisa na gajiba Amma dai tunda Zaki Taya din muje.

Saman suka hau suka tsaya a palon farko NURU batareda ta kalli kofar dakin lailah ba tace"

Ta Ina Zaki fara?

Kallon kofar dakin mum dinta tayi tace"

Zanfara da dakin mum.

Waiwayowa NURU tayi ta kalli afia din da wani sabon mamakin tace"

Daidai muyi iya inda yakeda amfani kawai kokuma kiyi kawai Bari naqarasa ciki nayi palon ciki.

Da mamaki afia ta dakata da cewa"

Kinsan akwai wani Palo cikine?

Shiru NURU tayi tareda wucewa tana share tambayar afia din Dan ita Sam palon na Farko ma batason tsayawa ta tura kofa Kai tsaye ta shige palon ciki din.

Da Kamar afia zata tsaya tayi Nan din saita fasa tabita tana cewa"

Bari dai mugyaro daga can din gaba daya.

Ko data shigo NURU ta fara gyara palon ganin afia tashigo yasa wani qayataccen murmushi sauka kan fuskarta batareda ta waiwayaba taci gaba da aikinta tana gamawa tace"

Ki kiyi mopping Bari na gyaro kurya.

Bata jira maganar afia ba ta wuce Kai tsaye kofar bedroom dinsa sbd tunaninta bayanan tayi knocking ahankali harso biyu babu amsa ta murda kofar ta shige tabar afia tsume ta dauke wuta da mamakin daya Gama kasheta.

Tana shiga dakin ta sauke wata irin kasalalliyar ajiyar zuciya sbd komai datayi cikin karfin hali da mamakin afia dason tabbatarda tunaninta tayisa.

Kallon dakin tayi akaro na farko sbd last time ba acikin hankalinta tashigoba harma ta fita din.

Ganin baya ciki yasata nufar shimafidar gadonsa data Gama gaurayuwa da qamshin jikinsa takai hannu zata saka han zanin gadon Dan gyarawa taji anbude kofar toilet ta juyo da sauri.

Tsayawa yayi Yana kallonta da mamaki dakuma wani kallon dabam kafin ya saki kofar ya fito gabaki daya cikin dakin

Da sauri ta juya zata fice tabi hanya tana cewa"

Yi hkr bansaniba""kofa ta nufa da sauri ta bude harta fita Taki ya riqo hannunta tareda dawo da ita cikin dakin ya tura kofar wadda kararta tasa afia firgita har tana jefa kafarta cikin bucket din Bata saniba da sauri ya cire kafar ta nufi kofa ta fita tana cewa"

I need a break,I need some fresh air kaina Yana sarawa.

Benen ma bibbiyu take hadawa gurin saukowa daqyar ta sauko tayi waje tana shakar iska tana sauke ajiyar zuciya a jejjere.

##MAMUH#

KUYI MANAGE YAU MA□

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/25, 8:52 PM] +234 706 452 3456: *_Mamuhgee 32_*

*_RANO NET_*

WHO NO LIKE BETA AWUUF THINGS?

INA MASU ZUBIN ADASHEN DA BA RANAR DAUKA NA DATA?

TO KU MARMATSO KUJI, KU KUMA SHARE HAWAYEN KU, MUNZO MUKU DA SABBIN TSARE TSARE NA DATA, WADDA KOWA ZAI IYA SAYA DAI DAI KARFIN SA. A FARASHI MAI RAHUSA

*RANO NET! RANO NET! RANO NET!*

(Afford data at chikini price)

MALLAKI DATA A KUDI KALILAN DA RANO NET

TSAYA KUJI, A RANO NET ZAKA IYA ZAMA RESELLER KO WHOLESALER KAI MA, EH ZAKA/KI IYA ZAMA MA SAYAR DA DATA A FARASHIN SARI MUKE BAYARWA, KAI/KI KAFA KASUWANCIN KU KUMA. DA KUDI KALILAN.

MUNA KUMA SAYARWA AKAN ‘DAI DAYA, KOWANE NETWORK MUNA SAYARDA DATA PLAN DINSA AKAN KUDI KALILAN, MASU FARASHIN SARA KUWA MA KU KUDIN BAI KAI HAKA BAMA

AIRTEL

9MOBILE/ETISALAT

MTN

GLO

DUK MUNA SAYARDA TSARIN DATA DINSU. KAMAR MISALI MTN MUNA SAYARDA 1GB.24MB AKAN FARASHIN NERA 300 KUMA YANA KAIWA WATA DAYA, GWARGWADON YADDA KAKE AMFANI DA DATA, 2GB 600, 3GB 900!!

DUKA WADANNAN TSARIN DATA DAMA NA SAURAN LAYIKA MUNA SAYRWA AKAN FARASHI MAI RAHUSA, WANDA KOWA ZAI IYA YIN TSARIN DAI DAI ALJIHUN SA

Ranonet.com.ng

_GA SITE DINMU NAN DAKE YANAR GIZO, KAI TSAYE ZAKI/KA IYA SIYAN NAKA TA NAN. _

_KO A TUNTUBE MU TA NAMBAR TARHON M1U: *_234 803 081 1300/
234 808 540 5215_*

KYAU, INGANCI, RAHUSA, ADADE ANA YAWO A YANAR GIZO SAI RANO NET.

RANO NET..!!!!

****

Da sauri ta dago ta kallesa lokacinda ya jinginata da kofar dakin bayan ya rufe, ta kalli faffadan kirjinsa dake bayyane sbd fitowarsa wanka kenan daure da brown towel ta 'dan juyar da kanta ahankali ta iya bude Baki tace"

Afia na Palo tare muke...

Wani kallo yayi Mata da idanuwansa dake kan fuskarta ya sake matseta jikin kofar har jikinta na mannuwa da nashi ta ja wani guntun numfashi tana Dora tafin hannunta kan qirjinsa batareda tasaniba

Hakan yasa maganar dazaiyi ta bace masa yayi shiru Yana kallonta

Ta sake dagowa ahankali sai suka hada idanuwa taji wani sanyi da kwanciyar hankali na shigarta sai fuskarta tafara yunqurin bayyanarda murmushi tayi saurin sauke Kai Tana motsawa ahankali sbd qamshinsa daya Gama cika hancinta Yana neman sage qafafunta.

Motsawar datake yasa qirjinta ringa gogarsa ya rintse idanuwansa Yana budesu akanta tareda yin baya Yana sakinta sbd Jin zata iya jawo damuwa.

Closet ya nufa batareda ya waiwayo ba bare ta iya gane halinda fuskarsa take ciki.

Bayansa tabi da kallo zuciyarta da dukkanin gangar jikinta na karbuwar da kowane irin sako ne yasoma isar mata.

Waiwayowa yayi ahankali ya kalleta idanuwansu suka shiga cikin na juna ta dauke kanta tana sakin wani boyayyan murmushi Wanda yasashi juyowa gabaki daya Yana Mata kallonda yasata bude dakin ta fito da gudu tanajin gabaki daya jikinta na daukar vibration Kai tsaye dakin farhat ta nufa ta zauna bakin gado tana sauke numfashi tana warware daurin gashinta Dan tasamu iska Tako Ina ya shigeta.

Farhat dataga shigowarta tabiyota dakin itama tana tsayawa gabanta tana kallon fuskarta da mamaki tace"

Aunt NURU you're smiling???

Dagowa NURU tayi ta kalli farhat din tana zuba Mata idanuwanta tana kallo kamanninta da mahaifinta ta janyota jikinta tayi kissing Kumatunta ahankali Yana rungumeta ahankali tace"

I love you sweetie.

Da farin ciki farhat ta maqale NURUn tana cewa"

I love you more my Aunt.

Zamansu sukayi a dakin saida kowa yashige sallar magriba tukuna ta fito ta haye saman batareda kowa yaganta ba taje sharp sharp tayo aikinta ta fito batareda shima yaganta ba sbd yafita sallah baya saman.

Kodata sauko takaiwa mum Sarah kayan gyaran dakin farhat Takoma acan tayi sallah tukuna ta fito Takoma kicin tasaka hannu a aikin hada abincin maleek din na

dare ta jera a tray takai saman tadawo ta nufi dakinsu tashiga tanajin nauyi da kunyar afia nason shigarta Amma ta daure ta danne tashigo dakin tana kallon afian dake zaune da littafi a hannunta tace"

Karatu Kuma ayanxu afia?.

Kasa kallonta afia tayi tace"

Eh wani Abu na dauko Ina dubawa.

Ok kitashi anyi sallah tun dazu.

Toilet ta wuce tayo wanka tana fitowa afia tabita da satar kallo tana cewa"

Kingama aikin?

Dakatawa NURU tayi daga shafa spray ajikinta ta 'dan waiwayo ta kalli afian tace"

Eh na gama na yau dai.

Cigaba tayi da abinda takeyi tagama tasaka kayan bacci ta fita dakin ta nufa dakin farhat acan sukasha oat suka sallar ishai sukai kwanciyarsu.

Washe gari tunda safe dakin padima ta nufa dan tayata shiri saidai padimar Bata buqata Kamar yanda tafada Mata Dan haka bata takura kantaba ta juya ta ficewarta ta nufa kitchen aikin breakfast tana gamawa ta nufi daki ta tada farhat tayi Mata wanka tareda Shirin school suka fito tabata breakfast da kanta ta rakata bakin mota driver ya wuce kaita tadawo ciki ta hadawa padima kayan breakfast a tray ta nufi dakin datake takai Mata sbd dama bakowa ke cin abincin a dining din gidan ba daga maleek sai iyalansa.

Tana shiga ajiye Mata kawai tayi ta fice

Qarfe goma driver ya kawo mota bakin kofar shigowa Palo Yana jiran fitowarsu jekadi wadda dukkanin saqon Anneti na miqawa NURU sauran Wanda ya rage ta shanye da safiyar suka fito NURU na gefen padima data matsu su Isa gizah rayuwarta itama ta canza gaba daya.

Shiga mota tayi ta zauna tareda kallon NURU tace"

Allah yabawa kowa rayuwar daya cancanta Dan haka gamo na alkhairi uwar renon farhat.

Wani qayataccen murmushi NURU tayi zancen padiman Bai tabataba ta dago tace"

Idan kinje Ina gaidasu abal da meryam, Jekadi zata Baki saqo a gizah da nawa Dana MALEEK duka kafin ki wuce delah,

Allah ya tsare hanya.

Maida kallonta kan jekadi tayi cikin kulawa tace"

Jekadi a sauka lafiya.

Da girmamawa jekadi tace"

Allah yasa mushrah Kuma godiya muke Allah ya qaro girma.

Shiga mota jekadi tayi aka shigar da kayansu motar driver yaja suka fice NURU na juyawa Takoma ciki direct ta nufi daki ta tube tafada wanka.

Tana fitowa ta zauna gaban madubi tana kallon fuskarta datakeson shafawa janbaki Dan Bata taba sawaba Sam ita Bata kwalliya iyakacinta shafa bronzer itama sama sama sai lip balm shima Mara Kara Amma yanzu son yin kwalliyar taji Kamar ya shigeta tana ra'ayi Dan haka tana gama shafa oils da creams dinta saita shafa face primer ta shafa powders kawai da liner cikin idonta ta dauki Nude lipstick tashafa akan lips dinta me sirkin pink pink.

Kallon fuskarta tayi aga kwalliyar tayi Mata sbd batai yawaba Kuma sbd Bata taba yiba sai tayi Mata kyau sosai.

Tashi tayi ta dauko doguwar English grown tasaka peach kala ta Sanya Sanya Dan kunne qarami ta fice daga dakin tabar afia da idanuwanta suka fara yaji yaji sbd kallon ikon Allah.

Tashi afian tayi itama ta nufi toilet tayo wanka tafito ta shirya cikin doguwar riga kusan irinta NURUn Dan dama kusan duk kayansu iri dayane.

Makeup tayi me kyau itama ta fito Palo daukeda laptop tazo ta zauna tareda bude laptop din tafara wani aikin tanashan tea data saka Fana hado Mata.

Murmushi kawai NURU dake zaune tayi tareda janyo musu firar wani program sunayi sbd kada shedan yasamu Shiga ranta.

Suna cikin firar Kiran lailah yashigo wayar afia

Suka kalli wayar atare kafin NURU ta dauke Kai tana miqewa tace"

Bari naje nataya Fana aikin abincin lunch.

Tana barin gurin afia ta maida kallonta kan wayarta tana tunanin daukan Kiran sbd tasani Babu wani abin kwanciyar hankali a wayar mum saina buqatarta wadda ita koyaushe abinda takeso shi zaayi Dole akuma lokacinda takeso din.

Kasa daukan wayar tayi ta saka wayar silent tareda Miqewa tabar palon ta nufi daki sbd kada NURU ta fahimci Bata dauki numbern mum dintaba.

Koda tashiga daki kashe wayar take kokarin Yi wani Kiran yasake shigowa ta sauke numfashi tareda dauka cikin sanyi tace"

Mum.

Dagacan bangaren lailah ta amsa da cewa"

Afia since when did you become this foolish dazan Kira kina ganin kirana bazaki daukaba?.

Ajiyar zuciya afian ta sauke tana Jin gajiya da halayen mum din tace"

Mum bana kusa Kuma Dan Allah mum kidaina wannan fadan kina bani tsoro ne sai inringa tunanin kina cikin wani halin ne sbd gabaki daya kinayi kaman bakya cikin kwanciyar hankali.

Wani baqin cikin afia ne ya tasowa lailah taji kaman ta zageta ko zata rage Jin abinda takeji na abinda yake gabanta na contact data rasa bayan dukkanin dukiyar data kwashe ta zuba Dan kawai ta samu contact din wanda zai sauya rayuwarta gabaki daya tazama abin gogayyar maleek saigashi ta rasa babban abin damuwar shine a qarqashin maleek contact din yatafi shiyasa yanzu a haukace take da buqatar komawa maleek kafin abinda take dashi yafara yin qasa Amma wannan wawuyar Yar tata tanayi kaman batasan abinda takeson tayi Mata ba.

Qaramin tsoki taja tana dafe goshinta sbd kanta dake sarawa tace"

Afia banason doguwar hayaniya sbd kaina Yana Dan ciwo Dan haka sai anjima idan na huta zankiraki Amma kafin Nan ki sanarwa dad dinki na shirya dawowa rayuwarku.

Shiru afia tayi da zallar mamakin mum din tace"

Mum inaga wannan ba hurumina bane ki nemesa kuyi mgn kokuma uncle jalal ya nemesa.

Da mamaki Lailah tace"

Nasan numbernsa Amma nace ki fada Masa ai.

Mum Dan Allah kidaina haka kufa iyayenane tayaya zanshiga cikin zancen maganar aurenku.

Baqin ciki yasa lailah cewa"

Idan bazakiyi abinda naceba afia karki sake kirana mum sbd bansan alaqata dakeba.

Kashe wayarta tayi tabar afia da idanuwa na cikowa da hawayen baqin cikin irin wannan uwa da Allah yabasu wadda duk duniya kanta kawai ta sani,buqatar kanta kawaice agabanta su 'yayanta amfaninsu kawai agurinta shine irin hakan idan ta taso Mata.

Kusan Rabin abinda Lailah tafada akan kunnuwan NURU datazo shigowane taji buqatar lailan.

Kasa shigowa tayi ta juya Takoma Palo ta zauna tana Shiga wani yanayi,

Lailah zata dawowa maleek to idan tadawo ita zata tabbata a 'yar renon farhat da gaske dinne kokuwa ma kila gaba tayi¿.

Numfashi ta sauke tareda dagowa ta kalli kofa da aka bude farhat ce tadawo daga school tayo gurinta da gudu tana Kiran sunanta.

Rungumeta daga zaunen NURU tayi tareda zare Mata school bag tana cewa"

Muje a cire Kaya ayi wanka.

Dakinta suka nufa ta tayata cire Kaya akai wanka ta dauko Mata riga da mini skirts ta Bata ta Sanya itakuma Takoma dakinsu tayi sallah tafito ta nufi kitchen tasa fana ta fito da komai suka shirya dining.

Tana Shirin komawa kitchen hada Masa nasa a tray tajiyo qamshin turarensa na shigowa ta dakata tareda juyowa daidai Yana shigowa dining room din ya zuba Mata idanuwansa dake Dan yawo akanta sbd qarara kwalliyarta da kyawun datayi suke a bayyane.

Kallonsa tayi tana bin bayan Fana data sulale ta fita da sauri ta bude Baki cikin sauti me taushi tace"

Barka da fitowa.

Bai amsaba ya qaraso gabanta kenan saiga farhat tashigo da gudu

Saiya zauna kan kujera Yana dauke idonsa akanta.

Murmushi tasakarwa farhat tana kallonsa tajata takaita kan kujera kafin ta koma kitchen ta dauko sauran ruwa da drinks takawo.

Sai data zuba Masa komai kafin tazo gurin farhat tazuba Mata kenan saiga afia ta shigo taqaraso ta zauna kan dining din tareda kallon dad dinta tace"

Barka da fitowa dad.

Kallonta yayi yana amsawa cikin kulawa.

Harsuka gama cin abincin idon hankalin afia baya jikinta gabaki daya ita Bata cikin nutsuwarta da walwalarta.

Yana lureda ita Kuma kallo daya yayi Mata yasan matsalarta bazata wuce lailah ba, Saida yagama ya goge bakinsa da Tissue ya dago ya kalleta cikin kamewa yace"

Afia akwai matsalane?hankalinki baya kan abinda kikeyi.

Aje spoon din hannunta tayi tareda sauke ajiyar zuciya me zafi da shakkarsa cikeda zuciyarta Amma tunda ya tambaya zata fada Masa mum dintace matsalarta.

Bude Baki tayi cikin damuwa tace"

Kayi hakuri Dan Allah dad mum tadawo.....

Tarin daya sarqe NURU ba shirine yasa kowa waiwayowa Banda maleek daya jefeta da kallo daya ya miqe yabar gurin Yana cewa"

Farhat kibawa Aunt dinki ruwa.

Ficewa yayi gabaki daya daga gidan Dan dama fita zaiyi.

##MAMUH#

*YERWA INCENSE & MORE**

(The scents with diff essence for YOU& your HOME)

(MASARAUTAR KAMSHI)

Ina masu neman kayayyakin kamshi yan nahiyar ketaran chadi da Senegal? Kai harma da ingataccen had’i yan bornu? To ku matso domin nesa tazo kusa...

YERWA INCENSE & MORE: Sun zo muku da kayayyakin turaruka kamar haka:

Khumra kowacce Iri.

Turarukan Wuta

Mopping khumrah

Washing khumrah

Bathing khumrah

body mist

kullaccam

scented hair cream/spray

wardrobe balls

carpet spray

air-fresheners

scented pebbles

body sprays

oil perfumes

Perfumes

kabbasa

burners

coal igniter

tong

kasko

english coal

dilke&halwa set

scented body mist

_kai dama sauran kayayyakin da bamu ambata, YERWA INCENSE AND MORE, Na tura kayayyakin su koina a fadin Nigeria da ketare. Domin tuntubar su. Suna instagram: _@yerwaincense_and_more. Ko Facebook site:YERWA _COLLECTIONs. Ko a duba su ta number su: ___08095215215/09044191709! _

suna bada kayan su kan sari ko sayi dai-‘dai[9/26, 5:59 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 33_*

RANO NET! RANO NET! RANO NET!

WHO NO LIKE BETA AWUUF THINGS?

IDAN KAJI GANGAMI DA LABARI....! INA MASU ZUBIN ADASHEN DA BA RANAR DAUKA NA DATA?

TO KU MARMATSO KUJI, KU KUMA SHARE HAWAYEN KU, MUNZO MUKU DA SABBIN TSARE TSARE NA DATA, WADDA KOWA ZAI IYA SAYA DAI DAI KARFIN SA. A FARASHI MAI RAHUSA

_RANO NET! RANO NET! RANO NET!__

(Afford data at chikini price)

MALLAKI DATA A KUDI KALILAN DA RANO NET

TSAYA KUJI, A RANO NET ZAKA IYA ZAMA RESELLER KO WHOLESALER KAI MA, EH ZAKA/KI IYA ZAMA MA SAYAR DA DATA A FARASHIN SARI MUKE BAYARWA, KAI/KI KAFA KASUWANCIN KU KUMA. DA KUDI KALILAN.

MUNA KUMA SAYARWA AKAN ‘DAI DAYA, KOWANE NETWORK MUNA SAYARDA DATA PLAN DINSA AKAN KUDI KALILAN, MASU FARASHIN SARA KUWA MA KU KUDIN BAI KAI HAKA BAMA

AIRTEL

9MOBILE/ETISALAT

MTN

GLO

DUK MUNA SAYARDA TSARIN DATA DINSU. KAMAR MISALI MTN MUNA SAYARDA 1GB.24MB AKAN FARASHIN NERA 300 KUMA YANA KAIWA WATA DAYA, GWARGWADON YADDA KAKE AMFANI DA DATA, 2GB 600, 3GB 900!!

DUKA WADANNAN TSARIN DATA DAMA NA SAURAN LAYIKA MUNA SAYRWA AKAN FARASHI MAI RAHUSA, WANDA KOWA ZAI IYA YIN TSARIN DAI DAI ALJIHUN SA

Ranonet.com.ng

_GA SITE DINMU NAN DAKE YANAR GIZO, KAI TSAYE ZAKI/KA IYA SIYAN NAKA TA NAN. _

_KO A TUNTUBE MU TA NAMBAR TARHON MU:
+234 803 081 1300/+234 808 540 5215_

KYAU, INGANCI, RAHUSA, ADADE ANA YAWO A YANAR GIZO SAI RANO NET.

RANO NET..!!!!

****

Ruwa farhat ta dauka a cup takai bakin NURUn cikin kulawa tana cewa"

Sorry Aunt.

Karban ruwan tayi takai bakinta Tasha bada yawaba ta ajiye cup din tana daukan Tissue ta goge Baki.

Kasa hakuri afia tayi sbd girman mamakinta ta kalli NURUn cikin son tabbatarwa da alamar tambayarta afili tace"

NURU menene matsalar?

Ina fatan dai ba maganata bane?

Kallonta NURU tayi tana ajiye Tissue din hannunta ta miqe tsaye idanuwanta kan afian cikin nutsuwarta tace"

Matsalar shine sarqewa nayi inacin abinci kila yawucin ba daidaiba.

Maganarki Kuma afia gabaki daya hankalina bayakai sbd ba hurumina bane Banda ikon saka kaina acikin maganarki da dad dinki.

Juyawa tayi tabar dining din ta nufi daki tashige tana Dan bubbuga kirjinta Dan har lokacin zafi yake Mata na sarkewarne koma na wani abin ne dabam batasaijin dadinsa.

Afia bayan tafiyan NURU sai alokacin yanda dad ya wuce Bai nuna yaji abin data fadaba kila baiji din bane Amma Kuma tanada shakka akan hakan Dan kuwa idan har yajita shareta yayi to tabbas zancen bamai karbuwa bane agaresa kenan sbd duk abinda yayiwa hakan Yana nufin Kar akuma kawo Masa maganar.

Jin tayi fargaba tashigeta sbd Koba komai yayi Mata gargadin sake tada maganar mum dinta cikin gidan Dan haka itadai bazata iya wannan tashin hankalinba kome mum zatayi bazata sake yiwa dad maganar ba.

Miqewa tayi tabar dining din ta nufi dakinsu Dan Kiran mum din saigashi tana shiga ta tadda NURUn kwance kan gado idanuwanta a lumshe sai takasa Kiran mum din tabari saita samu lokacinda Babu kowa akusa.

Qarasa shigowa tayi ta zauna kan sofa tana sake kallon NURU datayi shiru har lokacin idanuwanta a rufe ta nemi guri ta zauna tana tsirarwa kanta wani aikin da wayarta ranta dun a jagule.

NURU najinta Amma Bata bude idanuwanta ba saima numfashi data sauke tasake saukewa ahankali tana son bacci ya dauketa ko zata samu sararin Shan iska acikin kanta itama.

Da daddare bayan sungama cin abinci batareda MALEEK ba sbd har lokacin Bai dawoba kila basudai saniba suka koma daki afia tafara wanka tafito kafin ita dai Saida tayi sallar isha kafin tayi wankan tana fitowa ta Sanya riga da wando na bacci ta shafa body mist kawai ta fice zuwa dakin afia tana sake daurin gashinta dan Tasha iska gurin bacci.

Tana shiga ta taimakawa farhat tayi Shirin bacci suka kwanta bayan ta rage musu hasken wuta suna game a iPad sun Dade sunayi kafin bacci ya daukesu su duka.

Qarfe daya da mintuna goma Sha uku ya Murda kofar dakin ahankali cikin nutsuwa yashigo Dan duba farhat din sbd tafiya zaiyi gobe Kuma itace ba lafiyayya ba shiyasa yafi bada kulawa akanta.

Tunda ya bude yashigo yasan itama tana dakin sbd yaji qamshin _night alien,acqua di Parma_

Qarasowa yayi gadon ya tsaya akansu tareda zaunawa ahankali bakin gadon Yana kallon fuskarta kasancewar itace Baki farhat na kurya.

iPad din hannunta yazame ahankali tareda ajiyewa gefe ya janyo bargo ya gyara musu lullubinsu har zuwa kurji.

Fuskarta data juyo gefensa ya kalla zuwa wuyanta dake bayyane ya feso Masa kamshinta direct cikin hancinsa sai dumin numfashinta dake sauka ai tsaye kan hannunsa ya rintse ido ya bude ahankali sukai ido biyu da ita qamshinsa daya cika hancinta ya farkar da ita saidai Bata motsaba idanuwan kawai ta zuba Masa.

Kallonta yake ta lumshe ido tasake budewa cikin yanayi na daukan hankali sbd bacci baccin dabai saketaba duka.

Hakan datayi yasashi hadiye wani Abu dayasa maqoshinsa yin sama yadawo qasa tana gani sai hakan yasata Jin tsananin kunya baccinta na sakinta gabaki daya ta motsa ahankali zata juya ya Dora hannunsa cikin wuyanta tareda tallafo fuskarta daf da tasa tayi saurin lumshe ido daga kallonsa numfashinta na sauyawa ta matso da kirjinta ya mannu da nasa sosai take ya sake zuba Mata idanuwansa yanakai dayan hannunsa cikin rigarta ya shafi cikinta dayasata dauke wuta take tana qanqamesa tareda sake mannuwa dashi.

Bude idanuwanta tayi ahankali har lokacin fararen idanuwansa na zube akanta fuskarsu na Dab data juna sosai Dan dogayen hancinsu gugar juna sukeyi duk numfashinsa daya da qamshin spraymintt na Baki take shaqa Ahankali ta bakinsu

sukazo daf da juna har lokacin cikin idonta yake kallo idanuwansa na sake rurrusa kuzarin jikinta ta sake Masa gabaki daya cikin jikinsa tana matse dashi.

Kallon bakinsa dake daf da nata tayi sbd lips din kusan suna gugar juna ta lumshe ido tana tunowa a dakin farhat ne Kuma farhat na tashin dare Shan ruwa Dan haka zata iya tashi kowane lokaci Dan haka ta dago idanuwanta ta kallesa ta motsa zata bude Baki tayi magana bakinsu ya hade saijin farhat tayi tana Kiran sunanta cikin bacci.

Wani irin mummunan sanyi jikinta yayi takasa dagowa ta kallesa hakama takasa fitowa daga jikinsa tanaji ya zameta tareda Miqewa ya fice batareda ya waiwayo ba tabi bayansa da kallo jikinta na sake mutuwa Dan bama zata iya tashiba yanzu daukowa farhat din ruwa kafafunta bazasu iya daukanta ba.

Tana kokarin tashi taji bude kofar dakin tana dagowa Yana aje Mata ruwan roba biyu agabanta ya juya ya fice mamaki na shirin shideta ta kalli ruwan da sauri tadago tasake kallon kofar daya fice mamakinta na sake ninninkuwa.

Da sauri ta dauki ruwan ta Dora kan jikinta saiga wani siririn murmushi ya sauka kan innocent face dinta tana waiwayawa ta kalli farhat da batama farka ba har lokacin wato dazun motsawane kawai tayi cikin bacci takira sunanta.

Bude ruwan tayi ta 'dan Sha daya ta rufe ta ajiye har lokacin Dan boyayyan murmushinta Yana kan fuskarta ta zame ta kwanta tana lullubewa tareda rufe idanuwanta.

Washe gari sai 9 ta fito tana Yar miqa sbd tayi bacci me nutsuwa da qarfi ta nufi dakinsu ta shige Kai tsaye ta nufi toilet sai datayo brush tafito tazo gurin afia suna gaisawa tace"

Afia yaushe zakije siyayya akwai abubuwan danake buqata infact inason zuwa saloon yaushe zamuje?

Nima inason gyara kaina da qafafuna siyayya Kuma zanmana online shopping.

No banason online akwai abinda nakeso naje da kaina na siya dole sainaje da kaina.

Me kike buqatane?"afia ta fada tana zare dogon wandon baccinta Dan tubewa tashiga wanka.

Nighties Dina sun tsufa ina buqatan wasu and makeup stuff dai sai perfume danakeson sauya brand.

Ok Nima dai kusan duk buqatar dayace why not muje anjima.

No kikuma dai gobe ba.

Alright shikenan"afia tace tana qarasa cire kayanta ta nufi toilet tashige.

Bayan shigarta toilet din kenan wayarta tayi ringing NURU dake kusa ta dauki wayar zata daga tana dubawa taga sunan MUM baro baro akan wayar ta ajiye batareda ta daga din ba qarshema ta miqe ta fara gyara musu dakin tana kallo lailan nata Kira kusan ko bakwai kafin ta hkr zuciyarta na can na tafarfasa.

Wurgi da wayarta lailah tayi tana miqewa tsaye daga zaunen datake cikin bedroom dinta na qaton gidanta dake LA wanda zata Bari sbd hardashi duk ta rasa batason kowa ko duniya tafara sanin halinda take ciki shiyasa takeson lallabawa takomawa MALEEK batareda koshi yasan hakanba sbd mutane shegu sun nuna Mata wani abin Saida connection da zamanka wani sananne akeyi dakai,

Da farko farkon fitowarta kowa son huldar aiki yake da ita sbd zamanta da saninta Matar MALEEK UBAYD Amma tunda aka fara sanin sun rabu duk manya manyan mutanen datake taredasu sun janye sun nuna Mata sbd maleek ne wani abin shiyasa Dole yanzu Takoma Masa tunda dashi zata cigaba da amfana hartayi sunan da matsayin datake so Amma gashi wannan shashashar Yar tata da batada wayo tana Mata shirme sai ansan metake ciki gashi gidanta ma data saka acikin dukiyar Dan investment data shiga yashige ciki gashi bazata taba iya tambayar kowa kudi

ba ayanzu sbd ba girmanta bane bazata taba Bari kowa yasaniba bare raini yashigo tana matsayin Matar maleek guda.

NURU bayan tayi wanka sunyi breakfast tareda maleek ba sukasan baya gida suna gamawa tadawo Palo ta zauna tana Dan dudduba chats na wayarta bayan tagama waya da abal dinsu akan har lokacin su padima Bata isoba dayake tayi waya da jekadi akan sun Isa lafiya saita fada Masa sun Isa suna gizah padiman zata dawo idan suka huta a gizah aka sallameta da Haka suka bar zancen padiman suka danyi fira tsakaninta dasu aka Bata meryam sukai fira kafin ta kashe tashiga chats din.

Doorbell ne yayi qara tanaji ta Dan dago ta kalli kofar kafin taci gaba da chats dinta mum Sarah tazo ta bude

Mr Omar ne mum Sarah tabashi hanya ya shigo ya nufo gurin NURUn cikin girmamawa ya tsaya tareda Dan dagowa yace"

Maleek daga office zamuyi tafiyan kwana biyu zuwa Los Angeles.

Dagowa tayi ta kallesa batareda ta iya cewa komaiba harsaida yakuma maimaita Mata kafin ta gyada Kai ahankali tace"

Allah yakai lafiya adawo lfy.

Idan kaje ka sanar zamuje saloon tareda afia.

Kamar wani munafuki Mr Omar din ya boye Dan guntun murmushinsa yayi gyaran murya yace"

Duk inda Zaki anbaki dama Banda zuwa asibiti.

Kallon Mr Omar din tayi fuskarta na sauyawa ga tarin mamakin shine yake Bata damar fitar ne kokuwa

ganin hakan yayi saurin seta murya yace'

Saqo ne daga maleek ranki ya dade.

Shiru tayi kafin ta gyada Kai tace"

Nagode shikenan Allah ya tsare.

Juyawa yayi ya fice mum Sarah tabisa ta rufe kofar Takoma kitchen gurin aikin dasukeyi.

Kasa chat dinma tayi ta ajiye wayar gabaki daya tareda Miqewa ta koma daki ta kwanta.

Baccin Rana tayi sai bayan dawowar farhat da dadewa ta farka ta tashi tayo alwala tafarayin sallah tukuna ta fito taci abinci kadan tadawo gurin Islamic class da ake zuwa anayiwa farhat din kullum ta zauna sunayi da ita.

Sai dare dasuka kwanta NURU tasamu tayi bacci daqyar sbd 'yar damuwar datakeji hakanan kawai.

Washe gari fes ta tashi ranta ba damuwar komai sukai duk abinda zasuyi guraren karfe biyu suka fice zuwa inda zasuje Amma driver ne yake jansu.

Gurin shopping kayan make-ups da turaruka ta dauko ita saida sukaje bangaren kayan bacci suka daddauka set kaman yanda yawanci suka Saba me guda uku suda farhat saidai NURUn taqara da wasu wainda itama daqyar ta iya daurewa ta daukesu agaban afia din wadda takusa suman tsaye sbd mamaki da firgici Amma ta danne Bata nunawa NURUn ba sbd Bata tabbarda mezayi da irin wainnan sexy kayan baccinba wainda kwata kwata basa sakasu.

Daganan saloon suka tsaya acan suka Dade sai yamma lis suka dawo gida NURU na waya da abal dinsu cewan shi ko numbern padima baya samu tace Masa yabari zatakira jekadi taji meya Hana padiman komawa haryanxu.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/26, 5:59 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 34_*

*YERWA INCENSE & MORE*

(The scents with diff essence for YOU& your HOME)

(MASARAUTAR KAMSHI)

Ina masu neman kayayyakin kamshi yan nahiyar ketaran chadi da Senegal? Kai harma da ingataccen had’i yan bornu? To ku matso domin nesa tazo kusa...

YERWA INCENSE & MORE: Sun zo muku da kayayyakin turaruka kamar haka:

Khumra kowacce Iri.

Turarukan Wuta

Mopping khumrah

Washing khumrah

Bathing khumrah

body mist

kullaccam

scented hair cream/spray

wardrobe balls

carpet spray

air-fresheners

scented pebbles

body sprays

oil perfumes

Perfumes

kabbasa

burners

coal igniter

tong

kasko

english coal

dilke&halwa set

scented body mist

_kai dama sauran kayayyakin da bamu ambata, YERWA INCENSE AND MORE, Na tura kayayyakin su koina a fadin Nigeria da ketare. Domin tuntubar su. Suna instagram: _@yerwaincense_and_more. Ko Facebook site:YERWA _COLLECTIONs. Ko a duba su ta number su: ___08095215215/09044191709! _

suna bada kayan su kan sari ko sayi dai-‘dai

****

Suna shigowa gidan farhat tafara tarbonsu da gudu ta fada jikin afia tana Dan bayyanarda tsoronta afili tace"

Afia mum tazo tana ciki tundaxu da kuka fita.....

NURU data jefa qafarta Palo ta tsaya cak Jin abinda farhat tafada zuciyarta na dakatawa na 'yan mintuna kafin ta daga fuska tana kallon cikin palon da Babu kowa ta danne tashigo tareda nufar dakinsu direct tana shiga ta sa sauke ajiyar zuciya ahankali tareda fitarda numfashi ta nufi table din dake tsakiyar sofas din dakinsu ta ajiye shopping bags din hannunta ta zare qaramin gyalen dake kanta ta cire kayanta ta dauki towel ta nufi toilet tayo wankanta tareda alwala ta fito tashirya cikin riga da wando dogo marasa nauyi tazo ta tayarda sallah har lokacin afia Bata shigo dakinba.

Saidata idar da sallah tayi adduointa ta miqe ta kwashi bags din tasaka cikin wardrobe ta dauki hula tasaka akanta ta fice zuwa kitchen neman abincin tana Dan Jin yunwa.

Kodata fita Palo farhat na zaune ita kadai tana ganin NURUn ta taso tana cewa'

Aunt yunwa nakeji.

Da kulawa ta waiwayo ta kalleta tareda Kama hannunta suka nufi kicin tana cewa"

Sweetie Nima yunwa nakeji muje muga me Fana ta dafa.

Suna Shiga ta dudduba taga tuni angama jere komai a dining ta dauko musu melon drink suka dawo dining din suka zauna tafara zubawa farhat kafin tazuba suka faraci tana kallon yanda farhat din keci alaman taji yunwa sosai ta zuba Mata drink din a cup ta miqa Mata tana cewa"

Sweetie tunda Kika dawo school bakice abinci bane?

Gyada Mata Kai kawai tayi tana cewa"

Dana dawo mum Sarah zata kawomin saiga mum shine tace ta ajiye komai taje ayi Mata gyaran dakinta daganan banci komaiba.

Murmushi NURU tasaki tana cewa"

Shikenan yanzu kici abincin bazan qara Bari kiji yunwa hakaba Inshallah baby.

Suna cikin ci wani sabon qamshi ya doso dining room din Wanda ta tabbatarda kila lailah ce ke zuwa Dan haka saita dauki ruwa Tasha dama tagama saita miqe tana cewa farhat"

Sweetie nagama idan kingama kisameni Palo muyi kallon cartoon.

Juyawa tayi daidai shigowan lailah sanye cikin wata straight doguwar riga data tafi daidai tabi jikinta kanta a daure da band tana zuba kamshi hankalinta kwance tashigo tana ganin NURUn ta tsaya kallonta daga qasa zuwa sama sbd NURUn riga da wandone ajikinta dasuka sake maidata yarinya qarama sbd rigar Kamar shimi take sai wandon daya wuce gwiwa sosai Amma bekai qasa ba,

Fuskarta ta kalla taga yanda take wani maiqon kyan fata da gyaran datake samu tareda nutsuwa datake ciki datake qarawa mutum kyan fata.

Kallonta NURU tayi fuskarta Babu wani sauyi akai tace"

Barka da zuwa.

Kamar lailah bazata amsaba saidai ta dakata tareda juyowa ta kalli NURUn tace"

Karki sake zuwa dining cin abinci dagani sai 'yayana da mijina muke hawa dining a gidan Nan

Idan ada kina hawa yanzu nadawo banason tarkacen da hayaniya ki tsaya inda bazan ganki ba kafin me MALEEK din yadawo kisan matsayinki.

Tana Gama fadar hakan ta wuce ta nufi dining din tana cewa farhat ta tashi taje takira Mata fana tazo tayi serving dinta.

Aje spoon farhat tayi ta sauka daga kan dining din ta nufi dakin mum Sarah tafada Mata sbd Bata taba bi ta hanyar kicinba taje bangaren masu aikinsuba tunda take.

Daga gurin mum Sarah sidadawa tayi Takoma dakinta Bata koma dining ba.

NURU kuwa tunda Lailah tagama maganganunta ta juya ta fice Bata ce kalaba ta nufi Palo tayi zamanta tana kallo tana gani farhat tazo ta wuce dakinta batai yunqurin bintaba sbd gudun mum dinsu tace Kuma ga wani salon saitaci gaba da kallonta tana kallo afia ta fito ta nufi dining fuskarta ba wani walwala da alamar itama mum din batai Mata da Dadi ba.

Tana Nan zaune lailah tagama tafito ta wuce sama batareda ta lura da NURUn a Palonba datayi magana kila.

Sai guraren goma ta miqe ta nufi dakinsu tayi tayi duk abinda zatayi tazo gefen afia ta kwanta tareda rage hasken dakin sosai tanajin motsin afia din wadda da Alama batai bacci ba kwancen kawai take.

Bata Jima da kwanciyarba bacci ya dauketa Bata farka ba sai bayan asuba har gari yafara haske ta tashi tana miqa ahankali ta wuce toilet tayo brush da alwala tafito ta tada sallah.

Bayan tagama ta miqe ta nufa dakin farhat ta tada ita tayi sallah kafin tafara Mata Shirin makaranta suka Gama ta fito ta nufa kicin ta hada Mata breakfast dinta sukaci tare kafin aka tafi Kai farhat din school itakuma takomawarta daki ta kwanta ta shige bargo ta Dora sabon bacci cikin kwanciyar hankali.

Har Rana tayi Fana na aikin abincin safen aikin yaki karewa sbd kalolin abincin da lailah tasaka a daddafa din Wanda tasaba idan zataci abinci tafison ayisu kalolo daban daban sbd taci Wanda taga tanada raayinshi sukuma yanzu sun Saba aikin abincin gidan akan kaida akeyinsa tunda NURU tafara Aiko a kicin din gashi tun bayan tafiyar maleek NURU ta cire hannunta a aikin abincin iyakacinta ci idan anyi kamar kowa.

Koda ta farka ta bude idanuwanta taga afia zaune a dakin tanashan Cocoa Krispies da Madara ta mamaki take kallonta tana tashi zaune tace"

Afia yanzu da Rana kike Shan Krispies nagama bakyashansa be damekiba.

Kallon NURU afian tayi tana Kai spoon bakinta tace"

Yunwa nakeji ne sosai kodana tashi kaman naci Rami acikina sbd jiya da daddare banwani ci abinci ba juice kawai nasha bayan hakama ace haryanzu a gidan Nan ba'a Gama breakfast ba sai kace wasu celebrities dakecin abinci akan lokacinda suke zabarwa kansu bazan iya jiraba.

Murmushi NURU tayi tana cewa"

To kodai fana batada lafiya ne da aikin yakaita haryanzu?

Pass 11 fa.

Sanin dalilin hakan yasa afia batace komaiba taci gaba dashan abindake gabanta tana cewa idan nagama asibiti zanje Nanda 4 days zamu fara zuwa session training dinmu yaushe ne naku?

Tana saukowa gado ta nufi mirror tana cewa"

Namu sai next week Nanda kusan 10 days ma Amma Nima may b kwanakin Nan nafara lekawa court din.

Toilet ta nufa tashige tana cewa idan kinfita zanmiki texting din sunan wani littafi kizomin dashi idan Zaki dawo.

Wanka tayi tana fitowa daureda towel tana goge kanta da ruwa yadan jiqa ta alamar afia din ta fita ta nufi mirror kenan zata zauna aka shigo dakin ta Bata waiwayoba ta cikin madubin taga lailah wadda takusa hadiyar zuciya ganin NURUn a Haka sbd fatarta dake wani irin daukan ido sbd zamanta fresh ta kanne tareda dan yamutsa fuska ta kalli cikin dakin taga afia Bata Nan ta maido ta kallonta kan NURU dake abinda ke gabanta tace"

Karkicemin anan dakin kuke zama tareda afia?

Waiwayowa NURU tayi ta kalleta sai tace mata"

Barka da shigowa"tayi skipping wancan tambayar tana kokarin dauko Kaya tasaka ajikinta.

Sake kallonta lailah tayi tana cewa"

Wane irin toshewar Kai ne zaisa ki zauna a dakin AFIA bayan dakunan dake gidan Nan gasucan kusa Dana Sarah Amma kinzo nan kin gwamutsa ta Yaya mutum biyu

zasu zauna daki daya a matse wani na shaqan numfashin wani wannan masifa ne cuta na shigowa ciki.

Wannan karon tsayawa NURU tayi kallonta sbd tasamu fahimtar me mum dinsu afian ke nufi Dan dai ita abin yafara gundurarta Matar tacika tsirfa.

Fara hasala da kallon da NURU ke Mata Kamar wawuya lailah tayi tace"

Ba'a kallo Haka idan Ina magana ba sa'arki ke magana ba Matar uban gidankice ke mgn.

Hakan data fada yasa NURU kallonta gabaki daya saidai har lokacin Bata ce komaiba kafin ta juya ta dauki kayanta tafara sanyawa lailah taqara harzuka sbd ganin Kamar NURUn ta maidata hauka kawai takeyi saita dauki towel din afia ta riqo hannun NURUn dashi tajawota ta fito da ita dakin tasawa dakin key ta zare ta kalli NURUn tana Dan yamutsa fuska tace"

Next time idan Ina mgn saiki saurareni da kyau,

Kije dakunan dake kusadana Sarah ki dauki daya wannan banason tarkace ko gwamutsetse atareda yarana ciwo zai iya shiga.

Wucewa tayi tabar NURU a tsaye daga ita sai towel tayi shiru batareda tace komaiba har lokacin sai kawai ta juya ta nufi dakin farhat tashige Allah yasa tanada wasu Kaya adakin na farhat saita Sanya duk Dana shan iska ne saita fito taje kicin ta dauko drink da biscuits tadawo daki taci tayi sallah ta haye gadon dakin tana juya wayarta tanason kiran jekadi Amma saita fasa ta ajiye wayar.

Sai yamma afia tadawo ta tararda dokar mum dinta ta girgiza matuqar gaske ta kalli mum din zatayi magana mum din tayi Mata wani kallo tana numa Mata kofa sbd batason dogon zance bare hayaniya.

Koda afia ta fito dakin farhat ta nufa Kai tsaye sbd tasan NURUn na can tana shiga ta taddasu zaune kan kujera suna game da farhat hankalinsu kwance suna dariyarsu.

Wani iri taji na rashin Jin Dadin abinda mum dinta tayi Amma bazata iya take maganartaba sbd duk yanda take kaunar NURU mum dinta mum dintace saita kasa shigowa ta juya zata wuce NURU data lura da ita kalleta tace"

Charger na kawai nake buqata a dakin sai laptop Dina.

Tsayawa afia tayi tareda juyowa ta kalli NURUn taga ba damuwar komai akan fuskarta ta dake itama tace"

Ok zan Aiko mum Sarah takawo miki."tajuya ta tafi tabar gurin suka cigaba da abinda sukeyi zuciyar NURUn a dake Taki Bari abinda takeji ya rusata.

Koda dare yayi daqyar NURU ta iya rintsawa sbd dokokin lailan sunfara tsauri sbd ko dining din suna Gama cin abinci aka rufesa

Mum Sarah duk hankalinta ya tashi NURUn ta nuna Mata bakomai kadata damu Takoma daki ta kwanta.

Washe gari bayan tafiyar farhat school ma haka tashiga wani sabon cin zarafin ta daure dai Bata cewa komai bare ta tanka qarshe dai futa tayi taje restaurant taci abinci dagacan tace driver ya wuce da ita wani guri acan ta wuni sai qarfe bakwai tadawo gidan tana dawowa ta shige sbd komai na gidan da doka da iko sundawo qarqashin Lailah tadawo da duk qaidojinta da kaf masu aikin suka Santa dasu cikin kwana biyu ta dawo LAILAH MALEEK dinta Dan kuwa tani kowa yasake shiga taitayinsa.

NURU kuwa tsananin yafara Mata yawa Dan kuwa ko ruwan gidan Idan bana toilet ba batada ikon ganinsu bare tabawa Kullum tana daki idan taji yunwa ta fita taje taci abincinta qarshe dai abin duniya ya isheta sbd cin zarafi da ikon lailah yayi yawa Dan yanzu drivernma ta hanashi sake daukan NURU Dan Haka kwana biyu tana daki ga ciwon Mara tun jiya daya sakota gaba sai kawai ta sayi ticket din komawa gizah ta waya.

Tana kwance ciwon mararta yafara tsananta Mata ta tashi zaune riga da wandon baccin safene a jikinta qananu tun na safe Bata tashi tacireba tana dungule cikin gashi yau weekend ne farhat na gida duk taqara hanata sakat da hayaniyarta shiyasa duk Bata cikin nutsuwarta.

Tashi zaune tayi ta kalli farhat tace"

Farhat kije kifadawa mum Sarah takawomin tea me lemon.

Tashi farhat din tayi ta fita da gudu taje tafadawa mum Sarah ta jira Dan agama su taho dashi tana Taya mum Sarah fira.

Mum Sarah duk hankalinta ba kwanceba ta hadawa NURUn tea din tareda sabon cupcakes datayi yau da safen ta hado Mata a qaramin tray ta miqawa farhat din tana cewa"

Farhat ki riqe da kyau kije ki kaiwa aunt dinki kafin mum dinki tafito ko.

Karna farhat tayi ta fito tana tafiya ahankali sbd kada ya zube ta nufi hanyar Palo zuwa dakinta

tana kaiwa tsakiyar Palo sukai kicibis da mum dinta tafito cikin shigar Kuwait gown tana kamshi fuskarta taji kwalliyarta kamar ko yaushe sirrin kyau sai fita yake a fuskar.

Firgici da tsoro yasa farhat sake tray din ya zube Mata gabaki daya a qafa tasaki wani razanannan ihun da duk yasa kowa fitowa musamman NURU data qaraso daqyar da saurinta tayi kan farhat din ta kamota zata duba Lailah ta tareta da hannunta tareda turata baya cikin bacin Rai takalli su mum Sarah tace"

Tashin farko Wanda yayi wannan aikin da Wanda za'a kaiwa nakeson ji.

Tsit sukayi Wanda yasa ranta sake baci ta juyo ta kalli NURU dake kallonta wannan karon cikin qarewar hakurinta.

Tace"

Me kikeyi a dakin dakika fito?

Nace kibar dakin afia shine Kika koma na farhat kina tunanin cutar datasa na koroki daga dakin afia banawa farhat guduntane?

Sarah so nawa zanfada miki dokikina da tsarina acikin gidan Nan?

Kije dakin farhat Dana afia duk wani trash na yarinyar Nan akwasosu yanzu yanzun nan akaisu guestroom.

Dauke wuta dukkaninsu sukayi kowa yakasa motsi afia dataga abin na neman yawa ta matso gurin mum din tace"

Mum Dan Allah ki kyaleta tunda kin hanata zama dakina kince adaina Mata komai ko Bata komai

Mum harfa Edward kin hasa ya dauketa da mota yafita da ita

Mum Dan Allah kadaki kaita guestroom this is too disrespectful Koba komai Matar dad ce.....wani lafiyayyan Mari ta saukewa afia dayasa dawowa cikakken hayyacinta na sanin mum dinsu tabbas tasamu matsala kila.

Cikin tsawar lailan tace"

Ki fito da kayanta yanzu Nan nace....

Gyaran murya mr Omar yayi daga bayansu dukkaninsu suka juyo kowa na dauke wutar Shiga firgici musamman afia data juyo gabaki daya gabanta da mugun harbawa

Su mum Sarah kuwa kowa rawar jiki ya dauka suna sauke kawunansu.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/26, 5:59 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 35_*

RANO NET! RANO NET! RANO NET!

WHO NO LIKE BETA AWUUF THINGS?

IDAN KAJI GANGAMI DA LABARI....! INA MASU ZUBIN ADASHEN DA BA RANAR DAUKA NA DATA?

TO KU MARMATSO KUJI, KU KUMA SHARE HAWAYEN KU, MUNZO MUKU DA SABBIN TSARE TSARE NA DATA, WADDA KOWA ZAI IYA SAYA DAI DAI KARFIN SA. A FARASHI MAI RAHUSA

_RANO NET! RANO NET! RANO NET!__

(Afford data at chikini price)

MALLAKI DATA A KUDI KALILAN DA RANO NET

TSAYA KUJI, A RANO NET ZAKA IYA ZAMA RESELLER KO WHOLESALER KAI MA, EH ZAKA/KI IYA ZAMA MA SAYAR DA DATA A FARASHIN SARI MUKE BAYARWA, KAI/KI KAFA KASUWANCIN KU KUMA. DA KUDI KALILAN.

MUNA KUMA SAYARWA AKAN ‘DAI DAYA, KOWANE NETWORK MUNA SAYARDA DATA PLAN DINSA AKAN KUDI KALILAN, MASU FARASHIN SARA KUWA MA KU KUDIN BAI KAI HAKA BAMA

AIRTEL

9MOBILE/ETISALAT

MTN

GLO

DUK MUNA SAYARDA TSARIN DATA DINSU. KAMAR MISALI MTN MUNA SAYARDA 1GB.24MB AKAN FARASHIN NERA 300 KUMA YANA KAIWA WATA DAYA, GWARGWADON YADDA KAKE AMFANI DA DATA, 2GB 600, 3GB 900!!

DUKA WADANNAN TSARIN DATA DAMA NA SAURAN LAYIKA MUNA SAYRWA AKAN FARASHI MAI RAHUSA, WANDA KOWA ZAI IYA YIN TSARIN DAI DAI ALJIHUN SA

Ranonet.com.ng

_GA SITE DINMU NAN DAKE YANAR GIZO, KAI TSAYE ZAKI/KA IYA SIYAN NAKA TA NAN. _

_KO A TUNTUBE MU TA NAMBAR TARHON MU:
+234 803 081 1300/+234 808 540 5215_

KYAU, INGANCI, RAHUSA, ADADE ANA YAWO A YANAR GIZO SAI RANO NET.

RANO NET..!!!!

****

NURU dake tsayi tajisa tsayuwarsa a bayanta ta ta rufe idanuwa mararta na sake murdawa ta bude idanuwanta batareda ta juyowa taji takunsa ya tsaya gefenta tareda kallonta kafin ya juya ya kalli afia data sake Shiga rudu da firgici ta matso qafafunta na rawa ta bude Baki zatai magana ya dakatar da ita da idanuwansa dasuka sake gigita kowa agurin suka sake sauke kawuna suna tsuma.

Inda lailah ke tsaye Bai kallaba sbd har lokacin bayajin tasamu darajar samun lokacinsa ya waiwayo ahankali ya kalli gefen Mr Omar batareda yayi magana Mr Omar ya matso da sauri Yana kallonsu mum Sarah kafin ya juya ya kalli lailah cikin 'yat girmamawa ya tausasa murya yace"

Ranki ya dade ko zamuje na maidaki gidanki.

Wani wulaqantaccen kallo tayiwa Mr Omar din zuciyarta na tafasa da cin fuskar da akeson yimata gaban 'yan aikin gidan ta maida kallonta kan MALEEK zatayi magana ya wuce Yana barin gurin hannun NURU cikin nasa

zuciya ta taciyota tasha gabansa cikin baqin ciki da bacin Rai me qarfi tace"

MALEEK agabanka bawanka yake wulaqatani

Harni zaicewa nafito yakaini gida

Wannan tsaban wulaqanci ne gareni bazan daukaba wlh.....

Dakatawa yayi tareda juyowa akaro na farko ya kalleta tun bayan rabuwarsu ya zuba Mata idanuwansa dasuka so rudata daga masifar datake ya bude Baki ahankali yace"

Zakibar gidan Nan yanzu bada Bata lokaciba idan ba akan umarnina Mr Omar yafada hakan Dan Haka kin tabbatar kafin kisan matsayinki agaban masu aiki da 'yayanki respect yourself and just leave.

Waiwayawa yayi gefen afia data shanye jinin jikinta yace"

Mahaifiyarki har abada bazata taba sake zama Matar mahaifinkiba

Next time dazan sake fada Miki hakan ki tabbatarda bazakiyi awa goma agidana ba zan aurawa mr Omar ke

Now I gv you 10 min ki tayata kwashe kayanta.

Wucewa yayi yabarsu kowa ya sake dauke wuta musamman afia da lailah datai mutuwar tsaye idanuwanta nayin jajir zuciyarta na kasa gasgata abinda kunnuwanta suka ji..

A haukace tasake Shan gabansa da sauri tana yaqi da hawayen dakeson sauko Mata sbd taurin zuciyarta dake tarwatsewa a haukace tace"

Maleek wlh tallahi ban yardaba bazan bar gidan Nan har abada saidai ka kasheni ka fitarda gawata idan ka.....

Dan motsowa Mr Omar yayi cikin rashin Jin Dadin abindake faruwa gaban dukkanin Yan aikin gidan ba girman maleek bane Dan Haka yana matsowa maleek yayi masa kallo daya ya dakata Yana sauke Kai.

Kai tsaye Maleek ya watsa Mata wani kallo zuwa lokacin bacin ransa yagama bayyana afili sbd yanda idanuwansa suka sauya ya kalleta Yana controlling tsananin bacin ransa yace"

Afia I said I gv you 10 min to help your mother pack and leave.

Wani gigitaccen kuka ya kufcewa afia dukkanin hankalinta na sake tashi da tsananin bacin Rai data hangowa acikin idanuwan mahaifinta.

Lailah ta fizgo afia data Kama hanyar dakinta hado Mata kayanta ta sharara Mata marin data rAsa wazata saukewashi cikin tsananin tashin hankali,baqin ciki da masifa tace"

Babu inda zantafi maleek idan akan wannan trash din sa'ar 'yarka kake cewa nabar gidan Nan Babu inda zanje zanyi zaman 'yayana...

Kallonta dukkaninsu 'yan aikin sukayi cikeda mamaki da kunyar abinda take yiwa kanta suka sauke Kai bame ikon mgn

Maleek kuwa ahankali ya juyo ya kalli NURU da duk jikinta yagama mutuwa da ciwon dake damunta Dan ita yanzu Bata mamakin duk abinda Lailah zatayi shiyasa ko Kai Bata dagoba ta kalleta duk abindake faruwa.

Dagowa tayi ta kalli MALEEK dake kallonta da cikin wani yanayi ta dago ahankali ta kallesa ya kalli cikin tsakiyar idanuwanta Kai tsaye ya bude Baki yace"

Kina buqatan wani Abu anan din?

Kallonsa takeyi cikin idanuwansa abinda Babu Wanda ya Isa yayi hakan a gidan.

Bata dauke idonta akansaba ta girgiza kai alamar Babu.

Juyawa yayi Kai tsaye da ita ya nufa dakin farhat har lokacin hannunta na cikin nasa.

Mr Omar ya juyo yayiwa masu aikin kallo daya take suka watse

Ya waiwayo ya kalli mum Sarah dake riqeda farhat daketa kuka ahankali sbd tashin hankalin tsoron data shiga ya gyara tsayuwa Kai tsaye yace"

Ms Sarah abawa kowa order suyi packing na kayan sawa kawai kowa zai bar gidan yau." Yana fadar hakan ya juya ya fice ya nufi mota Yana jiran fitowar maleek da nuru.

Suna Shiga dakin farhat ya saki hannunta ya janyo rigar abayarta dake kan gado ya miqa Mata ta karba jikinta ba karfi ta Sanya ta ya sake kamo hannunta suka fito ta gaban lailah da afia suka wuce

Farhat dake hannun mum Sarah ta kwace tabiyosu da gudu ta riqe hannun NURU wadda ta tsaya sai alokacin idanuwanta suka fara kokarin cikowa da hawaye ta kalli farhat din tana sake qanqameta ta dago ta kallesa ya kalli hawayen dake kokarin sauko Mata yace"

Zakije da ita?

Gyada Masa Kai tayi da sauri

Ya kamo hannun farhat din da hannunsa daya suka fice

Suna fitowa Mr Omar ya budewa NURU kofa tafara shiga kafin MALEEK ya zagaya mr Omar din ya bude Masa shima yashiga ya rufe kafin ya kamata hannun farhat ya bude gaba ya sakata ya zagaya ya shiga motar yaja suka bar gidan.

Lailah datayi mutuwar tsaye hannu take neman dorawa akai Amma kunyar 'yartama data masu aikin ta hanata kurma ihu ta zame kan kujera tana kokarin shanye hawayen dake ciko Mata idanuwa su koma.

Afia kuwa kuka tasake wiwiwi me qarfi tareda zubewa qasa Dan kuwa mum dinta tagama da rayuwarta Kamar yanda tagama da tata Dan kuwa tafi kowa sanin halin dad dinta musamman yau da zallar bacin ransa ya fito danma agaban masu aikine yasa ya Hana fushinsa bayyanuwa.

Mum Sarah na ganin hakan ta juya da sauri tayi ciki ta Isa part din masu aiki tace kowa ya shirya kayansa yanzu yanzu za'a kwashesu zasu bar gidan zuwa sabon gidan NURU.

Da sauri suka mimmiqe suka hau hada 'yan kayansu na sawa

Mum Sarah din tafito ta nufi harabar gidan ta sanarda securities saqon Mr Omar daga maleek take suma suka tashi dama Babu me wani kayan shirgi komai na gidan a tsari yake har masu Aiki da masu tsaro.

Tana Gama sanarwa kowa ta nufa nata dakin ta jera kayanta cikin akwati tsaf ta fito ta nufa dakinsu farhat ta hadawa NURU da farhat kayan buqatansu cikin Yar karamar akwatin farhat din sai schoolbag din farhat Amma bataga kayan NURU ba dayake suna dakin afia sai Bata daukar Mata kayaba ta fito dasu takai dakinta daganan Babu Wanda yasake fitowa sbd tashin hankalin da masifar dasuka gani tsagwaro atareda lailah.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huđu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/27, 7:25 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 36_*

*YERWA INCENSE & MORE*

(The scents with diff essence for YOU& your HOME)

(MASARAUTAR KAMSHI)

Ina masu neman kayayyakin kamshi yan nahiyar ketaran chadi da Senegal? Kai harma da ingataccen had’i yan bornu? To ku matso domin nesa tazo kusa...

YERWA INCENSE & MORE: Sun zo muku da kayayyakin turaruka kamar haka:

Khumra kowacce Iri.

Turarukan Wuta

Mopping khumrah

Washing khumrah

Bathing khumrah

body mist

kullaccam

scented hair cream/spray

wardrobe balls

carpet spray

air-fresheners

scented pebbles

body sprays

oil perfumes

Perfumes

kabbasa

burners

coal igniter

tong

kasko

english coal

dilke&halwa set

scented body mist

_kai dama sauran kayayyakin da bamu ambata, YERWA INCENSE AND MORE, Na tura kayayyakin su koina a fadin Nigeria da ketare. Domin tuntubar su. Suna instagram: _@yerwaincense_and_more. Ko Facebook site:YERWA _COLLECTIONs. Ko a duba su ta number su: ___08095215215/09044191709! _

suna bada kayan su kan sari ko sayi dai-‘dai

****

Suna fitowa Kai tsaye wani qaramin underground gidansa dake cikin anguwar suka nufa Wanda keda 2 bedrooms rak da manyan Palo guda biyu sai kitchen me hade da dining acikinsa komai na gidan is milk Mr Omar ne kawai yasanda gidan Babu Wanda yasan gidan nasane Haka gidan komai a kip kip yake anan yake wasu private wayoyinsa da ayyukansa hakama wata maganar me buqatan tsananin sirri anan suke zuwa suyita da Mr Omar.

Parking Mr Omar yayi yafito ya budewa MALEEK yafito kafin yabudewa NURU ita saiya zagaya ya budewa farhat tareda kamo hannunta suka biyo bayan maleek dake gaba tareda NURU dake tafiya ahankali sbd ciwon Mara.

Suna shiga palon NURU ta dago ta kalli koina cikin palon cikeda mamakin tsaruwar gidan da cikin yafi wajenma kyau sosai saidai sbd yanayinta bazata iya qarewa koina kalloba a matse take data samu guri ta kwanta Tasha ruwan zafi masu zafi Sosai ko zata Dan fada Mata tasamu period din ya sauko wahalar ta rage Mata.

A palon farko ya dakata tareda kallonta Yana nuna Mata kofar palon qurya inda bedrooms suke cikin nutsuwa yace"

Ki Shiga ciki zanyi mgn da Mr Omar.

Dan dagowa tayi ta kallesa har lokacin ita yake kallo ta gyada Kai ahankali ta juya farhat na riqeda hannunta suka wuce cikin.

Palon cikin baiyi girman na farkon ba Amma yafisa tsaruwa ta juya gurin bedrooms din ta nufi Wanda yake damarta ta murda tareda budewa ahankali batasan lokacinda ta sauke ajiyar zuciyaba sbd ganin girma da tsaruwar dakin ga makeken gadon daya kusa cika dakin komai fes fes sai qamshi koina gidan keyi da Alama kullum Ana gyara koina agidan ayi mopping Dan ko yau kila anyi Dan qamshin dayake koina dagaji sabon gyarane.

Tana Isa bakin gadon ta sulale ta haye tareda kwantawa tana dungulewa guri daya tana dafe mararta rufe idanuwanta tana Jin Dan dama dama data kwanta din.

Sai daga baya ta bude idanuwanta ahankali ta kalli farhat da duk tayi wani iri sbd halinda aka shiga sai taji yarinyar tasake shiga ranta sbd tausayinta ta cire hannu daya takamota kusada ita ta bude Baki daqyar tace"

Sweetie kadakiji tsoro ko damuwan komai kinji daddy Yana Nan Nima Ina Nan Afia ma zatazo komai lafiya Inshallah,yanzu Kinga Banda lafiya I can't treat and drss your wound kije kifadawa daddy Akira mum Sarah tazo ko Dr aduba kafanki kafin anjima nasamu naji Dan sauki kinji.

Gyada Kai tayi tareda juyawa ta fice zuwa gurin daddynta din.

Tana fita NURU tasake nadewa guri daya kaman jira Marar keyi ta kwanta tasamu nutsuwa sai ciwon yasake taso Mata wani irin zafi da zufa suka fara karyo Mata ta tashi zaune daqyar ta kunna AC Takoma ta kwanta tana shigewa cikin bargon dake kan gadon me tsananin laushi fari tas.

Kallon Mr Omar maleek yayi yace"

Kasan abinda zakayi next idan an daukosu din.

Gyada Kai Mr Omar yayi Yana cewa"

Za'a kaisu wancan gidan ne na 7579 zibrian kowa yasan aikinsa yakama suyi gyaran koina Kafin zuwa gobe ko jibi ku Isa can din.

Gyada Masa Kai maleek yayi Kai tsaye zai juya saiga farhat ta qaraso gurinsa ta shige jikinsa tana cewa"

Daddy aunt NURU batada lafiya bazata iya duba ciwona ba tace Akira min mum Sarah ko Dr" taqarasa fada tana nuna kafarta.

Kallon kafar sukayi dukkaninsu inda ruwan zafin suka zubar Mata a kafa sai alokacin sukasani ga 'yar farar kafar tata har tayi ja

Maleek ya dago ya kalli farhat din yace"

Aunt dinki bazata iya duba Miki qafanba ta gyara?

Eh daddy tun jiya da daddare aunt NURU tace cikinta na ciwo haryanxu be Dena ba gurin karbo Mata tea ne ruwan zafin ya zuba a kafana mum taketa fada.

Shiru maleek yayi kafin ya dago ya kalli Mr Omar dayayi saurin rage kansa Yana cewa"

Za'a kaita gurin Sarah acan zibrian ta kula da qafar kafin ku iso zankira Dr Damien ma yazo ya duba kafan Inshallah.

Kama hannun farhat Mr Omar din yayi Yayi gaba suka fice ya nufi mota ya bude ya sakata ya zagaya yashiga Yana waya da Edward akan idan sun Isa zibrian din da kowa yace Masa eh ankai kowa Babu Wanda aka baro a tsohon gidan sai tsohuwan madam da princess afia.

Kashe wayarsa yayi ya fita harabar gidan yahau hanyar zuwa zibrian din Yana yiwa farhat 'yar Wasa tadawo yanda take sbd yarinyar ta Dan razana da komai daya faru.

Bayan tafiyar Mr Omar ya juyo Kai tsaye ya nufi hanyar dayan bedroom Wanda ba nasaba ya Murda Kai tsaye ya tura yana kallon koina baiganta acikiba ya fito tareda rufo qofar ya nufi bedroom dinda yake gefe dabam Wanda yake matsayin nasa Yana zuwa ya bude kofar ahankali ya shiga tareda rufowa yana kallon yanda ta kwanta a dungule ya ajiye wayoyinsa kan qaramin glass table dake gefen sofar dakin ya qarasa gadon tareda tsayawa akanta Yana kallonta har saidataji mutum tsaye akanta ta bude idanuwanta ahankali ta dago dasu ta kallesa ta Mayar ta rufe tana yunqurin tashi zaune ya dakatar da ita ta hanyar Kai hannunsa daya ya maidata kwance Yana kallon wuyanta daya taba yaji zafi.

Wayarsace tayi blinkin na wuta batareda ya daukaba ya waiwaya ya kalli wayar yaga massage din Mr Omar ne daya rubuto" _Dr Damien na ya iso Yana kofa_

Zaunawa yayi bakin gadon tareda yaye bargonta ahankali tareda tayarda ita zaune da kansa Yana kallonta ahankali yace"

Dr Damien zai dubaki.

Zuba Masa idanuwanta dasukai laushi tayi tanason ce Masa Bata buqatar likita Amma sai batace komaiba ta gyada Masa Kai tana matsowa bakin gadon ta zura qafafunta qasa ya miqa Mata hannunsa ahankali ta dago ta kallesa kafin ta Dora nata akai ta Kama nasa ya miqar da ita hannunta cikin nasa suka fito Palo suka sake wucewa zuwa na farko acan suka tararda Dr Damien tareda Mr Omar dake tsaye Yana ganin fitowarsu ya sauke Kai tareda juyawa ya fice Dan Basu guri.

Daga yanda Dr Damien yafara tambayarta tabashi amsa Kai tsaye Dr Damien ya fahimci ciwonta yace"

Bawani matsala bane menstrual pains ne kawai

Ya Bata pain reliever da wasu maganin ya miqe ya fice.

Kallonta maleek yayi Kai tsaye yace"

Kina buqatan wani Abu?

Gyada Kai tayi tana miqewa suka nufi ciki tana cewa"

Zanyiwa Mr Omar texting dinsu.

Kallonta yayi bayan sunshiga dakin ya matsota jikinsa sosai ya ranqwafo da kansa daidai fuskarta yace"

Kiyi online shopping akawo daga can Mr Omar baya buqatan sanin abubuwan dazaki buqata.

Kasa dagowa tayi ta kallesa sbd sai lokacin ma takejin kunyar ciwon nata da maganar Dan kuwa itama bazaso Mr Omar tayi Masa texting su pad da panties da kayan bacci da komaima.

Rintse idanu tayi tareda zamewa ta juya ta nufi bakin gadon ta zauna tana tunanin dame zatayi shopping din ba tunda batada wayarta atareda ita.

Miqa Mata wayarsa yayi bayan ya bude Mata password ya fice daga dakin.

Panties da bra dasu pad sai turaruka da kayan bacci data siya guda uku sbd tasan zuwa anjima ko gobe za'a kawo musu kayansu na sawa itada farhat sai brushes data siya musu itada farhat da kayan baccin farhat din tayi payment dakomai duk da komai nasa kafin ta aje wayar sbd Nanda mintuna goma zuwa Sha biyar kayan zasu iso ta miqe tareda zare doguwar rigar data Dora kan kayanta ta nufi toilet din dakin ta bude taga wani irin girmane dashi tashiga tana mamakin komai na dakin

da toilet din harta tube tasakarwa kanta ruwan zafi ta gasa mararta datai nauyi Dan har lokacin be saukoba period din.

Saidata Gama ta janyo towel ta daura zata fito ta drwer jere da kalolin shavers da hair clippers a jere masu shegiyar tsada ta dauko ta kalli towel din jikinta sai alokacin tunanin dakinsa ne wannan din kenan yashigo Mata ta dafe kanta tana Jin wani iri kafin tafito.

Tana fitowa Yana zaune kan sofa yayi crossing legs Yana waya ahankali cikin nutsuwa da kamewa Amma tunda ta fito idanuwansa suke kanta duk wayar dayakeyi Kuma batareda yanayinsa ya sauya ba.

Jin idanuwansa akanta yasa takasa fita daga dakin ta nufi gaban madubinsa ta tsaya tana tunanin abinyi sai kawai taji mutum a bayanta tsaye Yana kallonta ta cikin mirror din da ido ya nuna Mata oil na Neutrogena ta Kai hannu ta dauka ta zauna gaban madubin tana shafawa ahankali

Ganin yanda takeyi yasashi juyawa ya fice Yana gyaran murya sbd muryarsa data Dan shake da wainda yake wayar Dan Haka ya fice yaci gaba da wayarsa.

Tana gamawa saigashi yashigo ya ajiye Mata jakar kayan shopping dinta daya iso yakuma ficewa

Ta bude kayan ta dauki pant da bra tasaka ta shafa turare saita tsaya tunanin kayan sawa sbd gabaki daya ta manta da cewa kafin kayansu su iso saisun buqaci kayan sawa.

Kayan baccin ta daga taduba tana fitarda numfashi me zafi sbd wainnan kayan sanyima kamata zaiyi idan tace ta yini dasu ajikinta Dan babu ta arziki ita saiyanzuma tunanin waya kaita siyansu yafado Mata.

Tattara kayan tayi tasaka wardrobe ta dauki riga daya ta saka ta daure kanta tareda Dora jallabiyarta akai ta tada sallar la'asar da akai hadda azahar da batayiba.

Tana cikin yi yashigo dakin ya Dan kalleta ganin tana sallah saidai baice komaiba ya nemi guri ya zauna Yana waya da Mr Omar dake basa bayanin komai na tafiya akan tsari.

Tana idarwa ta miqe tareda warware nadin kanta takasa cire rigar jikinta batareda ya aje wayar dayakeyi ba yace taje ankawo abinci.

Tanajin yunwa Dan Haka Bata tsayaba ta wuce Ashe Yana bayanta ya zauna dining din me kujera biyu rak ta waiwaya ahankali tace"

Farhat zandubo tazo taci abinci...

Aje wayarsa yayi tareda kashewa gabaki daya yana cewa"

Batanan tana gurin Sarah zata kula da ita.

Da marairaice fuska ta kallesa bama tareda tasan tayi hakan ba

Ya Dan bude idonsa akanta ganin yarintar datake Shirin zuba Masa Dan kamar zatayi kuka ta langwabe kai.

Saidata zuba Masa komai kafin ta hada ruwan zafi da kanta tazo ta zauna Tasha black tea me zafi tana lumshe ido sbd nutsuwar datakeji ruwan dumin nashiga cikinta.

Abincin kadan taci Tasha magani ta Dan daddaure ta gyara gurin Takoma daki ta kwanta take bacci ya dauketa sbd maganin yanasa bacci shikuma ya hau duba wasu tarin emails daya samu duk a yau din hadda na jiya dabai Samu damar dubawaba.

Bacci tayi sosai sai magriba ta tashi bawai Dan ya saketaba saima kashe Mata jiki da maganin yayi ta tashi da qyar tayo alwala tazo tayi sallah tana gamawa tadawo Palo tadan zauna tareda kunna tv Amma tsoron ganin ita kadaice yasa tana ganin lokacin ishai yayi ta koma daki tayi sallar ishai din tana gamawa ta tube tasake komawa toilet taduba har lokacin shiri period din Bai saukaba sai tayi wanka tafito ta shafa turare kawai tasaka kayan bacci kenan tana tunanin yanda zata koma dayan daki ta kwana ita kadai saigashi yashigo.

##MAMUH#

ZAFAFA BIYAR□□□

Alkiblah--SAFIYYAH HUGUMA

Makauniyar qaddara--BILLYN ABDULL

Dalaal--MISS XOXO

Mabudin zuciya--HAFSAT RANO

Ubayd Maleek--MAMUH GEE

DUKA KUDIN WANNAN DADADAN BOOKS DIN SUNA KAN FARASHIN NERA 700. WATO KUDIN PAGES KENAN. DOCUMENTS IDAN AN KAMMALA SUMA KUDIN SU DABAN..

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki□□

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban shedan biyanku(evidence of payment)□□

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

[9/27, 7:25 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 37_*

RANO NET! RANO NET! RANO NET!

WHO NO LIKE BETA AWUUF THINGS?

IDAN KAJI GANGAMI DA LABARI....! INA MASU ZUBIN ADASHEN DA BA RANAR DAUKA NA DATA?

TO KU MARMATSO KUJI, KU KUMA SHARE HAWAYEN KU, MUNZO MUKU DA SABBIN TSARE TSARE NA DATA, WADDA KOWA ZAI IYA SAYA DAI DAI KARFIN SA. A FARASHI MAI RAHUSA

_RANO NET! RANO NET! RANO NET!__

(Afford data at chikini price)

MALLAKI DATA A KUDI KALILAN DA RANO NET

TSAYA KUJI, A RANO NET ZAKA IYA ZAMA RESELLER KO WHOLESALER KAI MA, EH ZAKA/KI IYA ZAMA MA SAYAR DA DATA A FARASHIN SARI MUKE BAYARWA, KAI/KI KAFA KASUWANCIN KU KUMA. DA KUDI KALILAN.

MUNA KUMA SAYARWA AKAN ‘DAI DAYA, KOWANE NETWORK MUNA SAYARDA DATA PLAN DINSA AKAN KUDI KALILAN, MASU FARASHIN SARA KUWA MA KU KUDIN BAI KAI HAKA BAMA

AIRTEL

9MOBILE/ETISALAT

MTN

GLO

DUK MUNA SAYARDA TSARIN DATA DINSU. KAMAR MISALI MTN MUNA SAYARDA 1GB.24MB AKAN FARASHIN NERA 300 KUMA YANA KAIWA WATA DAYA, GWARGWADON YADDA KAKE AMFANI DA DATA, 2GB 600, 3GB 900!!

DUKA WADANNAN TSARIN DATA DAMA NA SAURAN LAYIKA MUNA SAYRWA AKAN FARASHI MAI RAHUSA, WANDA KOWA ZAI IYA YIN TSARIN DAI DAI ALJIHUN SA

Ranonet.com.ng

_GA SITE DINMU NAN DAKE YANAR GIZO, KAI TSAYE ZAKI/KA IYA SIYAN NAKA TA NAN. _

_KO A TUNTUBE MU TA NAMBAR TARHON MU:
+234 803 081 1300/+234 808 540 5215_

KYAU, INGANCI, RAHUSA, ADADE ANA YAWO A YANAR GIZO SAI RANO NET.

RANO NET..!!!!

****

Kallo daya yayi Mata ya dauke Kai ya ajiye wayoyinsa tana ganin Haka ta dauke Kai ta nufi kofa ta fita tana sauke ajiyar juya ta nufi kitchen ta bude fridge ta dauki ruwa Mara sanyi sosai Tasha ta juyo tana rarraba ido kan kofofin palon tana tunanin zuwa ta kwanta saidai bazata iya zuwa dayan dakinba ta kwana ita kadai sbd baqon gurine gareta da gidane zata iya Kuma da farhat na Nan tsaf zasuyi kwanciyarsu ba wani tsoro.

Numfashi ta sauke tareda daurewa Takoma dakinsa dan ta nuna batamasan da wani dakinbaa a gidan

Ta bude kofar dakin tashigo ta rufe cikin sa'a bayanan Yana toilet

Ta nufi gaban madubi tasake fesa turare ta haye gadon bayan tasake gyarawa ta kwanta tareda shigewa bargo ta rufe kanta ta lumshe idanuwa tana sauke ajiyar zuciya ahankali.

Yana fitowa Bai lura da ita ba harya Gama shirinsa ya Sanya kayan bacci Basu santsi milk kala ya rage hasken wutar dakin ya nufo gadon yayi Bismillah ya hau tareda shiga bargon Yana miqa hannunsa zai gyara yajita kwance bayansa har lokacin idonta biyu saidai idanuwanta dake arufe.

Tashi zaune yayi ya Kai hannu daga kan gadon yaqara hasken dakin kadan ya waiwayo ya yaye bargon kadan Yana kallonta

Jin Haka ta bude fararen idanuwanta tareda tashi zaune batareda ta dago ta kallesa ta zura qafafunta qasa tana qoqarin sauka gadon harta sauka ta miqe tsaye taji ya riqo hannunta ahankali tareda janyota ta fado gadon kan jikinsa kirjinta dake bayyane cikin wata figaggiyar rigar bacci saiti da fuskarsa ya dago ya kalli fuskarta da itama shi take kallo kafin ahankali ya maida kallonsa kan jirkin nata da har shafar fuskarsa yanayi tana ganin hakan ta rintse ido da sauri tana zamowa qasa ahankali ta mannu da kirjinsa atare suka lumshe ido Yana zura hannunsa daya bayanta ya manneta da jikinsa gabaki daya Yana Kai hannunsa daya ahankali kan fuskarta ya shafa zuwa wuyanta dake bayyane sbd rashin hannuwa da wuyan rigar jikinta.

Wata shafawa yayiwa wuyanta data sata qanqamesa tana Dora tarin hannuwanta tsakiyar bayansa

Ya bude idanuwansa dasuka Dan sauya ya zuba Mata ta kawar da kanta gefe tana kin kallonsa sbd kusancin nasu yayi yawa Dan tanajin hannuwansa kan fatar cinyayoyinta dake bayyane sbd rigarta data Gama kwashewa ahankali taji saukar hannunsa kan mararta zuwa kirjinta ta sake rintse ido tana dauke numfashin dayashi hade fuskarshi da tata tana shaqar nasa numfashin ta bude idanu a wahalce ta kalli fuskarsa dake manne da tata tana kallo ya hade bakinsu guri daya tareda tanajin qamshin spraymintt da dandanonsa na gauraya cikin bakinta ta lumshe ido wannan karon jikinta na mutuwa gabaki daya tanaji hannuwansa na yawo jikinta dakin yadau shiru

Tanaji mararta ta murda da qarfi taji period dinta ya zubo ta lumshe idanu har lokacin bakinsu na hade hannuwansa na cikin rigarta daya zame yacire gabaki daya ya tallafota suna sauke sauke numfashi ahankali

Ya bude ido ya kalleta idanuwanta a rufe har lokacin suna manne da juna tanajin yafara sauya komai ta rintse ido ahankali tareda matso fuskarsa ta zare bakinta ahankali takai kan kunnensa can qasan maqoshinta tace"

Yazo....saita kasa qarasawa sbd tsananin kunya da sanyin jiki.

Dakatawa yayi ahankali sbd gane abinda take nufi ya lumshe idanu tareda rungumeta kawai Yana sauke ajiyar zuciya ahankali.

Shiru sukayi ahaka tsawon lokaci kafin bacci yayi gaba dashi ahankali cikin nutsuwa

Ta Dan dago fuska ta kallesa tanajin wani yanayi me qarfi azuciyarta game dashi ta gangaro da idanuwanta kan bakinsa tana tuno dandanonsa datakeji har yanzu acikin bakinta sbd mouth spray dinsa me qarfi da sanyi ne dayake dadewa abaki ta zame jikinta daga nasa ahankali ta sauka gadon tareda lalubo rigarta cikin bargon ta Sanya ta nufi toilet Dan duba kanta.

Period din yazo dai tadawo daki ta dauki pad da wani wandon ta gyara kanta ta fito ta haye gadon ta kwanta Bata jimaba bacci me Dadi yayi gaba da ita.

Da asuba Koda yatashi Bai tadataba tunda yasan batayi Yana gamawa yakoma ya kwanta Basu tashiba sai qarfe goma saura ita tafara tashi tayi wanka ta shirya ta Sanya riga da qaramin wando Suma na baccin ne ta nufi kitchen taga abubuwan da

Mr Omar yakawo musu tunda safe na breakfast ta jera a dining tareda dauko sauran abubuwan buqatan cin abincin tana gamawa Takoma dakin daidai yafito wanka yagama shiryawa ta kallesa tanajin nauyi ta danne ta Kuma kallonsa tana qarasowa ciki tace"

Barka da tashi.

Kallonta yayi ya amsa Yana nufota itama taqi tafiya yaqaraso gabanta Yana kallon kayan jikinta Kamar zaiyi mgn saiya fasa ya nufi kofa Yana cewa"

Ki siya kayan sawa ta online su kawo miki.

Da wani kallo tabi bayansa kafin tabiyosa zuwa cin abincin

Takasa sakewa ta kallesa sai idanuwansa datake na yawo jikinta Haka suka Gama ta miqe ta tattara gurin tagyara ta dawo Palo ta tararda Yana waya saita zauna ta kunna tv takai murya qasa sosai sbd lurada bayason qara ko kadan.

Cartoon ta kunna sbd kewar farhat

Yana gani ya tsaya kallonta Yana aje wayar ya kalleta ya kalli TVn sai abin Bai bashi mamakiba saima murya daya qara Mata ta remote ta waiwayo ta kallesa tareda sakin wani kyakkyawan murmushi batareda tasaniba tana cewa"

Thank you.

Akaro na farko ya saki murmushi kawai Yana daukan wani file da Mr Omar ya aje Masa wainda zai sakawa hannu.

Zamansa gurin yasa takasa kallon yanda takeso yana lureda yawan kallonsa datake saiya dan dago ya kalleta ya nuna Mata kusa dashi ta taso ahankali tadawo Nan ta zauna ya miqa Mata wayarsa Yana cewa"

Ki siya kayan.

Karba tayi tana cewa" thank you ahankalin shima ya maida hankali kan aikinsa.

Da daddare yau da zazzabi takwana sbd sanyi daya 'dan shigeta yinin sbd rashin kayan arziki ajikinta shiyasa har asuba tana cikin jikinsa a lullube sai abin yazo Mata da sauki Dan duk Rabin zafin jikinta a nasa jikin ya shige duk da hakan sunsamu yin bacci sosai.

Guraren Sha daya Mr Omar yakawo Dr Damien yazo yadubata yabata yace wancan maganin daya Bata na farkoma zaiyi tashasa kawai zata ji sauki.

Da daddare da kanta tace adawo Mata da farhat baice Mata komaiba sbd baida tsarin komawarta yanxu so yake taji sauki gaba daya ta dawo normal kafin su tafi can sabon gidan.

Sabuwar rayuwar su biyu kadai aka bude a gidan Dan kuwa tuni ta warke ba wani sauran ciwon komai atareda ita sai period dinta da duka duka kwana hudu takeyi zuwa biyar ya dauke Dan Haka gobema takesa ran yin wankan tsarki.

Da daddare Mr Omar ya sanar dashi wata tafiyar gaggawa da ake buqatan maleek din Dan haka yau din batai wani bacci ba da safe karfe goma Mr Omar yazo daukansu ta shirya cikin riga da wandon pencil jeans da doguwar kimono suka fito Mr Omar yasaka kayansu mota suka shiga suka wuce har lokacin hankalinsa duka na kan waya sbd al'amarin babbane Dan ayanda takeji kaman daga gizah ne.

Zibrian suka Isa cikin qatoton sabon gidansa dake cikeda ma'aikatansu na tsohon gida kowa yakomawa aikinsa tun na tsohon gida hakama kayanta nacan duk ankwaso muta abinda duka,

 suna shigowa har bakin kofar palon Shiga Mr Omar yayi parking mota suka fito Yana kallonta Yana karantar yanayinta

Suna shiga farhat ta qaraso da gudu ta fada jikin NURU tana cewa"

I miss you aunt.

Sakinta tayi tafada jikin dad dinta tana cewa"

I miss you both.

Janyota NURU tayi tana cewa"

Sweetie zo Naga kafanki

Ta warke ko?

Bata sakaki zazzabi ba ko?

Na warke aunt NURU kawai dai banajin Dadin bakya Nan Afia Bata nan daddy ma bayanan.

Murmushi NURU tayi tareda duba kafar tana cewa"

Shikenan ai gashi muntaho ko

So muje kifadamun me mum Sarah ke Baki Naga kin qara karfi.

Aunt kema me daddy yabaki kin qara kyau aunt, daddy Nima zanci abinda kasiyawa Aunt NURU.

Shiru NURU tayi cikin tsananin kunyar Mr Omar daya dauke Kai Yana sosawa da mum Sarah data Dan janyo farhat din tana cewa"

Muje mukaiwa aunt dinki kayanta dakinta.

Wucewa maleek yayi Yana Hana murmushinsa bayyanuwa ya nufi hanyar zuwa dakinsa

NURU ta miqe tabi bayan farhat data Kama hanyar dakin dasukace nata.

Kofar da maleek yashiga Nan suka Shiga wani palon ne dayafi na farko tsaruwa sai kofofin bedrooms guda biyu na maleek shine kurya nata farko Kuma da Alama nashin zaifi nata girma sosai sbd ta fahimci shi mutum ne me raayin makeken daki kokuma tace daga sarautane hakan.

Dakinta ta bude tashiga sanyin AC Dana qamshin turarukanta dake jere a gaban madubi Kamar za'a bude shago dasu suka doki hancinta ta qaraso tsakiyar dakin tana kallon koina cikin burgewa sbd komai na tsarin dakin Kamar ansan raayinta.

Wardrobe ta nufa ta bude tana waiwayowa ta kalli farhat saitaga ba ita zata tambaya ba ta maida kallonta kan kayan dake shaqe da wardrobe din ta waiwaya gefen kayan bacci batasan lokacinda tasaki murmushi ba tana Jin kunyar abinda tagani ta rufe tana duba bangaren takalma Suma dai kusan duk kowane designer brand akwai.

Gurin wayarta dake gaban madubi ta Isa bayan ta jera kayan data dawo dasu a dauka tareda kunnawa zata Kira gidansu saiga farhat data fita tadawo dakin tace"

Aunt kizo daddy na Kira.

Aje wayarta tayi suka fito tare ta nufi palonsa na cikin kofar bedroom dinsa suka Shiga tareda farhat Yana zaune kan kujera Yana duba wayarsa yaji shigowarsu Bai dagoba saidata kusa isowa dab dashi ya kalleta kafin ya kalli farhat data naniketa Kamar zata gudar Mata.

Kashe wayar yayi tareda Miqewa tsaye da wayar a hannunsa Yana kallonta yace"

Gizah zamuje da Mr Omar duk abinda zai faru ki sanar Dani a waya.

Akwai tight security anan Babu Wanda zai shigo bada izininki ba dan Haka ba kowa za'a bawa izinin shigowanba.

Wani card ya ajiye Mata akan table ya wuce harzai gota ta ya tsaya tareda kallonta yayo qasa ahankali setin kunnenta yafada Mata password na card din Yana fada Mata lips dinsa na gugar kunnanta ta lumshe ido ta bude ahankali tana kasa dagowa ta kallesa sbd kunya ga farhat a tsaye tana kallonsu cikin burgewa duk da batasan meyake faruwa ba farin cikin kawai takeyi.

Kallonta yayi yaso sakin murmushi ya fuske ya wuce ta biyosa baya daf da zai fice palon ta tsaya bayansa ahankali tace"

Allah ya yadawo dakai lafiya.

Yace Amin batareda ya waiwayoba ya fice tabi bayansa da kallo.

##MAMUH#[10/2, 7:32 PM] Sadeeya: *_Mamuhgee 38_*

*YERWA INCENSE & MORE*

(The scents with diff essence for YOU& your HOME)

(MASARAUTAR KAMSHI)

Ina masu neman kayayyakin kamshi yan nahiyar ketaran chadi da Senegal? Kai harma da ingataccen had’i yan bornu? To ku matso domin nesa tazo kusa...

YERWA INCENSE & MORE: Sun zo muku da kayayyakin turaruka kamar haka:

Khumra kowacce Iri.

Turarukan Wuta

Mopping khumrah

Washing khumrah

Bathing khumrah

body mist

kullaccam

scented hair cream/spray

wardrobe balls

carpet spray

air-fresheners

scented pebbles

body sprays

oil perfumes

Perfumes

kabbasa

burners

coal igniter

tong

kasko

english coal

dilke&halwa set

scented body mist

_kai dama sauran kayayyakin da bamu ambata, YERWA INCENSE AND MORE, Na tura kayayyakin su koina a fadin Nigeria da ketare. Domin tuntubar su. Suna instagram: _@yerwaincense_and_more. Ko Facebook site:YERWA _COLLECTIONs. Ko a duba su ta number su: ___08095215215/09044191709! _

suna bada kayan su kan sari ko sayi dai-‘dai

****

Bayan fitarsa Haka ta tsaya a inda take tana bin inda ya fice da kallo zuciyarta na rarraba tunanin shin so ne takamu dashi me qarfi kokuwa Jin dadine kawai na kusantuwa dashi?.

Waiwayowa tayi ahankali ta kalli farhat dake gefenta tana kallonta kamar Bata santaba sbd ganin bayan sabon gida da aka sauya musu hadda aunt NURU da daddy dinta kaman suma sababbine aka kawo musu.

Murmushi me qayatarwa NURU tasaki tana juyawa takoma cikin palon ta zauna tareda kunna tv da remote tana Nemo tashar waqoqin yarensu ta Amstar farhat tazo ta zauna jikinta tana cewa"

Aunt NURU Zaki fassara Mana waqan da akeyi ko?

Da mamaki ta kalli farhat din tana murmushi tace"

Sweetie bazan iya fassa Miki dalla dalla ba kawai dai suna waqan soyayyarsu ne.

Da Haka ta rufe zancen farhat din sbd bazata iya bi tana fassara Mata suba kalaman sunyiwa kunnuwanta nauyi bama zata ganeba ko fassarawar tayi Mata sbd kalaman so din ko ita datake sabon Shiga sun Mata nauyi.

Saida lokacin sallah yayi ta miqe ta nufi ciki da farhat a dakinta sukai sallar bayan tayi wankan tsarki

Suna gamawa suka fito babban Palo gaba daya cin abinci daga ita sai farhat din akan dining Haka sukaci suka tashi tunanin afia yadawo Mata

Tanajin kewarta sbd akwai shaquwa da kauna a tsakaninsu ta haqiqa Dan haka takejin kewarta tun ranarda suka baro can saidai tana Mata uzuri sbd Babu Wanda zai zabi wani yabar uwarsa koman lalacewarta Dan hakan yasa Bata ganin Jin illar afia ko kadan kawai dai laifinta daya shine

Barin mahaifinta ta zabi mahaifiyarta daba itakeda gaskia ba ko acikin matsalar ta iyayen nata cire tunanin zancen tayi daga kanta sbd wannan ba huruminta bane dazata shiga tsakanin 'ya da iyayentane.

Ranar dasu mum Sarah suka baro gidan bayan kowa ya fidda kayansa anzo andaukesu akabarsu su kadai har lokacin a palon suke afia na kukan rasa cikin mum da dad din wazatabi

Lailah dakejin wata masifaffiyar hauka na bijiro Mata Jin take kamar ta Dora hannu akai tayita rusa ihu tana tsinewa maleek sbd tunda Allah ya halicceta ba'a taba muzanta taba da wulaqanta taba harma agaban bainar masu aikinta dake tsoronta da Bata girma Kamar zasu bauta Mata sai yau maleek yayi Mata wannan mummunan tabon,

Cikin tsananin ihu da masifa tareda tashin hankali ta miqe tana cewa"

Allah ya Isa tsakanina dakai MALEEK Kuma wlh bazan yardaba wannan wulaqancin dakamun kanka kayiwa Dan saina tabbatarda ka fuskanci tozarci fin wannan Kuma wlh zama matarka ko zan rasa Raina saina dawo matarka alokacin karuwarka zatasan matsayinta da nawa bazai taba zuwa dayaba Dan kuwa wlh ko zata samu damar zama cikakkiyar matarka to saidai idan Ni Lailah bana raye.....

Da sauri afia ta rufe bakinta cikin tsananin baqin cikinta da wannan karon yakai maqura baya boyuwa hawayenta na tsiyaya tace"

Mum mekike fadarwa kanki Haka?

For God's sake meye amfanin hakan?

Tun farko nayi gudun hakan mum ba kalar rokon daban mikiba karki tafi sbd duk duniya Babu abinda zakije kisamu dayafi Miki 'yayanki da mijinki Wanda mum ga dukkanin abinda nasani nake Kuma gani dad bazai taba dawo dakeba kema kinsani sbd kinsan wayeshi,

Kin Mata umarnin da kaleeb yabaki mum duk Kika shure Kika tafi?

Mum na rokeki ki hakura ki aje komai tunda yabar Miki Nan din kiyi zamanki tareda Gina sabuwar rayuwa ki maida hankali kan aikinki I promise to be with you aduk

halinda Zaki shiga matuqar Zaki janye wainnan kalaman naki ki hkr da abinda zai ringa jawo Miki wulaqanci dacin fuska,

Mum menene amfanin wainnan maganganun na cewa saidai idan bakya raye

Mum ba'a yiwa Allah ganganci wainnan maganganun har daureki zasu iyayi Dan Allah mum Ina rokonki kadakiyi abinda zai cutatar da dad ko NURU sbd ita ba laifinta bane

Idan akwai me lefi nawane nice na hada auren...

Wani mahaukacin kallo lailah tajuyo tana yiwa afia da idanuwanta dasuka fiffito sukai jajir kamar me bori tace,

Kikace mene afia?????

Kallon mum din tayi tana dakewa tace"

Nice na hada auren batareda raayin ko dayansub.....

Wani gigitaccen Marine akaro na biyu ya sauka a fuskarta Saida tayi baya ta zube kan kujera a dimauce ta dago lailah tace"

Wannan na tabbatar min da kikai bare tafi Miki uwarki

Dan kuwa kece silar duk komai daya faru ayau tsakanina da dad dinki.

Juyawa tayi a masife tayi ciki ko gabanta Bata gani sosai ta nufi dakinta tana shiga ta rufo wani irin kuka dataketa dannewa tsabar baqin ciki ya subuce Mata ta zube kasa tana sakinsa tareda rufe bakinta da hannuwanta kada afia ta jiyota abin ya Mata yawa.

Afian ma kasa bin mum din Tata tayi ta zauna agurin tana kuka ahankali ahankali.

Da daddare daqyar kowannensu ya iya kwantawa Babu ci bare Sha hakama kwanciyar kawai sukayi Babu Wanda ya samun bacci ya daukesa sbd fargaba da tashin hankalin rashin ko masu gadi Babu ko motsin komai aduk girman gidan sai rashin tsaro da motsin yasa sukaji basa cikin kwanciyar hankali musamman afia data rasa tunanin me mum dinta keyi tareda tunanin meye niyarta.

Washe gari Lailah tarigada ta yanke shawaran zuwa gizah Dan takasa hkr a Daren takira NEGES datasan shikadaine yanxu zai iya saka Baki a maganar sbd kaleeb ko Ana Mata dukan mutuwa bazata fara tunkararsaba bare Anneti datasan duk duniya bazatabi bayan kowaba indai akan 'dantane MALEEK,

Tariga ta yanke zuwa gizah sbd dawo fry da matartabarta na matsayin Matar maleek bazata taba yardaba 'yar bayi jikar bayi tasha gabanta harta karbi matsayinta.

Koda afia tashigo dakin da safe lailan na zaune tana duba agogon hannunta Dana wayarta akai akai sbd tayi booking din ticket na tafiya jira take lokaci yayi ta nufi airport

Drivern dadyn Imran takira aturo Mata shi take jira yakaita airport din

Shigowar afia yasata dagowa ta kalleta da idanuwanta dasukai jajir sbd rashin rintsawa da tashin hankali tareda masifar datake ciki ta dauke Kai daga afian tana Dan yamutsa fuska tace"

Afia idan kinzo Nan danki dameni da koke kokenkin Nan kokuma wani shirmen daban kadaki fara sbd inada ciwon kan danake fama dashi already bana buqatan wani sabo Dan bama zan dauka ba kece naki ran zaiyi mummunan baci so just get out of here"taqarasa fada tana nuna Mata kofa da ido.

Tray din da afia ta jero Mata tea da soyayyan kwai takawo Mata ta kalla tana tsiyayar hawaye takasa cewa komai ta juya ta fice hawayenta na sake gudu tana zuwa kitchen ta ajiye tray din ta juyo ta fito kenan mum din tafito janye da akwati da handbag dinta sai wayarta a hannu

Da mamaki afia ta qaraso tana share hawayenta dasuka kasa tsayuwa ta bude Baki muryanta na rawa tace"

Mum Ina....

Bata qarasaba lailan ta katseta da cewa"

Gizah zantafi idan Zaki iya zama anan ne to saina dawo idan bazaki iya ba ki nema gidan dad dinki ki koma can dama kece Kika hada auren saikije ki qarasa cike ladarki ta qara musu dankon zama.

Juyawa tayi ta fice tabar afia sandare a tsaye cikin 'dibbin mamaki da tsoron mum din Tata da sauyawarta.

Da gudu taqarasa ta riqe mum din tana cewa"

Mum Dan Allah na rokeki kada kije ki wulaqanta kanki acan

Tozarci da sake tonarda asirinki kawai Zakiyi Anneti bazata karbekiba Dan Allah kada kije mum,

Mum na rokeki Dan Allah...

Cikin quluwa lailah ta cire jikinta daga nata tana cewa"

Baki fahimci abin Dana fada Miki kenan ba nace ki nemi dad dinki ki tafi gurinsa bazan iya wannan hayaniyarba afia please just go kina batan lokaci Ina buqatan Isa airport kan lokaci.

Rabewa tayi ta wuce ta miqawa driver akwatinta ya karba yasaka mota tareda bude Mata tashiga ta rufe ya zagaya ya shiga ya tada motar suka fice.

Ajiyar zuciya afia ta sauke ahankali tanabin inda suka wuce da ido tana rasa tunanin Yi akan mahaifiyarta sbd yau da mahaifiyarta tasake tsallakewa ta barta akaro na biyu ya rusa duk wani sauran hope datake dashi akan uwarta sbd duk uwar data tsallake babbar budurwa kamarta a qaton gida irin wannan Babu kowa ta tafi ta barta batareda tunani ko fargaban wani abun yafaruba tabbas babu 'yayanta cikin ranta,

Dad dinta tasani ta tabbatarda Koda Wasa bazai iya kwatanta wannan gangancin akantaba shida yake uba Amma uwarta mace takasa yadda ta runguma takuma yadda data zama uwa me nauyin 'yayanta akanta.

Sake sauke numfashi tayi tareda juyawa ahankali ta koma ciki tana daga qafafuwanta dasukai Mata nauyi daqyar.

Dakinta direct ta nufa ta zauna bakin gadon tareda dagowa ta kalli dakin tafashe da kuka ahankali tana sunkuyar da kanta sbd yau ta wayi gari batada kowa atareda ita bawai Dan tarasa kowa din ba.

Ta share awanni a hakan tana kuka cikin hali na ciwon dakecin zuciyarta kafin ta share hawayen ahankali ta miqe tsaye ta janyo akwatinanta tafara kwashe kayanta tana zubawa ciki harsaidata Gama kwashewa tadawo ta zauna tana tunanin Kiran mahaifinta datasan ransa abace yake da ita.

Kasa kiransa tayi Takoma ta kwanta kan gado tana tunanin meya hargitsa rayuwarta cikin kwana daya da awanni akai.

Kasa kiransa tayi Takoma ta kwanta har batareda tasan matsayar inda ta dosa ba sbd wata zuciyarta na Bata shawaran in mum dinta gizah sbd dakatar da ita ga wani abin dabai kamataba Wanda zai iya janyo zubewar mutuncin dad dinsu da ita kanta mum din saidai Kuma Tana Jin gwara ta qyale mum din tayi nisa zuciyarta batajin kira.

Wayarta ta dauka ta duba Babu available tickets na zuwa gizah Dan Haka ta yanke shawaran jira kwana biyu tagani.

Bayan kwana biyu haka tasake dubawa ba tickets sai jikinta yayi sanyi ta sawa ranta ba alkhairi cikin zuwan nata Dan Haka tasake daurewa ta zauna har gari yasake wayewa ta yanke shawara takira dad dinta saidai Bata samesaba sai kawai ta Nemo wayar NURU takirata Kai tsaye.

Da safe ne suna cikin bacci itada farhat a dakinta washe garin ranarda MALEEK ya wuce kenan,

Basu tashiba sbd guraren karfe takwas ne taji ringing din wayarta ta lalubo ta dauka batareda ta tantance sunan me kiranba saidataji muryar afia ta wartsake tana bude ido tareda dubawa taga sunan afia din ne cikin kulawa tace"

Afia kina lafiya kuwa?

Ajiyar zuciya afia ta sauke dagacan bangaren tareda bude Baki tace"

Kituromin Edward yazo yadaukeni anan tsohon gidan Ina jira.

Ahankali NURU tace"

Ok Bari nakirasa nafada Masa zaizo yanzu Inshallah.

Da haka suka kashe wayoyin kowacce cikin Jin nauyin 'yar uwarta.

Batareda ta sauko gadonba daganan kwance ta Nemo numbern Edward ta saka kiransa Yana dagawa ta sanar dashi yaje ya dauko afia yace ok.

Komawa baccinta tayi sbd Bai ishetaba kafin afian ta iso.

Cikin bacci tasakejin ringing na wayarta ta lalubo ta daga cikin bacci tace"

Mum Sarah lafiya kuwa?

Sorry na tasheki dama afia ce tazo nace zan sanar dake za'a Kai Mata kayanta asalin dakinta da aka ware Mata.

Guntuwar hamma tasake tana tashi zaune tace"

Mum Sarah shine sai angayamin Kuma?

Eh nafada Miki ne sbd umarnin maleek ne.

Lumshe idanuwa tayi sbd sunansa da aka ambata yashigeta tace"

Ok shikenan akaita dakinta ganinan ma fitowa.

Duk abinda ake fada afia din na tsaye tana saurare tareda kallon ikon Allah daya sake kasheta da mamakin saidai batace komaiba ta nufi dakinta tashige tana kallon koina na gidan daya fi wancan gidan nesa ba kusaba.

##MAMUH#

[10/2, 7:32 PM] Sadeeya: *_Mamuhgee 39_*

RANO NET! RANO NET! RANO NET!

WHO NO LIKE BETA AWUUF THINGS?

IDAN KAJI GANGAMI DA LABARI....! INA MASU ZUBIN ADASHEN DA BA RANAR DAUKA NA DATA?

TO KU MARMATSO KUJI, KU KUMA SHARE HAWAYEN KU, MUNZO MUKU DA SABBIN TSARE TSARE NA DATA, WADDA KOWA ZAI IYA SAYA DAI DAI KARFIN SA. A FARASHI MAI RAHUSA

_RANO NET! RANO NET! RANO NET!__

(Afford data at chikini price)

MALLAKI DATA A KUDI KALILAN DA RANO NET

TSAYA KUJI, A RANO NET ZAKA IYA ZAMA RESELLER KO WHOLESALER KAI MA, EH ZAKA/KI IYA ZAMA MA SAYAR DA DATA A FARASHIN SARI MUKE BAYARWA, KAI/KI KAFA KASUWANCIN KU KUMA. DA KUDI KALILAN.

MUNA KUMA SAYARWA AKAN ‘DAI DAYA, KOWANE NETWORK MUNA SAYARDA DATA PLAN DINSA AKAN KUDI KALILAN, MASU FARASHIN SARA KUWA MA KU KUDIN BAI KAI HAKA BAMA

AIRTEL

9MOBILE/ETISALAT

MTN

GLO

DUK MUNA SAYARDA TSARIN DATA DINSU. KAMAR MISALI MTN MUNA SAYARDA 1GB.24MB AKAN FARASHIN NERA 300 KUMA YANA KAIWA WATA DAYA, GWARGWADON YADDA KAKE AMFANI DA DATA, 2GB 600, 3GB 900!!

DUKA WADANNAN TSARIN DATA DAMA NA SAURAN LAYIKA MUNA SAYRWA AKAN FARASHI MAI RAHUSA, WANDA KOWA ZAI IYA YIN TSARIN DAI DAI ALJIHUN SA

Ranonet.com.ng

_GA SITE DINMU NAN DAKE YANAR GIZO, KAI TSAYE ZAKI/KA IYA SIYAN NAKA TA NAN. _

_KO A TUNTUBE MU TA NAMBAR TARHON MU:
+234 803 081 1300/+234 808 540 5215_

KYAU, INGANCI, RAHUSA, ADADE ANA YAWO A YANAR GIZO SAI RANO NET.

RANO NET..!!!!

****

Direct dakin afia din NURU ta nufa data fito farhat ma ta tashi tana biyeda ita suna shiga dakin ta waiwayo tana kallonsu farhat ta qarasa gurinta da gudu cikin tsananin farin ciki me yawa tana cewa"

Yeeee afia.

Rungumeta afia tayi cikin farin cikin ganinta da kewarta datayi kwanakin tace"

My baby I love you I love you.

I love you too afia Kuma nayi kewanki sosai musamman kafin Aunt NURU da daddy sudawo nikadai dasu mum Sarah munata Jin dadinmu.

Rungumeta tasakeyi tana kallon NURU dake kallonsu cikin murmushi ta qaraso tana kallon afia din tace"

Sannu da zuwa.

Murmushin afia tayi tareda sakin farhat taqaraso gaban NURUn suka Dan rungume juna NURU ta bude Baki ahankali tace"

Am sorry afia ban....

It's ok yawuce Dan nice yakamata na Baki hakuri akan abinda mum Dina ta...

No afia yawuce kaman yanda kikece abar maganar.

Zamewa sukayi NURU na gyara tsayuwa tace"

Bari natayaki jejjera kayanki a dakin kafin agama breakfast muci.

Tayata bubbude kayan tayi suka jere suna fira anan NURU ke sanarwa afia din gobe zata fara zuwa Court Inshallah ita dayake tafara zuwa asibitin kafin wannan rigimar ta dakata sai itama tace gobe zataci gaba da zuwa kada tun wuri rashin bada himma yashiga cikin aikin.

Suna gamawa NURU ta fito ta nufi dakinta tayo brush ta sauyo Kaya ta cire na baccin dake jikinta wainda takejin nauyinsu tun dazun agaban afia.

Afia dasuka zauna cin abinci Bata wani samu damar sakewa taci sosaiba sbd tunanukan dasukai yawa akanta musamman na mum dinta da batasan meyake faruwaba a gizah din ga dad dinta har lokacin wayarsa Bata Shiga gashi takasa tambayar NURUn dad saidai ta tambayi farhat tafada Mata yayi tafiya baya Nan.

Sosai NURU ke kokarin janta da fira sbd su samu duk su dukan su sake dan sukoma kaman yanda suke wannan sabon yanayin nasu bayayiwa kowaccensu Dadi

Da Haka dai gurin firar suka fara sakewa suna danne komai tareda qoqarin mantawa kawai ahaka dai har dare yayi suka kwanta washe gari kowannensu ya tashi kan lokaci sbd Shirin fara fita zuwa gurin ayyukansu

Sukai breakfast suka fito NURUn na sanye da white long sleeves da White pencil trauser sai black kimono har qasa sai brawn and white scarf dake kanta da takalmi wedges na _Le labo_ sai handbag da Jakarta rigarta

Afia kuwa cikin jeans da shirt take sai white coat dake jikinta ta likitocin asibiti suka fada mota Edward ya fita dasu aka fara aje afia kafin aka wuce aka Kai NURU.

****

Ranarda jekadi suka iso gizah tundaga shigowarsu padima ta 'dan kalli jekadi tana gyara zama cikin motar da aka daukosu daga airport tace

Saqona na NURU datace za'a bani ko za'a banishi tun ayau inason hada kayana guri dayane idan ba damuwa.

Waiwayowa jekadi tayi ta kalleta tareda sakin murmushin manya tace"

Babu matsala saqonki a Daren yau Zaki fara karban abinki basai kin damu kanki da tambayawarbama za'a Baki komai dukkanin abinda Kika cancanta.

Murmushi padima tayi tana dauke Kai tareda cewa"

Yawwa dai Ngd Sosai.

Suna Isa har kofar dazata sadasu da sassan Matar maleek ma'ana sassan NURU anan akai parking suka fito Kai tsaye suka shige hanyar suka wuce sassan NURU sukabi wata hanya sukai tafiya me tsayi datasaka padima fara waiwaye tana son yin mgna Amma tana dannewa sbd tasamu tafara riqe abinda za'a Bata din tukuna.

Sassan maleek suka nufa suka kusa can baya sosai inda wani boyayyan gurin sirrinsa yake jekadi ta waiwayo tareda kallon padima tana bude kofar tace"

Bismillah shigo daga ciki.

Ba wani tsoro padima ta qaraso tana leqawa ta shige sbd ganin kamar dakin ajiyar dukiyane ta qarasa ciki tana dube dube tanajin matsuwar abata abinda za'a Bata ta bar gurin sbd kaman tsoro da fargaban gurin na neman shigarta.

Mintuna biyar ba'ayi ba da shigarta saiga jekadi dauke da ruwa da drinks masu sanyi a tray ta qaraso tana ajiyewa kan table dake dakin tana cewa"

Bismillah.

Dagowa padima tayi ta kalli tray din kafin ta kalli jekadi tace"

Anan ne saqon yake?

Wannan karon jekadi Bata kalletaba tace"

Eh saqon ne za'a Baki idan kinyi hkr Yana isowane.

Shiru padima tayi cikin qaguwa da gagfawarta ta saqon yashigo hannunta tasaki guntun tsaki cikin ranta tareda Kai hannu ta dauki lemun takai bakinta tafara kurba ahankali tana kallon kofa tana Jin matsuwarta na qaruwa harta shanye lemun ta dauki ruwama Tasha kadan ta ajiye tareda Miqewa dagakan kujera daya tal dake dakin sai table da kayan adon daki masu kamar zaiba ta juyo tana kokarin komawa ta zauna taji wani irin gumi da zafi zafi me tsanani Yana tasowa daga cikin jikinta ta hadiye wani wahalallen yawu sbd bakinta dake gauraya da wani irin mummunan daci ta juyo da sauri tana share gumin fuskarta tana kallon jekadi da alamar tashin hankali da azaba tace"

Me Kika bani???

Me kikeson yimin???

Innalillahi wayyo Allah

Mutuwa zanyi azaba nakeji me tsanani....

Wurgi tayi da dankwalin kanta tana fige rigar jikinta cikin wata mummunar azabar dabata taba Jin makamanciyartaba arayuwarta ta zube qasa tana yagar jikinta tako Ina tana cewa"

Dan Allah ki taimakeni

Jikina cikinsa wuta ake hurawa

Dan Allah kibani ruwa

Zan mutu.....

Shure Shure tafara jikinta na rikidewa jajir duk inda ta Sosa Kota fizga saiyayi wani irin kumburi kaman wuta ta koneta a gurin take ta haukace tana Shure shuren azaba tana ihun mummunan yanayi Jin takeyi kamar ruwan dalma na sirkuwa cikin jininta da bargonta..

Ihunta yasa jekadi juyawa ta fice daga dakin tareda rufewa ta waje ta cire qaton mukullin ta bar gurin Takoma can kofa daganan ta dauki hanyar zuwa gurin Anneti da akaiwa isarwada sakon zuwan jekadi.

Da murmushi Anneti ta kalli jekadi tace"

Barkan jekadi da dawowa lafiya,

Muna fatan anbaro Mana su maleek da mushransa tareda 'yayansa lafiya?

Da murmushi akan fuskan jekadi cikeda biyayya tace"

Alhmdlh muka barosu Inshallah.

Masha Allah to Yaya bakuwar mushrah?

Da ita kuka dawo dai Ina fata?

Sauke Kai jekadi tayi tace"

Da ita muka dawo saidai tariga ta wuce delah inshallah Bata biyo ta Nanba.

Masha Allah shikenan kije kihuta kin debo gajiyar Kai baquwa da dawowa da ita Dan Haka kije ki huta na tsawon kwanaki shida bakya buqatan fitowa kawo gaisuwa nabaki daman hutawa tukuicin Kai baquwar NURU da dawo da ita.

Cikin tsananin farin ciki jekadi tace"

Allah yaqarawa Anneti tsawon Rai da lafiya tareda girma, jekadi godia take sosai da matuka.

Murmushi kawai Anneti tayi tareda gyada kai tana cewa"

Amin.

Tashi jekadi tayi ta fice tana sake miqa godiya.

Tana fita hamdala ta sauke sbd hutunta zaibata ikon rike aikin gabanta da kyau su samu su gano asalin maqiyin maleek da nahaifinsa daya rasu Wanda suka shafe shekaru suna bibiya.

Sassanta NURU ta nufa inda takeda babban Palo da daki tareda makeken toilet dinta ware musamman acikin sassan na NURU tareda makeken dakin bayin sassan dake gefen nata.

Wanka tayi ta huta taci abinci sai alokacin tasamu ta rintsa dataga tafara aikata aikin kaleeb da maleek wainda zata iya bada ranta akansu.

Washe gari da sassafe ta saci jiki Babu me gani ta nufa gurin padima daukeda abinci cikin kwando tana Isa ta saka mukulli ta bude kofar ahankali tareda shigowa ta maida ta rufe ta ajiye kwandon hannunta tana kallon padima da kamanninta suka Gama sauyawa zuwa wani irin yanayi na tsoro da firgici tana fidda wani irin azababben Nishi dake fitar Mata daqyar.

Gyaran murya jekadi tayi tana kallonta batareda taji tausayinta ko dayaba aranta.

Daqyar cikin tsananin azaba padima ta dago idanuwanta dasuka kumbura suntum dama fuskarta Baki daya

Dukkaninta tayi jajir koina jininta.

Da hannu jekadi ta nuna Mata abincin data shigo dashi tana cewa"

Ga abinci Nan kici zai taimaka Miki kadan gurin samun karfin iya daukan dose din anjima.

Wasu siraran hawayen azabane suka silalo Mata ta gefen ido ta bude bakinta daya kunbura batako iya motsashi daqyar can qasa ta iya furta"

Meyasa? Meyasa akemin Haka????

Numfashi jekadi ta sauke ahankali tareda kallon padiman tace"

Da zakiyiwa kanki adalci tun Baki lalace da yawaba da kin Fadi inda Kika samo wannan garin da kanki Amma nasan burinki da gurbataccen tunaninki bazai Bari ki zabi hanyaba.,

Wannan shine aikin da kikaje gidan 'yar uwarki aikatawa akan mijinta kokuma nace akan MALEEK sbd qyashi da hassada sungama cinye zuciyarki gashi kin samu kanki acikin abinda tun kafin kizo duniya yake Dan haka batareda wahalarda sauran rayuwarkiba kifadamun inda wannan garin meriz din yafito yashigo hannunki.

Rintse ido tasake Yi cikin wahala wasu siraran hawayen suka sake gangaro Mata tanason fashewa da kuka batada hali sbd batada qarfin iyawa tanaji tana gani jekadi ta fice tasake rufeta cikin dakin dakeda tsananin duhu da zafi ta daga hannunta dake rawa ahankali ta wawuro abincin taga flatbread na alkama da dafaffuyar madara

Jikinta na tsananin rawa takai madarar Baki ta shanye tana Gama shanyewa tasaki cup din tana zare idanuwanta dake firfitowa kaman zasu tsinko jikinta ya tsananta rawa ta kife agurin tana ihun da baya fita ko kadan sbd dushewar murya cikin azaba Dan Ashe anxuba meriz din ciki.

Kwanan padima biyu Ana shayar da ita meriz ahankali ahankali Wanda yagama illata dukkanin jini da gangar jikinta tareda fatarta da duk tagama sabewa Takoma Kamar wadda aka tsoma cikin tafasasshen ruwa takai takawo ko motsi batayi Wanda yasa hankalin jekadi tashi ta sbd ganin Kamar padiman zata mutu saita dakata da Bata saidai dai gabaki daya padima ta sabule tashiga cikin wani irin mawuyacin hali na azaba tanajinta Amma ko motsi Bata iyayi banbancinta da matacci numfashin datakeyi ne kawai Wanda shima cikin tsananin azaba takeyinsa,

Tayi kukan zuci Dana ido Wanda baida amfani sbd dukkanin nadamarta Mara amfani ce tunda yau Bata ganin iyayenta bare 'yar uwarta Susan halinda take ciki bare su yafe Mata ko haqqinsune yakamata yasata cikin wannan mummunan qaddarar.,

A da batada fatan datakeyiwa iyayenta da 'yar uwarta tabasu tsoro Dan tayi amfani dasu saina Kiran mutuwa yau gata zatayi mutuwar bama ta gataba ta wulaqanci wadda taso maleek yayi gashi ace itace zatayi.

Hawaye suka gangaro gefen idonta suna sauka kan fatarta dake radadin azaba tace"

Abal Dan Allah kuyimin adduar sauki da rahamar ubangiji Ina cikin tsananin hali da gurbatan zuciya ya kawoni ciki.

##MAMUH#[10/2, 7:32 PM] Sadeeya: *_Mamuhgee 40_*

*_ALBISHIRINKU MATAN AFRICA DA KEWAYE , SHAHARARRAR KUMA KASAITACCIYAR MAI SAIDA KAYAN MATAN NAN WADDA KUKAFI SANI MAMAN YUSUF YAR SOKOTO TANA YI MAKU ALBISHIR DA CEWA ZAKU IYA SAMUN KAYANTA ADUK INDA KUKE CIKIN FADIN NIGERIA DA NIGER KARKU MANTA MACE MAI GYARA KANTA BATA BORANCI_* □□□□□□□ 07069711327

Akwai zafafan kayan Mata masu kyau da arha cikin sauki da rahusa Kuma duk inda kike zamu aika maki kayanki cikin aminci da yardar Allah ba cuta ba cutarwa don a Dade anayi sai gaskiya uwargida da amarya ku garzayo Kar abaku labari

Munada kalolin Kaya kamar haka□□□□□□□□□□

Maganin sanyi sahihi Mai fatattakar sanyi cikin kankanin lokaci na maza Dana Mata

Maganin gyaran nono domin dawo da martaban nononki hadin gargajiya da bashida illah ajiki

Maganin hips Mai tado da hips cikin kankanin lokaci

Maganin kiba Wanda zaisa ki ciko dai dai misali kiyi kyau kema ki shigo cikin jerin Mata masu aji

Maganin rage kiba da tumbi Wanda zaisa ki sace ki koma Yar dai dai abin alfaharin kowane namiji,

Akwai kalolin gumbuna masu kyau da saukar da ni'ima

Maganin matsi masu ciko da gaba da matseki Kamar Yar budurwa uwa uba zasu Baki dandano Mai gamasar da maigida

Kalolin garrika masu bawa mace niima da jimawa ajiki

Kalolin tsumi Sha yanzu magani yanzu dasa Mai gida ihun Dadi

Zumar mallaka

Zumar goron Tula

Zumar ridi

Zumar Mai rubutu

Hadin mallaka

Turaren mallaka

Shu'umar humra

Turaren AL'AJABI

Matan gaske

Ak 49

Sirrin tafin k'afa

Turaren fuska

Hatsabibin turare

Kwallin mallaka

Zoben mallaka

Jigidar maida tsohuwa yarinya

Maltinar Mata

Karya gado

Yajin Mata (yajin Mai ciko da mace)

Yajin maza (domin Karin k'arfi)

Muna dahuwar Kaya kamar haka□□□□□□□□□□□□□□□

Dahuwar zabo (mallaka)

Kazar Yar gata

Yan shila

Ciccibi

Dambu

Zuciya

Yan ciki

Kwai ukku

Tsoka Tara

Kifi

Da sauransu

Akwai sirrika sosai da muke hadawa ga wacce kishiya ta addabeta ko wadda take fama da butsarin namiji ko mafadacin namiji ko namiji Mai yawon dare ko Wanda yake bin Mata insha Allah duk zaku samesu Kuma da yardar Allah za'asamu biyan bukata

Muna bada magani ga yarinyar da tsautsayi ya fad'a Mata ta rasa budurcinta ta hanyar fyade ko yaudarar da namiji Kuma insha Allah zaadace da yardar Allah

Abubuwan da yawa gsky Wanda in nace Zan lissafasu sai nakwashi tsawon lokaci maiso tabini PC don ganin kalolin kayan da muke dasu ,

Karku manta mace Mai gyara kanta Bata boranci taku ce maman yusuf Yar mutan sokoto 07069711327

.

Don Allah wadda Bata shirya ba tabari sai ta shirya sannan tayimun magana□□□□□ □□□□□ngd

07069711327

****

Tun ranarda jekadi tadawo labarin dawowarta ya Isa ga neges suka tsaya jiran Jin wani labarin dazai fito daga gareta Amma shiru ba wani zancen komai karshema daya bugi cikin Anneti saiya samu labarin maleek na Nan kalau daganan suka lalibi padima sai sukaji shiru babuta Babu labarinta amed yayi neman wayarta harya gaji Bata zuwa Nan abin ya daure musu Kai, Nan yakoob mahaifin amed neges yasakashi tsananta bincike akan al'amarin sbd 'batan padima Kai tsaye na nufi da akwai matsala babba sbd ko yayane dai tasan sirrinsu Kuma idan har ta tabbata 'bata tayi to maleek ya ankaro da akwai masu Masa zagon qasa kenan.

Kwana biyu yakoob na tsananta mugun nmbincikensa acikin gizah batareda sanin kowaba ko ankarewar kowa akan sha'anin bincikensa ya tabbatar Masa da cewan tabbas padima ta dawo gizah saidai Babu Wanda yaganta Kuma alamu da binciken da yayi a airport sun tabbatarda tareda jekadi ta iso gizah Kuma motar cikin masarauta ce ta dauko su take ya fada laluben drivern daya daukosu cikin direbobin masarauta suka cabkesa tareda boyesa wani mugun wuri cikin masarautar suka fara gana Masa muguwar azaba harsaida yafada musu cewar tabbas ya dauko jekadi da padima yafadi inda ya ajiyesu.

Gyara tsayuwa yakoob yayi tareda sauke Kai qasa Yana gurfanawa cikin tsananin girmamawa da sassauta harshe yace"

Allah ya taimaki neges tabbas tunaninka gaskia ne wannan yarinya tadawo cikin gizah tareda jekadin maleek saidai haryau Babu Wanda yaganta ko yasan inda take Wanda hakan ke nuni da MALEEK yasamu masaniyar akwai abinda yake faruwa Dan Haka yarinyar yanzu rayuwarta nada gargada akan sirrin Nan duk da batasan komai gameda aikin datayi ba saidai bama buqatar bawa kuskure kofa a dukkanin aikinka neges.

Wani numfashi neges AL'MANSOOR yasaki Yana gyara zaman mulkinsa kan wata doguwar kujerar hutawarsa dake cikin palon shaqatawarsa na kuryar sassanshi ya Dan waiwayo ya kalli amintaccen nasa yakoob yace"

Kartayi mutuwar banza ayi amfani da ita tunda ita tasaka kanta aciki,

Maleek Yana tsallake komai to Bari muga ta Yaya zai tsallake wannan,

Aci amfanin yarinyar na karshe

Tsohuwar matar maleek din takira da tata matsalar nabata damar zuwa dukkaninsu zasuyi Mana amfani Dan haka kasan abin daya kamata kayi.

Angama me delah da gizah.

Juyawa yayi ya fice daga Palon yabi ta wata hanyar dazata fiddashi sashen batareda kowa tagansaba ya fice.

Washe garin ranar lailah ta sauka a gizah Wanda yasa kowa cikin mamaki sbd sanin Bata taba zuwaba sai tareda maleek shima Saida babban dalili bare yanxu dasukejin kishi kishin rabuwarta da maleek sai zuwan nata yasaka kowa cikin mamaki musamman Anneti saidai Bata nuna Mata komaiba.

Matsalar farko data fara fuskanta shine sassanta shine akaiwa sabon gyara da tsari yazama na NURU saidai tun kafin zancen ya habbaka yazama wani al'amarin daban Anneti tasaka aka gyara Mata wani sassan daban Wanda beyi girman na NURUn ba ko kadan aka Aiko Mata da bayi biyu masu Mata hidima Wanda hakan yayi

mummunan baqanta Mata wato har anan dinma saita fuskanci wulaqanci irin wannan?

Hmm zatayi lokacin kowa daga baya har Annetin sbd bazata dauka wulaqanci irin wannan ba.

Wanka tayi sai alokacin tasamu damar Dan cin wani abinci Takoma daki ta kwanta Dan hutu take tsananin buqatar yi ayanxun ko kyawun fuskarta ya dawo daidai na rashin hutu da bacci da nutsuwar dabata samuba tun shekaran jiyan sbd fitinar dake gabanta Dan haka zata huta sosai kafin tafara fitowa aganta asan haryanxu tana Nan a LAILAH MALEEK dinta kyakkyawar mace me lokaci.

Ta bangaren jekadi kuwa ganin yadda jikin padima yarikice yasata kebe kanta cikin dakinta ta nemi numbern Mr Omar tayi Masa bayanin dukkanin komai ta Dora cewa lailah na gizah ta iso.

Shiru Mr Omar yayi tareda sauke Dan numfashi sbd baiso katse hutu da Jin dadin maleek ba Dan kuwa hutun gaske maleek din keyi a kwanakin Dan ko ayyukansu tuni suka taru suna Nan Yana Dan kokari Yana rage masu rayuwar sbd maleek din yasamu hutawa dakyau Amma Kuma wannan zancen Dole ya sanar Masa dashi.

Sake sauke numfashi yayi yace"

Zan sanar Masa duk abinda yace zakiji Amma dai kafin Nan inaga ki Dan Bata maganin meriz din kadan tasamu karfin Koda kyakkyawan numfashi ne sbd na tabbatarda maleek bazaiso ta rasa ranta ba dama amfanin riqeta din asan asalin su waye suke aikin Amma dai zan sanar Masa yanxu Inshallah.

Kashe wayar yayi tareda sake fitarda numfashi me zafi Yana tunanin Dole ya isarwada maleek wannan sakon batareda Bata lokaciba duk da ba Haka yasoba

Yaso ubangidansa yasake samun hutu wadatacce Dan kuwa tsawon shekaru Basu samu irin wannan hutawarba sbd kullum cikin aiki da bincike suke matuqar ba ciwoba maleek baya sati biyu a jere zaune baiyi tafiya sai kwanakin Nan dayaga alamar kila har fiyeda watama zasuyi suna hutawa yanxu ga wani aikin.

Ajiyar zuciya ya sauke akaro na biyu kafin ya daga wayarsa ya Nemo numbern MALEEK ya saka Kira Yana nutsuwa tareda daidaita murya

Saidata kusa yankewa kafin maleek din ya daga cikin kamewa yace"

Yes Mr Omar.

Barka da hutawa MALEEK,

Dama saqone daga gizah, jekadi takira jikin yarinyar Nan yakasa daukan meriz tana cikin mawuyacin halinda kowane lokaci zata iya rasa ranta shine jekadi ke neman qarin umarnin taci gaba da aikinta kokuwa ta dakata daga Bata din?

Shiru yayi na wasu seconds daidai fitowar NURU daga wanka fatar jikinta na daukan ido ya zubawa fuskarta fararen idanuwansa batareda ta ankareba yaji tunaninsa na sauyawa akan padiman ya sauke boyayyan numfashi ahankali tareda Miqewa tsaye ya fice daga dakin ya nufi Palo Kai tsaye yace"

Kada ta Bari wani Abu yasameta ta Bata magani sosai

Zamu sauya tsarin bincikenmu batareda yarinyar ba ta jinyaceta ta warke a maidata gida gurin iyayenta

Kada abari iyayen su San abin daya faru da ita sbd kada su 'dagawa 'dayar 'yarsu hankalin.

Angama maleek.

Sai maganar Mahaifiyarsu li'iliti tana gizah ta Isa Kuma ga dukkanin bayaninda jekadi tayi Kamar da umarnin neges ta Isa can sbd bada umarninkaba,badana Anneti ba badana kaleeb ba to tabbas idan badakuba shikadaine yakeda ikon Bata damar zuwa tunda ba sauran ummnnn wannan a tsakakaninku."ya qarasa fada Yana Dan rawar murya fada sbd girmama auren MALEEK din duk da ya rabu.

Shiru maleek yayi Jin abinda mr Omar yace

Ya Dan sake gyara tsayuwa Yana tunanin Dole akwai dalilin neges na bawa Lailah damar zuwa gizah ta zauna itakuma gata idanuwanta sun rufe gabaki daya batada tunanin komai yanxu saita yanda zata farfado da kanta ta jikinsa take ya yanke shawaran zuwa gizah ya bude Baki cikin nutsuwar murya yace"

Kayi Mana Shirin komai gizah din zamuje wannan karon Ina buqatan tunatarda wasu waye maleek Incase idan sun samu mantuwa.

Yes maleek"Mr Omar yafada Yana kashe wayar maleek din take yakira ya sanarda tafiyar maleek aka garzaya karban tickets da komai.

Yaso barinta anan gidan yaje yadawo tukuna Amma Kuma bazai iyaba sbd duk tsoron dazai Bata hankalinsa zaifi kwanciya idan tana cikin mutane shiyasa ya maidata can gida zibrian gaba daya kafin suka wuce.

A gizah kuwa sosai yakoob yagano akwai abinda jekadi ke boyewa musamman Dama sunsan Dole itakadaice tasan inda padima take sbd itace wadda tashigo gizah din da ita Dan Haka ya kasa ya tsare cikin taku sosai harya gano inda take zuwa acan bayan sassan maleek duk da Bai Isa cikin sassanba ya isa kofar yasan akwai babban abinda maleek yasakata take boye gurin dangane da padima Dan Haka yakoma yafadawa neges komai

Cikin wani irin yanayi neges ya murmusa Yana jinjina Kai yace"

Ayi aike gurin tsohuwar matar maleek lailah cewa nabata damar zuwa muyi mgn.

Allah yaqara ma girma da lafiya."yakoob din yafada Yana yin baya baya ya juya ya fice.

Ta bangaren lailah kuwa yau ta samu damar Isa gurin hutawar neges Dan maganar aurenta da maleek data kawota har cikin palon akai Mata iso ta qaraso gabansa ta gaidashi cikin girmamawa kafin ta zauna cikin tata isar ta zamtowarta Matar asalin me mulkin

Take aka fara shigo da kayan marmari dasu Zuma da kayayyakin tabawa aka cike gurin tsab ta dago ta kalli kayan tareda dauke Kai sbd hakan tamkar cin fuskane ga maleek ace macen dake matsayin matarsa tana zaune gaban wani Wanda ba

maleek ba har akawo Mata abinsha Dana ci Ana nufin taci gabansa wannan rashin darajar yayi yawa tana matsayin Matar maleek guda.

Numfashi ta sauke tareda waiwayowa ta kallesa Kai tsaye cikin tausasa harshe tace"

Allah ya taimaki neges me gizah ta yanxu ina maka barka da hutawa tareda barka da ganin wannan lokacin.

Kallonta yayi daka zaman hakimcen dayake ya Dan saki fuska wani murmushin dattijantaka na sauka kan fuskarsa yace"

Neges ya amsa Kuma Yana biki barka da fitowa medakin maleek na gizah.

Lailah tunda tashigo cikin zuriarsu take tsaye a wuyansa sbd mace ce me tsananin son mulki da Isa tareda kwadayin komai yazama Yana qarqashinta da ikonta Dan kuwa Jin take kamarma itace maleek din sbd sosai ikonta da gadararta ke bayyanarda mijintane me kujerar sosai take shigar Masa hanci Yana dannewa sbd taku da zamanta sirikarsa amma zai Bata darasi daidai da ajinta sbd ita takawo kanta gurinsa yanzu neman mafitar matsalarta da maleek.

Cikin nutsuwa da kulawa ya Dan juyo da Kai a kame yace"

Abu dayane akan matsalar aurenku da maleek shine karkata da hankalinsa yayi ta wani bangaren

Ma'ana wani Abu daya rinjayi tunaninsa akan iyalinsa.

Dagowa tayi cikin mamaki tace"

Akwai abinda ya rinjayesa kuwa bayan wannan auren da yayine...

Wani murmushin yakuma saki Yana cewa"

Mace bazata juyarda maleek ba ko wacece kuwa nafi sakaran wani Abu daban Wanda Banda sani akai Amma Dole saikin Saka ido kin bincika kin gano kafin asan inda gyaran zai faro.

Shiru tayi tana nazarin zancensa sbd Bai wani shigetaba zancen Dan kuwa duk me lafiya ya kalli al'amarin dakyau zai fahimci cewan Babu wani dalilin sauyawar maleek zallar halinsane rashin daukan reni ko kadan sai aure daya qara take hasaso wani abun daban Amma tunda yafadi hakan zata bincika tagani Dan a shirye take da maganin dukkanin abinda zai shata Mata layi da zamowa Matar maleek.

Batareda ya kalleta ba yasake Dora Mata tunanin bibiyar daddaqin abinda maleek ke tunani ta hanyar bibiyar jekadi sbd itace mafi amintar maleek a duk gizah da rayuwarsu bayan kaleeb da Mr Omar ko mahaifiyarsa Anneti batasan sirrinsaba sai wainnan mutanen uku.

Da wannan tunanin sosai lailah tasakawa jekadi ayar tambaya Dama tajima da sanin jekadi maqiyiyarta ce ba kauna atsakaninsu munafukartace kodan yanda tasamu cikakken bayanin jekadi itace tsaye akan komai na NURU a rayuwar maleek Dan Haka ta kanta zata fara saita rusa yardar dake tsakaninsu da maleek bayan tasan menene matsalar tukuna.

Bayan tabaro can sassan Anneti ta nufa akaiwa Anneti shelar isowarta tashigo cikin shigar alfarmarta kamar koyaushe ta zauna ta gaida Annetin Kamar dai yanda suka Saba cikin yanayi na Ni Matar neges nikuma Matar MALEEK Babu wata qarin Hira akai sbd Lailah har cikin ranta duk tsanarsu da qiyayyarsu takeji sbd sune munafukanta dasuka tsayawa NURU akan auren MALEEK Dan Haka Bata wani tsayaba ta wuce tabar Anneti da bin bayanta da kallon mamakinda baigama sakintaba saidai bazatani takan zancen lailah ba zata jira maleek yazo tana buqatan bayanin dawowan lailan.

##MAMUH#

[10/2, 7:32 PM] Sadeeya: *_Mamuhgee 41_*

Are you guys looking for where to buy ur skincare product @ mg's skincare is the best plug for you

Do you wish to have that flawless skin that's free of all skin prblm

Do you wnt to achieve that milky skin that turn heads wherever you go☺

Try mg's product nd I assure you you'll never use any other product except mg's product

Mg's will gv you the best out of all

With mg's product ur skin is clear,fresh,smooth nd ur skin will absolutely glow all day

We have herbal whitening black soap now nd beauty set available

Nd both the soap nd the beauty set is for all skin type everyone can use it

Just gv it a try now nd see wonders

Chat:08062991549

Call:08064532391

Soap price:3k

 set:11k

Follow us on

Instagram@glow_with_mgs

Facebook:mg's skincare

 Nd guess wht

Duk Wanda zesiya Kaya daga yau Alhamis 30-9-21 zuwa Nanda 5days that is ranar talata there will be 20% off discount a soap nd the set😍so what are you guys waiting for hurry nd grab urs now is the time to glow♀

Pamper ur skin

Shine like a bride

be part of the glow team karkubari abaku lbr

Just chat 08062991549 to plc ur orders😘

Do not forget to follow us

Like nd comment pls dearies😘

Patronize us

mg's always serve you the best❤

****

Tun dasukai magana da neges tasakawa jekadi ido sosai akan motsinta takai har bibiyarta tafarayi Amma sbd jekadin ta iya takunta fiyeda tunani lailan Bata taba samun damar sanin komai dangane da wani baqin yanayi ko sirri atareda jekadin ba harta fara sarewa daga bin daddaqin na jekadi sbd Sam ba dabiarta bace Dan ita ta dauki kanta tanada abinyi hakama ba girmanta bane tsayawa irin wainnan labe laben ga abun duniya yafara sakota gaba sbd yanzu rayuwarta ta wayi gari kowa baya tareda ita tun daga kan mijinta har yayanta su danginta ba'a magana sbd ta Jima da watsar dasu dama mahaifiyarta ta Dade da rasuwa mahaifintane kawai shima tsufa yacisa sosai har baya gane kowa sai anfada Masa wannan waye shiyasa batada lokacin kowa saina Gina rayuwarta sbd gidansu kaf kowa yazamo wani hamshaqan kansu duk da ita kadaice mace sai tana alaqanta kanta da matsayinsu suda suke maza bazata taba yadda itama ta zauna tana amfani da alfarmar wani ko sunansa so take ta Gina kanta da kanta ta yanda za'a fadeta da matsayin datake dashi badai da matsayin wani datake a qarqashinsaba shiyasa ta rufe ido ta watsar da 'yayanta da komai Amma yau ta wayi gari ko 'yan aiki batadasu sai guda biyu kacal da ganinsuma baqin ciki yake sanyata sbd Kamar Saida aka zabo wainda suka fi Muni da rashin kakkamtuwa aka Aiko matasu batada 'da, batada miji, batada gidan kanta bare matsayin kanta ko sunan Wanda zatace a qarqashin alfarmarsa take batada Dan Haka gabaki daya yanzu Jin take kamar ta rasa nustuwa da tunaninta Bata iya tunanin komai kanta ya toshe zuciyarta bayan kwashe kwashen tunane tunanen duniya dasuka kusa haukatata Babu abinda takeyi tarasa wazata zauna dashi ko masifa tayi ta rage abinda takeji bare.

Tunanin 'yarta afia ne yafado Mata Rai take taji idanuwanta na neman cikowa da hawaye ta hadiye tana miqewa zuwa bakin window ko zataji sanyi sanyi Amma takasa Saida hawayen suka tsinke Mata ta zauna bakin windon tana fashewa da

wani irin kuka Mara sauti tana buqatan mutum atareda ita Wanda zai dubeta ya saurari damuwarta.

Afia take tsananin buqata ayau din sbd ta Dan duk duniya yanzu 'yartace kawai me iya rarrashinta ta rungumeta ta saurari duk haukar dazata iya fada da wadda zata iyayima kaf duniya yanzu 'yartace kawai me iya Mata wannan bayan ita ko maleek tasan bazai taba kallonta da idon sauki Kona mutunciba

Dan Haka hankalinta yaqara tashi tana jinta cikin mummunan yanayi na baqin cikin rayuwarta da Kamar tayi hasara.

Ta Jima Yana boyayyan kukan daya Gama kumbura idanuwanta da fuskar datake masifar ji da ita sunyi jajir sunyi suntum duk da hakan bataji wani sauki ko sassaucin komaiba ta miqe ta nufi toilet jiki amace ba kwari ta wanko fuskarta tareda yowar alwala Dan ko wankan batada karfin Yi tafito ta goge fuskarta ta tayarda sallar ishai da akai tun dazu bayan tagama akaro na farko bayan tsawon lokaci yau ta daga hannu tana rokon Allah sassauci da mafita sbd ada ganin tagama samun komai na rayuwa yasa sallah data zama Dole kawai takeyi Amma adhkar da sauran adduoi gurin ubangiji basa gabanta sbd duk abinda takeso tagama samu.

Agurin take zaune tana tsiyayar hawaye ta gefen fuskarta batareda ta iya tashiba takai hannu ahankali ta dauki wayarta ta Nemo sunan afia akaro na farko bayan tsawon lokaci taji qaunar 'yayanta na dawo Mata sbd haryanzu tasan kome zata zama arayuwa 'yayantane kawai bazasu taba iya guduntaba musamman afia datake kaunarta fiyeda komai saidai takasa duba kaunar da yarinyar ke Mata sai yanzu take ganewa Dan kuwa a yanda takeji yanzu ko 'yayanta abata ta zauna dasu zataji saukin duhu da kuncin da zuciyarta ke ciki.

Numbern afia takira tayita ringing No answer harso biyar take jikinta yasakeyin sanyi hannuwanta sukai sanyi ta juyar da kanta ahankali tana kallon qasa kafin ta daga wayar ahankali ta shiga gurin saqo ta rubuta mata" _Kiyi hakuri afia_

Tura Mata tayi tareda ajiye wayar tana rufe idanuwanta zuciyarta na wani irin nauyi da kunci.

Jekadi jin tsarin na barin padima tareda tattalata tasamu lafiya amaida gida yasata sauya nata tsarin itama nabin umarninsa tafara bawa padima magani tareda kulawa da goge Mata fatarta data Gama konewa tana shafa Mata magani akai akai Wanda take padiman tafara dawowa hayyacinta Dan hartana Dan iya bude Baki Kuma tana

iya zaunawa sai hakan yasaka jekadi sake bada himma sosai cikin kwana biyu padima tafara dawowa mutum sosai a ranar da padiman tafara iya bude Baki sbd tsananin farin ciki jekadi ta fita ta kebe tasake Kiran Mr Omar ta sanar dashi komai alokacin suna hanyar tahowa gizah suna cikin jirgi Amma Basu riga sun tashiba Dan Haka baida damar ganin maleek sbd Yana first class Dan haka yabari harsu Isa tukuna.

Dayake da daddare ne sosai jekadi ta fito tayi wayar adaidai lokacin lailah Tana zaune taji motsi me girma ta window din dakinta Kuma Kamar harma da mutum tagan gilmawarsa saita tashi zaune dakyau tana kallon windon zuciyarta na Dan harbawa Amma takasa riqewa ta miqe tsaye ta nufi windon tana Dan daga manyan dogayen labulayen windon saitaga kaman sake gilmawar mutum Kuma idan idonta ya gani kamar da kyau jekadi tagani.

Kallon hanyar tayi tana dawowa cikin dakinta zuciyarta na gargadarta da bin jekadin saidai Kuma wata zuciyar tana ingizata ga zuwan ta rintse ido tana komawa ta zauna saidai Kuma takasa nutsuwa tanason bin jekadin

Ta miqe da sauri tareda daukan wayarta ta fito sanyeda slippers tabi hanyar baya ta fice daga sassanta tabi inda jekadin tabi tana tafe tana waige waige har tayi Dan nisa saitakasa gane inda jekadin tabi tafara waigawa koina tana dubawa saikuma tsoro yashigeta ta juya da sauri zata juya saiga jekadi ta fito ta wata hanya tabi hanyar Nayan sassan maleek tana tafiya cikin nutsuwa sbd kada tabar qarar sawu.

Da fargaba da mamaki me tsanani take kallon jekadin tareda rintse idanu tabude mamakinta na neman komawa tsoro sbd kayan dake jikin jekadin bashine kayan data ganiba ajikin jekadin data wurga ta windontaba Kuma tabbas Bata Isa ace yanzu yanxu ta sauya kayanba.

Kodai idanuwanta ne ke Mata gizo kokuma wanine ya wurga ta windon ba jekadiba?

To idan wanine waye?

Meyasa yayi irin shigar jekadin?

Girgiza Kai tayi da sauri cikin tsananin tsoro dason tabbatarwa tabi bayan jekadin cikin sanda tana Nemo camerar wayarta tareda kashe hasken flashlight sbd idan ba tabbarwa tayi da wacece jekadin acikinsu hauka zata iya kamata Dan haka a sidade sidade tabi bayan jekadin tana waiwaye cikin tsananin tashin hankali sbd Jin kamar Kuma Ana binta itama san'da san'da abayanta.

Wata boyayyar kofar dataga jekadi ta fita yasata zare idanuwa cikin mamaki da tabbatarda zancen neges kenan dai da akwai wani Abu da maleek ke boyewa¿Aikuwa yau saitaga ko menene to Amma Kuma ta Yaya tunda jekadi rufe gurin zatayi..

Tunani tafara ta yanda zata samu Isa cikin dakin Kota halin qaqa taga abinda kila zai dawo da aurenta da maleek Dan Haka bazata Bari wannan damar ta wucetaba.

Waige waige tahau Yi cikin sauri Idonta ya fada kan wani qaton katako Wanda batama tsaya mamakin ganinsa a guri irin wannan ba ta dauka da sauri ta lallaba taqarasa bayan jekadi dake kokarin rufe kofar da mukullin ta waje bata tsaya wata wataba ta daga katakon ta buga Mata akai bada karfi ba sbd Jin bazata iya da qarfinba sbd kadata illatata sai kawai ta tureta gefe ta Fadi ta qarasa dakin da gudu ta tura kofar ta fada ciki tana dubawa.

Faduwar da jekadi tayi ganin lailan ta nufi cikin da gudu yasata miqewa da sauri tana Kiran sunanta saidai kafin tayi wani yunkuri wani mummunan duka ya sauka akanta me tsananin azaba take ta sulale agurin ta zube a some jini na fita ta goshinta batareda taga Wanda yayi Mata dukan ba.

Lailah kuwa ganin mace a kwance cikin dakin cikin wani yanayi na Kamar majinyaci yasata takowa ahankali zuciyarta na harbawa cikin tsananin mamaki da tsoro ta iso har gabanta zata Kai hannu ta tabata padiman ta bude idanuwa ahankali baccin daya fara daukanta na sakinta ta zubawa lailah idanuwanta ahankali tana kallonta da mamaki Jin motsi abakin kofar shigowan yasa padima kallon bayan lailah mamakin ganinsa nasata kaikata Kai tana kallonsa dakyau ahankali ta bude Baki tace"

AMED????

Da sauri lailah ta juya zata waiwaya wani mugun duka ya sauka a tsakiyar kanta batareda ta waiwayo ba ta yanke jiki ta Fadi agurin sama sama tanajin padiman nasake maimaita amed har idanuwanta suka rufe numfashinta na daukewa.

******

Ruwan sanyin dake sauka kan fuskarta zuwa jikinta masu tsananin sanyi ya sanyata fara numfasawa tana motsa idanuwanta dasukai tsananin nauyi tafara budesu ahankali ahankali tana rufewa tana budewa sbd hasken dayayi Mata yawa harta budesu duka suka sauka kan mutanen dake zagaye da ita tafara Binsu da ido daya bayan daya kafin ta tsayar dasu akan fuskar maleek da yayi Mata kallo daya ya dauke Kai

Ta juyar da kanta gefe taga manyan jami'an tsaro tsatsaye agurin take ta zabura da sauri tana miqewa zaune tana sake kallon mutanen dake gurin ga qarin mamaki da firgicin ganin safiyace tas idanuwanta suka sauka kan mutum kwance miqe sambal anrufesa da farin kyalle har fuska Wanda ke nuni da gawar mutum ce,ta hadiye wani mugun yawu daga bakinta daya bushe kyam Nan take tana miqewa tsaye kanta na sarawa ta dafe kan tana Jin wani tashin hankali na shigarta sbd jekadi tasan tabari agurin jiyan da daddare bayan ta tureta, wani sabon tashin hankali da faduwar gaba me qarfi tashiga kardai wani Abu yasamu jekadi Dan dukan da turewar datai mata???

waiwaye waiwaye tafara tana neman rikicewa jikinta take yafara rawar tashin hankalinda Bata saka Masa ranaba ta nufi maleek da sauri tanajin ma ta wartsake daga ciwon da kanta keyi me tsanani ko gabanta Bata gani saidata Isa gaban maleek zatayi mgna idanuwanta suka sauka gefensa daya da jekadi ke tsaye sunkuye da Kai goshinta duk jini daga gani itama tana cikin tsananin tashin hankali

A haukace lailah ta waiwaya ta kalli gawar dake rufe agurin taji qafafunta na sagewa tayi baya zata Fadi macen dake sanye cikin uniform na hukumar qasar ta tareta tana riqeta dakyau da alamar dama ita ake jira.

Ta fizgo da qarfi tana kallon maleek bakinta na rawa cikin tsananin tashin hankali tace"

Wanene???

Me yake faruwa anan?

Kallo daya yayi Mata ya juya yana sauke siririn numfashi sbd gabaki daya al'amarin ya sauya acikin qanqanin lokacinda basuyi zatoba.

Kallon gawar padima yayi akaro na hudu Yana tunanin yanda 'yar uwarta zata iya handling wannan mummunan al'amarin Sam an shammacesa a guri mafi mufi Dan kuwa yanzu acikin jekadi da lailah baisan wazai fara wankewaba duk da dukkanin shedu lailah suka nuna ita tayi kisan sbd baro baro jakadi ta fada cewar lailah ce tazo ta bugeta ta Suma itama lailan ta nuna hakan ta Yaya za'a fitarda lailah daga wannan ta bangare daya ta Yaya NURU zataji wannan mummunan labarin?

##MAMUH#[10/4, 3:51 PM] +234 906 689 9135: *_Mamuhgee 42_*

Assalamualaikum warahamatullah taala wabarakatuhu

08121491609

Aisha s bayero traditional medicine and herbal reaserch center

08121491609

08121491609

1_maganin sanyi

2_maganin niima set

3_maganin nankarwa

4_maganin kiba babba 8kkkarami

5_maganin hips

6_maganin gyaran nono

7_maganin rage kiba

8_maganin saka feeling

9_maganin cida kwai

10_zuma yar asali

11_maganin basir kowanne iri

12_hodar niiama

13_maganin mallaka

14_gumbar nonon rakumi 10k boket😩

15_gumbar madara 10k boket😩

16_turaren farin jini

17_kaza Mara kwai

18-turaren mallaka 3step

19_hadin matar minister

20_ kaza me kwai

Step 2

1.Turaren mallaka me kwalba

2. Me kunama Dan matsi 3k

3.tuaren goshi

4.turaren girji

5.tauwadar Mata

6.memory

7.kahon mallaka 8.yajin maza tea din maza

9. Dambun matsi

10. Man ayu 11.man damo pure daga zuwa sama

12. Kwallin idonka idona

13 garin Sha daka me kyau

14. Kubewar Mata gasunan dai da yawa bazan iya lisaafawaba harda na kyakkayin cinyoyin da matse matsi kina shafawa zakiji wasai

08121491609

dadai sauransu serious buyer yabiyoni private

me shawara ta bari saita gama karki batamun lokaci plx

**08121491609

****

Kasa hakuri lailah tayi cikin sabuwar qaramar haukar dake Shirin kamata agurin take tafara kwacewa tana kallon maleek da sauran mutanen dake gurin cikin tsananin ihun dukkanin jikinta na rawa take cewa"

Meyasa zaku tafi Dani?

Bani nakashetaba wlh,

Dan Allah ki tsaya nayi muku bayanin abinda yafaru wlh tallahi bani bace

Dan girman Allah maleek kace su barni kasan bazan taba iya aikata wannan mummunan abin ba

Ba halina bane,

Dan Allah ki sakeni wallahi bani bace ku tambayi jekadi Dan Allah maleek karka Bari su tafi Dani....

Tana ihun tashin hankali dukkanin jikinta Babu inda baya wani irin mazarin tashin hankali da ficewa hayyaci musamman data tabbatarda tabbas kisa akai Kuma itace ake nufin tayi kisar kenan kasheta za'ayi itama tabar duniya da 'yayanta

Tunanin hakan ke saka haukatarda kwanyarta tafara fizgewa tana kokarin zuwa gurin maleek dake tsaye batareda ya dago ya kalletaba sbd kunyar hakan da baqin cikin hakan dake cinsa koba komai ita din uwar 'yayansace matarsa ta farko wadda koman lalacewarta za'a kirata da matarsa ta farko har qarshen rayuwarsu.

Dayake har bakin kofar sassansa qatuwar baqar motar jami'an tsaron take suna Isa aka sanyata aka rufe tana wani irin kuka da neman ceto daga maleek tana rantsuwar ba ita din bace har muryarta tafara dishewa musamman daya zamto kallon karshene takewa koina Dan tasan hukun kisarta bazai dauki delay ba tunda komai a bayyane yake tasake sakin wani mahaukacin kuka tana buga kanta da tint windon motar da qarfi tana kuka tana Kiran sunan maleek cikin dukkanin bada imaninta ga shikadaine zai iya cetonta

Haka aka janyo jekadi itama aka saka cikin motar aka rufe Kafin

Ja motar suka wuce sai alokacin maleek ya dago ya kalli Mr Omar dake tsaye a gefe tsaye kansa sunkuye cikin yanayi na tsananin jimami idanuwansa suka kada sukai jajir ya dago Yana kallo 'yan motar asibitin dasuka Kira suka matso Dan daukar gawar su wuce da ita saiga shelar sanrwar tahowar NEGES da kansa zuwa sassan Dan tuni abinda yafaru ya karade gizah saidai Babu Wanda yasamu iko ko damar shigowa sassan hakama Babu Wanda yasamu masaniyar shin wanene aka kashen daga jami'an tsaron da Mr Omar yakira sai motar asibitin da jami'an tsaron sukazo dasu Dan daukan gawar sai Anneti data iso sassan cikin tsananin tashin hankali tana zubda hawayen ganin wannan mummunar qaddararriyar ranar ace kisa acikin gizah Kuma daga sassan maleek qari da Dadi tsohuwar matarsa da jekadinsace cikinsu daya ya aikata wannan mummunan Abu me duniya zatayiwa MALEEK kallo?

Gashi Anki bude gawar bare asan wanene aka kashen.

Neges na zuwa cikin tsananin jimami da tashin hankalin wannan mummunan al'amarin ya kalli MALEEK Yana bayyanarda damuwarsa da rashin Jin dadinsa akan al'amarin yace"

Ina me jajanta maka wannan al'amari

Saidai nayi maka alqawarin hukunta duk Wanda aka tabbatarda shine yayi kisan a tsakaninsu biyun Dan kuwa wannan al'amari babbane dazai iya tana darajarmu gabaki daya da ikonmu Dan Haka komai zai tafi abisaga adalci da doka wannan alqawarinane.

Sai alokacin maleek ya dago ya kallesa da idanuwansa dake bayyanarda zallar bacin Rai da wani irin zafi na iko da mulki dake yawo jininsa ahankali ya bude Baki cikin kamewa yace"

Godiya maleek yake Kuma Ina fatar zaka tuna wannan alqawarin naka Dan cikakkene jinin delas basa alwawarinda basa cikawa Ni nayi maka alqawarin tayaka cika wannan alqawarin za'a tafiyar da komai bisaga adalci da doka.

Jinjina Kai neges yayi Yana danne abinda yakeji gameda maleek din ya sassauta kallonsa zuwaga gawar da aka dauka za'a shigar ambulance ya waiwaya ya kalli yakoob Yana cewa"

A tabbatarda gawar kafin su tafi da ita.

Matsowa Mr Omar yayi Ya tarewa yakoob hanzari Yana sauke Kai cikin tsananin girmamawa ga neges Yana sassauta harshe da cewa"

Allah yaqarawa neges girma

Ina neman afuwar rashin barin abude gawa irin wannan agabanka sbd darajarka fifitacciyace dabazai yiyu irin wannan abudeta a gabanka sbd dukkanin suturarta a yage take Wanda ya nuna alamar Tasha dama da makashinta kafin samun nasararsa

Ni zanyi shedar tabbarda gawar aduk lokacinda buqatan hakan ta taso agurin Sharia.

Cikin jinjinawa yace"

Shikenan hakan yayi Allah ya kyauta Amma duk da hakan Ana buqatan tabbarwan.

Matsawa mr Omar yayi tareda bawa yakoob hanya ya wuce Dan ya tabbatar din saidai Yana Kai hannun zai bude jami'an tsaron dasuke jiran ambulance su tafi tare suka dakatar dashi cikin yanayi na dokar aikinsu da girmamawa ga neges shugaban yace"

Allah yaqarawa neges girma Babu Wanda zai sake taba gawar Nan ayanxu sbd Babu abinda mukai bincike akansa zamuje da gawar lab muduba komai ayi aune

aune daga lokacin ne bayan angama komai zamu bayar da gawar ayi Mata janaixa daganan ne kowa zai iya tabawa Amma yanxu muna bawa neges matuqar hkr

Saidai idan hankalinka yafi kwanciya da kwakwariyar shedane zamu iya cewa tunda maleek yagani hakan zai gamsar da Kai.

Numfashi boyayye neges yasake Yana jinjina Kai tareda kallon maleek cikin yanayi na kulawa da damuwa yace"

Duk yanda za'a ayi kada abari media suji wannan mumman labarin ayi komai a sirrance tunda hukumarma a sirrance suka shigo suka fice.

Motar asibitin tafara wucewa daukeda gawar kafin akabar jamian tsaro uku da sauran securities din maleek a bakin sassan na maleek sbd shima Yana cikin wainda hukumar zata tsare sbd komai a qarqashin bangarensa yafaru Dan Haka an saka tsaro a sassansa babu inda zashi zai zauna aciki bame Shiga sai mr Omar kawai aka bawa dama shima abincin kawai zai ringa shiga dashi yafito sai zuwa headquarter aduk lokacinda aka buqaci ganinsa harsai antabbatarda cikin su biyun lailah ce ko jekadin ce tayi kisan.

Da hakan zancen yasake qamari hankalin jama'ar gizah yayi mumman tashi musamman Anneti tana tsananin buqatan ganinsa saidai ba dama Haka Takoma sashenta cikin tsananin tashin hankali da damuwa tana daga hankalinta da rokon Allah sassaucin wannan mummunan masifar har lailah take roqawa sassauci sbd ita uwace tasan wannan Abu wani babban al'amarine daga ubangiji kowa na neman doki daga garesa Dan Haka kowa zata rokar Masa.

Ta bangaren Mr Omar Yana fitowa gizah tareda maleek cikin sirrantacciyar mota sai motar jamian tsaro da securities dinsa fitowarsu gizah kenan ga tarin dibbin mamakinsu 'yan media ne birjik suka yo kansu tareda zagaye motocinsu suna jeho tambayoyin dasuka kusan hargitsa tunaninsu su dukan Dan kuwa bayani ne akan cewa"

Shin me maleek zai iya cewa akan tsohuwar matarsa da jekadinsa dasuka taru suka kashe 'yar uwar matarsa?????

Tsit sukayi dukkaninsu Mr Omar na dagowa ya kallesu kafin ya 'dan waiwayo ya kalli MALEEK dake duba wayarsa hankalinsa kwance ya girgizawa Mr Omar din Kai take Mr Omar yabawa motar wuta sukai cikinsu da gudu sukaita kansu suna tsananta wutar al'amarin a social media da cewar tsohuwar matar UBAYD MALEEK M KALEEB tayi hadin gwiwa da jekadinsa gurin kashe yayar matarsa a Daren jiya.

Ganin yanda abin ke ruruwa Kamar wutar daji yasanya Mr Omar Kiran mum Sarah da gaggawa ya Bata umarnin duk wani Abu daya shafi kallon news ko wayoyin NURU da afia duk ta lalata kada tabari su samu news na abinda yake faruwa.

Ta bangaren iyayensu nu NURUn kuwa Abu Kamar hadin Baki Koda gari ya waye labarin ya baza duniya babusu Babu Wanda yasan Ina suka bace bat a dare daya ga 'yan kawo rahoto da 'yan jaridu daketa yawon gidansu sunason ganawa dasu akan al'amarin Amma babusu sai hakan yaqarawa tashin al'amarin girma sbd take aka fara kokarin Bata sunan MALEEK da cewar shine ya batarda iyayenta Dan boye laifin tsohuwar matarsa da jekadinsa.

Headquarter dasuka Isa wasu sabbin rubuce rubucen report aka shigar musamman akan ta Yaya 'yan jaridu sukasan macece aka kashe Kuma Yar uwar matarsa sbd Babu Wanda yasan gawar waye dagashi sai mr Omar ko jamian tsaro Kai tsaye ya hanasu duba gawar aka barta akan se Yan asibiti sungama nasu aikin tukuna

Kuma 'yan asibitin ma mutum biyune Kuma a asibitinda Babu Wanda yasan da ita aka aikasu to tayaya zancen yafita zuwaga 'yan media.

Suna dawowa gida ya shige sashensa ya zauna tareda sauke ajiyar zuciya ahankali tareda rufe idanu ya bude ya kalli gefenda Mr Omar yake tsaye Kai tsaye yace"

Kayi komai kaje da kanka ka taho dasu at any cost kada wannan labarin ya samesu harsai sun iso.

Dan dagowa Mr Omar yayi ya kalli MALEEK yace"

MALEEK anan din aikin Nan barinsa nada hadari.

Kaje komai Yana yanda ake son shi.

Angama Inshallah maleek.

Ficewa yayi Kai tsaye yakira Yana booking tickets Allah ya taimakesa washe gari da asuba jirjgin zai tafi Dan Haka Kai tsaye ya wuce ba wani delay.

Sai tsakiyar dare sosai ya Isa gidan Bai samu shigaba ta waya ya sanarda mum Sarah ta sanarda NURU da afia su shirya gizah zasu.

Da mamaki suka kalli juna lokacinsa mum Sarah ta sanar dasu saqon

NURU ta kalli wayarta da jiya ta wayi gari taganta a farfashe ta waiwaya ta kalli afia da tata ma tafi ta NURUn tashi aiki cikin sanyin murya tace"

Kina tunanin lafiya komai yake?

Sauke ajiyar zuciya afia tayi tana Dan duba agogo tace"

Inshallah lafiya."tafada hakan ne Dan bawa kanta qwarin gwiwa da bama NURUn positive answer Amma tun jiya takejin kanta cikin tsananin damuwa musamman dataga miscalls na mum dinta data kirata Bata kusa wayar na silent tunda ta karanta massage dinta taji tana kewar soyayyar uwa saidai Kuma zuciyarta na tunatarda da ita amfani mum dinta keson Yi da ita kawai tunda take nemanta.

Babu wani dogon musu sukahau shiru tsaf suka shirya hankulansu a tashe Babu me nutsuwa daurewa kawai kowannensu keyi Dan qarfafa Dan uwansa.

Sai washe gari da asubar fari jirginsu ya daga suka wuce Basu isaba sai cikin tsakar dare har lokacin 'yan jerida na daddabe boye a wajen masarautar gizah suna jiran rahoto

Dayake Mr Omar yasani saida sukazo gate din Yan jaridar na tasowa yace driver yayi cikinsu da mota duk da hakan sama sama afia taji dayan na jeho tambayar data sakata kallon waje da sauri inda Yan jaridar ke kokarin biyo motar askarawan securities din makeken gate din shiga masarautar suka taresu da sauri suka koma maboyarsu suna jiran sa'a.

Afia jitayi tana gigicewa da abinda kunnuwanta suka ji cewar

Tsohuwar matar maleek tayi kisa

Kenan shine dalilin daukosu da gaggawa ba shiri?

Rawa jikinta yafarayi ta dago idanuwanta nacikowa da hawayen tashin hankali ta bude Baki zatayi magana daidai tsayawan motar bakin sashensu a fixge tasamu damar fizgo maganar daqyar ta bakinta tace"

Mum tayi kisa?????

Da sauri NURU ta waiwayo ta kalleta gabanta na mummunan faduwa

Saidai ganin afian na kallon Mr Omar da idanuwanta da take sukai jajir yasa NURUn juyowa tana kallonsa da jiran amsarsa Dan kuwa take jikin NURUn yaso fin na afia daukan rawa Dan kuwa a yanda tasan lailah kila maleek ne kawai Wanda zata iya kashewa sbd kishi da baqin cikin abinda yayi Mata batasan lokacinda bakinta Yana rawaba ta furta"

Wa aka kashen???

Sauke Kai Mr Omar yayi cikin tsananin jimami da kasa fadar komai akan tambayoyinsu Wanda yasakasu tabbatarda maganar kenan Haka take abindaya faru kenan.

Take hawayen afia suka balle duk inda hankalinta yake Yana tsananin tashi

Mr Omar yayi saurin fitowa ya budewa afia kofa suka fito har NURUn tsabar rudewa ta manta da sashenta za'a qarasa da ita.

Afia tayi ciki da sauri ko gabanta Bata gani sbd tashin hankali wani takeson tambaya taji shin da gaskene kokuwa gizo maganar tayi Mata,

NURU kuwa sagewa dukkanin kafafuwanta sukai ta nufo cikin tana daga kafa daqyar farhat datai bacci saidai bayinda suke shigarda kayansu afian suka shigo da ita

Tana shigowa palon daidai lokacinda baiwar da afia ta dakawa tsawa tana cewa"

Ki fadamun abinda ke faruwa a cikin delah gizah nace.."taqarasa fada cikin tsananin karajin daya tsorata baiwar a firgice tace"

Kisa akayi a...a..sassan MALEEK.

Innalillahi'wainna ilaihirrajiun" shine abinda afia tafara maimaitawa cikin tsananin fita hayyacinta tana girgiza Kai da sauri da sauri.

NURU kuwa Jin sunan maleek a maganar yasa jiri dibarta Saida mutum biyu sukai saurin tarota dama Mr Omar yasakasu kiranta Dan qarasawa da ita Bata masaukin suka fito da ita ko ganin gabanta batayi sosai kokai dake aiki jikinta ya tsaya harta shiga mota aka ja Bata saniba,

Suna Isa bakin masaukinta mr Omar ya bude Mata kofar Motar

 gabaki daya Bata lurada wani sashene aka kawota dabam ba asalin nataba Dan tafiyar kawai takeyi batasan inda take jefa qafa Haka Mr Omar ke bude Mata kofofin palukan dasuke wucewa har zuwa na karshe daya bude ya dakata ta shige ya janyo kofar ya juya ya koma Yana ficewa daga sassan gabaki daya.

Hankalinta baya jikinta saidata takunta yafara nisa cikin palon taji iskar numfashinta ya sauya da qamshin dayake shiga hancinta ta dakata ahankali tareda dagowa ta kalli inda take tana waiwayawa gefen damarta numfashinta saidaya kusa daukewa sbd bazatan yanayin datashiga ganinsa zaune kan kujera sanyeda jallabiya brown fuskarsa na fidda wani irin zatin kwarjini Yana kallonta da fararen idanuwansa dake zube tas akanta...ta rufe ido ahankali ta bude ta tabbatarda shi dinne

Zuciyarta da gangar jikinta sunkasa hakura ta nufesa da wani irin gudu dake bayyanarda dukkanin sirrin zuciyarta akansa idanuwanta na cikowa da hawaye,

Yana ganin hakan ya miqe tsaye ahankali daidai isowarta ta fada jikinsa yayi sama da ita kamar yarinya qarama Yana kallon idanuwanta da hawayenta suka tsinke take suna gudu kan fuskarta ya sauketa tareda matseta jikinsa ahankali Yana kallon kyakkyawar fuskarta da fararen idanuwanta dake fidda hawaye sosai

Ya dauke gira daya Yana sake boyayyan murmushi tareda kamo fuskarta da tafin hannuwansa biyu Yana kallon cikin idanuwanta data dago ahankali tana kallonsa itama har lokacin idanuwanta hawayen sun kasa tsayuwa

Ahankali ya matso da fuskarsa dab da tata yakai bakinsa kan kunnenta Saida ya sauke wani numfashin daya sanyata dauke wuta cikin sirrantacciyar muryar da Bata taba jiba a hankali yace"

Kukan menene wannan??

Rintse idanuwa tayi da qarfi tana sake qanqamesa kirjinta na mannuwa da nashi yayi baya Ahankali Yana dafe kan kujerar dake bayansu Yana riko numfashinsa dake neman sauyawa ya lumshe ido tareda budewa ya kallon idanuwanta zuwa hancinta dayayi ja sbd kukan datake

Ya zura hannunsa daya zuwa bayanta ya riqo qugunta Yana sake Kai bakinsa kan kunnenta can qasa yace"

Kina tsoron mutuwana ne??....

Wani sirirn kuka ta fashe dashi Jin abindaya fada sbd har lokacin Bata gama fitowa da mummunan tashin hankalin tunanin rasashiba

Ya kamo hannunta suka zauna Yana kallon fuskarta tareda tallafo fuskar da hannuwansa Yana cikin yanayi na kulawa yace"

Ok shikenan ya Isa haka,

Ban mutu ba,Babu abindaya sameni ok?.

Rungume kanta yayi Yana shafa bayanta ahankali Yana zuwa kanta hartagama kukan tafara sauke ajiyar zuciya sai alokacin shima ya sauke boyayyar ajiyar zuciya

tareda lumshe fararen idanuwansa yanajin nutsuwa na shigarsa sbd kukan nata ya wargaza duk wata nustuwarsa dama tunanin komai.

Saidaya tabbatarda tadawo hayyacinta tagama samun nutsuwa ya dagota ya kalli fuskarta datai qasa da ita sai alokacin takejin kunyar kanta ta Dan juyar dakai tana Jin sanyi da nutsuwa na dawo Mata.

Hannunta cikin nashi suka nufi bedroom dinsa da komai ya nuna yakuma bayyanarda Nan din ne asalin turakar sarki Dan kuwa duk wani Abu dake tsare a dakin me adon zaibane(golden) sai makeken gadonsa dako rabinsa ya ishesu su biyun hadda saurama

Sai wasu dogayen labulayen windunansa dasukafi Kama da kofofi sbd girmansu ta waiwaya inda madubinsa yake ya cinye kusan Rabin bangon gefen dayake ta tsaya gaban madubin tana kallon kanta cikin nutsuwa da nazartar rayuwa sbd wato Babu Wanda yasan me ubangiji ya tanadarwa rayuwarsa agaba.

Ta cikin madubin suka kalli juna ta sauke kanta ahankali tana juyawa daga kallon madubin ta taka ahankali tabar gabansa ya riqo hannunta Yana dawowa da ita baya gabansa wannan karon kallo daya yayi Mata ya dauke Kai sbd kokarinsa kada ya tashi a banza Dan kallonta kawai na canja Masa tsarukansa da dama.

Zamewa tayi ahankali tareda nufar toilet dinsa tashige ta rufo kofa tareda sauke ajiyar zuciya me sanyi tana rufe ido cikin sanyi tace"

NURU why did you loose your control¿

Ta Jima ahaka tana sauke numfashi harsaida tadawo nutsuwarta gabaki dayanta kafin ta zare kayanta ahankali ta daure gashinta tsakiya ta yanda bazai jiqeba tayo wanka ta janyo towel dinsa blue ta dauro ta fito.

Kwance tasamesa a tsakiyar gadon takasa kallon gefen ta nufi madubinsa turare kawai tashafa ta juyo tarasa abinyi sbd sallah takeson Yi

Dole doguwar rigarta ta Dora kan towel din tayi sallolinta tana idarwa ta miqe ta zare rigar ta waiwaya takallesa a sace taga kaman yayi bacci saita sulalo ahankali ta hau gadon ta kwanta gefensa tana fuskantarsa ta zubawa kyakkyawar fuskarsa idanuwanta tana sauke ajiyar zuciya a boye, ta gangaro da idanuwanta kan dogon hancinsa da duk farhat shi ta dauko

Ta lumshe idanuwanta lokacinda taji hannunsa na sauka jikinta ahankali ta cikin bargon dasuke rufe dashi

Daga hakan Bai qare komaiba sukai bacci cikin nutsuwa da kwanciyar hankali.

##MAMUH#

_*ZAFAFA 2021! NEXT LEVEL_*

_*ZAFAFA 2021! NEXT LEVEL_*

_*ZAFAFA 2021! NEXT LEVEL_*

□□☄□ □

_*INA MASOYA MAKARANTA ZAFAFA BIYAR MASU SON SAI ZAFAFA SUNYI NISA ZASU SAYA? TOH KU MATSO, DOMIN ZAFAFAN LITTATTAFAN NAKU SUNYI NISA, DAI DAI DAD'IN KARATU_*

_*YAN BIYAR DIN NAKU KAMAR KO YAUSHE SUNA TSAKA DA RUBUTA DADAD'AN LITTATTAFAN SU MASU TAFIYA A TSARE, CIKE DA FADAKARWA, NISHADANTARWA DA KE TAFE DA RANTSATTSIYAR KAUNA MARAR GAURAYE.._*

_*SHIN YAR KUWA KINA DA LABARIN ZAFAFAN WANNAN KARON MA KUDIN SA NA PAGES NA YADDA YAKE KAMAR NA BAYA? DUKKA LITTAFAN BIYAR DIN BABU NA YARWA, KOWANNE DA KALAR DADIN SA_*

1

_*DAGA TASKAR SAFIYYAH HUGUMA: WANNAN KARON TA ZO DA WANI SABON SALON LITTAFINTA MAI SUNA : *ALKIBLA* *(THE BATTLE OF LOVE) WANDA KE KUNSHE DA FADAKARWAR RAYUWAR SAMARI DA YAMMATAN YANZU, AKWAI RANTSATTSIYAR KAUNA DA KE WATANGARIRI DA ZUKATAN MUTANE BIYU: ZAHRA DA ALIYUU❤_*

2

_*SAI DAGA ALKALAMIN HAFSAT RANO, WANNAN LEVEL DIN TAZO DA NATA KALAR RUBUTUN MAI TAKEN: MABUDIN ZUCIYA! (LOVE/HATRED) MABUDIN ZUCIYA NA TAFE DA FADAKARWA AKAN HAKKIN GASKIYA DA AKASINTA, CAKWAKIYA CE DAUKE DA LITTAFIN WANDA WARWARAR SA NA GA ZUKATA BIYU, RAFEEQ DA AYSHA_*

3

_*DAGA ALKALAMIN MAMUH GEE! WANNAN TAFIYAR TAZO DA NATA SALON MAI SUNA: UBAYD MALEEK(ROYALTY/LOVE) WANNAN KARON KASAR ETHIOPIA TA SHALLARA TA DAKKO AL'ADUN SU MAI CIKE SA FADAKRWA, MUSANMAN AKAN ZAMANTAKEWAR AURE, YA ZATA KAYA NE GA SOYAYYAH GA SARAUTA? WANNAN AMSAR NA WAJEN UBAYD DA NURU!_*

4

_*SAI DAGA ALKALAMIN NANA HAFSATU (MISS XOXO) WANNAN KARON TAZO DA NATA TAKEN LITTAFIN MAI SUNA: DALAAL! (A NEW WORLD/DESTINY's LOVE) LITTAFIN NA DAUKE DA FADAKARWA MUSANMAN DANGANA DA HAKURI, YA ZATA KAYA NE DA SOYAYYAR ZUKATU UKU, HABEEBULLAH TAGWAN (TWIN) HAFEZULLAH, GEFE DAYA GA DALAAL DA AKEYI AKANTA?SHIN WA ZAI YARDA YA BARWA DAN UWAN SA?_*

5

*SAI DAGA KARSHE, BILYN ABDULL! NA TAFE DA NATA SALON MAI SUNA: MAKAUNIYAR KADDARA!!! (BLIND LOVE) LITTAFI NE DAKE DAUKE DA FADAKARWA MUSANMAN KAN KADDARA DA KE FADAWA DAN ADAM, NATA SALON KADDARAR MAKAUNIYA CE, GEFE DAYA LITTAFIN NA DAUKE DA SALON RANTSATSSIYAR KAUNA AKAN ZINNEERAH... DA BATALIYAR MASOYANTA, MUSANMAN MODIBBO!□□_*

_*DUKA WADANNAN LITTATTAFAI NA ZAFAFA NE DA AKEYI A HALIN YANZU, KUMA KUDINSU NAIRA 700 NE PAGES. DUKA BIYAR DIN. KU GARZAYO KU MALLAKI NAKU TUN DA TURURUN SU, LITTATTAFAN ZAFAFA SUNYI FICE A YANAR GIZO, KU ZO A DAMA DAKU A WANNAN TAFIYAR TA NEXT LEVEL, MASU SANA'OIN HANNU MA MUNA TALLATAWA AKAN FARASHI MAI RAHUSA_*

_*DOMIN MALLAKAR NAKU, KU TUNTUBE MU TA:_*

*_★ AL-KʻIBLA_*□

Na Safiyya Huguma

*_★ MABUƊIN ZUCIYA_*□

Hafsat Rano

*_★ DALAAL_*□

Na Miss xoxo

*_★ UBAYD MALEEK_*□

Na Mamu gee

*_★ MAKAUNIYAR KꞌADDARA_*

Na Bilyn Abdull

Lalai daga ji babu tambaya bana ma ZAFAFAN ku da turirinsu suke tafe. Dan dagani kasan za'a ragargaza cakwakiya, soyayya. Tare da nishaɗi.

Gasu duka akan farashi mai rahusar gaske.

Kamar haka

Ɗaya___300

Biyu____400

Uku_____450

Huɗu____500

Biyar_____700

Zaku biya kudinku acikin wannan asusun namu na banki

0225878823 Hafsat Kabir Umar GTB

saiku turawa wannnan numban ta whatsapp shedan biyanku(evidence of payment/Account name)

*_08085405215_*

IDAN KUMA KATIN WAYANE KO VTU/TRANSFER ZAKU TURA TA WANNAN NUMBER TAREDA SHEDARKU□□

0903 234 5899

□□□□□□□□□□

TEAM----ZAFAFA BIYAR□😘□😍

[10/4, 3:51 PM] +234 906 689 9135: *_Mamuhgee 43_*

*LAVENDER RESTAURANT..*

(Palace of mouthwatering food/delicacies)

IDAN KUKAJI GANGAMI DA LABARI, INA MASU SON INDA ZASU SAMU INGATACCEN ABINCI MAI DADI DA LAGWADA? KAI BA ANAN MUKA TSAYA BA, INA SABBIN AMARE? MAMAs, YAYYU? DA KANNEN MU MASU SON KOYAN GIRKUNAN YAN GAYU NA KASAR NIJERIYA DA KETARE?

_*TO KU MATSO...! AT LAVENDER RESTAURANT GOTS YOU COVERED. ABINCIN KASASHE DA DAMA MUKE KOYARWA,,COME LETS UPGRADE YOUR FOOD TIME TABLE, MATSO KUSA YAR UWA GA DAMA DA ZAKI CANZA YANAYIN ABINCIN GIDAN KI, KOWA YASAN IYA SARRAFA ABINCI NA TAKA RAWAR GANI A GIDAJEN AURE. KAI KO BUDURWA CE INDE KIN IYA GIRKI ZAKIGA KOWA YANA HABA HABE DAKE.._*

_*UNCLES, DADDIES, BROTHERS., NEWLYWED HUBBYS..! KU ZO KU YIWA 'YAYAN KU, MATAN KU DA KANNEN KU RAJISTAR WANNAN HARKA TA KOYAN GIRKI.._*

_*Lavender catering school zamuyi practical class. zamuyi 30 dishes continental,snack & desserts, traditional dishes, drink. Fee din 40k NE. phone number WhatsApp and call 09080299283 akwai discount na 5% ga mutum uku farko wadanda sukai register aranakun independence 1/10/2021 to 3/10/2021 Nigeria @ 61_*

_*ZA’A FARA CLASSES RANAR 14/10/2021. WATO SHA HUDU GA WATAN OKTOBAR DA MUKA SHIGA YAU._*

_*GIRKE GIRKE GUDA 30😫😩AKAN DUBU 40 KAWAI, HARDA BONUS NA SNACKS, DESSERTS, TRADITIONAL AND MODERN DRINK, GARGALIYA DA ZAMANI□WATA DAYA CHAS ZA’AYI ANA KOYAN GIRKE GIRKEN. _*

_*KU SAKE KARANTA WANNAN BONUS DIN□□RIGIJI GABJI_*

_*Nigeria @ 61 _*

_*COOKING COMPETITION!!!_*

_*from lavender Catering ina masu son koyon girki ga dama zaku shiga gasarmu ta girki bayan kunyi register damu akan 10k,wanda yazo na 1zai shiga ajin mu free hade da wasu prize din na 2 da na 3 kuma zasu bayar da rabin kudine da wasu prize suma saura kuwa zasu ayi musu ragin 5% da wasu prize wannan gasa zamu yita ranar lahadi ne 3/10/21 zamu rufe registration na gasar ranar asabar_*

_*LAVENDER RESTAURANT: NA GARIN KANO, CLASSES DIN AKWAI PRACTICAL AND ONLINE CLASS GA WANDA KE NESA_*

****

Washe gari latti ta farka daga bacci

Ta motsa ahankali tana bude idanuwanta gabaki daya tana duba kan makeken gadon data ganta ita kadai bayanan, ta tashi zaune tana gyara daurin towel din data kwana dashi tana miqewa tsaye tana kallon kofar toilet saidai Jin Babu motsi ta tabbatarda baya cikin dakin ta nufi toilet tayo alwala tazo tayi sallah tana idarwa ta miqe ta koma ta kwanta sai lokacin tafara tunanin maganar kisar da akece mum dinsu afia tayi

Ta tashi zaune tana shiga sabuwar damuwar tausayin afia da farhat musamman afia da sai yanzu take tunanin halin datake ciki,

Yaya zata iya daukan wannan mummunan al'amarin sbd tasan yanda Afia takejin mahaifiyarta cikin ranta wannan al'amari abune me tsananin wahala da azabar dauka Dan Haka afia na tsananin buqatanta akusa da ita gaskia.

Tashi takuma Yi tareda saukowa kan gadon ta janyo kayanta na jiya ta maida jikinta tareda fitowa Palon tana gyara rufar kanta da qaramin gyalen datazo dashi daure akai

Babu kowa palon da Alama dai fita yayi gaba daya Dan Haka Kai tsaye ta nufi kofa ta fice kofa kofa ta palukansa harta Kai kofar ficewa gabaki daya ta fito

Dayake safiyace sosai Sosai Babu mutane tsit koina sai securities din maleek dake koina tafiya daya biyu saika gansu bayi ma na can kowa na aikin gyara da aikin abincin uwayen dakunansu kafin su tashi tasamu ta 'dan rufe fuskarta tana Dan sauri sauri harta Isa sashen Babu Wanda ya ganta tana shiga ta zare rufarta tareda nufar ciki Kai tsaye daga Palo bedroom din afian ta wuce ta shiga hankalinta na tashi dajin shiru a palon.

Zaune take kan dadduma tunda tagama sallah Bata tashi daga gurinba idanuwanta sun kumbura sosai sai fuskarta datai jajir ta dago ta kalli NURUn da duk hankalinta yasake tashi ganin yanayin afian take idanuwanta suka ciko da hawaye ta qaraso da sauri ta rungumeta da tsananin sanyin murya da kulawa tace"

Sorry baby.

Sai yanzu afia tasamu me lallasarta tunda wannan baqin labari ya sameta ta zube jikin NURUn tana sake sabon hawaye tana son magana tana kasawa sbd nauyin Baki dana zuciya

NURU ta girgiza Mata Kai tana tsoyayo hawaye ahankali tace"

Karkice komai kiyi shiru Ina Nan

Gani tareda ke.

Shiru sukai ahaka tsawon lokaci NURU na shafa bayanta ahankali ahankali tana Dan lallashinta tareda tunatarda ita tana tareda ita komai zaizo da sauki inshallah har afia din tasamu Dan sauki tanata sauke ajiyar zuciya akai akai.

Miqar da ita NURU tayi suka nufi gado ta zaunar da ita tareda Dora Mata kafafunta kan gadon ta ja bargo ta Dan rufe Mata Rabin jikinta ta kalleta da nata idanuwan dasuka sauya cikin kulawa da sanyi tace"

Bari nasa akawo Miki wani Abu kici

Jikinki ba qwari.

Fita tayi zuwa Palo takira masu aikin sashen tace akawo abinci Mara nauyi sosai da tea me zafi Sosai na lemun tsami da Zuma.

Da sauri cikin tsananin girmamawa suka amsa da to suka juya da sauri Dan ciko umarninta ita Kuma ta juya Takoma dakin taqaraso ta zauna gefen afia tana shiga nazari da tunanin asalin abin dayake faruwa kokuma yafaru sbd haryanzu takasa sanin takamaimai abindaya faru zancen guntu guntu kawai ta samunsa

Ta kalli afia ahankali tanason taga Bata cikin halinda zata iya tambayarta wani abun a yanzu

Gashi dad dinsu afian ma batajin zata iya tambayarsa Dan kuwa tambayar maleek kaman rashin girmamawa ne garesa saidai shi ya tambayeka Dan Haka bazata iya tambayarsaba saidai ko jekadi, idan tafita Takoma sashenta zata tambayi jekadi komai inshallah idan harta dawo daga delah daga Kai padima gida.

Da kanta ta bawa afia tea da 'dan flat filled bread guda daya ta taimaka Mata Takoma ta kwanta cikin kulawa tace"

Kiyi bacci kina buqatan hutawa Kona awa biyu zuwa uku ne ke likitace kinsan kina buqatan hutu kafin kisamu nutsuwar yin wani tunanin ok?

Lumshe ido tayi tana gyada Kai

NURU ta juya tana cewa"

Zankoma Nima nayi wanka naci abinci.....riqe hannunta daya afia tayi tana kallonta da idanuwanta dasuka sauya take suna neman cikowa da hawaye ahankali ta bude Baki tace"

Karki barni Ni daya NURU wlh ina buqatan wani atare Dani sbd zuciyata da shedan na ingizani kaman na kashe kaina na huta da wannan rayuwar,

Bana tareda soyayya ta uwata danake tsananin buqata da kwadayin samu Amma bantaba samuba tun Ina qanqanuwata mahaifiyata Bata taba zaunawa tabani soyayyar uwaba,

Mahaifina haryanzu Banda masaniyar ko fushin dayake Dani ya sauka Dan haryanzu bansamu ganinsaba bare yasan halindanake ciki,

'yar uwata ta jini yarinyace qarama da banama fatan taji abindayake faruwa,

Kakanni na mulki da rayuwar mulkice kawai agabansu banida kowa saike Dan Allah ki zauna taredani.

Kallonta NURU keyi cikin yanayi na damuwa da tausayi jikinta nayin sanyi tadawo ta riqo hannun afia din ta tayar da ita zaune tana cewa"

Muje can sashena zakifi samun nutsuwar hutawa farhat ma na can jekadi na kulawa da ita inshallah..

Da sauri afia ta dago ta kalli NURUn bakinta na rawa da mamaki tace"

Jekadi Kuma????

Ganin yanda Afia din ta firgita da Jin jekadi yasa NURUn Dan dakatawa da Mata kallon mamaki tace"

Lafiya dai ko??

Girgiza Kai afia tayi da sauri tace"

Mum da jekadi sune abin yafaru dasu ta Yaya jekadi zata dawo??...

Mummunar faduwa gaban NURU yayi tana yiwa afia kallon tashin hankali jekadi aka kashe kenan ko me???

Innalillahi wainna ilaihirrajiun..

Juyawa tayi tana neman ficewa afia tayi saurin biyota ta riqota tana cewa"

Ta Yaya akai Baki saniba bayan kin kwana a sashenki kinkuma ga bakiga jekadin ba,

Shin tadawo ne?

Gabaki daya NURU kasa amsa tambaya daya tayi sbd toshewar Kai

Harga Allah jekadi tamkar uwa ko Kaka take agurinta wadda takejinta Kamar jininta sbd a rayuwarta bayan iyayenta jekadi tafara nuna Mata qauna tamkar ta jini Dan haka bazata iya daukar zancen mutuwar jekadi Kai tsaye daga sama ba tana buqatan cikakken bayanin abinda yake faruwa ta dago jajayen idanuwanta ta kalli afia da itama itan take kallo cikin zaquwar Jin da gaske jekadin tadawo tace"

Kimin bayanin abinda yake faruwa

Acikin duhun komai nake akan al'amarin, shin meya samu jekadin da mum dinki Ni komaima bansaniba

Meyake faruwa"" zuwa lokacin hankalinta yafara mummunan tashi sbd Jin take al'amarin toko yayane ya shafeta sbd yanda rashin nutsuwa da tsoro dayake shigarta.

Afia ma sake rikicewar tayi tana kallon NURU zatai magana saita fasa ta koma ta janyo jallabiyarta me hula ta saka ta fito ta fice sbd dad dinta kawai zata iya gani

yanzu kanta neman kuncewa yakeyi ta tsaya gaban NURU data kasa cewa komai tace"

Muje sashen naki Ina buqatan ganin Mr Omar Dan Allah.

Da ido NURU kawai ke binta sbd ita idan tashiga shock kasa komai takeyi Kamar Mara tunani Haka takama hanya suka Isa sashenta tun a palon ta tsaya tana kallon sauran masu aikinta dake tsatsaye suna jiran isowarta tun jiya Bata isoba gari na wayewa sukai ayyukansu suka Gama suka sake dasa jiran isowartata

Ko gaisuwarsu Bata samu amsawa Kai tsaye ta kalli Akira wadda take matsayin babbarsu idan Jekadi Bata Nan tace"

Akira menene yafaru akan matsalar mum dinsu afia??

Shiru Akira tayi tana sauke Kai Suma tuni kowa ya sauke Kai

Akira ta Dan dago cikin shakkun tsoma Baki cikin al'amarin sbd babban gargadi daga mr Omar na kada Wanda yafadi Wanda aka kashe din wa NURU Koda Wasa.

Sake maimaita tambayarta tayi wannan karon da 'dan daga murya

Akira ta sake sauke Kai ahankali cikin tausasa harshe tace"

Kisa akai a sassan maleek a Daren shekaran jiya, Matar MALEEK ta farko itace ake zargin tayi kisan sai jekadi da aka tafi da ita itama sbd ansameta a gurin da abin yafaru.....

Kai tsaye NURU tace"

Waye aka kashen???

Tsit sukayi Akira na sake sauke kanta

Qasa cikin nutsuwa tace"

Babu Wanda yasani tukuna.

Shiru sukayi dukkaninsu daga NURUn har afia sbd tashin hankalin da mamakin al'amarin.

Zamewa afia tayi ta sulale kan kujera ta zauna tana rasa tunanin Yi

NURU ta zauna kusada ita tareda kallonta cikin tausayawa da sanyin yanayi tace"

Kaddarace wannan ki dauka daga ubangijine Kuma Inshallah zata samu kanta idan har batada hannu aciki

Sbd dad dinku bazai taba barinta cikin wannan halin ba komai zaizo ya warware Inshallah.

Kasa dagowa afia tayi tana sauraren abinda NURU take fada Mata Wanda hankalinta baya Kai tayi zurfi cikin tunani ta dago ahankali ta kalli NURU da jajayen idanuwanta tace"

Idan ta tabba cewan itace ta aika wane hukuncine zai hau kanta a shari'ancen Court??

Shiru NURU tayi tana kallonta cikin tsananin tausayawa kafin ta Dan dauke Kai cikin sanyi tace"

A shari'ancen musulunci shine Wanda ya kashe da gangan a kashesa,

A shari'ancen kotu ma idan dukkanin shedu sun bayyanarda yayi kisan da gangan ne ba bisaga qaddara ko dalilin Kare Kai ba ko dalilin ceton Rai to tabbas kisa ce ta Kai tsaye zata hau kansa....

Saurin dafa afian tayi ganin tana neman fita hayyacinta cikin sauri tace"

Dukkanin wannan kadaki yanke ko daya sbd bakisan akan me kisar ta afkuba kika tayine Dan kariyar Kai ko bisaga kaddara kadaki cire Rai daga sauqin ubangiji kiyi kokari kiriqe jarumtar fuskantar komai Inshallah ba hakan bane Ina Mata fata.

Miqewa NURUn tayi Jin tahowar farhat dake kiranta tun daga cikin bedroom ta juya ta kalli kofar dakin kafin ta dawo da kallonta kan Afia a natse tace"

Ina zuwa Bari nadubo ta.

Wucewa tayi zuwa dakin dake gefen nata Wanda aka tsarashi da komai na yara domin farhat din tana shiga ta qaqalo murmushi tana kallon kallon farhat din data shirya cikin riga da wandon asalin yadin qasar na sarauta me kyau ta qaraso gurinta tana cewa"

Heyy sweetie you look more pretty.

Cikin Jin Dadi ta qaraso gurin NURUn tana fadawa jikinta suka juyo zuwa palo tana cewa"

Aunt jiya Ina Kika kwana Kika barni Ni kadai?

Siririn Murmushi NURU tayi tana kawar da zancen tareda Dan dagowa ta kalli inda afia data bari Palon tana fatar Bata jiyo zancen da farhat din tafada ba ta kamo hannun farhat din suka nufi gefen da dining yake ta miqawa Akira hannunta tana cewa"

Kije da ita taci abinci Ina zuwa.

Komawa bedroom dinta tayi tayi wanka cikin sauri ta shirya cikin doguwar royal gown ash ta fito Akira dake jiran fitowarta ta gyara tsayuwa suka nufi sashen Anneti

Dan sai yanzu tunanin zuwa Kai Mata gaisuwa ya shigeta musamman tasan tanacan cikin damuwar al'amarin itama tabar afia zaune agurin tana saqa da warwarar yanda zata tarbi al'amarin wa mahaifiyarta sbd ko kowa ya yadda da ita ta aikata hakan bazata taba yadda da mum dinta zata aikata hakan ba.

Koda aka sanarwa Anneti qarasowar NURU gurinta sai farin ciki ya shigeta taji ta Dan samu nutsuwa da saukin abindayake cin ranta ta fito daidai shigowan NURUn data qaraso har gabanta ta durqusa har qasa ta gaisheta cikin girmamawa

Da farin ciki Anneti ta dagota tareda nuna Mata gurin zama tana amsawa cikin kulawa tace"

NURU ya kike?

Kina lafiya dai ko?

Alhmdlh"tafada cikin nutsuwa tana Dan dagowa bayan sun gama gausawar tace"

Ashe abin daya faru kenan¿Allah ya kawo mafitar wannan al'amari tareda tsare gaba.

Ajiyar zuciya Anneti tasake tana gyara zama ahankali cikin bayyanarda 'yar damuwarta tace"

Allah ne kawai masanin wannan al'amarin Amma dai koma Yaya yake

Allah ya fitar da kowa yakawo mafita

Musamman shi maleek da abin yafaru a qarqashinsa Wanda yasa Yan jaridu keta fidda labarai marasa Dadi akai

bana fatan hakan yazamo matsala agaresa, ki kula dashi sosai kibashi kulawa Dan Yana cikin tsananin damuwa na tabbata.

Shiru NURU tayi dukkanin jikinta nayin sanyi da wannan sabon bayanin data samu.

Boyayyan numfashi ta sauke tanajin tsananin buqatar son ganinsa Dan Bata lurada cewa halinda yake ciki ba kenan tun jiyan da bazata baro gurinsa ba gashi yanzu batada ikon maida kanta batareda ya nemi ganintaba.

Miqewa tayi jiki Sanyaye ta fito Takoma tanajin danuwarsa na lullubeta tana shiga Kai tsaye daki ta wuce tafara tubewa ta saka Kaya marasa nauyi tayo alwala tazo tayi sallah tana idarwa ta kwanta tareda lafewa kan gadon tanajin kaman zazzabi na neman shigarta.

Baccine yafara fizgarta cikin tunanin datai nisa daga sama sama taji Ana Kiran sunanta ta bude idanuwanta ahankali dasukai nauyi sbd kanta daya fara ciwo tuni, ta dishi dishi taga kaman jekadi take gani gabanta ta bude idanuwanta gabaki daya tana waresu akanta.

Jekadi data fahimci NURUn Bata gasgata ita bace saita Dan murmushi ahankali tana cewa"

Allah qarawa MUSHRAn maleek kyau da lafiyar bacci.

Da sauri ta tashi zaune har batasan lokacinda tafada jikin jekadin ba ta rungumeta da qarfi idanuwanta na cikowa da hawayen farin cikin ganinta da tausayinta tace"

Alhmdlh Masha Allah jekadi kindawo kindowo.

Farin cikine yakama jekadi ta zame tana kallon NURUn wadda Allah ne ya hada kauna tsakaninsu tun farko ta kalli idanuwanta dasuka ciko da hawaye tace"

Karkiyi kuka Allah zakiyiwa godia Allah yaqaro haske a rayuwarki kinji,share hawayen ki gyara fuskanki maleek ke buqatan ganinki tareda afia.

Sai alokacin ta tunoda lailah ta kalli jekadi cikin sanyi da tausayin afia dayake sake kameta tace"

Mum din afia fa??

Ajiyar zuciya jekadi tayi tareda dagowa a natse tace"

Tana hannun hukuma haryanzu sbd anyi bincike an tabbatar itace saidai haryanxu takasa tsayawa ta nutsu tayi bayaninda zai taimaketa.

Shiru sukayi dukkaninsu NURU na jajanta abin cikin ranta da yanda Afia zata dauki abin.

Ficewa jekadi tayi tana cewa tana jiranta a Palo itakuma ta nufi toilet ta wanko fuskarta ta fito ta Dan gyara ta sauya Kaya zuwa doguwar jallabiya maroon ta fito tana qamshin turaren _bosslady_ dayake fita ajikinta ahankali Bata saka sosaiba sbd kada taqarawa afia damuwa akan tata hakama Bata shafawa fuskarta komaiba duk sbd afia Dan batason saka Mata damuwar wani tunanin daban.

Data fito kallo daya jekadi Tai Mata tana karanto Mata adduoin tsari daga sharrin ido Dana Baki sbd ko Yaya NURUn tafito ita din kyanta me sanyi ne.

Afia kuwa Batada wani kwanciyar hankalinda zaisa tayiwa NURUn kallon tsaf itama dai tayi kokari ta shirya kanta suka fito jekadi na gaba suna baya sai su Akira dake take nasu bayan har zuwa bakin sashenshi kowa ya dakata daganan daga jekadi saisu suka qarasa ciki a palo na biyu suka taddashi zaune Yana sauraren bayaninda mr Omar keyi Masa hankali kwance Yana sanye cikin wani coffee brown kaftan dasuka fiddo da qyallin da fatarsa keyi kwarjininsa yana sake bayyana tareda cika idon me kallonsa

Yana Jin shigowarsu Bai waiwayoba saima takardun daya bude Yana karantawa na sakin jekadi da akai a yau din

Mr Omar kuwa sauya bayanin dayakeyi yayi da kallon gefensu NURU da cewa"

Barka da shigowa.

Da Kai NURU ta amsa Masa ahankali tana satar kallon gefen maleek din kadan Wanda Bai nuna ya San da shigowar tasu ba

Afia kuwa Batada karfin amsa Masa

Zama sukayi kafin ya dago ahankali ya zubawa NURU idanuwansa dasuka sata saurin cafko numfashinta daya tashi barin jikinta sbd kallon tajisa ajikinta sosai, ta dago fuska ahankali ta kallesa ya juyarda kallonsa kan Afia tausayin 'yar tasa na kaunarta na sake shigarsa sbd yanason 'yayansa fiyeda yanda ake gani

Ya bude Baki Kai tsaye cikin kulawa da kamewa yace"

Afia maleek yaya?kina lafiya dai ko?

Shiru tayi Idanuwanta nason cikowa da hawaye ta dago ta kallesa tana hango kulawa da kaunarta gurin dad din nata sai hawayenta suka gangaro ta girgiza Masa Kai ahankali tana cewa"

Bana cikin nutsuwa dad.

Dan gyara zama yayi Yana ajiye takardun hannunsa ya sake kame muryarsa yace"

Mum dinki itace damuwarki right?

Gyada Kai tayi tana sauke Kai kalar tausayi.

Afia idan kinmin alqawarin Zaki kwantarda hankalinki ki nutsu kodan karatunki da bawa Taki rayuwar mahimmanci ki daina biyewa tunani irin na mum dinki then namiki alqawarin Babu abinda zai samu mum dinki zata fita cikin case dinnan lafiya Amma Zaki Bata shawaran ta tafi ta inganta rayuwarta ta wani hanyar kin saurari abinda nake fada right??

Dagowa tayi ta kallesa da hawayen dake gudu akan fuskarta ta gyada Kai tana cewa"

Yes Dad namaka alqawari Inshallah dagani har ita zamu cika wannan alqawarin.

Daukan takardun gabansa yayi ya bude tareda karban biro a hannun Mr Omar yasaka hannu cikin takardun tareda rufewa ya miqawa Mr Omar yace"

Ka sameta tabaka sunan lawyernta shine zai qarasa aikin yakai takardun can zasu saketa kada abari 'yan media su sani ko kadan infact dagacan a haura da ita tabar qasar gabaki daya.

Da sauri afia ta qaraso gabansa tana Masa godiya cikin tsananin farin ciki tace"

Imran ne lawyern mum zankirasa zaizo ayau Inshallah dad.

Sunan Imran data ambata yasa NURU kallon afian ta sauke kanta.

Fita afia NURUn ma ta miqe zatabi bayanta jekadi zata dakatar da ita maleek yayi Mata kallon ta barta ta wuce.

Bayan fitarsu ya kalli Mr Omar yace"

Ayi Mata takardun ganin likitan tabin hankali kada a taba barin afia tasan mum din Tata tasamu tabin hankali sbd shock din wannan al'amarin

a fitar da ita abar Mata gidan Vegas tazauna can taringa ganin likita akai akai har Allah ya yaye Mata

Afia Kuma iyakacinta da ita airport.

Allah yaqarawa maleek tausayi da adalci.

Sai maganar Dan jaridar daya fara wallafa cewan 'yar uwar.....'dan shiru yayi Wanda yasa Mr Omar da jekadi kallon juna suna Dan murmushin dasu kadai sukasan ma'anarsa

Mr Omar ya karbi zancen da cewa'

Za'a shigarda bayyananniyar qarar shariar sama akan Wanda yafara wallafa labarin ankashe 'yar uwar mushrah sbd haryanxu bayan mu da hukumar dake hannunka babu Wanda yaga asalin gawar ta Yaya yasan wacece aka kashe hadda alaqarta da mushrah,

Dan Haka inda bayanin yafara fitowa zai fada.

Ahankali maleek ya gyada Masa Kai Yana cewa"

Daga gobe kada abarsu fitowa kowa ta zauna a sashenta a tsananta tsaro a hanyoyin bangaroransu sbd komai zai iya faruwa idan aka fallasa zancen qarar Dan jaridar sbd kada asan inda yasamu zancen.

Juyawa sukai suka fice suka bar sashen nasa sbd wayar dazai fara da kaleeb.

Sbd tsaro Koda afia Takoma sashenta doka aka bayar kadata sake fitowa sai gobe Dan Haka ita Bata damuba take tasaka aka kawo Mata sabuwar waya dayake tana tareda layinta na qasar saita Sanya ta nemi numbern Imran.

Cikin tsananin damuwar halinda suka samu labarin abindaya faru cikin tsananin damuwa yake tambayar afian Yaya case din ke tafiya sbd case ne na masarauta babu me halin Shiga danma sunyi mamakin da hukuma tashiga zancen Dan masarauta irin delah gizah sune suke hukuncin komai daya shafesu da kansu Amma Kuma ace MALEEK dakansa ya bawa hukuma damar shigowa ciki duk da hukumarma tasace sai abinda yace suke amfani dashi.

Cikin nutsuwa afia tace"

Ni yanxu duk wannan bana tunaninsa yanxu sbd ya amince zai sa asaki mum a sirrance tabar qasar Dan Haka kana buqatan isowa cikin gaggawa gobe ka isarda takardun abaka ita ku tafi

Dan Allah kamun alqawarin zaka kularmin da ita sbd nasan yanzu tana cikin tsananin hali na tashin hankali.

Dan shiru yayi Yana cewa"

Bazai yiyi nazo gobe ba sbd Kar takardun nikadai lawyer bazan iya zuwaba Dole sai munje tareda wani lawyern Wanda zai duba takardun dazanje dasu agurin dama wannan Dole 2 lawyers ne suke zuwa Dan Haka Ina buqatan time Zan nemo wani lawyer din Wanda zai bamu time dinsa yazo taredani.

Shiru afia tayi cikin tsoro da tashin hankali tace"

Baza'a iya jiraba damace dad yabawa mum Dan Allah kazo kawai an zamu samu wani lawyer din.....

Shiru tayi cikeda nazarin abin data tuno na cewan NURU ma lawyernce

Wani sanyi ya lullubeta ta maida wayar kunnenta tana cewa"

Kazo NURU is here nasan zataje tareda Kai Inshallah zanyi mgn da ita.

##MAMUH#*_Mamuhgee 44_*

*LAVENDER RESTAURANT..*

(Palace of mouthwatering food/delicacies)

_IDAN KUKAJI GANGAMI DA LABARI, INA MASU SON INDA ZASU SAMU INGATACCEN ABINCI MAI DADI DA LAGWADA? KAI BA ANAN MUKA TSAYA BA, INA SABBIN AMARE?

MAMAs, YAYYU? DA KANNEN MU MASU SON KOYAN GIRKUNAN YAN GAYU NA KASAR NIJERIYA DA KETARE?_

_*TO KU MATSO...! AT LAVENDER RESTAURANT GOTS YOU COVERED. ABINCIN KASASHE DA DAMA MUKE KOYARWA,,COME LETS UPGRADE YOUR FOOD TIME TABLE, MATSO KUSA YAR UWA GA DAMA DA ZAKI CANZA YANAYIN ABINCIN GIDAN KI, KOWA YASAN IYA SARRAFA ABINCI NA TAKA RAWAR GANI A GIDAJEN AURE. KAI KO BUDURWA CE INDE KIN IYA GIRKI ZAKIGA KOWA YANA HABA HABE DAKE.._*

_*UNCLES, DADDIES, BROTHERS., NEWLYWED HUBBYS..! KU ZO KU YIWA 'YAYAN KU, MATAN KU DA KANNEN KU RAJISTAR WANNAN HARKA TA KOYAN GIRKI.._*

_*Lavender catering school zamuyi practical class. zamuyi 30 dishes continental,snack & desserts, traditional dishes, drink. Fee din 40k NE. phone number WhatsApp and call 09080299283 akwai discount na 5% ga mutum uku farko wadanda sukai register aranakun independence 1/10/2021 to 3/10/2021 Nigeria @ 61_*

_*ZA'A FARA CLASSES RANAR 14/10/2021. WATO SHA HUDU GA WATAN OKTOBAR DA MUKA SHIGA YAU._*

_*GIRKE GIRKE GUDA 30😩😩AKAN DUBU 40 KAWAI, HARDA BONUS NA SNACKS, DESSERTS, TRADITIONAL AND MODERN DRINK, GARGALIYA DA ZAMANI□WATA DAYA CHAS ZA'AYI ANA KOYAN GIRKE GIRKEN. _*

_*KU SAKE KARANTA WANNAN BONUS DIN□□RIGIJI GABJI_*

_*Nigeria @ 61 _*

_*COOKING COMPETITION!!!_*

_*from lavender Catering ina masu son koyon girki ga dama zaku shiga gasarmu ta girki bayan kunyi register damu akan 10k,wanda yazo na 1zai shiga ajin mu free

hade da wasu prize din na 2 da na 3 kuma zasu bayar da rabin kudine da wasu prize suma saura kuwa zasu ayi musu ragin 5% da wasu prize wannan gasa zamu yita ranar lahadi ne 3/10/21 zamu rufe registration na gasar ranar asabar_*

_*LAVENDER RESTAURANT: NA GARIN KANO, CLASSES DIN AKWAI PRACTICAL AND ONLINE CLASS GA WANDA KE NESA_*

****

Shiru Imran yayi Jin sunan NURU data ambata Yana nazarin abin cikin ransa sbd baya fatan samun wani kebantaccen lokaci dagashi se NURU Dan bazai iya riqe zuciyarsa ba,bazai iya danne kansa daga Mata tambyarda yaketa son Jim amsarta daga gareta Dan Dan kuwa zuciyarsa takasa amincewa ta yarda ba auren tilas neba akaiwa NURU Dan batada gata,

Yanason ji daga bakinta cewar ta aminnce da auren kokuwa haryanzu tana sonsa Dan a shirye yake daya qararda duk abinda shida mahaifinsa suka mallaka Dan ya kwatar Mata yancinta a warware aure abarta da Wanda ta zaba Dan Haka wannan alqawarinane duk suka hadu harsuka samu damar magana yanada burin sanin raayinta akansa da aurenta Duk da Haka baiso haduwarsu tazo ta wannan hanyarba Dan shi me kishine bazaizo NURUn taje irin wurin Nan ba duk da aikintane Amma baida niyar barinta Koda shine ya aureta ta ringa shiga irin wainann cases din.

Numfashi ya sauke tareda boyayyar ajiyar zuciya ahankali kafin ya bude Baki yace"

Ba damuwa zan bincika tafiyar inshallah zanyi kokari ko cikin Daren nan ne na taso ko gobe tunda safe kifada Mata.

Aje wayar yayi Yana sauke ajiyar zuciya da numfashi atare Yana rufe idanuwansa da Basu Gama dawowa daidaiba tun ciwon dayayi ya warke

Ya miqe tsaye Yana jefar da wayarsa kan kujera sbd wasu feelings dinsa da afia ke Shirin tado Masa kokuma Tama tado Masa shi akan soyayyar NURU data fara koyawa kansa dangana.

Afia kuwa tana aje wayar taji hankalinta ya Dan kwanta sbd tanada tabbacin mum dinta zata samu damar fara wata kyakkyawar rayuwar koba a gidan dad dinta ba

tana Mata fatan samun rayuwa kwanciyar hankali da nutsuwa tareda sauyawa Dan kuwa wannan al'amarin daya faru babban darasine gareta.

Tana buqatan mgnar da NURU gashi ba waya hannun NURUn sai kawai ta fito da kanta zata nufi gurin NURUn tasamu tsaro a bakin sashinta tareda umarnin ba fita koina sai gobe.

Da mamaki ta kalli Wanda yake shugaban tsaron tace"

Daga Ina umarnin yafito?

Sauke Kai yayi cikin nutsuwa yace"

Daga gurin MALEEK.

Siririn numfashi ta sauke tareda hakura ta juya Takoma batareda tace komaiba sbd daga yanxu umarnin dad dinta abune me girma a rayuwarta da bazata iya tsallakewaba badan alfarwar da yayiwa mum dinta kawai ba hadda tabbatarwa datai shine komai nata samun mahaifi kamarsa sai antona.

Dawowa tayi ta nufi bedroom dinta Kai tsaye ta tube sai alokacin tasamu damar qwarin watsawa jikinta ruwa tanajin al'amarin ya warware Mata Inshallah.

Acikin Daren ranar Mr Omar yayi qwalailar bincikensa tareda yonasi wani jami'in tsaron maleek suka gano jaridar data fara wallafa labarin

Suka zurfafa binciken daya nuna Kai tsaye jaridar ta fitarda labarin ne tun qarfe shida na safiyar ranar alhalin ba'a Kuma maganar kisan Bata bayyanaba sai qarfe takwas na safe ma su maleek suka Isa gurin Kuma Basu Kira hukuma ba sai qarfe Tara hakan ke nuni da labarin yasamu masu jaridar ne kamar ma tun cikin Daren da abin yafaru kenan kafin afkuwar abin ma.

Da wannan aka Isa gidan jaridar Kai tsaye aka kama shugaban companyn zuwa headquarters Kai tsaye Maleek yabada umarnin rashin sassauci ga binciken mutumin Wanda dam jira suke su Kuma jamian tsaron suka hau gana Masa azabar data sakashi saurin bada bayani Nan take cewar wani ne acikin Daren yakawo Masa information din saidai baiga fuskarsa sosaiba.

Kallonsa commissioner din yayi Yana jinjina Kai yace"

Me kagani Wanda zaka iya tunawa game dashi Wanda zai taimaka Mana nemosa da kanmu?

Wahalallen numfashi ya sauke Yana hadiye yawunsa dasuka gama gauraya da jinin dukan da akai Masa yace"

Idanuwansa zuwa saman hancinsa sbd Yana sanyeda baqin nose mask.

Ajiyar zuciya commissioner ya sauke tareda Mr Omar Wanda dama Allah Allah yake su samu bayani me kyau dazai bada hujja me ma'ana ya kalli commissioner Yana cewa"

Zansaka aturo Mana Wanda zai Mana sketch yanzun Nan kafin safe nakeson agama inshallah.

Juyawa yayi ya fice commissioner yasa aka maida managern aka rufe Kafin a me sketch din yazo.

Daganan Kai tsaye Maleek Mr Omar yakira ya sanar Masa komai

Shiru MALEEK yayi na 'yan mintuna kafin ya Dan motsa tareda bude Baki yace"

Kaje da kanka gurin tareda wani me sketch din gurinta itama ayo na idanuwan Wanda yakai Mata meriz sai ahada agani Dan nasan mutum dayane sbd tabbatarwa.

Bayan Mr Omar ya tabbatarda anfara zana fuskar Wanda managern gidan jaridar yagani tukuna cikin tsakiyar Daren ya wuce delah Ana fitowa sallar asuba Yana sauka ya wuce Dan aiwatarda dayan aikin.

Qarfe takwas na safe afia ta Isa sashen NURU Kai tsaye bedroom dinta ta nufa har lokacin NURUn na bacci ta tashi ba saidai kasa hakurinda afia tayi yasa ta tada ita ahankali tana Kiran sunanta.

Bude ido NURUn tayi ahankali tana kallon afia dake tsaye tana kallonta cikin kulawa tace"

Sorry na tasheki

Ina tsananin buqatan taimakonki ne Dan Allah.

Da mamaki NURUn ta tashi zaune tana tattare gashinta ta dauki band gefen gadon ta daure gashin tana yaye bargonta tace"

Lafiya dai Ina ko??

Ajiyar zuciya afia ta sauke tareda juyawa ta nufi sofa ta zauna tana kallon NURUn tace"

Ki kimtsa tukuna sai muyi mgnar.

Zuro qafafunta qasa tayi tareda miqewa tsaye sanye cikin kayan bacci riga da wando masu santsi farare tas sun lafe jikinta ta nufi toilet tashige tana waiwayen afia akan tunanin ko wani abun yakuma faruwane.

Brush kawai tayi takasa wanka sbd hankalinta yafara tashi akan tunani da wasi wasin lafiya.

Tana fitowa Palo ta fito inda afia din Takoma ta zauna tana Dan kallon tv sama sama Amma hankalinta nakan yanda NURU zata karbi zancen saidai tasan yanada wuya takasa Mata wannan alfarman tunda aikintane.

Zama NURU tayi kusada afia din tana kallonta dukkanin hankalinta akanta tace"

Gani menene??

Numfashi afia tasake sauke akaro na biyu tana kallon NURUn cikin nutsuwa da nuna damuwarta da mahimmancin da maganar take dashi agurinta tace"

Maganar mum dinace yau nazo neman alfarma dama taimako agurinki,

Kinsan yanda nakeson mahaifiyata dakuma yanda nasamu wannan sassaucin yazo gareta, Dan Allah ko Zaki min alfarmar cika sauran formalities na karbota a matsayinki na lawyer duk da nasan Baki Gama zama cikakkiyar lawyer din ba Amma dai kinada damar zuwa.

Akaro na farko yau Ina roqonki wata alfarma Ina fatan Kuma Zakiyi sbd Ni Dan nasan abinda mum tayi Miki Bata cancanci ki taimaka din ba Amma Kuma Ina roqonki kiyi sbd Ni da farhat.

Tsit NURU tayi tana dauke wuta sbd Bata taba tunanin wannan maganar ba bama ta taba kawo tunanin shiga cikin wannan al'amarin ba gaba daya

Musamman na mum din afian Wanda shigarta kamarba bazai yiyuba sbd ba ita ke ikon kanta ba hakama ita tayaya zata iya zuwa Kai tsaye wannan aikin?¿

Kasa cewa komai tayi ta dago ta kalli afia batamasan me zata ce Mata ba Dan neman alfarma agurinta da afia tayi kamar abune da bazata iya cewa aa ba hakama Kuma tanajin shakkar amincewar sbd batamasan ta Yaya zata sanar da Wanda yake ikonta zancen.

Ganin Shirun NURUn yasa afia shiga damuwa takira sunan NURUn tana cewa"

Bazaki iyaba right???

Zubawa afian ido NURU tayi tana sake shiga tunanin rasa abin cewa ta girgiza Kai ahankali ta bude Baki tace"

Afia Babu alfarmar dazaki roqa gurina nakasa Miki matuqar Bata sabawa ubangiji bace saidai ta Yaya za'a sanarwa dadynki Kuma Kinga.....

Katseta afia tayi da cewa"

Dad dakansa jiya gabanki yabada damar komai gameda case din mum din wannan maganar ta sirrice yanzu idan nace zamu dauko lawyer daga waje then komai zai iya sauyawa

So please NURU ki amince dan Allah dad Bai taba dakatar damuba ko hanamu harkan data shafi karatu bare yanzu aiki Dan Allah ki yarda Ina roqonki.

Dagowa NURU tayi takalli afian tareda Dan sauke ajiyar zuciya tace"

Na amince Amma sai dad dinki ya amince Zan nema izininsa.

Shiru afia tayi tana kallon NURUn tana nazarin abin data fada din saidai tunda ta amince batada zabin daya wuce itama amincewa da bayanin tace"

Thank you.

Miqewa tayi zata fice ta dakata da cewa"

Anjima Imran zai iso inshallah saikuyi mgna.

Ficewa tayi tabar NURUn zaune mamaki na kasheta Jin da Imran zasu tafi kenan.

Faduwa gabanta yayi sbd tunani biyu dasuka shigeta take,

Na farko ta Yaya zata fadawa MALEEK maganar zuwan harda qarin Imran ne abokin aikin,

Ma biyu tayaya zata iya fita daga ita sai Imran bazata iyaba sbd tasan Imran din sai yayi kokarin tado Mata da maganarsu data wuce wadda hakan baya cikin abindata shirya dawowa dashi.

Bangare daya afia nason daureta da jijiyoyin jikinta.

Daqyar ta iya tashi daga Inda afian ta barta ta nufi bedroom tafada toilet jekadi dake jinsu batace komaiba ta juya ta fice daga sashen Kai tsaye ta nemi numbern Mr Omar ta fada Masa komai yace idan yadawo zai sanarda maleek.

Qarfe goma Sha biyu na ranar Mr Omar ya sauka a airport na gizah na dawowarsa Dan yagamo abinda yaje Yi Kuma adaidai lokacin Imran jalal ya sauka a airport din cikin sa'a suka hadu dukkaninsu motar masarauta tazo daukansu shi Mr Omar drivern maleek yazo daukansu shikuma Imran drivern Anneti afia tasaka yazo daukansa.

Kallon kallone yashiga tsakaninsu Mr Omar ya saki wani murmushi Yana miqawa Imran din hannu yana kallonsa yace"

Barka da zuwa Barr Imran jalal and all the best.

Miqa Masa hannu Imran yayi Yana cewa"

Thank you Mr Omar.

Murmushi Mr Omar yasake sakewa Yana Dan kallon gefen Imran din yace"

Kai kadai kazo??

I mean nasan kasan kana buqatan wani lawyern ga aikin.¿

Sai alokacin Imran yasaki murmushi Yana kallon Mr Omar din yace"

Aikina ne Kuma nasan da hakan shiyasa lawyern da nake buqatan muyi aikin tare tana Nan Dama

Fata dai kawai idan zaka iya jimirin ganin hakan.

Wani irin Murmushi me Fadi Mr Omar yasake Yana sake cewa"

Good luck with that too."ya juya ya wuce Yana sake sakin murmushi yashige mota aka jashi sukabar Imran din a tsaye Yana bin motar da kallo kafin ya sauke numfashi me zafi yashiga tasa motar da akazo daukansa suka wuce Suma Yana Jin tamkar zuciyarsa nason karbuwa da qiyayyar Mr Omar sbd koyaushe shine yake shiga hancinsa da kudundune Amma sbd qiyayya bata cikin abindayake Bari Yana shigarsa yasa yake yaqar hakan Yana dannewa sbd ya dauki qiyayya wani aikin wahala da kake dorawa kanka yazo Kuma ya ringa wahalar dakai ka rasa focus da sukunin rayuwa karshe ka wargaza kanka agurin qiyayyar wani.

Kai tsaye dukkaninsu masarauta suka nufo cikin sa'a kusan atare motocinsu suka iso Mr Omar ya wuce Kai tsaye sashen maleek daukeda sketch din dayazo dashi daga delah shikuma Imran afia ce da kanta ta bada umarnin kaisa sashen baqi na musamman kafin ya huta suyi mgn.

##MAMUH#*_Mamuhgee 45_*

*_Mamuhgee 44_*

*LAVENDER RESTAURANT..*

(Palace of mouthwatering food/delicacies)

IDAN KUKAJI GANGAMI DA LABARI, INA MASU SON INDA ZASU SAMU INGATACCEN ABINCI MAI DADI DA LAGWADA? KAI BA ANAN MUKA TSAYA BA, INA SABBIN AMARE? MAMAs, YAYYU? DA KANNEN MU MASU SON KOYAN GIRKUNAN YAN GAYU NA KASAR NIJERIYA DA KETARE?

*TO KU MATSO...! AT LAVENDER RESTAURANT GOTS YOU COVERED. ABINCIN KASASHE DA DAMA MUKE KOYARWA,,COME LETS UPGRADE YOUR FOOD TIME TABLE, MATSO KUSA YAR UWA GA DAMA DA ZAKI CANZA YANAYIN ABINCIN GIDAN KI, KOWA YASAN IYA SARRAFA ABINCI NA TAKA RAWAR GANI A GIDAJEN AURE. KAI KO BUDURWA CE INDE KIN IYA GIRKI ZAKIGA KOWA YANA HABA HABE DAKE..*

*UNCLES, DADDIES, BROTHERS., NEWLYWED HUBBYS..! KU ZO KU YIWA 'YAYAN KU, MATAN KU DA KANNEN KU RAJISTAR WANNAN HARKA TA KOYAN GIRKI..*

_*Lavender catering school zamuyi practical class. zamuyi 30 dishes continental,snack & desserts, traditional dishes, drink. Fee din 40k NE. phone number WhatsApp and call 09080299283 akwai discount na 5% ga mutum uku farko wadanda sukai register aranakun independence 1/10/2021 to 3/10/2021 Nigeria @ 61_*

_*ZA'A FARA CLASSES RANAR 14/10/2021. WATO SHA HUDU GA WATAN OKTOBAR DA MUKA SHIGA YAU._*

_*GIRKE GIRKE GUDA 30😫😩AKAN DUBU 40 KAWAI, HARDA BONUS NA SNACKS, DESSERTS, TRADITIONAL AND MODERN DRINK, GARGALIYA DA ZAMANI□WATA DAYA CHAS ZA'AYI ANA KOYAN GIRKE GIRKEN. _*

_*KU SAKE KARANTA WANNAN BONUS DIN□□RIGIJI GABJI_*

_*Nigeria @ 61 _*

_*COOKING COMPETITION!!!_*

_*from lavender Catering ina masu son koyon girki ga dama zaku shiga gasarmu ta girki bayan kunyi register damu akan 10k,wanda yazo na 1zai shiga ajin mu free hade da wasu prize din na 2 da na 3 kuma zasu bayar da rabin kudine da wasu prize suma saura kuwa zasu ayi musu ragin 5% da wasu prize wannan gasa zamu yita ranar lahadi ne 3/10/21 zamu rufe registration na gasar ranar asabar_*

_*LAVENDER RESTAURANT: NA GARIN KANO, CLASSES DIN AKWAI PRACTICAL AND ONLINE CLASS GA WANDA KE NESA_*

****

Sai yamma lis ta fito suka hadu da Imran din suka nufi sassan Anneti sbd sosai yake girmamata itama duk cikin familyn lailah shine yaron datafi ganin hankalinsa fiyeda kowa har iyayensa shiyasa akwai mutuntawa a tsakaninsu ba laifi tana yaba Masa.

A palon Anneti din na farko suke zaune suna gaisawa tana sake tambayarsa family tareda jajanta Masa abin daya farun na lailah Yana jajanta Mata itama.

Duk maraice NURU na zuwa gurin Anneti din hakama yau Kai tsaye ta nufo sassan cikin sanyi da nutsuwa tareda jekadi tana sanye da doguwa riga dark purple suka qaraso sashen da sallama dauke abakinta tashigo

Dukkaninsu suka dago kowa na zuba Mata ido da nasa tunanin.

Ganin Imran datai shine abu na qarshe da Bata tsammanaba ta sunkuyar dakai tana kokarin juyar da hankalinta daga kansa ta nufi Anneti ta zauna kusada ita tana gaisheta cikin biyayya Kamar ko yaushe

Cikeda kulawa Anneti ta amsa tana miqewa Dan amsa wayar da ake Mata ta shige ciki tana cewa"

Ina zuwa.

Murmushin qarfin hali NURU tasaki tareda Dan waiwayowa ta kalli su afia din a natse tacewa imran"

barka da zuwa.

Boyayyar ajiyar zuciya ya sauke tareda dagowa ya 'dan kalleta ya dauke Kai Yana cewa"

Thank you.

Yi afia tayi Kamar batasan meya taba faruwa tsakaninsuba ta gyara zama tana fuskantar kowannensu tayi musu godiya tana cewa"

Anjima zata karbo takardun daga hannun Mr Omar yabawa imran.

Qala NURU Bata samu cewaba sai Dan yaqen murmushi datayi ta miqe tana cewa"

Zan koma.

Tashi sukayi dukkaninsu suka fito tare afia na kokarin Jan kowannensu da zance sbd su samu sakewa kada itadai asamu matsala agurin fitar mum dinta.

Suna fitowa kofar sashen gabaki daya daidai isowar MALEEK Mr Omar na gefensa Yana Masa wani zancen Wanda kullum baya rasa zance tsakaninsa da MALEEK.

Kwarjininsa da cika musu idon yayi yasa dukkaninsu sauke Kai Banda NURU data dago ta kallesa zuciyarta na narkewa saidai dukkaninsu Babu Wanda yasamu ko kallo daga garesa ya wucesu ya shige saidai abin mamaki Yana shiga din saiga dukkaninsu sun dawo Banda NURU wadda ta nufi sashenta zuciyarta ba dadi.

Ba wani fargaba ko tunanin komai afia ta sanarda dad dinta gameda zuwan Imran da aikin dasuyi din shida NURU tareda amincewar NURUn sai daidai lokacin ya dago ya kalleta da idanuwansa dasuka sata Jin tana neman fara rawar murya.

Ya maida kallonsa kan Imran ahankali kafin ya juyarda kallonsa kan Mr Omar ba wani zance Mr Omar ya kalli Imran yana cewa"

Bismillah muje abaka takardun.

Dan kallon maleek Imran yayi Dan Dole cikin girmamawa yace"

Ka huta lafiya" ya juya yabi kofa da Mr Omar yake nuna Masa suka fice.

Kasa sukuni afia tayi ta juya ta fice da sauri itama tana cewa"

Kafito lafiya dad.

Tana fitowa ta wuce sashen NURU Kai tsaye saidai Koda ta isa NURUn Bata wani cikin walwala sbd cewa tayi kanta na ciwo sai tabarta Dan tasamu ta huta sbd goben.

Juyar da Kai NURU tayi tana Dan rufe idanuwanta kallo daya maleek ya Aiko Mata Yana dawo Mata sbd itakai ta lurada kallon Wanda yasa duk taji Kamar zazzabi na neman kamata ta sauke qaramin numfashi ahankali tareda tashi zaune sbd sallar magriba datayi ta nufi toilet tashiga tayo alwala tana fitowa farhat na shigowa a Sanyaye tace"

Jeki kiyo alwala sweetie muyi sallah ko.

Zaune yake cikin palonsa bayan sallar magriba Yana kallon sketches din guda biyu dasuka nuna mutum dayane da Wanda yakaiwa Yan jaridar da Wanda yabada meriz ya sake kallon idanuwansa

Cikin nutsuwa Mr Omar yace"

Yakoob ne.

Dan waiwayosa maleek yayi cikin kamewa yace"

Ya aika sketches din gurin hukuma tareda bayanin komai da aka hada akan case din gobe ko jibi Inshallah za'a Kai karshen matsalar Ina buqatan komawa Paris.

Dan shiru Mr Omar yayi Yana Dan Sosa tsakiyar kansa kadan cikin Dan tausasa harshe yace"

Maganar shigar mushrah cikin maganar MSS LAILAH akwai hadari sbd abune na sirri dakuma hadari sbd neges nada mutane ko Ina

Akwai hadari zuwanta is too risky Kuma tareda umnn ummn Imran din ma is....

Wani Abu maleek din ya Dan hadiye batareda ya kalli mr Omar din ba yace"

Yaushe ne tafiyar daukan lailan??

Gobe ne Inshallah da karfe Tara na safe yace sbd jirginsu zai tashi karfe goma na safe.

Shiru yayi na wani lokaci kafin ya miqe tsaye ya fuskanci kofar shigewa palonsa na kurya cikin kamewarsa da muryar asalin MALEEK dinsa yace"

Kaji da aikin fitarsu lailan daga qasar ita wannan ko haske waje gobe bazata gani ba zanji wannan.

Dan sunkuyar da Kai mr Omar yayi Yace"

Maleek tariga ta amince da cewar zataje ko Zan sanarda jekadi dokar kada abarta fitowa din sbd kada taje din batareda ankarewar muba....

Kallo daya maleek yayi masa yayi saurin Dan soke Kai Yana cewa"

Nagane zanji da fitarsu lailan gobe

Saida safe ahuta lafiya.

Sidadewa yayi ya fice daga sashen gabaki daya Yana murmushin dayasan na menene shikadai sbd duk duniya ko motsi maleek yayi yasan me yake nufi bare kallonsa wannan wata baiwace da Allah ya hadasu akanta shiyasa Babu me iya sanin sirrin tsakaninsu cikin ransu Allah yasaka musu qaunar junansu Dan dai shi Yana qarqashin maleek din ne yasa maleek nasa kulawan yake a boye shikuwa dama ko ransa zai iya badawa akan maleek.

Yana fitowa gabaki daya daga sashen na maleek ya ciro wayarsa ya Nemo numbern jekadi ya Danna Mata Kira Yana kokarin daidaita kansa Dan cika aikin ubangidansa tana dauka Kai tsaye yace"

Zuwa anjima maleek na buqatan ganinta a rakata sbd tsaro.

Yanayin yanda yayi maganar yasa jekadin amsawa tana satar kallon NURU wadda ke zaune Palo farhat na jikinta suna kallon cartoon din da hankalinta baya wani kai duk da dai tana Dan murmusawa kadan idan akai abin dariya.

Sai da akayi sallar ishai suka tashi sukai sallah suna idarwa tasa aka jera abinci sbd farhat Dan ita Bata wani Jin yunwa tadaisha sabuwar madarar raqumi me dumi wadda kullum ake kawowa safe da dare daga sashen Anneti.

Suna gamawa suka nufi daki farhat ma dakinta ta nufa tayi wanka Da kanta ta shirya cikin kayan bacci tazo dakin NURUn ta haye gado ta kwanta.

Wanka NURUn tayo itama ta fito ta shafa Dan neu oil kadan ajikinta tareda shafa body mist da sprays masu sanyin qamshi ta daure gashinta da band qarami ta dauko rigar bacci me tsantsi tasaka ta nufi gadon zata hau taji knocking din kofar dakin ta juya ahankali tana kallon agogo kafin ta qarasa jikin kofar Dan tasan jekadice ta bude Kai tsaye.

Ajiyar zuciya jekadi ta sauke tareda kallon NURUn tace"

Maleek na buqatan ganinki yanzu.

Shiru tayi tareda kallon jekadin cikin mamaki a natse zatai magana saita fasa ta juya Takoma ta dauko sabuwar free jallabiya ta saka akan rigar baccinta dako bra batada ajiki ta zari qaramin gyalen rigar ta rufe kanta ta kalli farhat tana Dan shafa kanta yace"

Ina zuwa sweetie kinji.

zuro slippers tayi ta fito jekadi na gefenta suka nufi sashen nasa.

Suna Isa har kofar palon kuya jekadi ta rakata ta dakata daganan tareda kallonta cikin nutsuwa tace"

Afito lafiya" ta juya ta fice daga sashen gabaki daya masu tsaron gurin suka sake rufe sashen duka.

Bude kofar tayi a natse tashiga da siririyar sallama bakinta.

Sanyi da qamshin turarensa ne suka cika palon ba motsin komai sai tv dake aiki itama murya can qasa kaman Koda yaushe.

Baya palon Dan Haka ta daga Kai ta kalli kofar shiga bedroom dinsa sai taji shakkar qarasawa ciki Kai tsaye

Ta dauke Kai tana Dan sauke numfashi bugun zuciyarta na sauyawa ta daure ta taka ahankali ta Isa kofar dakin ta Dora hannu ahankali kan handle din kofar daidai ya bude kofar shima.

Tsayawa tayi cak tareda dagowa tana kallon fuskarsa dake fidda sirrin zallar kyawunsa.

Fararen idanuwansa ya zuba Mata Yana kallon fuskarta Batareda kowannensu ya motsaba.

Wani yawu ta hadiye tana sauke kanta qasa sbd Jin yanda suka matse sosai gashi qamshinsa direct yake shiga hancinta kamar yanda nata ahankali yake tashi Yana shigarsa.

Motsawa tayi ahankali zata kauce matsa daga kofar ya riqo hannunta ahankali tareda janta zuwa cikin dakin suka koma tareda rufo kofar ya saki hannunta ya nufi kujerar dake dakin ya zauna tareda daukan wayoyinsa Yana kashewa daya bayan daya batareda ya dagoba ya bude Baki cikin kamewa zaiyi magana ta qaraso gabansa cikin nutsuwa ahankali ta rigasa da cewa"

I'm sorry.

Dagowa yayi ahankali ya kalleta da fararen idanuwansa batareda yace komaiba ta dauke nata idon daga nashi tareda sake bude Baki zatayi magana ya miqe tsaye ya tsaya gabanta har suna Jin dumin numfashin juna ahankali can qasan maqoshi yace"

Uhum Ina sauraronki.

Shiru tayi sbd zuwa lokacin bugun zuciyarta yagama sauyawa ta rintse idanuwa ahankali ta bude tana sake motsowa cikinsa take wani yawu ya wuce Masa da sauri ta maqoshi ya kalleta zaiyi magana ta dago idanuwanta ta kallesa sai ya kasa maganar Ya kalli idanuwanta dake neman cikowa da hawaye ya lumshe ido yanajin mamakin saurin hawayenta dasuka bashi matsala aduk lokacinda yagansu

Ahankali ya daga hannunsa ya kamo qugunta ya qarasa mannota da jikinsa gabaki daya

Ta lumshe idanuwanta hawayen dasuka cikasu suka gangaro kan kumatunta yabisu da kallo yana zura hannuwansa cikin jallabiyarta ya zage zip din dake gaban rigar ta zame gabaki daya ta zube aqasa rigar baccinta ta bayyana ya kalli wuyanta zuwa qirjinta dake sama Yana qasa sbd numfashin datake fitarwa na bugun zuciyarta daya sauya

Kafin ya dago ahankali Ya kalli cikin idonta tasake rufe idanuwan sbd Jin hannuwansa cikin rigarta Yana zamewa

Rigarta na zamewa kasa ta shige jikinsa tareda qanqamesa sbd kunya da mutuwa da jikinta keyi ahankali.

Qanqamesa datayi shiya haifar Masa da tonuwar asirin zuciya da gangar jikinsa ya dago da fuskarta Yana kallonta idanuwanta a rufe taji bakinsa kan kunnenta Saida ya sakar Mata wani numfashi me dumin dayasa kafafunta sarewa ta zube gabaki daya ajikinsa ya riqeta dakyau Yana sauke numfashin kirjinta dake gugarsa dakyau can qasan maqoshi da wata irin murya taji yace"

*_Befik'iri wisit'i nenyi_*

sumewa takusa Yi ajikinsa lokacinda kalmomin suka shiga kunnuwanta

Dukkanin jikinta ya dauki rawa ta bude fararen idanuwanta dasuka sauya take hawaye suka ciko cikinsu ta dago amatuqar sanyi ta kallesa tana kasa yadda da abinda yace saiga hawayenta na gangarowa

Ya Dora hannunsa a inda yasata rinte ido da sauri Yana dauke numfashin kafin tajin saukan bakinsa cikin nata tareda dagata sama gabaki dayanta ya Dora kan gadonsa har lokacin bakinsa na cikin nata wannan karon tun daga Nan tasan yau labarin dabam ne musamman dataji Yana sauyawa bakinsa gurin zuwa nishinsa na daukan sauti ahankali ahankali.

Karfe bakwai na safe afia ta qaraso sashen NURUn cikin shirinta tsaf duk da bada ita za'a ba ita airport zataje ta jirasu acan zatai bankwana da mum dinta.

Kallon farhat dake bacci ita kadai kan makeken gadon NURUn tayi cikin mamaki kafin ta waiwaya kofar toilet da bataji motsin komaiba ta nufa kofar toilet din tai knocking tareda budewa tana leqawa da Alama ma toilet din Babu Wanda yashiga Dan babi digon ruwa a kasa

Ta dawo ta zauna bakin gadon ahankali tareda Dan taba farhat tana tada ita ciki kulawa tana cewa"

Baby tashi lokacin sallah yayi kiyi sallah.

Bude idanuwa farhat tayi cikin bacci tana cewa"

Zanyi tareda Aunt NURU idan tadawo daga gurin daddy.

##MAMUH#*_Mamuhgee 46_*

*LAVENDER RESTAURANT..*

(Palace of mouthwatering food/delicacies)

IDAN KUKAJI GANGAMI DA LABARI, INA MASU SON INDA ZASU SAMU INGATACCEN ABINCI MAI DADI DA LAGWADA? KAI BA ANAN MUKA TSAYA BA, INA SABBIN AMARE? MAMAs, YAYYU? DA KANNEN MU MASU SON KOYAN GIRKUNAN YAN GAYU NA KASAR NIJERIYA DA KETARE?

_*TO KU MATSO...! AT LAVENDER RESTAURANT GOTS YOU COVERED. ABINCIN KASASHE DA DAMA MUKE KOYARWA,,COME LETS UPGRADE YOUR FOOD TIME TABLE, MATSO KUSA YAR UWA GA DAMA DA ZAKI CANZA YANAYIN ABINCIN GIDAN KI, KOWA YASAN IYA SARRAFA ABINCI NA TAKA RAWAR GANI A GIDAJEN AURE. KAI KO BUDURWA CE INDE KIN IYA GIRKI ZAKIGA KOWA YANA HABA HABE DAKE.._*

_*UNCLES, DADDIES, BROTHERS., NEWLYWED HUBBYS..! KU ZO KU YIWA 'YAYAN KU, MATAN KU DA KANNEN KU RAJISTAR WANNAN HARKA TA KOYAN GIRKI.._*

_*Lavender catering school zamuyi practical class. zamuyi 30 dishes continental,snack & desserts, traditional dishes, drink. Fee din 40k NE. phone number WhatsApp and call 09080299283 akwai discount na 5% ga mutum uku farko wadanda sukai register aranakun independence 1/10/2021 to 3/10/2021 Nigeria @ 61_*

_*ZA'A FARA CLASSES RANAR 14/10/2021. WATO SHA HUDU GA WATAN OKTOBAR DA MUKA SHIGA YAU._*

_*GIRKE GIRKE GUDA 30😭😭AKAN DUBU 40 KAWAI, HARDA BONUS NA SNACKS, DESSERTS, TRADITIONAL AND MODERN DRINK, GARGALIYA DA ZAMANI□WATA DAYA CHAS ZA'AYI ANA KOYAN GIRKE GIRKEN. _*

_*KU SAKE KARANTA WANNAN BONUS DIN□□RIGIJI GABJI_*

_*Nigeria @ 61 _*

_*COOKING COMPETITION!!!_*

_*from lavender Catering ina masu son koyon girki ga dama zaku shiga gasarmu ta girki bayan kunyi register damu akan 10k,wanda yazo na 1zai shiga ajin mu free hade da wasu prize din na 2 da na 3 kuma zasu bayar da rabin kudine da wasu prize suma saura kuwa zasu ayi musu ragin 5% da wasu prize wannan gasa zamu yita ranar lahadi ne 3/10/21 zamu rufe registration na gasar ranar asabar_*

_*LAVENDER RESTAURANT: NA GARIN KANO, CLASSES DIN AKWAI PRACTICAL AND ONLINE CLASS GA WANDA KE NESA_*

****

'Dan shiru afia tayi Dan Kamar Bata fahimci abinda farhat din tafada ba ta sake Kiran sunanta tana tadota gabaki daya ta zaunar da ita tana cewa"

Ina aunt dinki tashiga bangantaba.

Mutsitsika idanuwa farhat tayi tareda budewa tana 'yar guntuwar hamma ta baccin yasaketa ta kalli afia din tace"

Bata Nan jiya jekadi tace Daddy na Kiranta tatafi.

Shiru afia tayi tana neman dauke wuta sbd wani dumm dataji kunnuwanta na dauka saidai har lokacin takasa fahimta gwari gwari takeson ayi Mata Dan Haka tasake kallon farhat din tace"

Dad ya Aiko Kiran jiya da dare?

Data tafine haryanxu Bata dawoba kokuwa tadawo yanzu tasake fita??

Saukowa gadon farhat tayi tana cewa"

Bata dawoba."toilet ta nufa ta shigewarta tabar afia daskare agurin tana dulmiya cikin wani irin dogon nazarin tunanin

Shin lafiya dai??kokuma tace menene zaisa NURU kwana gurin dad?kodai wani abin yakuma faruwane Dan ita Sam Bata kawo wani alaqar aure a tsakaninsu sbd sanin yanda auren ya wakana da sanin Koda dad dinta da mum sun rabu har abada NURU sa'ar'yarsace ko kallon Mata baya Mata bare har wani Abu da Mata ke iya yiwa Miji Dan Haka Bata kawo wani tunaninba bayan na wani abun yafaru ita babbar damuwarta yanzu lokaci na tafiyar Mata.

Dagowa tayi tana kallon agogo kafin ta miqe tsaye ta fita zuwa Palo tana duba wayarta cikeda takaicin yanzu ko waya NURUn batada bare ta kirata.

Da jekadi dazata kitchen da Akira gefenta daukeda wani qaton tray da abubuwa akai saidai rufe da wani farin kyalle me adon zaiba ta kallesu ta kalli tray din ta maida kallonta kan jekadi tace"

NURU fa???

Kallonta jekadi tayi cikin Dan Bata nata girman tace"

Batanan saidai ko Zaki dawo zuwa anjima ko gobe.

Anjima ko gobe???"tafada cikin mamaki da Dan daga sauti kafin ta Dora da cewa"

Yanzu nake buqatan ganinta uzurine me girma.

Murmushin manya jekadi tayi cikin ranta kafin ta kalli afian tace"

Uzurin gabanta ya zarce kowane uzuri idan Kuma a matse kike da magana da ita ki Fadi sakonki Zan isar mata.

Da kaina nakeson isarda saqon tana Ina?

Kai tsaye jekadi tace"

Ki nemi maleek zai sadaki da ita.

Wucewa jekadi tayi Akira tabi bayanta suka wuce kitchen Dan fara hadin kayan dasuka zo dasu Wanda musamman na NURUn ne.

Kamar wawuya Haka afia ta tsaya agurin harsuka bace Mata

Take taji tashin hankali na neman shigarta sbd Bata fatar abin dazai kawo matsala akan fitar mum dinta hakama takasa yadda Sam da cewa Wai NURU gurin dad dinta takwana

Shin dama tana zuwane itace Bata saniba kokuwa yaune zuwan na farko?

Sashenta Takoma ta zauna tana sake duba agogo saura AWA daya da mintuna atafi can din

Bata tsaya tunanin komaiba ta daga wayarta ta Nemo numbern dad dinta Kai tsaye ta Danna kiransa.

Kiran duniya tayiwa wayoyinsa Babu me Shiga karshe ta Nemo numbern Mr Omar ta saka Kira tana fatan shi tasamu tasa wayar.

Ringing din dataji wayar tafara yasata sauke ajiyar zuciya tana fatan Yana tareda dad dinta duk da tasan da wuya idan takalli lokacin.

Cikin nutsuwa ya dauka Yana cewa"

Good morning princess.

Morning Mr Omar

Inason magana da dad ga wayoyinsa duka akashe.

Shiru Mr Omar yayi kafin ya Dan gyara murya cikin nutsuwa da basarda zancen yace"

Wayoyinsa suna kashe ne sbd ayyukan da suka Dan Sha kansa kwanakin Nan musamman akan wannan case din kiyi hkr zuwa anjima idan yasamu kansa zai kunna wayoyin Zaki samesa Inshallah.

Cikin damuwa da Dan daga murya tace"

Maganar mum dinace ta Yaya Zan iya Bari zuwa anjima lokaci na tafiya Ina buqatan mgn dashi Akan NURU ne.

Ajiyar zuciya Mr Omar yasaki Yana sake daidaita murya Kai tsaye yace"

Maganar dayan lawyern miss lailah cikin dare anrigada an Samar muku wani lawyern sbd dayar lawyern da kuka dauka banajin zata samu damar zuwan Dan Haka ki nemi Imran jalal Kai tsaye Dan nahadashi da lawyern

Ki huta lafiya princess.

Kashe wayar yayi yabarta zaune tana fadawa cikin sabon tunanin abinda yake faruwa data kasa fahimtar komai amma dai babban abin dayafi Mata komai yanzu maganar mum dintace tunda anbasu lawyer abin yazo Mata da sauqi sauran zancen sayishi daga baya tsakaninta da NURU taji inda tashige.

Ahankali ta Dan motsa tana bude idanuwanta dasukai Mata nauyi sosai sbd rashin bacci da mutuwar da dukkanin jikinta yayi

Akan fuskarsa dake daf da tata idanuwanta suka sauka ta lumshe ido tana budewa ahankali kan bakinsa zuwa dogon hancinsa da idanuwansa dasukafi komai narkar da kuzarinta

Da Alama baccin yakeyi har lokacin be tashiba ta sake motsawa ahankali daidai fararen idanuwansa da gabaki daya suka sauya zuwa wani sabon yanayi na budewa ya zubasu akanta

Ta rufe Bata ahankali tana shigar da kanta jikinsa dake manne da nata

Ya motsa ahankali tareda matso da fuskarsa ya hade hancinsa da nata yana sakar Mata numfashinsa me dumi ya bude Baki yace"

Good morning.

Bude idanuwanta tayi tana kallonsa a kasalance da kunyar gaisuwar saidai gabaki daya bakinta ya mutu murus batada qarfin iya magana

Ganin kallon datake masa kwayar idanuwanta na bayyana sirrin zuciyarta akansa ya riqo hannuwanta Yana sarqewa da nasa suka sauke ajiyar zuciya atare

Ya matso da fuskarsa Yana zura kansa cikin wuyanta dake bayyane ba Kaya ajikinta har lokacin sbd bayan tasamu tayi sallar asuba daqyar ya sake rabata da komai ya qarasa bude hanyarsa dabai Gama budewaba Dan Haka baccin wuya da muguwar kasala ya dauketa sai yanxu data farka

Tanajin dumin lips dinsa cikin wuyanta Yana saukar Mata da wasu irin kisses tareda numfashinsa me dumi da sauti ta lumshe ido tana sake Rena kanta Dan kuwa ita kadai tasan irin tsananin wuyar datasha tsakanin Daren zuwa safiyar sbd ko qafarta daqyar take iya motsata

Tanajin hannuwansa na yawo tsakanin wuyanta zuwa kirjinta zuwa cikinta da bayanta ta qanqamesa cikin tausayin kanta Dan kuwa Babu inda baya ciwo ajikinta musamman kirjinta daganan numfashinsu ya sarke Yana daukan sauti musamman nashi dayake fita sosai Yana fada Mata wasu kalmomi cikin yarensu acikin kunnuwanta wainda suke Bata qwarin jure Masa.

Baccin wahalane yakuma daukanta wannan karon wuyar dataci a bayyane take qarara sbd ko numfashinta ahankali yake fita cikin sanyi datake baccin

Ya kalleta Yana gyara Mata kwanciya ajikinsa tareda shafa fuskarta Yana lumshe ido.

Qarfe goma Sha daya harda mintuna ya farka ya zare jikinsa ahankali daga nata ya gyara Mata rufa Yana shafa lips dinta dasukai kaman sun bushe alamar tsutsan dasuka kwana suna Sha ya saki guntun numfashi tareda Dan rankwafowa yai kissing dinsu ya juya ya shige toilet.

Bayan fitowarsa shiryawa yayi cikin wasu fararen Armani kaftan dasukai matuqar daukan fatarsa dake glowing fuskarsa a kame yafito Yana kunna wayoyinsa Kai tsaye ya nufi palonsa na farko daya ganawa da Mr Omar Yana Isa Mr Omar na palon tsaye Yana waya da commissioner daya tabbatar musu da ankama yakoob Wanda yaqi fadar komai sai cewa komai duk azabar da ake bada.

Kashe wayar Mr Omar yayi ya waiwayo yayiwa MALEEK kallo daya ya Dan sauke kansa cikin 'yar sakewar murya yace"

Barka da fitowa MALEEK.

Zama yayi Yana amsawa tsananin kwarjininsa da qamshinsa na cika palon da idanuwan Mr Omar din

Ya matso ya zuba Masa lemon tea me zafi ya ajiye gabansa Yana Dan fara Masa wasu bayanin sama sama shikuma Yana sauraronsa batareda yace komaiba.

Shigowar jekadi ne daukeda tray na silver me Dan girma daukeda dafaffiyar Nonon raqumi da wani ruwan madaran na musamman sai Dan breakfast Mara nauyi

Sai wata kyakkyawar qaramar jaka dake hannunta na akayan NURUn dake ciki wainda ayau din akai odarsu aka kawosu

Cikin girmamawa tace"

Allah ya qarawa maleek lafiya da walwala

Barka da tashi.

Da Kai ya amsa Yana daukan wayarsa dake ringing ta sudada ta wuce cikin palonsa na gaba ta ajiye komai akan dining ta koma palondasu maleek din suke shima ta zuba Masa breakfast kadan yafara ci Mr Omar naci gaba da koro Masa bayanai.

Sai Sha biyu ta farka ta bude idanuwanta dasukai mugun nauyi fuskarta harta Dan kumbura kadan ta dafa ta tashi zaune tana sauke ajiyar zuciya ahankali tareda rufe ido ta bude tana zuro qafafunta qasa saidai abinda takeji batajin zata iya tashi tsaye.

Shiru tayi agurin zaune tana kokarin miqewa cikin dauriya taji anbude kofar dakin

Bata buqatar dagowa sbd tasan shine yashigo

Jin shiru yasata dagowa daidai isowarsa dab da ita ya rankwafo baice komaiba ya dauketa gaba daya

Tayi qasa da Kai tana rufe idanuwanta yakaita har cikin toilet ya kwantar cikin ruwan dumi ya kalleta tareda shafa gefen fuskarta ya matso da tashi fuskar yakai bakinsa kunnenta ahankali ya furta"

Sorry.

Zamewa tayi ta kallesa ya sake shafa fuskarta ya juya ya fice yabarta da mamakinsa Bata fito daga mamakinba sai ganin jekadi tayi cikin toilet din da sauri ta zame cikin ruwan tana shigarda jikinta ruwan tana rufe ido

Kenan shine yake cewa tayi hkr.

Cikin nutsuwa jekadi ta qaraso gurinta tana cewa"

Ni tamkar uwace karki ji komai magani kawai zanbaki wannan sirrinkine da mijinki Nima sbd baisan yazaiyi mikin bane kisamu kyakkyawar kulawa.

Ruwan zafi ta kunna ruwan da NURUn take ciki suka dauki zafi Sosai

Ta bude wata babbar kwalba cikin kayan data shigo dasu ta zuba cikin ruwan take toilet din yadauki wani qamshi NURU kuwa tanajin ruwan na shigarta ta koina jikinta yafara Dan sakewa Yana Mata wani iri

Jekadi taqara zuba Mata wani abun daban kafin ta dibi ruwan zafin ta zuba cikin wata roba tayi hade hadenta ta ajiye Mata tace"

idan kingama wankan kiyi tsarki da wannan.

Juyawa tayi ta fice sbd tausayin NURUn takeji sbd alamun dasuka nuna tana cikin mawuyacin hali.

Wanka tayi sosai taji dadin jikinta tayi tsarki da ruwan da jekadin ta jiye Mata tun alokacin taji wani irin sauyi Sosai agurin ta Gama tafito ahankali daureda towel ta nufi gaban mirror dinsa ta shafa mansa tareda spray ta dauki kayan data gani an ajiye Mata Wanda da Alama jekadi takawo ta daga kayan tana kallo dukkaninsu Babu me nauyi duk na Shan iska ne

Bata wani damuba sbd jirin datake gani ta saka wata doguwar qaramar riga Mara nauyi tayi drying gashinta daqyar ta 'daure da sabon band fito palon tana tafiya ahankali jekadi dake tsaye dining tana jiranta tai Mata sannu tareda ja Mata kujera ta zauna tana gabatar Mata da abubuwan dazata fara Sha kafin komai.

Daqyar ta daure Tasha duka ko abincin Bata iya tsayawa taci ba Takoma daki ta kwanta

Jekadi ta tattare kayan ta fice dasu

tana fita Mr Omar ya sulale yabi bayanta Dan bawa maleek lokacin hutawa

Ya miqe ya koma ciki Yana duba lokacin sallah da yayi.

##MAMUH#*_Mamuhgee 47_*

Bacci takeyi har lokacinda ya Shigo din,ya kalleta tareda sauke boyayyar ajiyar zuciya ya juya ya nufi toilet yayo alwala yazo ya fice batareda ya tada ita ba Dan baccin Yana Bata nutsuwa da damar yanayinda takeji.

Yana fita bada jimawaba ta farka ahankali ta tashi zaune itama tayo alwala tazo tayi sallar Takoma ta kwanta tanajin zazzabin datake ji na qara shigarta ta lumshe ido tana sake shigewa bargo idanuwanta a rufe.

Qarfe goma aka Isa da lailah airport acikin wata sirrantacciyar mota

Lokacin afia tafi mintuna ashirin agurin tana jiran isowarsu Dan Haka tana ganinsu ta fiddo doguwar jallabiya da Dan qaramin mayafi da goggles datazowa da mum din Tata dashi ta nufi motarsu itama tata fuskar Bata bayyanataba yanda za'a gane itace ta bude motarsu ta shiga baya inda mum dinta ke zaune tana kakkama jikinta tayi wani duhu cikin kwana biyu ga wani irin tsamin dauda da wahala na tashi ajikinta

Cikin tsananin baqin cikin ganinta Haka da kaunar mahaifiyarta me qarfi afia ta rungumeta gabaki daya tana cewa"

Mum.

Zarewa Lailah tayi ta kurawa afia ido idanuwanta na cikowa da hawayen tsananin baqin ciki da dumuwa tarema da tsoron halinda rayuwarta tashiga kokuma ma Wanda tariga tashiga,

Ahankali ta bude Bakinta dake rawa wani tsamin Baki ya feso yacika motar Amma afia ita Sam batama jisa sbd Babu abinda uwarta zata zama ta gujeta da rawar murya tana hawaye tace"

Afia,afia my baby,afia my little princess I'm sorry baby ki yafewa mum dinki Amma ki yarda Dani bantaba aikata kisa ba Kuma bazan taba aikatawaba...ban aikata ba...bazan taba iya aikatawaba...ban aikataba...banyiba...

Riqota afia keyi tana cewa"

Mum mum na yarda Baki aikataba

Mum na yarda

Na yarda mum".ganin mum din takasa daina fadar Bata aikataba cikin firgici Kamar lokacin abin ke faruwa yasa afia rikicewa tana korarin kwantar Mata da hankali cikin kulawa hankalinta na neman tashi sbd ganin alamun kaman mum din har lokacin tana cikin shock saidai Kuma....

Imran ne cikin hali na damuwa daya shiga akan lailan tun lokacinda Mr Omar yayi Masa bayanin komai gameda Dan tabuwa da kan lailan yayi sbd Shiga hali na shock lafiya zata ringa komai Kamar yanda take sai dai idan ta tuno abindaya faru na kisan abin zai dawo Mata zata fara fizgewa tana fadar ba ita tayiba cikin tsananin tsoro da firgici,

Shi kansa bazaiso afia tasaniba sbd hankalinta zai tashi yakoma kan kula da neman lafiyar mum dinta bazata taba maida hankali kan karatuntaba Kuma Dan Haka shima ya shirya kula da al'amarin bazai Bari tasaniba yanzu sai tagama kammala karatunta tsaf yanama fatan zuwa lokacin lailan tasamu lafiya Dan Haka shima ya yanke shawaran komawa Vegas gabaki daya zai zauna da lailah Dan nema Mata lafiya ta dawo daidai ta gyara rayuwarta ta ingantata yanzu kan tunani da hanyar dazata bullar da ita sbd Lailah tamkar uwa ya dauketa Dan kuwa itace wadda tafi sonsa aduniya bayan iyayensa sbd itanema yake Paris baibi iyayensaba Koda tabar maleek dasu afia Basu rabu ba shida ita Kuma sbd itane yake tareda maleek Yana aiki a qarqashinsa farko sbd ya kula dasu farhat dasuka shaqu.

Ajiyar zuciya ya sauke ahankali tareda fitowa ya zagayo yashigo bayan ya zauna dayan gefen lailan suka sanyata tsakiyansu ya dago ya kalli afia data fara shiga firgici cikin kulawa da kwantar Mata da hankali yace"

Tana cikin damuwar abin daya faru sbd case na zargin kisa wani abune da bakowa ne zai iya daukaba

Dole zata shiga wannan halin musamman yanzu data fito Kuma taganta agabanki Dole zataji wannan damuwar da shauqin son sanar dake ba halinta bane.

Hawayene suka gangarowa afia ta rungumeta tana sakin siririn kukan tausayin mum dinta ta dago tana kallonta tace"

Mum Inshallah komai yariga ya wuce bazai sake dawowaba

Ki yarda da wannan wata jarabawace Allah yayi Miki danki gyara Kuma Inshallah nasan kin gyara mum kimin alqawarin bazaki sake zuwa gizah ba sbd bakida abinda yarage Miki anan sai tarihi.

Kallon afia kawai lailah keyi da idanuwanta dasukai jajir tanajin radadin abubuwa da dama data rasa arayuwarta sanadin son zuciya da son Rai,

Ta rasa MALEEK namijin da bazata taba samun kamarsa ba a fagen komai Dan kuwa ya nuna Mata so da kauna da gata da kulawa da komaima Amma duk ta watsar ta tsallake a tunaninta zai zauna dakon jiranta,

Ta rasa Farhat dinta yarinyar da Bata morewa komai na soyayya ko kulawar mahaifiyaba da shaquwa Dan kuwa tasan NURU tariga tashiga ran farhat ta yanda bazata iya rabuwa da itaba ko yiwa wani kallon uwa idan ba NURUn ba,

Ta rasa darajarta,sunanta,mulkinta, dukiya da career dintama gabaki daya

Afia ce kawai abindake gareta yanzu sai Imran datasan har abada shima bazai gujetaba adaidai yanzu datafi buqatan masoyanta atareda ita.

Kama hannun afia tayi ahankali hawayenta suka gangaro kan fuskarta ta kalli afian tareda gyada Mata Kai tace"

Nayi alqawarin Inshallah bazan qara zuwa gizah ba sbd Nima na tabbatarda banida sauran komai anan sai tarihi Wanda bana alkhairi ba Dan kowa zai ringa tunoni amatsayin wadda tayi kisa labarinta ya Bata.

Sake karyewa zuciyar afia tayi da tausayin mum dinta ta yanda lokaci daya ta rasa komai Kuma tana fatan zatai tawakalli ta karbi hakan.

Kayan data shigo Mata dasu ta Sanya Mata tareda rufe Mata fuska ta Sanya Mata goggles din ta bude motar suka fito dukkaninsu ta sake damke hannun mum din cikin kulawa da qauna ta tsakanin 'da da mahaifi tace"

Mum ki kula da kanki Zan ringa kawo Miki ziyara lokaci lokaci kinji¿

Ajiyar zuciya lailah tayi tareda kallon afian akaro na farko rayuwarta tace"

Allah yayiwa rayuwarki albarka afia

Allah yabaki 'yayan dazasu San darajarki irin Haka da Miki biyayya.

Amin tace ahankali tana dagowa ta kalli Imran tace"

Mum na hannunka.

Guntun murmushi ya saki Yana gyada Kai yace"

tana hannu mekyau.

Murmushin yaqe tayi tana cewa"

Thank you.

Kama hannun lailan dake waiwayen afia tana daga Mata hannu yayi suka wuce itama afian tana musu har suka bace Mata ta saki numfashi a hankali tanajin nutsuwa ta juya ta fada motar da kanta ta jawo ta tada taja tabar airport din.

Ko data koma sashenta ta nufa sai alokacin tasamu nutsuwar cin abincin data manta rabon dataci

Taci ta koshi ta miqe ta wuce bedroom dinta tayi sallar azahar ta kwanta Dan tasamu baccin dazai qarasa wargaza damuwarta Dan kuwa dukkanin damuwarta ta yaye takeji.

NURU zazzabi yakamata sosai Wanda ya Hana musu bacci da daddare daga ita har maleek din sbd sosai jikinta yayi zafi tana kwance cikin jikinsa Yana rage Mata zafin jikin da nasa Dan kuwa yanajin yanda dumin jikin nata ke shigarsa Yana saukan Masa da kasalar sake shigar da ita jikin nasa itakuma tana lafe tana sauke numfashi ahankali cikin sanyi.

Kallonta yayi cikin Dan qaramin hasken dakin Ya shafa bayanta ahankali Yana sake ce mata"

Azinalehu (Sorry) cikin kunnenta da wata sirrantacciyar muryarsa da tsakanin jiya zuwa yau tasanta.

Ahaka yayita lallabata suka samu bayan sallar asuba tasamu bacci ya dauketa me nauyi sai alokacin yasamu nutsuwar kansa ya gyara Mata kwanciya tareda fitowa Palo sanyeda milk jallabiya me taushi ya zauna Yana daukan wayoyinsa ya kunna sbd yau yakeson Kai qarshen matsalar komai tunda sungama hada dukkanin shedodinsu dasuka tabbatar musu da zarginsu Akan Wanda suke zargi

Yana buqatan komawa Paris kodan rashin lafiyan Nan daya sameta.

Mr Omar yakira Kai tsaye yace"

A bayyanarda duka shedu akan yakoob a cikin kotu yau.

Cikin girmamawa Mr Omar yace"

Maleek haryanxu Yana maganar son ganin 'dansa Kuma idan aka bayyanar a kotu cewan 'dansa ne ya mutu zai iya bayyana komai a gaban kotu Wanda zai taba gizah da Kuma Anneti sbd al'amarin zaizo Mata da tashin hankali tunda Bata taba tsammanin hakan ba daga Wanda take aure

Kana ganin yakamata mu fitar da zancen duka a kotu?

Yan media zasu yada abin fiyeda komai ta yanda zai Yi Muni.

Shiru maleek yayi na wasu mintuna kafin yace"

Yanada damar yasan mutuwar dansa saidai baida damar fadar komai bayan abubuwan daya aikata da wannan za'a yanke Masa hukunci basai anbari yafada komaiba bayan wannan.....

Shiru yayi Yana kokarin daure abin dayake ji a zuciyarsa dasuka bayyana a idanuwansa yaci gaba da cewa"

Neges Kuma sbd daraja ta auren Anneti zanji da matsalarsa ta cikin gida batareda duniya tasan abin daya aikataba sauran haqqin Rai dake kansa Kuma tsakaninsa da ubangijinsane.

Cikin yanayi na sanyi shima Mr Omar yace"

Allah ya kyauta ya sake tsare imaninmu

Allah Kuma yaqara maka tsarkin zuciya.

Ba Haka suka so ba duk su dukan Amma Kuma wani lokacin kanayin abinda shine zaman lafiyar kowa da Hana fitina.

Lokacinda aka tafi da yakoob har mortuary aka jawo gawa tareda yaye Masa yaga gawar 'dansa amed datai fari tas sbd ajiya da sanyi.

Sarewa qafafuwansa sukai sbd firgicin ba zata daya fizgesa lokaci daya da wannan mugun ganin dayayi

Cikin tashin hankali ya zube gaban gawar Yana ihun Kiran sunan"

Amed Amed Inidēti ibakíhìni¿

Yaushe wannan mummunan Abu yasameka batareda nasaniba?

Amed katafi kabarni Banda kowa sai kai.

Dagowa yayi cikin ficewa hayyaci da tashin hankali ya kalli Mr Omar Yana cewa"

Meyasa???meyasa??

Ta yaya?

Yaushe kuka kashesa?

Meya muku?

A Daren ranar daya tafi aikin neges yamun saqon cewa Yana lafiya tafiyan gaggawa yayi.....ko shekaran jiya yamun sakon Yana lafiya Dana kira..yaushe kuka kashesa.....

Kukan tashin hankalin masifa yakeyi sbd sanin tsaf wannan umarnin maleek ne ya sake gangaro da hawayen baqin ciki jikinsa na daukan rawar Shiga tashin hankalin rashin tsammani na wannan afkuwar dabai taba kawowa aransaba ya rasa dansa kwalli kwal Wanda duk suke wannan fafutukar rayuwar dansu tsira su Tara abin kansu su gudu wani gurin su Gina rayuwa.

##MAMUH#

KUYI MANAGE YAU INADA UZURI DAN ALLAH.[10/10, 7:27 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 48_*

Kallon yakoob Mr Omar yayi Yana gyara tsayuwa yace"

Allah ya yafe Masa kurakurensa tareda Kai mahaifinsa daka dorasa akan irin wannan rayuwar da batada hanyar bullewa ko a duniya ko agurin ubanginka,

Son Rai da bin zuciya qarshensa baida Dadi yakoob Amma tunda kune kuka zabi hakan hakan shine daidanku,

Babban kuskuren daka aikata yakoob shine sako 'danka da baida kwarewa acikin wannan harkar dakai ka Jima da dadewa acikinta Dan kuwa gashi kuskurensa yakaisa ga Haka kaima yakaika ga hakan.

Allurar meriz ce ta kashesa kaman yanda kukai amfani da ita Dan kashe tsohon NEGES mahaifin maleek Kuma kukaso kashesa da ita,

Kun aikashi kashe padima saidai kun manta cewan a sashen maleek ne take

Kuma a sashen Babu wani lungu da Babu camera a maqale Wanda idonku da zuciyarku sun rufe da aikata hakan kuka saka Amed disconnecting dinsu Wanda ko karatun addini bayadashi bare na zamani Dan Haka ta Yaya kuke tunanin zainiya ciresu.

Ranarda muka samu labarin zuwan lailah gizah muka tabbatarda akwai dalilin zuwan nata Wanda anyi kirantane Dan ayi amfani da ita hakan yasa muka sauya tunani ta hanyar Dena shayarda padima meriz sbd ga hanyar sauki tazo Mana,

Tunda neges yayi magana da lailah tafara bibiyar jekadi Wanda jekadi tagane hakan ta sanar Mana daga lokacin mukasan meyake faruwa har lokacinda muka tabbatarda amed na bibiyar lailah itama bamui wani motsiba muka barku Dan ku aiwatar da naku Shirin dazai bamu tamu damar.

Kaf gizah Babu Wanda yasan da padima na cikin masarautar shiyasa muka kyaleku Dan munsan Dole bazaku barta ba duk da batasan ainihin waye yasakata aikin daya sakata ba ahaka rashin nasararku yakaiku aika amed kashe padima wadda taji sauki da kanta zata iya Kare komai kuma a Daren ranar jekadi ta miqa Mata allurar meriz a hannunta ta sanarda ita duk Wanda ya shigo kawo Mata farmaki ta tabbatarda ta kwaci kanta da allurar Wanda hakan zai fidda ita daga wannan rigimar gabaki daya har abada.

Padima na son ranta fiyeda masoyinta amed Wanda shima yakeson dukiya fiyeda rayuwarta Dan Haka a Daren ranar abindaya faru shine bayan yaja lailah da dubara zuwa gurin Dan kisan ya hau kanta mun gani Kuma mun sanarda jekadi komai kafin isowarsu gurin Dan Haka jekadi tasake nanatawa padima tana sane ya fito lailah ta doketa saidai bamuyi tsammanin amed yaqara doke jekadin ba yasamu ya qarasa dakin ya bige lailah ta hanyar kwada Mata katako akai Wanda ganinsa yasa padima shiga tashin hankali saidai Bata Bari tsoronta yabarta barin amed yasamu sa'ar kashetaba tayi amfani da matsayinta na mace ta nuna Masa kanta amatsayin su Raya darensu na qarshe kwadayin Zina yajasa ga rasa ransa batareda yasamu abinda yake kwadayinba.

Babu Wanda yasan padima na kasar tayaya Yan jaridar suka San waye aka kashe bayan Babu Wanda yaga gawar da idanuwansa wannan shine babban kuskurenku na biyu daya kawo karshenki batareda ansha wuyar hakan ba,

Padima ta kashe amed sbd Kare Kai itama Allah yabata nata sakamakon ta hanyar rasa cikakken hankalinta kamar lailah Da Haka kowa zai girbi nasa aikin.

Allah ya tsare Mana imaninmu yabamu kariya daga mutane kamarku Wanda suka Tara arziki ta hanyar kisa da miyagun ayyuka gashinan dukiyar Zaki tafi ku barta abawa mutane suna Kuma tsine muku.

Juyawa yayi ya fice yabar yakoob din tsaye cikin rashin sanin makamar tunanin Yi sbd dukkanin gangar jikinsa da jininsa sun tsaya cak Babu abinda yake motsi ajikinsa bayan zuciyarsa dake bugawa ahaka aka jasa Yana tangadi aka fice dashi

Take 'yan jarida aka sakar musu labarin suka fara yadawa cewan

Yakoob amintaccen bawan neges ne ya kashe tsohon NEGES na gizah

Take aka bayyanarda shedu dasuka hada da garin meriz dake ciki sarkar da padima ta taba boyewa da aka samu a sashensa gurin bincike.

Hankalin jama'ar gizah ya tashi tareda girgiza matuqa sbd kishin kishin fara zargin NEGES da akai Wanda yasa akai gaggawar yankewa yakoob hukuncin kisa ta hanyar cire kansa sbd kada ragewa fitinar tsayi

Amma duk da hakan ba a daina bayyanarda zargin NEGES ba Wanda yasashi kasa fitowa sbd tsananin kunyar kansa da baqin ciki me nauyi daya lullubesa sbd Kai tsaye ko an boye laifinsa saidai yasa jama'a yin shiru Amma wannan zargin da laifinma gabaki daya bazai rufu ba musamman da kaleeb da maleek sukai shiru sunki saka Baki a maganar sai hakan yasake bawa jama'a kwarin gwiwa aka fara kishin kishin sauke neges jama'a da jinin sarautar gizah da 'yan delah gabaki daya kowa yafito ya nuna sha'awarsa ta sauyin neges sbd kobabu saka hannunsa zamtowar bawansane ya aikata hakan to tabbas hakan ya shafesa Dan Haka gabaki daya kusan ya rasa girmansa da mutuncinsa a idon jama'a

Musamman Anneti da yakejin Kamar bazai iya hada idanuwa da itaba sbd girman kunyar abindaya aikata Wanda yasan itama yagama fahimtar komai saidai kawai tayi shiru sbd wani abin basai kafadaba Allah ya kyauta kawai yafi maka saukin fada

Da wannan ya kebe kansa da kansa a sashe dabam bayan ya fitar da wasiqar sauka mulki da kansa ya aika har delah gurin kaleeb Wanda har lokacin yaqi cewa komai bare maleek daya fara Shirin barin qasar bayan ya bayarda sunan Mohan YONAS (autan kaleeb) amatsayin Wanda za'a nada sabon NEGES na riqon kwarya kafin lokacinda zai karba Dan haryanzu Yana buqatan wani Dan lokaci kadan kafin yadawo gabaki daya ya karba gizah din.

******

Zazzabinta yayi sauki sosai ba laifi Dan kuwa Daren tasamu tayi bacci sosai sbd wani magani da jekadi ta kawo Mata Dan Haka gari na wayewa tun karfe shida da mintuna ta fito cikin doguwar jallabiya data rufeta koina ta nufi sashenta tana Isa ta wuce bedroom dinta tashige tana sauke numfashi ahankali kafin ta dago ta kalli farhat dake kwance kan gadonta tana bacci cikin nutsuwa

Ta qarasa gadon ta zauna tana kallonta tasaki murmushi ahankali tace"

Sweetie nayi missing naki da surutunki sosai.

Miqewa tayi ta zare rigar jikinta ta jefa cikin wardrobe ta nufi toilet ta shige.

Kodata fito komawa gadon tayi ta haye ta kwanta gefen farhat ta gyara musu rufa Takoma bacci sbd baigama isartaba.

Qarfe tara ta farka lokacin har farhat ta Jima da farkawa ta bude idanuwanta ahankali tana kallon farhat dake Kiran sunanta cikin murna da farin ciki tace"

Aunt NURU yaushe kika dawo?

Tashi zaune tayi tana gyara gashinta da murmushi akan fuskarta tace"

Sweetie na barci nadawo

Ya kike?

Fadawa jikinta tayi ta rungumeta tana cewa"

Next time idan zakije tare Dani Zaki Zan biki kinji Aunt NURU.

Wani irin Murmushi ne ya saukowa NURUn ta kalli hancin farhat din zuwa bakinta dasuke Zak Zak Dana dadynta saita sake sakin murmushi tana saukowa gadon tace"

Kinyi brush?

Biyota tayi tana cewa"

Eh nayi nace next time zakije Dani??

Tsayawa tayi tareda juyowa ta kalli farhat din ta kamo fuskarta taja hancinta ahankali tana murmushi tace"

Wannan hancin Ina sonsa sosai kaman yanda nake son sweetie dan haka kidainama tambayan idan zanje wani guri ba dakeba ok¿.

Cikin murna tace"

I love you too lewa.

Knocking kofa akai ahankali tareda bude kofar aka shigo

NURU ta dago tana waiwayowa kofar sukai ido biyu da afia dake kallonta da dukkanin hankalinta tana nazarin NURUn da akace batada lafiya saidai bataga alamar ciwo atareda NURUn ba jikinta ba inda ya nuna alamar akwai ciwo tareda ita ta karaso ahankali cikin 'yar kulawa da alamar tambayarta tace"

Jekadi tace bakida lafiya da fatan dai ba wani serious ciwo bane ko??

Murmushi NURU tasake tana matsowa gaban afia din tace"

Naji sauki kawai gajiya ce da rashin isashen bacci Amma yanzu lafiyana kalau.

Kallon cikin idanuwanta afia tayi tana kokarin karanto idan da akwai ciwon atareda NURUn tace"

Mezaisa ki kasa samun isashen bacci bayan kina samin hutu sosai bakida aikin komai a gabanki....

Aiki dad dinku yabani Wanda duk ya kawo hakan yanzu dai inason Baki hakuri akan rashin samun damar zuwana gurin mum dinki I am really really sorry for that Kuma Ina fatan komai yatafi yanda ake fata?

Ajiyar zuciya afia ta sauke tana qarasawa bakin gadon dakin ta zauna tana cewa"

Komai yatafi yanda akeso mum Dina tana Las Vegas tareda Imran Wanda yakoma can yanzu da zama da aiki sbd su manta rayuwarsu ta baya su fara sabuwar rayuwa Mara damuwa da Danasani.

Numfashi NURU ta sauke cikin ahankali tareda ajiyar zuciya tana kallon Afia da taushin murya tace"

Ina musu fatan kyakkyawar rayuwa me Dadi da amfani.

Thank you afia tace tana kallon fuskar NURUn data sauya Mata gabaki daya.

Wanka NURU tashiga ta fito cikin nutsuwa ta shirya cikin doguwar riga golden me sequence ajiki suka zauna dukkaninsu su ukun anan sashenta sukai breakfast tare suna gamawa suka dawo Palo suka zauna NURU na Shirin zuwa gurin Anneti afia ta kalleta tareda dawowa gefenta ta zauna cikin nutsuwa ta kalleta tana tattaro abinda zata fada Mata tace"

Shin kinsan case din kisan da mum take ciki padima ce wadda ake cewa ta kashe.....

Wani irin kallo NURUn juyo tanayiwa afia din da dukkanin fararen idanuwanta.

Wata ajiyar zuciyar afia takuma saki tana dafa hannun NURUn tace"

Padima ce wadda dukkanin labarai da duniya ta shedarda an kashe....

Hawayen dasuka ciko fararen idanuwanta dasuka koma ja Nan take suka gangaro kan fuskarta ta sake kallon afian da kyau tana kasa gasgata zancen sbd bazai yiyuba babban zance irin wannan a boye Mata

'yar uwarta jininta aka kashe ace Bata saniba sai yanzu bayan wadda tayi kisan har ansaketa ta tafi Kuma maleek na sane da hakan,wane hali iyayenta suke ciki gameda wannan mummunan al'amarin na rasa padima itakuma Bata tareda dasu a lokaci irin wannan miqewa tayi zuciyarta da idanuwanta na rufewa da wani irin yanayi Mara Dadi da damuwa

Afia tayi saurin riqota tana Miqewa tsaye cikin nutsuwa da kulawa tace"

NURU ki kwantar da hankalinki anyi bincike angano komai da cewan ba padima bace kawai yan media ne suka juya zancen sbd basusan ainihin wayeba aka kashe angano komai yanxu tareda gano Wanda sukeda hannu a komai har kisan tsohon NEGES wato mahaifin dad dinmu komai ya wuce yanzu Inshallah...

Girgiza Kai tafarayi ahankali hawayenta na tsananta gudu cikin wani irin yanayi na toshewar Kai tace"

Bani wayanki inason Kiran abal Dina Ina buqatan Jin halinda suke ciki,

Ina buqatan magana da padima

Mezaisa padima ta zauna Nan har irin wannan Abu yasameta,

Ni gabaki daya ban fahimta ba,abal nakeson magana dashi yanzun Nan.....

Cikin sanyi da son kwantar Mata da hankali afia ta miqa Mata wayarta tana cewa"

Dan Allah ki nutsu kada ki dagawa su abal din naki hankali idan har Basu saniba, ki tambayeshi ta yanda bazaki daga hankalinsu ba muji idan padiman na taredasu.

Bata tsaya sauraren sauran bayanin afia ba ta hau saka numbobin abal dinta ta Danna Masa Kira zuciyarta na rawa.

Kamar zata tsinke saigashi ya daga cikin nutsuwa da kwanciyar hankali yayi sallamar data Sanya NURU saurin riqe numfashinta tana seta muryarta tace"

Abal.

Jin muryar NURU yasa abal din tashi zaune daga kishin giden dayake Yana kallo a tv cikeda kewarta da kaunar 'yarsa yace"

NURU kece?

Kina lafiya?

Ya kike?

Yaya maleek da yaransa?

Shiru tayi zuciyarta na sake bugawa ahankali muryarta na rawa tace"

Abal Ina padima?

##MAMUH#

[10/10, 7:27 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 49_*

Shiru yayi Yana kallon padima data lallabo ta tsaya gefensa Jin sunan NURUn daya ambata tana kallonsa da idanuwanta dasukai wasu iri kaman me jiran sammaci ya Dan gyara zama Yana sake murya cikin farin cikin Jin NURUn yace"

NURU me padima zatai Miki??

Shiru tayi sbd jikinta daya fara sanyaya ta bude Baki da qyar tace"

Abal labarin rasuwarta nake samu yanzu duk tsawon lokacin Nan bansan meyake faruwaba Ina matsayin 'yar uwa Kuma 'ya acikinku

Dan Allah abal ka sanar Dani komai Kuma idan padima na Nan inason jinta ko yayane..

Wasu hawayen takaicine da sanyin jiki suka gangarowa ammynsu Jin abinda NURU ke fada

Abal kuwa nutsar da murya yayi cikin kwantarwa da NURUn hankali da murya Kai tsaye ta matsayinsa na mahaifinsu su duka yace"

NURU dagani har ammynku da meryam munanan lafiya cikin kwanciyar hankali da nutsuwa sakamakon Miji na gari me adalci da Allah yabaki,

Muna cikin masarautar delah a kebe cikin walwala da wadata tareda ni'imar duniya,

Saidai har gobe da kullum zuciyata takasa samun kwanciyar hankali na uban daya haifi 'yar da Babu Allah ko miskala zarratin acikin ranta face zuciya irinta kafiran farko da qyashi da hassada tareda taurin Rai yagama cikata,

Padima na nan da ranta saidai banajin tanada sauran qimar da Zaki cigaba da kiranta 'yar uwarki sbd ta nunawa duniya cewan Babu qauna ta jini a tsakninku har abada

Muda muka haifeta Dole zamu zauna da ita Amma ke Kam ba Dole sbd ta wuce iyakarta....

Tsananin sanyi jikinta yayi da kalaman abal dinsu ta sulale ta zauna bakin kujera ta zauna cikin sanyi da sagewa tace"

Abal meya faru?

Me padima tayi wannan karon?

Kai tsaye yace"

Padima taje gidanki da niyar rusa kyakkyawar rayuwar da Allah yabaki ta hanyar niyarta ta kashe mijinki Wanda tabawa gubar meriz yasha wadda Allah ne kawai yayi da kwanansa agaba da babushi Kuma niyarta shine su maqala Miki wannan sharrin da ita da mahaifin amed dama amed din....

Innalillahi wainna ilaihirrajiun

Innalillahi wainna ilaihirrajiun"

Shine kawai abinda tasamu bakinta yake iya furtawa ahankali idanuwanta na bushewa sbd tsananin firgici da tsoron maganar da abal din yafada cikin rawar murya tace"

Abal abawa padiman wayan Dan Allah...

Shiru yayi Yana shakkar hakan sbd har cikin ransa baya buqatan alaqar NURU da padiman yanzu ya dago ya kalli padiman datai tsamo tsamo da idanuwanta dasuka Gama jemewa ya miqa Mata wayar.

Karba tayi ta Dora akan kunnenta cikin sanyi tace"

NURU

Dakakkiyar ajiyar zuciyar karfin hali NURU tasake cikin kasa gasgatawa tace"

Padima menene abindaya faru???

Numfashi padiman ta sauke cikin muzantuwa da wata irin kunya da wulaqanta saidai Babu yanda zatayi bayan fadan gaskia ta bude Baki ahankali tace"

Dukkanin abinda abal yafada hakane,

Banida ciwon komai nai Miki karya naje gurinki da burina na dabam Wanda yakaini ga sawa maleek garin meriz Wanda zai kawo karshen rayuwarsa saidai hakan be faruba suka gane nice na aikata hakan

Sukaso hukuntani saidai Kuma Basu kaiga yin hakanba amed sukaso kasheni Dan boye tonuwar asirin dayasa na kashesa batareda nasan Yaya zanyiba

Maleek ya zabi da a boye Miki komaine sbd gudun shigarki damuwa....

Zubewa qasa tayi duk da NURUn Bata gabanta cikin tsananin damuwa da kanta daya fara juyawa alamar zata birkice tace"

NURU ki yafemun kinji

Kisa maleek ya yafemun kinji

Kisa abal ma ya yafemun kinji

Kisa ammy ma ta yafemun kinji

Bani nakashe amed ba shine ya kasheni na gudu na boye bayan maleek kinji,

NURU kisa mutanen gizah ma kowa ya yafemun kinji

Nima kisa na yafewa padima kinji,

Padima Tama lalata rayuwarta gashi yanzu takoma Kamar Mara hankali nake gani

NURU kinyafemun ko???.....

Shiru NURU tayi dukkanin jikinta na sake yin sanyi sbd daga maganganun padiman tagama gane kanta ya juye wannan rayuwar dame tayi Kama?

Wannan wace irin masiface me mummunan karshe Wanda zaikai bawa ga irin wannan makomar gashi padima da kyanta da cikar zatinta Takoma kayan kwankwani saika kwankwasa kaji sauti.

Cikin sanyin jiki da muryarta data toshe tace"

Na yafe Miki padima Allah ma ya yafe Miki yabaki lafiya idan kinada rabon warkewa.

Karban wayar abal yayi Yana cewa amin dukkaninsu jikinsu a Sanyaye sbd idan abin ya juyo padiman nada tausayi wani lokacin sbd lafiyayyan budurwa takoma saidai zaman gida sbd Babu Wanda zai iya aurenta ahaka saina Allah musamman abubuwan nata sunyi yawa,

Ga rashin budurci,ga mummunan zuciya data kaita ga hakan ga na karshe rashin hankali daya shigo.

Kallon meryam ammy tayi tana cewa"

Rakata daki ki zaunar da ita har abin ya lafa ta 'dan dawo daidai.

Kallonta Meryam tayi tana kamo hannunta ta jata itakuma tabita tana 'yan maganganunta qasa qasa batareda kowa yamaji me take fadaba sbd sanin batada zance saina a yafe Mata ba ita takashe amed ba amed ne ya kasheta.

NURU najinsu tayi shiru tana sake Jin al'amarin har cikin ranta dukkanin gabobinta sun saki takasa cewa komai

Abal cikin sanyi shima yace"

Maleek da kansa yasa aka kawomu Nan Dan mu samu sauyin rayuwa tareda boyewa duniya abinda padiman tayi Wanda bazamu taba daina gode Masa akan hakan ba

Ya allah yakara rufa Masa asiri duniya da lahira yayiwa rayuwarki taredashi albarka da zuriar dazaku samu agaba.

Amin ta furta daqyar sbd toshewar da muryarta tayi da mamaki da firgicin dukkanin abin dataji yanzun.

Miqawa ammy wayar abal yayi ammyn najin muryan NURU taji hankalinta ya kwanta sbd Koba komai sunada sauran 'yaya biyu dasuke fatan su zamo tafarki na gari agaresu Wanda zasuyi alfahari dasu duniya da qiyama.

Meryam ce ta sake sosai tayi magana da NURUn Wanda har lokacin Bata dawo hankalinta duka ba da Haka ta ajiye wayar tanajin sauran bayanin da afia ke koro Mata na NEGES da sauran labarin.

Sai alokacin hawayen tsananin son mijinta Da kaunar iyayenta suka gangaro Mata ta miqe ta nufi dakinta ta turo kofa ta zauna bakin gado tareda fashewa da wani irin kuka Mara sauri sosai tana rufe fuskarta da tafin hannuwanta sbd tabbas idan tace batajin tausayi da kaunar Yar uwarta tayi qarya saidai Kuma bazata iya cigaba da rabartaba Dan kuwa wannan wani al'amarine me girma daya rusa rayuwar farin cikin gidansu dasuka taso dashi Dan kuwa iyayenta har abada bazasu daina Jin damuwa da baqin cikin ganin padima acikin wannan halinba Dan haka tasan farin cikinsu Yi zai ringayi Yana daukewa Dan 'da duk lalacewarsa acikin Rai yake.

Sai yamma lis tasamu damar fitowa bayan ta sauya wanka da Kaya idanuwanta da fuskarta a 'dan kumbure

A shirye ta fito Dan zuwa gurin Anneti farhat da afia ma dake sashen har lokacin sbd takasa tafiya tabar NURUn cikin wannan halin suka miqe tareda jekadi da Akira suka nufi sashen Annetin wadda itama tana Dan daurewane sbd ita qaddara ba'a canzata Amma tana cikin hali na damuwa da baqin cikin wannan al'amari daya faru na NEGES Wanda a safiyar ranar ya tattara yakoma delah gabaki daya da zama sbd shirye shiryen Nadi da aketayi Wanda ake qara la'antarsa akan wasu abubuwan da dama

Anneti kuwa maleek ya hanata zuwa koina yace tayi zamanta a gizah sbd dama auren kawai sukedashi a tsakaninsu babu wani kebewa irinta ma'aurata dasukeyi sbd tsufa da manyanci daya Kama.

Ganinsu yasanyaya ranta musamman NURU wadda tagama samun tabbaci daga gurin jekadi cewar tazama cikakkiyar macen UBAYD MALEEK wadda a fili ya nuna hakan Kuma ko agurin kwanciya da ita ya nuna hakan sbd alamu dasuka nuna ba so daya ya sadu da itaba acikin daren wannan shine cikakkiyar alamar tasace ta har abada tasamu guri me girma a zuciyarsa da rayuwarsa da yardar Allah.

Kayan marmari aka kakkawo aka jere musu Anneti tasa aka kawowa NURU nata hadin wani sirrin daban suna 'yar Hira sama sama jekadi na miqo Mata tana Sha a Dan kunyace harsuka Gama sukai sallar magriba Basu barota ba sai bayan ishai

Suna fitowa afia ta kalli NURU cikin sakewa tace"

Meye sirrin wanna maganin da Anneti ke Baki?

Kodai na.....

Kallonta da NURU tayi yasata dakatawa da zancen tana 'yar dariya.

Murmushi NURU tayi tana tafiya a natse tana cewa"

Idan nafada Miki sirrin bazaki iya bacci ba nikuma inason ki ringa samun bacci yanzu sbd ki koma AFIA UBAYD MALEEK dinki ta asali duk wannan 'yar ramar ta fice.

Murmushi afia tayi tana cewa"

Thank you Ms NURU YONAS.

Suna Isa ko zama basuyiba saqon mr Omar ya samesu na cewa gobe zasu koma Inshallah Dan Haka su shirya.

Wanka kawai tayi tayi Shirin bacci ta haye gado ta kwanta da wuri sbd ciwo ciwon Kai datake ji.

Washe gari da safen kayanta ta hada acikin qaramar akwati saina farhat data saka Akira ta hada Mata ta shirya tsaf ta nufi sashen Anneti tareda jekadi dake gefenta tana sake nanata Mata wasu maganganun akan zama na aure.

Koda suka Isa ga mamakinta kusan kayayyaki ta tarar jere a tray Ana jiranta Kai tsaye Anneti ta nuna Mata kujera tana cewa"

Zauna jekadi ki nuna Mata komai yanda yake ta shanye shekara daya zasuyi ajikinta suna aikinsu.

Miqewa tayi ta shige sbd ganin yanda NURUn kejin kunyar Sha din

Tana shigewa jekadi ta zage tana zuzzuba matasu tana Bata tana shanyewa a wahalce sbd sunyi Mata qarfi sosai a Baki daqyar ta shanye kusan duka sauran daya rage ganin tana neman yin amai yasa Dole jekadi ta qyaleta.

Koda Anneti ta fito daukeda kyautar Dan qaramin akwatin turarukansu na asalin hadin Ethiopia masu wani irin kamshi kamar na turarukan oud ko itacen turaren wuta qamshinsu dai me sanyi da Sanya nutsuwa ta miqawa NURUn tana cewa"

NURU Allah yayiwa aure albarka.

Amin jekadi tace tana karbanwa NURUn wadda take godiya cikin girmamawa da ladabi kafin sukai bankwana suka fito.

Qarfe goma Sha daya suka fito zuwa airport har lokacin Babu Wanda yaga MALEEK acikinsu har suka Isa airport suka shiga jirgi jirginsu ya daga Saida suka Isa Paris suka sauka tukuna suka San bataredashi suka dawo ba shi sai bayan nadin sarauta zai dawo.

Ajiyar zuciya dukkaninsu suka sauke lokacinda suka fito daga cikin motar data ajesu daidai kofar shiga palon gidan

NURU ta lumshe ido tareda karanto adduar samun zaman lafiya da ingantacciyar rayuwa a gidan auren nata tayi bismallah ta jefa kafarta ciki da sallama tana kallonsu mum Sarah dasuka jera suna Mata sannu da zuwa cikin farin ciki da murnar dawowarsu.

Afia ma kusan adduar samun nasarar rayuwa da qarfin gwiwan cigaba da rayuwa kaman da tashigo tana murmushi wa su mum Sarah dasune kusan suke taredasu tun suna yaransu haryanzu Dan Haka yanzu ta yarda da cewa basai Wanda ya

haifeka yake iya zama uwa agarekaba hakama basai jininka ne kawai zai amsa sunan 'dan uwa agareka.

Da wannan kowaccensu ta nufi dakinta sukai wanka da salloli suka fito cin abinci,

Sanyeda wasu riga da wando marasa nauyi ta fito gashinta a daure kyakkyawar fuskarta tayi fayau ta nufo dining din afia tabita da kallon burgewa sbd ita akoda yaushe tana yiwa NURU kallon kyakkyawar halitta me sanyin kyau da shiga zuciya saidai takasa ganewa ko ta yadda dad dinta da NURUn zasu iya rayuwar aure a tsakaninsu.

Ganin kallon da afia ke Mata yasata sakin murmushi Tana zama kan dining tace"

Thank you.

'yar dariya afia tayi tana cewa"

Kinma riga kinsan Ina yabawane kenan.

Wani murmushin takuma saki tana cewa"

Nariga nasan ko kallonki me yake nufi ai.

Suna Gama cin abincin kowaccensu ta nufi daki sbd gajiya da baccin dasuke buqata musamman gobe kowaccensu tayi niyar fara fita makaranta sbd satin zasu fara exams dinsu na karshe Inshallah kafin sukama ayyukansu na Gina career dinsu.

Rashin waya a hannunta yasa washe gari kafin su Isa makaranta tasa aka tsaya wani qaton shagon waya ta siya waya tasaka layinta suka wuce tana gani sakon baquwar number na shigowa wayarta batareda ta duba ba ta saka wayar jaka ta shige class.

Sai yamma suka dawo wanka tafara yi kafin ta Dan kwanta tayi hutun AWA daya da rabi kafin lokacin sallar magriba yayi ta tashi tayo alwala tazo tayi sallar ta Dan dauko takardunta zatai karatu sai alokacin ta duba wayarta ta bude sakon daya shigo dazun taga ansaka"

Inidemìní āderíki kwēn of GIZAH

(Gud morning Queen of gizah)

Wani irin Murmushi ne ya sauka kan kyakkyawar fuskarta har tana Dan dafe goshinta sbd wani yanayi data tsinci kanta bayan karanta sakon tasake kallon numbern ta Dan sunkuyar dakai tana murmushin sbd sanin tabbas MALEEK ne yayo sakon ta daga wayar ahankali tanason yimasa reply Amma takasa sanin me zata rubuta saita ajiye wayar tareda daukan takardunta tana karatu Wanda fiyeda Rabin hankalinta baya Kai Yana kan tunaninsa.

Kwana shida sukai da dawowa suna zuwa school aka fara exams Dan Haka kansu yadauki zafi Sosai musamman afia dasuke likitoci gabaki daya basuda lokacin kansu bare na gida shiyasa farhat ta daga musu kafa Dan itama nata karatun Yana daukan zafi yanzu sbd tashiga secondary yanzu.

Daga NURUn har afia gabaki daya kashe wayoyinsu sukai suka ajiye Saida suka kammala Kuma har lokacin maleek be dawoba sbd abubuwan dayakeson saisun daidaita a gizah kafin yabarota shiyasa shima ayyaukansa na Nan Paris suka taru ga hutu dayake buqata na duk wainnan gwagwarmayar da akai Yana buqatan samun nutsuwa.

NURU ce tafara gamawa da kwana biyu kafin afia Nan hankalinsu ya kwanta suka hau Taya juna murna tareda farin ciki har wani Dan party suka hada acikin gida na tsananisu su uku da farhat saisu mum Sarah da 'yan aikin gidan NURU da kanta tayi musu katoton cake suka yayyaknka abinsu aka bawa kowa sunata farin ciki dayake ciki Palo ne sukai abinsu Babu me wasu kayan nauyi ajikinsu

Ita afia jeans ne three quarter da blue da purple riga Mara dogon hannu

Itama NURUn pencil jeans ne dogo dayafi na afia tsayi ajikinta Ash daya kwanta jikin dogayen sirarun cinyoyinta da fadin hips dinta sai farar riga me hannun shimi ta nufi kitchen ta wanko hannunta daya Dan baci da cake ta fito duba massages dinta

saiga Kiran abal dinta ta daga cikin farin ciki suna tayata murna da Dan mamaki tace"

Abal waye yafada muku?

Murmushi abal dinta yayi kawai ya bawa amminta ta tayata murna itama tareda Sanya Mata albarka aka bawa meryam Nan tahau ihun tayata murna tabawa afia itama sukai Mata adduoi da Taya murna ta karba wayan kenan ta Dora a kunnenta taji qamshinsa daf da ita sosai Yana Shiga hancinta tayi saurin juyowa ahankali tana sauke wayar daga kunnenta

Sukai ido biyu dashi Yana tsaye daf da ita a bayanta fararen idanuwansa nakanta Yana Mata kallon daya sata juyawa ta kalli gefen Afia ahankali wadda itama gabaki daya Bata lura da shigowar dad din nata ba

Ahankali ya bude bakinsa daya motsa kadan ba sauti yace"

Congrats lewa.

Wani irin Murmushin farin cikine me tsanani ya lullubeta ta matso ahankali ta matsu dashi sosai ta lakaci tsakiyan cake din dake gefenta kadan da babban yatsanta takai bakinsa ya bude bakin ahankali ta zura Masa yatsan ya kame ya kasa hannun da harshensa ta lumshe ido ta bude tana zare yatsan sbd Jin yanda yake tsotsa ya Kai hannu ahankali zai kamota

Farhat data lura dashi alokacin cikin tsallen murna tace"

Yeeeehhh daddy yadawo.

Matsawa baya NURU tayi ahankali tana dauke idonta daga kallon dayake Mata ta juyar da Kai tana boye kyakkyawan murmushin dake kan fuskarta

Afia ta juyo da sauri cikin farin ciki tana cewa"

Barka da dawowa dad.

Thank you and congratulations to you Dr AFIA UBAYD MALEEK.

Wani qayataccen murmushin farin ciki tasaki sbd ganin alfari da ita a fuskar dad din nata ta matso ta 'dan rungumesa tana cewa"

Thank you dad.

Dafa kanta yayi Yana cewa"

Ina Miki fatan nasara da albarkatacciyar rayuwa agaba.

Amin ya furta tana kallon NURU dake tsaye gefe tare dasu mum Sarah ta miqa Mata hannu tana cewa"

Dad ka Taya NURU murna itama.

Kallon NURUn yayi Yana dauke Kai ahankali yace"

Allah yayi Mata albarka yabata sa'ar rayuwa.

Amin afia da farhat sukace suna kallon NURUn data ki dagowa ta kallesa sbd Jin idanuwansa dake yawo ajikinta wainda tun anan tanajin kaifi da Dafin son dasuke dauke dashi.

##MAMUH#[10/10, 7:27 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 50_*

Zame jikinsa yayi daga 'yayan nasa ya nufi hanyar shigewa palonsa Yana amsa gaisuwar su mum Sarah dake Masa barka da dawowa

Dama shi mr Omar Yana sako Kai yaga shigar dake jikinsu NURUn da shagalin dasuke yaci ribas ya juya Yana bawa MALEEK hanya Yana shigowa daga cikin palon inda su NURUn suke taredasu mum Sarah dasu Fana.

Ahankali ta Dan dago tabi bayansa da kallo harya shige ta qaraso gurinsu afia suna cigaba da Yan hotunansu da videos ta kalli farhat da hankalinta yafi tafiya sosai agurin hotunan da cake ta maida kallonta akan afia da itakuma Imran yakirata video call da mum dinta suna tayata murna cikin tsananin farin cikin tareda fatan Allah yabata nasara

Ta ajiye qaramin plate din hannunta na cake ta juya tabar gurin batareda kowa ya lura da Barinta gurinba ta nufi palon tashiga cikin nutsuwa tana gyara rigarta data lafe ajikinta gashi ko bra Bata sakaba sbd rigar data kamata sbd robace me taushi da rashin damuwa tana shiga palon ta nufi dakinta ta sake wanke hannunta tafito ta sake shafa turare tana gyara daurin gashinta daya fara warwarewa ta nufi fridge din dake can gefe cikin palon ta dauko ruwa marasa sanyi sosai da power horse energy drink dinsa dake jere acikin fridge din ta dauki qaramin tray ta dorasu akai ta nufi bedroom dinsa Kai tsaye tana sake sakawa kanta nutsuwa ta murda kofar dakin Kai tsaye ahankali ta shiga ta rufo kofar tana kallon dakin sbd Bata taba shigoshi ba ta ajiye tray din sbd MALEEK din baya dakin da Alama Yana cikin toilet

Saita nufo kofa zata fice tana bude kofar Yana fitowa daga toilet daureda towel Brown a qugunsa ta sauke boyayyar ajiyar zuciya kafin ta waiwayo ahankali ta kallesa ganin yanayin dayake saita sauke kanta daga kallonsa cikin nutsuwa da laushin murya tace"

Barka da dawowa.

Hannu ya daga ya miqa Mata batareda yace komaiba Yana kallonta da idanuwansa dasuka Sha kewar ganinta acikinsu,

Ta dago fararen idanuwanta ahankali ta zuba Masa tana kallonsa kafin tafara takowa ahankali ta Isa ta Kama hannunsa ya jawota jikinsa Yana lumshe ido suka sauke ajiyar zuciya ahankali atare ya shigar da ita cikin jikinsa Yana zura hannayensa bayanta ya mannota da jikinsa da Babu Kaya ajiki ruwan wankan jikinsa suna taba fatarta me tsanani laushi wadda take haduwa da tasa fatar me laushin shima sukai shiru ahaka kowa na sauraren bugun zuciyar 'daya idanuwanta a lumshe suke shikuma ya zuba Mata nashi kafin ya dago hannuwansa ahankali ya kamo fuskarta ya hade da tasa Yana goga Mata ruwan fuskarsa a tata fuskar wainda suke kashe jikinta ta 'dan qanqamesa tana sake rintse idanuwa ya sake rankwafowa Ya Bata light kiss abaki Wanda yasata bude idanuwan ta kallesa ya

hura Mata iska kadan acikin idanuwan Yana sake Bata kiss wannan karon me tsayi Dan sai dataji kafafunta suna gazawa ta qanqamesa tana zamewa tareda shigewa jikinsa ta rungumesa dakyau tana sauke Dan boyayyan numfashinta daya sauya.

Murmushi yasake ahankali tareda Kama hannunta suka nufi gaban mirror ya zauna yana nuna Mata gaban mirror din da ido ta kallesa ta kalli gaban madubin tasaki 'kayataccen murmushi tana Kai hannunta ta dauki oil na Neu ta zuba a hannunta kadan ta kallesa ya daga Mata gira daya Yana murmushin daya kusa rikitata takai hannuwanta ahankali ta Dora kan qirjinsa tafara shafawa ahankali ahankali take ya riqe hannunta Yana kallonta da idanuwansa dasukai wani iri ahankali ya bude Baki yace"

Zakiyi kisane?????

Wata irin mummunan kunya tasata zare hannunta da sauri ta juya ta nufi kofa ta bude da gudunta ta fice tabarsa zaune Yana duba kansa Dan kuwa data cigaba numfashinsane zai tsaya cak sai ya hada da inhaler kafin ya fizgoshi.

Dakinta ta nufa ta zauna gaban madubi itama tana kallon kanta kunyar zancensa har lokacin tana jinta ta miqe ta fada toilet ta wanke hannuwan tareda yowar alwala ta fito daidai shigowan Afia data shigo fuskarta da 'yar damuwa ta qaraso tsakiyar dakin tana kallon afian tace"

Lafiya dai ko?Naga kin canza.

Zama tayi kan kujera Yana ajiye wayarta gefenta tace"

Mum nason naje ne kafin nafara aiki na zama Banda lokacin zuwa

Nima inason zuwa ganinta sbd yanzune nakeda duka wannan lokacin Amma dad bazai barni ba

Inama ganin rashin dacewar fada Masa Dan Haka Zan hakura har gaba Inshallah.

Dan murmushi NURU tayi tana cewa"

Ki gwada tambayan Inshallah zai barki tunda dama akan karatunki ne Kuma yanzu kingama Dan haka inaga kaman bazai hanaki zuwa ganin mum dinkiba tunda abune dayazama kaman tilas.

Sauke numfashi tayi tana cewa"

Zangwada tambayan Inshallah.

Tana Gama sallar magriba din ta fito ta nufi kitchen tasaka hannu sharp sharp akan abincin Daren da Saida akaga maleek din aka Dora da niyarsu ciki cake da drinks su koshi suyi kwanciyarsu dama su mum Sarah sunsaba da irin wannan kwalamar dake Hana aci abincinma ko anyi.

Suna gamawa da kanta ta jere komai ta fito kitchen din tabar Fana na gyarawa itama tana Gama gyarawan ta fice daga sashen gabaki daya ta koma sashensu na masu aiki.

Wanka tayi tana fitowa ta shafa Mai kadan ajikinta sai turarukan da Anneti taba data shafawa jikinta ta Sanya doguwar straight riga ta roba wadda ta kwanta jikinta duk daga sama har qasa ko bra kin sakawa tayi sbd lafewar da rigar tayi ajikinta saidai ba'a gane Bata saka bra din ba ta daure gashinta batareda ta shafawa fuskarta komaiba ta fito zuwa dining lokacin duk su afia da dad dinsu nakan dining din ta nufosu tana qarasowa

Cikin hancinsa ya jiyo sabon qamshinta tareda takunta na nutsuwa data Saba.

'dan dagowa yayi a natse ya kalli inda take tahowa ya zuba Mata ido fitar numfashinsa na 'dan sauyawa

Kallo daya yayi Mata ya gano Bata saka bra ba wani kyakkyawan murmushi yaso sauka kan fuskarsa ya dauke Kai Yana Dan kamewa sbd kame Kai kada ya fita control.

Yanaji ta iso dining ta 'dan kallesa cikin lallausan muryanta tace"

Barka da fitowa.

Juyawa gurinsu afia tayi da dama duk yanxu suka zauna Basu kaiga fara cin abincin ba

Afia ta miqe tayi serving dad dinta kafin tayi nata NURU Kuma ta zubawa farhat kafin ta zuba Bata suka fara cin abincin cikin nutsuwa.

Suna gamawa kafin ya miqe yabar dining din afia ta kallesa cikin nutsuwa da kwantar da Kai tace"

Dad Ina roqon alfarmar zuwa Las Vegas kafin takarduna su fito.

Sunkuyar dakai tayi cikin Dan sanyin jiki tana jiran Jin abinda zai fada.

Shiru yana kallon afian datake jiran amsarshi ya juyarda idanuwansa kan NURU datake cin abinci ahankali har lokacin Bata gamaba yasake maida kallonsa kan Afia din ya miqe tsaye yace"

Mr Omar zai shirya muku komai zakije tareda farhat itama ta duba mahaifiyarta nabaki sati biyu.

Da mamakin bazatar amincewarsa da har sati biyun daya Bata suka dago dukkaninsu suka kallesa

Kafin NURU ta sauke kallonta ahankali tana daukan ruwa ahankali Tasha Jin ta koshi suka bi bayansa da kallo.

Cikin tsananin farin ciki Afia tace"

Thank you, thank you dad.

Rungume NURU tayi da sauri tana cewa"

Zanyi missing naki sweetie.

Murmushi NURUn tasake tana kallon afian a 'dan shagwabe tace"

Nice zanyi missing naku nida zaku Bari Ni kadai I will miss you guys like crazy musamman my sweetheart farhat darling please kudawo da wuri.

Yar Dariya Afia tasake tana cewa"

Karki damu su mum Sarah zasu dauke Miki kewa.

Sake shagwabe fuska tayi tace"

Nima inason zanje gida Nagano su abal da ammyna Zaki tayani tambaya Nima Allah yasa abarni.

Amin Afia tace tana Miqewa suka bar dining din suka nufo palonsa afia ce Agaba sai ita NURUn na gefenta suka shigo cikin sa'a Yana zaune palon Yana amsa waya be Shiga na kurya ba

Ya Dan waiwayo ya kallesu ya dauke Kai Yana cigaba da amsa wayar kafin ya taqaita ya kashe batareda ya sake kallonsu ba yace"

Unhum????

NURU lafewa tayi tayi shiru sai afia ce ta bude baki tace"

Dad NURU ma tanason zuwa dubo su ammynta sbd zaman kadaici kafin mudawo tare.

Sai alokacin ya Dan waiwayo ya kalli NURUn data sake lafewa ya dawo da kallonsa kan Afia da muryarsa me Dadi da nutsuwa yace"

Wayene yace zatayi zaman kadaicin????

Tsit sukayi musamman NURU dataji wani iri sbd zancen nasa kamar da ma'ana ta sauke Kai daga irin kallon dayake Mata gaban afia din taji kunya na neman kamata ta Kama hannun afia zasu juya afia tace"

Dad Dan Allah ka duba zancen.

Batareda ya kalli afian ba Kai tsaye yace"

Itama mr Omar zai Shirin tafiyarta.

Miqewa yayi ya shige ciki yabarsu tsaye suna farin ciki kafin afia ta fita ta wuce dakinta NURU ma kallon kofar dakinsa tayi tana Jin farin cikin zuwa gida na shigarta ta nufi dakinta tayi sallar ishai ta zauna tana Dan duba chats har zuwa karfe Tara kafin ta aje wayar ta tashi ta nufi toilet ta wanko fuskarta da hannuwanta ta fito ta shafa Dan Mai tasake shafa turaruka ta cire rigarta ta dauko wata fingilalliyar rigar bacci tasaka ta kalli kanta cikin madubi taga bazata iyaba sbd rigar tayi lalata da yawa ta daure gashinta ta dauko wasu riga da wandon baccin masu qaramin guntun wando tafara zame rigar taji anbude kofar dakin tayi saurin juyowa sbd yanayin rigar jikinta Bata fatan ko afia taganta da ita ajiki.

Dan fiddo da fararen idanuwanta tayi ganin Wanda Bata taba tsammani ba ya tsaya daga bakin kofar Yana kallon jikinta ta cikin rigar baisan lokacinda kafafunsa suka kawosa gabanta ba saijin ya jawota jikinsa ahankali tayi

Ta dago tana kallon fuskarsa data koma kamar ta sabon tashen saurayi sbd tsimuwa acikin soyayya ya lumshe ido Yana sake matseta jikinsa takai hannu ahankali ya zare daurin gashinta

Gashin ya sake yakai hancinsa ya shaqa qamshin dake fita cikin gashin ya lumshe ido Yana sake zagayeta da hannuwansa.

Sake dagowa tayi ta kallesa ya dage Mata gira daya tareda daukanta gabaki dayanta cak ya fita daga dakin da ita tana sake lafewa jikinsa.

Suna shiga dakinsa ya kwantar da ita kan makeken gadonsa Yana kallon fuskarta zuwa wuyanta kafin ya gangara da idanuwan zuwa kirjinta Yana tuno rigar data saka dazun gurin cin abinci take ya lumshe ido Yana zura hannuwansa cikin rigar baccinda da ita da Babu duk daya ya shafo lafaffen cikinta daya kusa saka numfashinta barin jikinta ta qamqame wuyansa Wanda ya matso dashi ahankali ya kamo bakinta da nashi Yana zura harshensa ciki ahankali Yana qarasa hade kirjinsu Wanda yake mugun kashesa.

Jin irin Nishin dayake fitarwa cikin Jin Dadi da samun nutsuwar abinda yake yasata sake shigewa jikinsa tana goga Masa nata jikin tana qarasa kunnashi gabaki dayansa.

Qarfe tara ta fito zuwa kitchen a matuqar gajiye take ga baccin dabai ishetaba Dole ta girgije tafara aikin breakfast tareda Fana

Suna cikin Yi afia ta shigo itama suka hau aikin tare

Suna kammalawa kowaccensu tayi daki Dan yin qanka.

Wanka tayi tareda Yar simple kwalliyarta ta sako doguwar turkian gown me shape daga sama kawai ta fito tana fidda sanyin kamshi ta nufi dakinsa tana shiga Yana Gama shirinsa tsaf cikin black Armani's kaf ta kallesa shima ita ya kalla ta qarasa gabansa cikin 'yar yanga da taushin murya tace"

Good morning.

Jawota yayi yayi kissing bakinta da hot red waterproof lipstick dinta ya zaunu 'daram a bakin ya Kai bakinsa kunnenta ahankali yace"

Wannan kwalliyan nawane right???

Wani lafiyayyan murmushi tasaki Saida haqoranta suka bayyana ta dago ta kallesa murmushin na kashe jikinsa yace"

Unhum right??

Ahankali ta juya tana sake sakin murmushi ta nufi kofa zata fita

Ya riqota Yana dawo da ita ya rungumeta ta baya Yana cewa"

Ok nagane basai kin fada.

Fitowa sukayi tare hannunta na sarqe cikin nasa suna kawowa hanyar fitowa main Palo ta dakata tareda zare hannunta ahankali tafara wucewa yabiyo bayanta zuwa dining daidai fitowar afia sai farhat data riga kowa fitowa

Afia ta gaida dad din cikin kulawa da girma afin farhat ta qaraso ta riqe hannunsa tana cewa"

Good morning Daddy.

Morning princess"yace Yana kallon fuskarta.

Basu wani jimaba gurin cin abincin maleek din yagama ya fice tareda Mr Omar zuwa office.

Shirye shiryen tafiya sukai ranar

NURU ma qaramin akwati daya ta hada sai handbag data saka su id cards dinta da sauran abubuwan buqatan.

Sai dare maleek ya dawo sbd tarin ayyukansu dasuka taru Dan haka tea kawai yasha baya buqatar abinci suka kwanta.

Washe gari da yamma su afia suka wuce suka barta da tsananin kewarsu musamman farhat ma daqyar ta yadda tabi afia din da tace ita NURU zatabi delah Amma NURU tayi Mata dubara da 'yan nasihu akan mum dinsu kafin ta amince tabi afia suka tafi.

Sai washe gari nata jirgin ya tashi saidai tareda maleek zasuyi tafiyar ta cikin ticket dinta taga inda sukai ba delah ba wato _Maui Hawaii_

Murmushi kawai tasake tareda Dan dagowa ta kallesa kafin ta kwantarda kanta jikinsa tana lumshe ido.

Sai cikin dare suka Isa Kai tsaye driver yazo daukansu ya nufi masaukinsu dasu Wanda mamaken 5star hotel din yake kusada ruwa Wanda yaqara gurin ni'ima da nutsuwa ga tight security dake kewaye dako Ina gurin Sam gurin ba hayaniya akwai tsaro sbd gurin manyane kawai aciki.

A gajiyen datake sallah kawai tasamu tayi daqyar ta bayan tayi wanka da ruwan zafi Sosai ta saka kayan bacci ta haye gado ta shige bargo take bacci yayi gaba da ita me Dadi ko abinci Bata tsaya nemaba.

Saida yagama komai shima ciki hadda waya da Mr Omar kafin ya hawo gadon ya kwanta tana shigewa jikinsa

Shima baccin yayi me nutsuwa.

Sai qarfe bakwai na washe gari suka tashi har sunyi lattin sallah

Sukai sallar sai alokacin yunwa ta taso Mata

Yayi Mata odar abinci lafiyayye baa dauki mintuna da yawaba aka kawo ta tashi taje kan table tafara ci yazo ya zauna kusada ita suna ci tare duk da Bai saka hannuba da hannunta sukeci.

Bayan sungama wanka sukai suka sake komawa bacci sai Rana sosai suka tashi sukai sallah suka Kara cin abinci

Gabaki daya ranar dai a kwance suka yini sallah da cin abinci kawai ke tadasu ko washe gari ma Haka Saida sukai kwana biyu kafin suka fara fita da qafa yawon Shan iska cikin qananun Kaya Wanda ta mutu da mamakin duniyanci da iya zallar soyayyar da maleek din ya iya musamman dayake yazaba Nan dinne sbd Ana rayuwane anan ta couples sbd yawanci Yan honeymoon ne.

Kwanaki sukai suna fita wani irin shaquwa da sabuwar soyayya me qarfin gaske tasake shiga tsakaninsu musamman da yariga yagama busar Mata da idanu akan soyayyarsa ko Ina Babu ruwansu kissing juna sukeyi musamman shi ko magana take Masa wani lokacin Haka zaibi bakin Yana kissing sbd komai nata kashesa yakeyi.

Yau ba awani gajiye suka dawoba Dan Haka suna dawowa yaqarasa gajiyar dasu akan gadansu aikuwa taqarasa gajiyar gaske kafin sukai wanka suka kwanta bacci.

Wata irin sabuwar rayuwa suke a qasar ta zararrin masoyan da basa ganin kowa sai junansu

Dan kuwa yanzu ko irin kayan datake saka Masa cikin daki sun gama makantar da idanuwansa da ganin kowa bayan ita musamman da yanzu ya koya Mata batada gurin zama sai kan cinyoyinsa da jikinsa.

Tana waya dasu afia sosai saidai har lokacin takasa fada mata inda take tadai sanar da ita Bata tafi delah ba tana gida sbd cewa abata su abal su gaisa afian datai.

Su abal ma dadin duniya da farin ciki ya ishesu duk lokacinda sukai waya da 'yarsu

Itakuma padima kullum akai waya da NURU sai kaman ciwon ya tashi sbd ta ringa Kiran sunan NURU kenan yinin tana cewa ta yafe Mata.

Satinsu uku cif suka dawo gida har lokacin su afia Basu dawoba sbd afia data gane mahaifiyarta tana samun 'yar matsalar juyewar Kai wani lokaci shiyasa takira dad din tasake rokon yaqara Mata sati daya yakuma qara musu din.

Koda suka dawo kallo daya mum Sarah tayiwa NURUn ta dauke Kai tana yaba zallar kyau da cikar data Karo shi kansa oga kwata kwatan Mr Omar dinga satar kallonsa yayi Yana Masa barka barka akai akai har Saida maleek din ya kallesa yace"

Yaushe ka zama me saka ido Mr Omar?

Murmushi yayi Yana shafa Kai yace"

Allah dai yaqara maleek lafiya da kwanciyar hankali.

Dan guntun murmushi shima yasaki Yana share Mr Omar din sbd dama yasanshi da 'yar Karan saka Masa ido musamman daga baya bayan Nan.

Kwanansu biyu da dawowa yayi tafiya tareda Mr Omar bayan yagama aikin bada Baki sbd kedaicin dazata shiga basu afia babushi

A ranar kafin ya wuce yakira afia yace su biyo jirgin washe gari su dawo gida

Afia tace to.

Washe gari da yamma saigasu sun dawo cikin tsananin farin ciki da murna tarbesu ta rungume farhat kafin ta rungume afia din tana cewa"

Oh my God I missed you guys so much

Musamman wannan beautiful sabuwan likitan tamu" taqarasa fada tana kallon farhat data tsuke fuska zatai mgn ta tareda da Bata kiss a goshi tana cewa"

My sweetie kinsan kece farko a zuciyana basai kince komaiba kinji.

Har dakin afia din suke duk su dukansu suka zauna afia na sauke ajiyar zuciya tana lumshe ido tace"

Alhmdlh Ya Allah

Gida me Dadi.

Murmushi NURU tayi tana tayata janye akwatin ta gefe tace"

Keda Zakiyi aure wata Ran kitafi

Amma nidai har banason tuna ranar

I don't wnt you to leave us" taqarasa fada tana kallon afian cikin kwabe fuska.

Dariya Afia tayi tana miqewa ta dauko wayarta cikin Jakarta tadawo kusada NURUn ta zauna tana cewa"

Hmmm ki shirya to babe sbd nakusa tafiya idan kina maganar aure ne sbd....

Wani tsananin farin ciki NURU tace"

Yaushe kika fara soyayya Banda labari¿

Wane me sa'ar ne wannan?

Dan wani blushing afia tayi tana kallon NURUn kafin ta miqe ta nufi toilet tana cewa"

Zanfada Miki komai kinsani Amma saina hutu yau da daddare akwai fira.

Murmushi kawai tayi tana cewa"

To ahuta lafiya Bari naje na saka hannu a abincin yau abincin dakukafi so za'ayi.

##MAMUH#

[10/10, 7:27 PM] Anty Rabi'at: *_Mamuhgee 51_*

Sai dare suka samu kansu a dakin afia din ma suka kwana bayan sun kwanta

Afia ta fuskanci NURUn ta sauke ajiyar zuciya da numfashi ahankali tafara cewa"

NURU mum Dina tasamu matsalar juyewar Rabin Kai dayake Dan tashi wasu lokutan idan tana tuno abinda daya faru na wannan al'amarin.

'dan shiru tayi tana sake juya al'amarin cikin ranta ta bude Baki tacigaba da cewa"

NURU mum ta rokeni alfarmar na amince na auri Imran sbd nuna sha'awarsa da yayi ga aure Dan samun cikakkiyar nutsuwar Bata kulawa shine ta nuna sha'awarta nason auren Hadi a tsakaninmu idan har dad Dina ya amince,

Na zauna nayi nazarin maganarta NURU Nima inason kasancewa tareda ita Dan samun lafiyarta Dan Haka na amince da maganar auren saidai bansaniba ko hakan danayi nayi daidai kokuwa?....

Ajiyar zuciya ahankali NURU tasaki tana kallon afian cikin tsananin tausayinta da qaunarta sbd a rayuwa tasamu gata da dukiya da kyakkyawan asali da ilimi da komaima na rayuwa Allah yabata Amma ta bangaren mahaifiyarta ta hadu da jarabawa me qarfi wadda gashi dai daga karshe tayi sacrificing rayuwarta kacokan akan auren Hadi sbd neman lafiya da kawo sauyi a rayuwar uwarta Wanda hakan yaqarawa NURUn ganin girman afian fiyeda koyaushe sbd tabbas tsakaninta da Allah takeso da kaunar mahaifiyarta komai halayenta kuwa.

Cikowa idanuwansu duk su biyun sukai da hawaye NURU tace"

Ina Miki fatan kyakkyawar nasara arayuwa fiyeda kowa afia,

Allah ya dasa Jin Dadi da kwanciyar hankali tareda soyayya me girma acikin wannan auren Kuma Inshallah dad dinku ma bazaiqi hakan ba sbd burinsa dama akanki karatunki ne Kuma kin kammala Dan Haka burinsa na gaba akanki bazai wuce aurenki ba.

Ahankali ta furta"

Thank you NURU.

Murmushi tasaki tana dafa hannunta ta girgiza Mata Kai.

Washe gari a washe suka tashi kowa da nasa farin cikin sbd takardunsu dasuka fito Kai tsaye tare data aikinsu

Murna da farin ciki a ranar ma Saida sukai partynsu cikin Palo wannan karon afia harda rawa Tasha

Farhat da itama farin cikin ganinsu cikin farin ciki duk ya lullubeta itama tasha rawarta duk da Bata iyaba

Saiga Imran yakira afia din vcall ta zauna sunayi tana gyara gashinta data sauyawa kala daga baqi zuwa dark brown suka fara fira sama sama wadda yawanci idone yake kafe dasu sbd wasu halayenta da kyakkyawar kamilalliyar fuskarta dasuka fara saka Masa Sonta.

Mum dinta yafita yakaiwa wayar suka hau murna mum dinta na cewa"

My baby I love Allah ya albarkaci rayuwarku duka.

Amin ta amsa tareda janyo NURU dake can gefe tana waya da Alama duk wanda take wayar dashi yanada mahimmanci a rayuwarta ta kara Mata wayar tana cewa"

Mum ki gaisa da NURU ki tayata murna itama.

Kallon kallo sukayiwa junansu tareda yin tsit na wasu sakanni kafin NURU ta Dan ago tana kakalo murmushi cikin nutsuwa tace"

Ina wuni?

Ya gida?

Ajiyar zuciya tareda numfashi lailah tasaki kafin ta kalli NURUn cikin nutsuwa tace"

Congrats to you.

Thank you.

Sake kallonta lailah tayi tace"

Kiyi hkr da duk abinda yafaru abaya Ina fatan Zaki yafemun komai ya wuce?

Murmushi NURU tasaki tana girgiza Kai a natse tace"

Yariga yawuce na Dade da yafe Miki sbd girma da darajarda afia take dashi a zuciyata.

Nagode sosai" lailan tafada tana sake murmushin daya qarawa kyakkyawar fuskarta kyau ta Dora da cewa"

Ina gaida farhat.

Jawo farhat NURUn tayi tana cewa"

Sweetie zo ga mum dinki ki gaisheta.

Zama farhat tayi tana karban wayan fuskarta daukeda farin ciki sbd yanzu tafara sakewa da mum din tasu sbd ta sauya sosai yanzu har cikin ranta takeson yayan nata ita Kuma farhat dama tsorone yasata take shakkar kusantar lailan.

Har Imran suka gaisa dashi kafin NURU ta miqe Takoma ga tata wayar datakeyi da Bata oga kwata kwatan Wanda duk wayar datayi da lailah da gaisawa datai da Imran duk yanaji Kuma shima hakan yasashi farin ciki ganin atlast dai afia tasamu soyayyar mahaifiyarta dataketa kwadayi tun tasowarta.

Da daddare sbd gajiya tunda suka kwanta Basu farka ba sai qarfe takwas na safe suka miqe cikin sauri sukai sallah kowa yafara Shirin fita aiki musamman afia datafi NURU buqatan fita da wuri sbd yanayin aikin nasu ba daya ba.

Cikin ikon Allah kowaccensu tafara aikinta cikin aminci da kwanciyar hankali har sun Dan fara sabawa cikin kwanaki kadan.

Yau NURU ce tajasu suka fita tare suka biya ta ajiye afia asibiti kafin ta wuce gurin aikinta tana sake trying numbern MALEEK dabata shiga tun safe rabonta dashi tun jiya cikin Daren dasukai vcall.

Tunanin rashin samunsa yasakar Mata ciwon Kai da damuwa qarshe Bata Bari yamma tayi sosaiba ta tattara ta baro office din harta Kama hanyar zuwa gida ta fasa ta nufi asibiti gurin afia sbd tayita kiranta tafada Mata zata wuce gida idan tagama takira zata Aiko Edward yazo ya dauketa Amma afian Kuma Bata dauki wayarba shiyasa Mata biyawa asibitin Dole tana sakin Dan qaramin tsaki sbd kanta dake tsananin sarawa

Tana yin parking cikin asibitin saidata dakata cikin motar ta sauke ajiyar zuciya da numfashi sbd yanzu Kam kaman hadda jiri tana gani Haka ta daure ta fito sanyeda shades sbd Rana ta nufi ciki.

Direct hanyar office din dazata samu afia wato office din Dr Damien ta nufa saidai kafin ta qarasa tana daf da Isa ta dakata sbd wani jiri daya dibeta tayi gefe zata Fadi afia data hangota zuwa ta taso tana kawowa ta tareta cikeda mamaki da 'yar damuwa tana kallonta tace"

Lafiyanki kuwa???

Gyara tsayuwa NURUn ke kokarin Yi tana Dan dafe goshinta ahankali tace"

Bansaniba kawai ciwon Kaine yake damuna yanzu Kuma Kamar karna baro office jiri yafara kamani Ina ganin stress ne da rashin bacci.

Kallonta afia keyi da kyau kafin ta gangaro da idanuwanta zuwa kirjin NURUn ta kalla tasake maida idanuwanta kan fatar hannuwan NURUn saitaga kaman Bata gani sosai ta kalli NURUn tana cewa"

Bana tunanin stress ne kadai muje nadubaki mugani sbd jiri matsala ne zai iya jefar dakai inda zaka halaka kanka.

Suna Shiga office din Dr Damien ta zaunar da NURUn tana juyawa ta dauko ruwa takawo Mata ta Bata Tasha ta durqusa gabanta tana cewa"

Muji pulse dinki.

Bata hannunta tayi ta riqe tana Jin pulse din NURUn tayi shiru zuciyarta na bugawa

Duk Bata yarda ba ta juya da ita kan gadon scanning din dake office din Dr Damien din NURU ta kwanta tana gyara Mata kafafunta.

Tana Dora Mata abin scanning din take cikin jikin NURUn ya bayyana baro baro ta ajiye abin tana kallon NURU da cikakken mamaki da tsoro harma da shakku da firgici duka

Bakinta na rawa Kai tsaye ta fuxgo kalmar cikin tsananin mamaki tace"

NURU you are 7weeks pregnant.

Da sauri NURU ta kalleta tana saukowa daga gadon tana goge jikinta da tissue ta Dora hannunta kan cikinta cikin son tabbatarwa tace"

Pregnant???

Ni¿

Wani irin Murmushin farin cikin da Bata taba tsammanin yiba ta sake dafe cikin tana dagowa ta kalli afia datai mutuwar tsaye tana kallonta cikin mugun mamakin da batasan lokacinda bakinta ya furta"

Dad ne???

Sai alokacin kunyar afia din takama NURU ta Dan takaita farin cikinta tana kallonta ta daga Mata Kai ahankali tana cewa"

Yes wannan qaninki ne afia.

Wani yawun sabon mamaki afia ta hadiye tana sake dulmiya cikin tunani da tsananin mamaki alokaci daya Kuma hadda kunya tana kamata

Daga ita har NURUn sai suka samu kansu da kunyar juna afian tayi saurin juyawa tana zaro takardar scanning din da batama Gama dubawa ta miqawa NURUn ba shiri bakinta na furta"

Congratulations.

Kallonta NURU tayi ahankali tace"

Thank you tana sakin murmushi.

Bakin afia mutuwa yayi murus da mamakin al'amarin dakuma kunyar dad dinta Haka ta raka NURUn har mota Dan Dole itace taja motar tabar gurin aikin ranar saidai Kuma gobe suka nufo gida tana satar kallon NURU wadda farin cikine fal cikin ranta Allah zai Bata 'da ko 'yar kanta.

Suna shigowa gidan tun daga motocin maleek dake harabar gidan taga alamun an sauya musu parking wanda hakan ke nuni da yadawo kenan

Cikeda murna ta fito motar tana mantawa da komai ta nufi hanyar office dinsa na cikin gidan dayake aikin office aciki sbd hango Mr Omar agurin tasan Yana can Dan Haka ta nufi gurin cikin tsananin farin ciki da murna.

Tsaye suke daga bakin kofa tareda baqinsu 'yan China dasukazo wani aiki harsun Gama magana sun fito kenan zasu wuce ya hangota tana tahowa

Sanin sabon daya koya Mata da yanayin yanda take tahowar ya tabbatarda abinda zai faru ya hadiye wani 'dan yawu ya waiwaya ya kalli Mr Omar Wanda take yagane kallon ya matso Yana washewa bakin Baki Yana nuna musu hanya da cewa"

chairman Zhou let me see off please?

Gyada Kai sukai suna sake bawa maleek hannu suka tareda Mr Omar zuwa gurin motocinsu da securities ke zagaye suna jiran fitowarsu.

Da gudu ta qarasa qarasowa ta fada jikinsa tana Dora bakinta kan nasa ta bashi wani lafiyayyan kiss daya sanyashi dagota ya kalli fuskarta kafin yasake maida fuskarsa yayi kissing din lips dinta Yana fidda wani lafiyayyan murmushin dayasa afia kusan suman tsaye sbd Bata taba ganinsa akan fuskar dad dintaba

Ita gabaki daya daburcewa tayi ganin abinda idanuwanta suka ganar Mata wato dai ba yanzu bane al'amarin ke faruwa sbd komai data gani ya nuna dad dinta ya dade da tsunduma wata sabuwar daddadar rayuwa hakama NURUn.

Wayyo Allahna" tace tana juyawa da sauri zata bar gurin sbd ita duk kunyar komaiba ya rufeta Jin take Kamar ta nutse a qasa

Tana juyowa saura kadan suyi Karo da Mr Omar da shima yake tsaye agurin Yana jiran sugama soyewar ya qarasa.

Kallon kallo sukai itada Mr Omar dake sakin murmushin Haka yakeson ganin megidansa ya sake kallon gefen su maleek din ya juyo ya kalleta da ido yayi Mata alamar tasake waiwayawa tagani

Ta juya ahankali daidai lokacin NURU ta Dan daga duga duganta takai bakinta kan kunnensa daya rankwafo yana riqeda qugunta cikin rada tace Masa"

Nenyì Irìguzí (Am pregnant).

Wani irin Abu yashigesa ya dagota ahankali yana kallon cikin idanuwanta da ido yake tambayar" da gaske??

Kai ta gyada tana zagayo da hannuwanta qugunsa tana cewa"

And I missed you yau duka bani muryanka ba.

Dago fuskarta yayi ya hade bakinsu yabata wani irin lafiyayyan kiss daya sata kallonsa a kasale tace"

Are you this happy??

Kamar yaro haka ya daga Mata Kai Yana kamo hannunta suka nufo ciki

Afia da Mr Omar sukai saurin barin gurin har suna ture juna tayi saurin fadawa Palo ta nufi dakinta da gudu tana cewa"

Heyyyy

NURU kin wuce tunanina

Dad kuma bazan iya cewa komaiba sbd yau Naga asalin MALEEK da bakowa zai taba samun damar ganiba sai su Mr Omar 'yan kullum da kullum din MALEEK.

Suna shigowa dakinsa suka wuce Kai tsaye acan aka qarasa sauran murnar da farin cikin cikin Wanda yasata mamakinsa Dan Bata dauka yanada sauran son haihuwa har hakaba.

Sai dare gurin cin abinci Afia tasamu ganinsu lokacin ba kunya NURU tayi wanka tana sanye da wata lalatacciyar riga Mara tsayi Sosai gashinta daure tsakiyar Kai kaman baby shikuwa akai akai idanuwansa na kanta

Duk sai taji abin wani iri saidai Kuma farin cikin data gani taredasu din ya tabbatar Mata da ba qaramin so sukewa juna ba

Ta ajiye spoon dinta ahankali ta dago ta kallesu cikin farin ciki tana murmushi tace"

Congratulations dad you are having another child Allah yakawo manashi lafiya.

Murmushi yasake Ya kalli afian yace"

Thank you princess Afia.

Da ihu farhat tayi kan NURUn tana cewa"

My aunt zata haifamuna baby me kyau kamanta.

Murmushi NURU tasake tana kissing kumatun farhat din.

Tun daga dining din Babu Wanda yakuma ganin NURU sai washe gari da safe dasuka fito cin abinci sai alokacin afia tabada shawaran NURUn tafara ganin likita musamman akan jirin aikuwa ba Bata lokaci Mr Omar dakejin kaman ya taka kan jariri yakira Dr Damien yazo har gida ya duba NURUn daganan yafara zuwa dubata akai akai.

Lokacinda su abal dinta suka samu labarin cikin hadda sadaka ammynta tayi meryam kuwa tuni tafara takura tanason zuwa gurin NURUn saigashi kuwa maleek da kansa yasa jekadi taje har Delah ta daukota dama Kuma itama jekadin tana Shirin zuwa ne harsai NURUn ta haihu.

Zuwan jekadi da meryam da sati biyu maleek ya dauketa suka tafi _Maldives_ inda sukai zamansu acan suna hutawa Saida cikin yashiga wata na budu kafin suka dawo lokacin anfara maganar auren afia Imran Wanda tun kafin suyi tafiya dad din Imran din ya nemesa yayi magana da afia tace da amincewarta take yace ya Basu aka tsaida Rana.

Imran yadawo Paris gabaki daya da lailah sbd gidansa a Nan Paris yake bazai zauna gidan mahaifin matarsa ba ba girma bane Dan Haka murna kan murna agurinsu NURUn da afian sbd bazasuyi nesa da juna ba take aka hau Shirin biki gadan gadan musamman uwar amarya lailah da ba laifi yanzu ta warke harta fara komawa ayyukanta zata fara daga farko Dan ma a qarqashin kamfanin dad din Imran din take aiki.

Sosai akai shagali a gizah na auren afia din Wanda hatta iyayen NURU sun halarto tareda kaleeb sosai tayi farin cikin ganin iyayenta Suma sunyi farin cikin ganinta musamman cikinta daya fara tsufa a gizah kowa yasan MALEEK na gaf da samun magaji kila suke fata.

Padima dai ba laifi tananan sama sama wani lokacin kalau wani lokacin Kuma abin ya Dan juye ahaka aka gama bikin suka tattara suka dawo Paris afia ta tare a babban gidan mijinta Wanda mum dinta take sashe guda na musamman da Imran din ya ware Mata.

Ranarda afia tacika wata hudu cif da aure ranar nakuda ta tasowa NURU

Maleek ya tattara mulkin da sarautar ya ajiye suka dunguma zuwa asibiti sbd ganin gidan zata wahala bazai iya jure ganin hakan ba

Saigashi cikin ikon Allah suna Isa ta haifi qatoton jaririnta me Kama da farhat sak.

Koda maleek ya karbi Dan wata hamdala yasaki Yana godewa ubangiji yayi Masa huduba da sunan Mr Omar tareda yiwa Mr Omar wata gagarumar kyautar datasaka Mr Omar din rungumesa Yana hawayen godiya duk dai yatara tarin dukiya me yawa a qarqashin maleek din Amma sai bazai iya dainawa maleek din aiki ba sbd sunzama kaman jini.

Acikin motarsu ta dawowa gida duk yabita ya lashe da kisses itada baby Omar Wanda hotonsa tuni yafara yaduwa a duniya Matar UBAYD MALEEK me gizah ta haifar Masa baby boy.

Daqyar ya suka iya raba gurin kwanciya sbd jekadi data Dan sako NURUn agaba har aka samu sukai 50days daga Nan delah suka tafi tayi sati biyu gurin iyayenta daganan suka dawo gizah tayi kwana biyar kafin tadawo Paris su afia sukazo aka wuni gidan suna Yan kus kus dinsu na kayan datazo dasu suka raba

Washe garin ranar maleek ya dauketa suka tafiyarsu _Santorini_ sbd wata sabuwar duniyar da NURUn ta jefasa a Daren jiyan inda sukai wata daya kafin suka dawo

Saidai Koda ta dawo da sabon ciki ajikinta wanda yazo Mata da Dan laulayi da son jiki Haka shima duk ya shirirce gurin tattalinta da jinya sbd koyaushe tana lafe ajikinsa karshe dai Mr Omar Dole ya rungumi wasu ayyukan da kansa yakeyi a office.

##MAMUH#

ALHAMDULILLAH YA ALLAH

*MUNZO QARSHEN WANNAN LABARIN ME SUNA UBAYD MALEEK WANDA NAKE FATAN KURA KUREN CIKI DA ABUBUWAN DANAYI BA DAIDAIBA ACIKI ALLAH YA YAFEMABA GABAKI DAYA HAKAMA KURAKURAI IRIN NA MANTUWA DA TYPING ERROR DUK INA FATAN ZAKUMIN UZURI HAKAMA WAINDA ZASUGA BAI KAI MUSU INDA SUKESO BA SUYI HAKURI AMMA DAI KYAN L

LABARI AGAMASHI ANA MARMARINSA BASAI MUNKAI INDA ZAKUJI YA GUNDUREKU BA NIMA BASAI NAKAI INDA RUBUTASABA ZAI GUNDURENI DAN HAKA INA FATAN NUSHANDIN YAYI DAIDAI YANDA ZA'A DADE ANA TUNAWA*

NAGODE SOSAI SOSAI DA KAUNA DA KUKA NUNAWA LABARIN KUMA INSHALLAH INA MANA FATAN HADEWA A GABA DA LABARIN DAZAIFI UBAYD DA NURU DADI 😝😝

NAGODE

*_MAMUHGEE_*